*BADARIYAH*

An dauko wannan littafi daga shafin www.dlhausanovels.com.ng ku ziyarci shafin na www.dlhausanovels.com.ng domin samun kayatattun littatafan hausa kama daga kan na yake yake dana soyayya

Marubuci ko marubuciya zasu iya turo mana da littatafansu mu dora masu a shafinmu kyauta don masoyansu su rika Downloading a online,

Sannan marubuta zasu iya turo mana da tarihin rahuwarsu da tarihin rubutunsu, dama sharhin littatafansu don masoyansu su gani kuma su karu da hakan
Domin turo mana da littafi ko tarihin rayuwar marubuci ko marubuciya sai ayi mana magana ta whatssap da wannan nambar +2348140419490

A lura dakyau - kyauta muke saka littafi a shafinmu bama amsan ko sisin marubuci, duk wanda ya amshi kudinku da sunanmu babu ruwanmu,

Alura dakyau - manazarta bama tura littafi ta private ku dena binmu private kuna neman mu tura maku littafi, duk mai bukatar littafi yaje website namu

Alura da kyau - Littatfanmu suna fitowa cikin manhajoji uku ne PDF,TXT da DOC amman munfi amfani da PDF da TXT masu amfani da wayar android ko tablet ko computer zai fi kyau ku riga dauko PDF da DOC

Masu amfani da kananan wayoyi java ko mara java TXT zakuna zaba don shine daidai wayarku

This hausa novel was uploaded and downloaded from www.dlhausanovels.com.ng
You can download more hausa novels there
Also you can send us your novel to upload it in our website for your fans to download it online
It is free we do not charge for uploading novel
Also if you are an Author be it online or Non online you can send us your biography including your book summary,commentary and others via this number +2348140419490 its free we do not charge for our services

Note that - we do not charge for our services we uploaded novels and posted biography free, any person that collect your money in our name is your fault do not blame us

Note that - pls readers stop calling us and be asking us to send you a novels we are not sending novels through whatssap or private our novels is public at any day, any time you can visits our site and download it

Note that - our ebooks came as PDF,TXT or DOC format but the popular format are PDF or

TXT, those with android or tablet or pc we suggest you to download PDF or DOC
those with java phone or non-java phone we recommend you to download TXT

—

®☄

*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION✍*
{Gaskiya d'aya ce daga k'inta sai b'ata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar duniya da kuma lahira}

🎐 G• W• A🎐
*GASKIYA DOKIN K'ARFE*•🏇

*WRITTEN BY AUNTY NICE*

*PAGE*1️⃣

Ni Badariyah Ibrahim haifaffiyar garin bauchi ce cikin karamar hukumar ganjuwa cikin kafin madaki, mahafina Abba Ibrahim a kafin madaki aka haifeshi, su uku iyayensu suka haifah, mahaifina shine da na farko a wurin malam mustapha Abba bafulatanine na asalin garin kafin madaki, bayan an haifeshi ne, da shekara biyar aka haifi gaggo Ai, bayan shekara uku kuma aka haifi goggo Fatima.

Abba nah yakasance farine kyakyawan bafulatani amma Allah yayishi mai yawan shiru, iyakacin Abba nah primary, SBD rashin kudi na mahaifin su bai samu yacigaba da Karatuba, akwai abokinshi Abdullahi dan makotansu ne shiyasamu ya cigaba da karatunshi na sakandare, kakana malam mustapha mota yake ja, kuma mahaifina wani lokacin yafi zama a shagon wani tela yana mishi yaron shago.

Mahaifina bayida wani buri irin yaga yayi karatu amma Allah bai yaddah ba, lokacin da abokinshi Abdullahi yagama sch sai bappan shi ya daukeshi suka koma bch yasaka shi a makaranta, yana diploman shi a bacas, a lokacin Abba na yadage da koyan dinkinshi inda ya saka goggo Aisha da goggo Fatima a makaranta, xuwa lokacin goggo Aisha tana aji daya a

secondary ita kuma goggo Fatima tana aji hudu a primary.

Mahaifiyar su Abba nah mai suna zainabu amma suna kiranta ummah itama bafulatana ce kyakyawar gaske amma ita ba fara bace bakace saidai amma bakinta mai kyau ne gata bata cika tsawo dayawa ba, duk da rayuwar kauye ce amma kana ganinta xaka ga asalin kyau da diri irin na 'ya mace, gata da gashi mai duhu ga tsawo ga cika, kuma dukkan sajenta gashi ne gashi har goshinta, idan ka kalli bayan wuyanta shima duk suma ne, gashi akwaita da hakuri da rashin magana Wanda a wurinta mahaifina ya dauki shirunta da HAKURI.

Duk cikin yaran gidansu babu wacce tayi kyaun umma da kalanta duk farin mahaifinsu suka dauko da tsayinshi.

Lokacin da abokin Abba nah yagama karatun shi, sai bappanshi yasama mishi aiki a PRIMARY EDUCATION BOARD, inda bappanshi yake aiki a natsayin chairman na wurin ba bata lokaci Abdullahi ya tattara yanashi yanashi ya koma bauchi gaba daya, xuwa wannan lokacin goggo Aisha tana aji hudu a secondary, lokacin kuma Abba Abdullahi ya bijiro da maganan yana son autenta, amma malam mustapha Wanda suke kiranshi da bappah yace yayi hakuri ta kammalah karatunta, amma Abban bauchi yaki amincewa yanemi alfarmar amusu baiko hankalinshi zaifi kwanciya, haka bappah yayi badon yasoba, don shima burin shi kenan yaga sunyi karatu mai zurfi amma idan iya secondary ne ma tasamu ta kammalah.

Bayan shekara biyu lokacin anyi bikin Abban bauchi da goggo sun tattara sun koma bauchi inda suka zauna a fadaman mada kusa da gidan bappan Abban bch, bayan wani lokaci Abban bch yanemawa Abba nah shago a kasuwar winti wurin nuhu tela dayake shine telan matan bappanshi, ba a dauki lokaciba Abba na ya kware da dinki kaman yayi shekaru a wurin tunin ya tara customers, amma bai yadda ya zauna a gidan abban bch ba sai Yakama haya a cikin unguwar gwallaga sbd yafi mishi kusa da winti.

Bayan shekara daya goggon bch ta haihu inda tasamo danta namiji mai tsananin kama da abban bch saidai yayi farin goggon bch, bayan suna yaro yaci suna Aliyu, sunan mahaifin Abban bch amma ana kiran shi haidar, akwana a tashi yau har goggo Fatima tagama sch inda ta taho bch don tasamu admission a school of nursing bauchi ba bata lokaci ta tattaro tadawo, amma a cikin sch taxauna cewar bappah dayace hankalin shi zaifi kwanciya akan ace ta tare gaba daya gidan addanta saidai karshen sati ta dinga zuwa musu.

Abba na alokacin ya  fito damagana auren shi da 'yar kawunshi yayan umman shi mai suna Halimah Wanda muke kiranta ummi, ba a dau lokaciba akayi bikin amma yabarta a can kafin madaki bayan sati yake zuwa mata kafin yasamu gida, don baya son gidan haya mai mutane dayawa,.

Alokacin kuma goggo Aisha tasake haihuwar danta na biyu Wanda yaci sunan Abba nah, Wanda ranan sunan aka saka mishi Ibrahim Khalil, bayan sunan Khalil da sati biyu Abba nah yasamu gida a cikin gwallaga, gidane mai dakuna biyu a Jere sai kitchen da toilet kawai sai filin

tsakar gida mai Dan fili kadan, dayake ummin mu mai tsafta ce sai yaxama gidan ko kai waye kashiga saikayi shaawar shi.

Ummi nah ita kadai ce a 'yayan 'yan uwa ta dauko kamanni umman su Abba nah sak kasancewar itama kalan su daya kuma hakurin su daya, daga ummi nah har Abba nah halinsu daya shiyasa ko kadan ba ajin Kansu, har Allah yabata haihuwar danta na fari Wanda babu abinda yabari akamannin abban mu, Wanda ranan suna yaro yaci sunan bappah wato mustapha amma muna kiran shi walid,
Walid tsakaninsu da Khalil bai wuce watanni biyar ba, sai suka taso abokanan juna, suna da shekara biyu ummi nah ta haifi abubakar Wanda yaci sunan mahaifin abban bch muna kiran shi sadiq, ita kuma goggon bch ta haifi nata akasaka mishi bappah amma ana kiran shi bappah.

A wannan lokacin ne goggo Fatima ta gama na ta karatun tana practical acikin specialist bch alokacin ta hadu da Alhaji Nuhu umar  Wanda shine C.M.D na  wurin, mutumin haifeffen garin jama'are ne na jihar bch, yana da mata daya shuwa ce 'yar Maiduguri Wanda ake kiranta hajiya zahra matar fara ce mai asalin kyaun shuwa, tana da tsananin kishi akan mijinta kuma tana da son yaranta guda hudu Wanda Allah yabata, danta na fari mai suna *UMAR* da yaci sunan kakanshi, wato waxeerin jama'are kuma kakanshi yace bai yadda acanja mishi suna ba a kirashi da sunana shi kawai mai bi mishi kuma Babagana Wanda yaci sunan mahaifin mamanshi Alhaji Ahmed amma suna kiranshi babagana, sai Abdullahi da abdulrahman.

Lokacin daya hadu da goggo Fatima sai yaji duk wani alkawari da yayi yau zai karyashi kodan irin takurin da iyayenshi suke mishi yaji yana son wannan bafulatanan mai sanyin hali ga sanyi kyau kamar wata yar India, bai dauki lokaciba yasanar da magabatanshi kuma suka yi abin cikin gaggawa don suma burin su kenan Dan su yayi aure ko Allah zaisaka yan uwa su iya rabanshi,

Duk wani Abu na al'adah anyi angama ansaka ranan aure Wanda har lokacin matar gidan bata da labarin,don ana gudun tashin hankalin da zatayi,

Yaune ake shirin tafiya kafin madaki domin daurin auren Fatima da alhaji nuhu umar, kuma alokacinne aka wuce da hajiya zahra asibitin ni'imah clinic domin yankan jikin datayi ta suma.

Idan ya muku zan cigaba da typing idan naji shiru sai wani lokacin

*DAGA ALKALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻

*BADARIYA*

®☄️
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION✍️*
{Gaskiya d'aya ce daga k'inta sai b'ata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar duniya da kuma lahira. }

🎐 G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN KARFE*•🏇

*Story and written*
*By*
*AUNTY NICE*

*PAGE*2️⃣

Hajiya Fatima ba ita ta farka ba har saida 'yan daurin aure suka dawo,  a cikin dakin datake banda kuka babu abinda takeyi , "ita kamanta ace alhaji nuhu yamata kishiya wannan ae ya toxarta tane,"

Kusa da ita yazo ya zauna, cikin nutsuwa yakira sunan ta, *ZAHRA* batare da ta dago ido taganshiba ta cigaba da kukanta, can tace ka kaini wurin hajiyata ni indai baka fasa maganan auren nanba, toh saidai ka sakeni.

Murmushi yayi cikin nutsuwa yace yanxu dai kiyi hakuri, hajiyan ma tana hanya tana tahowa, maganan afasa daurin kuma, banda ke hajiya mai yara har hudu mai wannan yarinyar zata tare miki? Ni a tunani na babu wani Abu dayayi saura a wurina Wanda zaki daga hankalinki akan na auri wata, mexata kwace miki Wanda da baki same shi ba? Babu,...  Kawai ki kwantar da hankalinki kada mutane su miki dariya,..  Aure kuma har an riga da an daura, kuma don ma kada su daga miki hankalinki, nace suyi wuninsu gaba daya a can, ko su 'yan jama'aren suwuce daga kafin idan angama wuni, .... Ko haka bai miki ba?

Mtsss nidai wlh baka isa ba daga kai har munafukan y'an uwanka da ita amaryan zaku hadu dani,    tunda auren baka fasa a sanyi zuciyaba toh zakayi  cikin tashin hankalinki,...   Tana

maganan tana kukda

Murmushi yayi yatashi yafita, yana cemata idan kingama shiriritan ki sameni a mota, yasa kai ya fita,... Yafi karfin minti 30 dabarin dakin kafin ta fito tashiga motan tana hararanshi, babu Wanda ya kula wani har suka isa.

Abdallah da Abdulrahman ne suka fito da gudu gudun su suka rungume mamansu, ...." Mama kinga yayah umar ya hanamu kunnan TV ko, inji Abdullah, rike hannun su tayi tana cewa kuyi hakuri daga yau babu wani Dan iskan da zai takurako agidan nan koyafi uwarshi da ubanshi, don nan gidan ubankune kuma babu wani Dan uba da kuke dashi, shima umar din halin ubanku ya dauko shiyasa bai gaji mutunciba.

Kada kai yayi kawai yana murmushi batare daya kulata ba, wucewa dakinta tayi kai tsaye tana ta zage zage sukuma suna binta a baya daidai shiga falonta ta hadu da babagana yana fitowa da sauri yakarasa ya rungumeta yana mama yayah jikinki? .... Riko hannun shi tayi suka shige dakinta gaba dayansu inda ta tarar da umar kwance akan gadonta yana rike da remote a hannun shi,...
Da sauri ya taso ya riketa yace mama mai yasameki? Mundawo akace kina asibiti, mama nah bakida lpy ne? A take hawayen dake idonta suka zubo tace bakusan babanku yau ya kara aure ba? .......mama aure babanmu yayi cewar babagana, amma mama shine kike kuka akan ya Kara aure inji umar! ... Don Allah kiyi hakuri mama tunda ba haramun bane kuma kada kibari masu aikin gidan nan su gane, a hankali suka cigaba da bata baki har tabar kukan ta tashi tashiga toilet don tayi wanka.

A kafin madaki kuma bayan an daura aure, kasancewar dama rannan jumm'a ne sai suka cigaba da hidimomin su na shirin walima da zasuyi bayan la'asar a cikin unguwar tasu mai suna *BADAU* cikin wani gida a gefen gidansu mai yalwatacciyar fili,
Bayan kowa ya shiryah aka wuce wurin waliman amma banda ummi na kasancewar tunda suka gama aikin abincin waliman taji jikinta bayamata dadi kasancewar cikinta dayayi nauyi, ... haihuwa yau ko gobe duk zai iya zuwa mata.

Washe gari ranan asabar ake wunin bikin, a nufinshi idan yamma tayi sai akaita gidanta dake bch a umguwar GRA cikin makurdi road, ita kuma ummi nah dauriya kawai takeyi SBD tanaso suna zuwa kai amaryah ta wuce asibiti,.... Haka abin yatafi zuwa yamma aka tafi da amaryah.

Isowar maman hajiya ZAHRA komai yasake burkice mata banda kuka babu abinda takeyi tana ta korafiwa ummanta, ...." Hm nace ki kwantar da hankalinki ZAHRA duk kinsa yaranki hankalinsu ya tashi, nace kibarni dasu duk zasu gane kuransu,, da sauri umar ya kalli kakarsu yace mi zaki musu kuma kaka? Baku yadda da kaddaran mutum ba kenan,? Don Allah ka tashi kafita kabamu wuri gaba daya baka kishin uwarka, anya umar akwai zuciyar imani kuwa a ranka?....cewar hajiya! Da sauri mama ta juyo ta dubi hajiya tace bayida imani kuma?

Haba hajiya kidaina irin wannan furucin, ....toh uwata na daina tunda ke babu hali kiyi kawaici akan yaranki Allah ya shiryeki, yanxu dai ni gobe kafin akawo amarya xantafi SBD musan abinyi.

Ummi na da kyar ta daure aka kai amaryah, sannan ta kamo hanya ta tafi gidanta, a gida tasamu abbanmu dasu walid da sadiq a zaune suna cin abinci, cikin dauriya tamusu sallama, sannan tanemi wuri da kyar ta zauna tana ya mutsa fuskarta,
Cikin kulawa Abba na ya dubeta yace jikinne halimah? Saida nace miki basai kinje bikinanba, amma haka ki kaki, toh tashi muje asibiti.

Ummi nah sai wurin asuba Allah ya sauke ta,ta haifeni tun isowata duniya kowa ya kalleni sai yayi mamaki don babu ko Dan farin jariran nan, babu abinda nabari a kakata, kamanni mu har ya baci, ga gashi kaman zai rufemun idonah.... "Masha Allah kawai Abba nah yake fada bakinshi yaki rufuwa da farin ciki sai addu'a yakemun yana tofawa, umminah said kallon shi kawai takeyi tana mamakin wannan murnan da yakeyi don ko haihuwar yayah na walid baiyi haka ba.

Gari na wayewa aka sallame mu lokacin kuwa har kakarmu ta iso. Kowa ka ganni sai farin ciki yake kaman ba'a tabaa haihuwa ba.

Goggon bch ce ta juyewa ummi ruwan wanka sannan takawo wani daki Wanda za'a wankeni , kusa da umma ta ajiye tana bismillah umma ga kishiyar ki wanketa subul banda kishi, kowa a dakin saida yayi dariya, sannan Abbah nah yace haba yyh zatayi kishi da takwaranta?
Da sauri umma ta dubeshi tace na dauka autana zaka saka, SBD taxo taya goggonta murnan aure,? Goggon bch tace nima nayi tunanin haka,.. . cikin sanyin muryan Abba na yace toh ae ba komai ummah duk yadda kikace haka za'ayi dama ban riga danayi huduba ba, dama nafiso naji shawaranki,..." Toh kasaka sunan y'ar uwarka, Allah ya muku albarka ya kara hadamun kanku,,.....Ameen suka amsa gaba dayansu!!

Ranan suna aka rada mun *FATIMA* Wanda Aunty nah tace akirani da *BADARIYAH* gaba daya jitake kaman ta kasheni don so. Kaya sai da tacika akwati na mai suna, sannan tayiwa ummi nah, kai hattah Abbah nah sai daya samu nashi.

Rayuwar gidan Aunty nah sai a hankali, asalin kitanta da aunty ya farune da dagewan Alhaji nuhu akan yaranshi suce mata Aunty, Wanda saida akayi dabi da uwarsu, kowacce mace tanada sashenta a gidan, na mama dakuna hudu ne da falo biyu, don kowacce akwai side din babansu a gefenta, falon shi da daki, sai kuma kowa falon ta da three bedroom aciki, kowanne da toilet dinshi, duk yaddah mama tayi kada yaranta su rabi aunty abin yaki yiwuwa SBD daga babagana har su abdallah da abdullahi kullum suna gefen aunty amaryah, cewarsu tana kunna

musu cartoon kuma tana koya musu karatu, amma shi kuma umar babu mai fahimtan alkiblanshi SBD ko a fuskanshi da kyar ka fahimci mai yake ciki,  shidai kullum yana tare da mahaifiyar shi don Allah yasamasa tsananin kaunanta da yimata biyayyah, kuma kullum takama korafin ancuceta anmata kishiya yana tausaya mata saidai bazai tofah ba.

Umar yana da 12yrs lokacin yana jss 2 alokacin yana Atap secondary school, shikuma babagana yana 8yrs shikuma yana primary 4 duk dai a Atap suke, sukuma twins suna da 4yrs alokacin suna nursary 2 amma su a sunshine suke,.

Yaran Alhaji nuhu dukkansu fararene  kasan cewar daga baban har maman farare ne, sai duk yaran sukayi fari babuma kaman umar danashi bai bar komai na mahaifiyarshi ba, kunsan dai irin kyaun shuwa kaman wani balarabe yake, saidai halayenshi babu abinda yabari wa babanshi.

Akwana a tashi ba wuya har yau nakai shekara 3 lokacin abbanah yasamomin makaranta a cikin gwallagan wani makarantane na y'an izalah, ana hada boko a Arabic, tunda na taso nakeda farin jini a wurin yan matan unguwarmu, kullum ana mun wanka za azo a daukeni sai ummi nah ta ganni.
    Cikin masu dauka na akwan wata da gidan suke yake makwaftaka Dana mu, mai suna humairah babanta wani babban costume ne duk cikin unguwar mu babu gidan dayakai nasu kyau, a lokacin humairah tagama jss dinta zata tafi ss class dinta, suma duk yaran gidan su biyar duk mamansu daya, su hudu duk mata ne, namijin su daya shiyake  bin humairah, mai suna kamal, Dan gayune na karshe ga raha, shima yana jss 1 lokacin,.

Maman su hummairah mai sona mummy cikakkiyar yar kasuwace, gata da alkhairi, sukama mutanen alkaleri in,badai kirki da kyautaba, gata da son surutu kuma Allah yasakamata son a da umminah.

*DAGA ALKALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*

®✍

*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION ✍️*
{Gaskiya d'aya ce daga k'inta sai b'ata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar duniya da kuma lahira. }

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN KARFE*•🏇

Story and written
By
*AUNTY NICE*

*PAGE*3️⃣

Rayuwa akwana a tashi bawuya wurin Allah, yau ni *FATIMA* *BADARIYA* nake gama xana jarabawata nagama jss 3, wanda alokacin kuma yayi daidai da gama karatun Aisha humaira a university of Maiduguri inda ta karanci fanin chasa da kididdiga na kudi, wato *ACCOUNTANCY*

Mummy banda shirye-shiryen dawowar humairah babu abinda takeyi,
Nikuma nida autar su nafisa dama tare muka taso, kuma albarkacin ta daddyn su daxamuje primary one ya hadamu a school daya, wato *DOLPHIN MARIA*
Kamal kuma yana Sudan inda yake karatun shi na law, sai mai bishi hafsat Wanda ita haka yanxu tana school of nursing, sai umaimah da take jss 3,... Allah yahada kanmu da nafisa duk da ita mai yawan hayaniyace kaman Adda humairah gasu dukkansu mayun son gayune, a inda dole saida na taso da son ado, nafisa itama farace kaman yan gidansu, kuma duk saitaxama tafisu kyau, don batada maraba da umaimah da kamal, don babu abinda suka bari na mummy,
Gidan akwai su dason junansu gwanin ban sha'awa, don duk abinda daya yakeso shi daya yakeso, a wannan lokacin kaman babu gobe haka sukeji domin da wowar yar uwarsu.
Sanadin aunty Fatima itama tana aure gidan kudine sai naso yaxo daya da mummy yawan zuwanta gidanmu yasa suka kulla kawance duk da ba sa'annin juna bane.

Zuwa wannan lokacin Aunty nah yaranta uku, gidado shine babba Wanda nabashi shekara daya, sai khalifah mai sunan kakanmu mustapha, sai kuma Mujaheed Wanda shine autan gidan Wanda yanxu haka baifi shekara hudu ba, wato gidan aunty dai Allah bai baso arxikin diya mace ba, daga Aunty har mama, shiyasa aunty ta dauki son duniya ta daura mun, a nufinta bata ki Abba nah ya bar mata niba, Wanda shima yakasa kawaicin bata ni, don a gaskiya su Abba nah Allah ya saka musu zumunci a tsakaninsu, Wanda idan ka ganmu da goggon bch zaka dauka nan duniya ita ta haife mu, haka idan kaganmu da Auntyn mu, haka zalika abban mu yaddah yakeji da yaransu, tunba ma haiday ba, kasancewar shine jika babba a family mu, Abba nah yana sonshi so mai tsananin gaske tamkar dan da ya haifah, kuma duk abinda

hammah haidar yafada toh ya zauna, a dukkan gidaje ukun, don Allah yabashi nutsuwa sosai, hammah haidar likitane a fhaidar yagama karatun shi na likita a zaria yanxu haka yana service dinshi a Aminu kano, pediatric Dr ne.

Khalil kuma Dan goggon bch yanxu haka ATBU shida walid inda suke 300 level a computer science, tsananin amintakarsu ne yasa suke course daya,
Sai kuma sadiq da bappah inda yanxune suka gama secondary su, suna shirin tafiya buk inda haidar yasa ma musu admission sukuma zasu karanta mass com, daya kuma civil law.

Rayuwar gidan Aunty yana nan jiya ya yau, don tsananin jajercewa irin na babansu gidado shiyasa mama takasa raba kan gidan, saidai tayi nasaran raba su gidado da shigowa side dinta, amma su Abdallah wurin aunty shine filin baja kolin su, xuwa wannan lokacin hamma umar baya garin, kasancewar shi a maiduguri yake aiki soja ne, bai Dade dagamawa ba, dayana Kaduna naifi 3month ba ya koma Maiduguri, Wanda mama taji dadin hakan don tana so sukara hada kansu da zainab yar kanwarta, zainab ba yarinya bace don yanxu haka tana service ne a maidugurin tsakanita da babagana babu nisa baifi watanniba, inda shikuma babagana yanxu ne yake final year dinshi a Maiduguri, .... Su twins kuma yanxu ne suka shiga lavel 1 a Zaria.

Aunty tazama hamshakiyar hajiya kuma babbar ma'aikaciya a T.H , tabawa yaranta tarbiya mai kyau Wanda basu raina nagaba dasu, gidado yana jss 2, khalifah yana primary 4, auta mujaheed kuma yana nursay 2, kasancewar yaranta akwai interval na 5yrs a tsakaninsu,

Ni BADARIYA ina samun kulawa sosai a family mu kasancewar ni dayace jika mace, sannan ba yabon kaiba duk familyn babu mai kyauna don ni kadaice nayi kalan umman mu, kuma na kwaso asalin kyaunta kamar ka lasheni, duk inda na wuce idon mutane na kaina kowa na maganan na cika yanga da sakalci, babu abinda yake daukan hankalin mutane akaina shine suman dayayi mun rumfah ta ko 'ina, ga idanuna manya da cikar gashi da gashin gira, duk yadda na mutsa bakina zanyi magana sai na juya idona Wanda nikaina bansan inayiba, saidai naji yan class dinmu suna toh yauki, sannan cikar cinyana da hips dina kadai idan ina tafiya sai yaja hankalinku duk da ina 'yar shekara sha uku amma kamar Wanda tayi 16yrs, ni BADARIYA babu abinda nakeso sai kamshi, inason kamshi kaman yar kanuri.

A family mu kowa yatashi yimun hidima yakemun, idan akace sallah yaxo har rasa kayan wa zan fara sakawa nakeyi, kakanuna ji suke kaman sunfi iyayena sona, duk inda na daure fuska kowa kasa jin dadi yakeyi.
Tsakanin goggo nah da Aunty nah nakan rasa waye tafi sona acikin su, domin wani lokaci idan goggona ta xuba mun ido har hawaye takeyi, idan an tambayeta takance Allah ne kawai yasan yyh takeji a ranta idan taganni, Aunty na kuma komai tagani zakaji tace na baby nane, Wanda har yau nakasa tashi daga matsayin baby a wurinta, sannan duk bayan 2wks zata so ta daukeni nida nafisa nah muje saloon da ita, a wanke mana a mana kitso babu abinda yake data fashi saidai idan bata gari, toh mummy CE zata karbeta.

A fannnin mummy kuwa duk fitan datayi Dubai sai kunga kayan datake jibgo mana, nida nafisa iri daya, adda umaimah da adda hafsat iri daya,

A fannin Adwai. humairah kuma, duk wani kudi da ake aika mata a sch, toh sayayyah zatayi wa ni da besty nah nafisat, amma gidan mu babu Wanda yakai hammah walid da abbah na nuna mun soyayyah, ummi nane kawai take mun fulatanci, hammah sadiq kuma bana gane mishi kullum muka sauna sai munyi fada, amma idan wani ya taba ni sai inda karfin shi yakare,... Idan tsokanashi ya tashi kuma zakaji yana waka wai "BADARIYA baka danginta farare" hmmm duk abinda nakeyi sai na fasa ihu ina Abba mai yasa nice baka acikinsu, da kyar ake rarrashina, shikuma hammah walid yace sai ya fente mishi fuska shima.

Soyayyah mai zafi akeyi tsakanin zainab da hammah umar a Maiduguri, duk da tsarinsu ba dayaba hammah bamai hayaniya ba amma zainab irin masu surutu kaman aku, ga ta tashi a gidan naira don mahaifinta yataba yin gwamna a maiduri zamanin mulkin soja don tsohun soja ne, kuma dama family su masu kaxamin kudine, yagaji arxiki mai yawa, zainab ko pant dinta mai gyaran dakine takeyi mata tsabar gata,
Babu yadda maman zainab batayi da hamma ya xauna a gidanba, amma fir yaki yaddah, donshi bayason takura, kuma bayason hayaniya gidan kuma sai a hankali.

Besty! Besty!! Daguda na nafito daga dakin ummi nah danake gyara mata, saura kadan muci karo da besty nafee, da sauri na matsa ina kallon yaddah take hakki nace besty yyh how fah? .." Adda tadawo" da sauri na turata gefe na xari gyalenah na riga aa tafiya gidansu, da sauri itama ta biyoni tana besty jirani tana dariyan yadda nake tafiya, tana dariyah tana ikebe super wannan kayan kashin suna shan juyi 😄, ko kulata banyiba don nasaba jin wannan shegan da takemun, gudu gudu muka fada cikin falon mummy inda mukejin shewansu, kai yaran mummy akwai hayaniya, da gudu nafada jikin addah nah, itama cikin murnan datakeyi ta rungumeni tana kai kai kai mummy haka yan matan am suka girmah? Tana jin dadin ganinmu,
"Adda ina tsaraban mu? cewar besty nah" ..... Ku miko mun wannan jakan inji Addan mu, da Saudi Adda umaima ta miko tana wlh nafisatu kinji kunya ko hutawa Adda batayiba kike neman tsaraba? Amma dai Adda kada kiyi fushi bamu kawai tunda tayi magana, dama babu Wanda yakai umaimah abin dariya agidan,.... Hafsat na dariya ta rike jakan race Adda rabo dasu kije ki huta basu da tsoron Allah kwanannan mummy tadawo daga Dubai takawo mana tsaraba.

Rabu dasu sunci albarkacin sister nah BADARIYA, zan basu hankalinsu ya kwanta, mummy datake jikin dinning tana ta dariyansu don dadi takeji idan taga yaranta hankalinsu akwance suna raha.

Wani laida ta mikawa hafsat tace sis ganaki da irin abun da takike so, tana budewa raga wasu English wears ne kusan set biyu da turare, sannan ta miko na umaimah shi kuma wasu materials ne guda biyu da turare, sannan ta mikawa nafisat nata ita kuma lace ne guda biyu da Mayan make-up da turarukanta, sainawa dogin riguna guda biyu da laffayah guda biyu da

kayan make-up da turaren wuta da humrah gasu ribbons kala kala, bansan lokacin dana sake rungumeta ba ina sai Aunty nah, kowan my sai murna yakeyi,   mummy CE taxo wurin tana gaskiya Doug kin burgesu a gode, kowa kinsane choice dinshi, dukkan mu godiya muke mata kaman zamu lasheta, tana dariya ta mike tayi daki tana cewa barinayi wanka nayi sallah na huta.

Hammah umar ne da abokinshi Yusuf a zaune akan dinning din gidan Aunty falmata suna cin abinci hankali kwance, ....." Aboki gsky zainab ta hadu kuma tana sonka sosai, nima ina fatan Allah yabani mai sona irinta kyakkyawa,"cewar Yusuf.  Hararanshi kawai umar yayi ya juyar da kanshi baice komai bays cigaba da cin abincinshi,  zuwa can saiga zainab tafito saga side dinta cikin wani dogon rigan lace baki, kasancewarta fara bakaramin haskata yayiba, kujeran da umar yake zaune ta nufa da Sauri cikin rawan kai tace honey ina ta sauri naxo nayi saving dinka, Ashe har kunfara takai mishi kiss a gefen kunnen shi tana ta smiling,
Kara daure fuskan shi yayi yana cewa meye haka mine? .... " Yusuf ko banda dariyansu kasa kasa babu abinda yakeyi, shi kan a duniya waye zai iya saka abokinshi fara'a ne? Yadauka a gaban zainab sai saki ranshi still itanma baya wani walwalah kaman Wanda aka mishi dole bayan yana da tabbacin umar shiyace yana sonta, kai al'amarin abokinshi sai shi.

Aboki kana lpy? Inji zainab dake kallon Yusuf, yana murmushi yace mun sameku lpy? Batare da ta amsa ba ta maida hankalinta kan ummar tace yi hkr mine, " bai kalleta ba ya kada kanshi kawai.

Honey toh yaushe zakazo? Naji kana cewa mumcy zaka tafi bch dis commig weekend? ..... " uhmm kawai yace yana duba wayanshi, hannu shi yana rike da kofan Motan, shi kuwa Yusuf banda dariyansu babu abinda yakeyi yana ganin wannan irin hadin ko tayayah za ayi?  Batare daya sake kulataba ya shige motanshi yaja sukayi gaba.

*DAGA ALKALAMIN AUNTY NICE*   ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*

®✍
*GASKIYA* *WRITERS*
*ASSOCIATION* ✍🏻
{Gaskiya d'aya ce daga k'inta sai b'ata, burinmu mu fadakar da al'umma domin ribantar duniya da kuma lahira.}

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN KARFE*•🏇

Story and written
By
*AUNTY NICE*

*PAGE*4️⃣

"Adda Humairah kinga Besty taki k'arasa nata aikin, ni kuma yau ba xan taya ta ba, don ina gamawa zan tafi gida na shirya, don da wuri driver Aunty nah zaizo ya daukeni".

Sannan ta maida hankalinta kan aikin data keyi.

"Yanxu sister har murna kikeyi kitafi kibarni ko?, bakya so ma kiga zuwan yayankin ko? Toh shikenan sisi nah".

Lahhh Aunty ba haka bane, kawai dai kada taga kaman naki zuwane, amma dana jirashi mun gaisa,cewar *BADARIYA*.

Da sauri-sauri nagama abinda nakeyi na mik'awa Adda, sannan na musu sallama nayi gidanmu,

K'arfe shabiyu da rabi drivern su Aunty yaxo d'auka na, bayan ya dawo daga d'auko su Gid'ad'o daga Islam, cikin farin ciki da murna muka kama hanyan zuwa G R A.

Ina shiga palon Aunty na tarar da ita tana kallon wa'azin sheikh Isa Ali Pantami, da sauri na fad'a kanta ina murnan ganinta, itama cikin murna take cewa.

" Lale maraba da y'ar Aunty, yaya su Ummi da Abba?".

Fuskanta d'auke da fara'a.

nima cikin farin ciki nake tashi daga jikinta ina cewa duk suna gaisheki.

Sannan na d'auki jakan kayana na tafi d'akin da nake sauka, na gefe dana Aunty, ina shiga

Mujaheed yana bina sai labari yake bani.

"Adda Riyah yau Hamman mu zaizo, zai kawo mana kaya dayawa Adda Riya".

"Haba Autan Aunty, Ashe yau zaka bani naka nasa ka ko?".

Yana dariya yace harda bindigan shi zai kawo mun inje in harbe turkey.
Juyowa nayi ina kallon shi ina dariya nace.

"Turkey yana binka kenan ko?".

Adda Riyah Hamma Gid'ad'o ne ya zuba mishi albasa sai kawai turkey ya biyoni, nayi super saina fad'i a kasa, shine na gayawa Hamma nah, yace zai kawo mun Gun d'in shi na harbe turkey ma.

Aunty ce ta shiga don jin dariyan danake tayi tace.

"keda amininki ko?, ai yau bazai barki ki huta ba da labari, idan kin gama kixo muje kitchen ki tayani gyaran wurin don yau da wuri nakeso nagama aiki nah".

Aunty nah ce yau xata karbi girki, shiyasa tun 4:30 muka shiga kitchen had'a wannan had'a wancan kawai mukeyi, ni kuma Aunty tace na mata ferfesun kaji amma na kalwa, sannan na had'a zobo, wuraren magarib mukaji ihun su Mujah da khalifah saboda shigowan motan hamman su, da gudu sukaje jikin motan, dai-dai lokacin da Gid'ad'o ya fito daga d'akin su yayi Alwalah zaije mosque, shima da sauri yayi hanyar waje don taryo hammansu,.... Duk da kasancewar hamman baya wasa da kowa, amma dabi'ansune daga d'ayansu yayi tafiya idan yadawo zaka gansu kaman su lasheshi shima kuma duk tsaurin shi, baya hantaransu harsai yabasu tsarabansu tukun yake daure fuska kuma.

Bayan an idar da sallan ishaa ne, Baba ya shigo tare da Hamma Umar, Wanda suka had'u a masallacin k'ofar gidan.

Direct polon Baban suka shigo na side d'in Aunty suka zauna suna ta hiran yana yin mulkin kasan, a haka Auntyn ta shiga ta samesu, Wanda sai a lokacin Hammah yake gaisheta cikin risinawa, shidai har a kullum tsaftar matan da biyayyanta yana bashi sha'awa kuma haka tana bada tarbiya sosai wa yaranta.

Aunty ce ta kalli Gid'ad'o tace.

"Kacewa Riyah ta taimaka maka Ku fito da abincin babanku".

" Auntyn yarah yau y'ar kice a gidan?,yana murmushi yana duban Auntyn".

Itama cikin farin ciki ta ke amsa mishi,"Wallahi kam, yau kan da k'yar sun barta taxo mana hutu".

Gid'ad'o ne ya fara shigowa sannan ni na biyo bayanshi da tiren dana d'aura Jug da cups akai, kan dinning mukaje muna jerawa, sannan nayi main palon domin nagaida baba.

Yana fara'a yana "Yau ga amaryar Mujahid, don yau a k'wando zamu rufeki Fatima har sai ya girma ya iso ki".

Inji Baba, gaba d'ayanmu dariya mukeyi idan kacire Hammah dako d'aga kanshi baiyi ba ballantana ya ga abinda mukeyi.

Sunkuyawa nayi har k'asa ina murmushi domin Mujaheed da sauri ya rufe fuskanshi wai ance nice amaryar shi, sai dariya yakeyi, ina dubanshi ina murmushi nace.

" Baba mun sameku lafiya?".

Yana dariya yace." Lafiya k'alau Fatima yaya su umminkin?,ya kuma karatu, ina fatan babu wani matsalah ko?".

Kaina a sunkuye  cikin kunya na amsa mishi da Alhamdullih baba babu matsalan komai.

Sannan na juya na dubi Hamma a hankali nace, "Sannu Hammah kazo lafiya?". Bai d'ago ya dubeni ba yace.

" Lafiya k'alau".

Nima mik'ewa nayi zan wuce ciki, saiji nayi Mujaheed yana cewa. "Aminiya kidawo kiga bindigar Hammanmu, idan yabani zan baki aro".
Kowa na dake cikin palon saida yayi dariyan shi, shima Hamman saida ya d'ago idon shi yana d'an murmushi yana duban Mujaheed d'in, domin shi mamakin yaron yakeyi kaman bad'an 4yrs

ba idan yazaro magana, don isuwarshi da kyar ya barshi yaje yayi magarib sannan yazo ya basu tsarabarsu, amma duk da haka saida yaron ya rik'e hannu shi yace.

"Hamman ina bindigan da zaka kawo mun?".
Dafa kanshi yayi yace.
"Sorry s autan baba, namantane amma zan duba maka a garinnan".

Sannan yasamu ya barshi suka taho da tsarabarsu shikuma yayi side d'in mamanshi.

Baban ya dubesu yace. "Ku zo muci abinci kada dare yayi ko".
Duk kansu suka tashi sukayi kan dinning d'in amma banda Hammah, har saida Aunty ta mishi magana tace.

" Hamman su kataso mana kaima kaci towun buskine fah".

Cikin d'an gajeruwar murmushi ya mik'e ya nufi dinning d'in, shidai haka kawai yakejin kunyar matar kuma ya kasa sabawa da ita.
Kowa ya hallara akan dining d'in sai k'aran cukulah kawai kakeji, tarbiyan yaran Aunty ne idan anacin abinci bakajin muryan kowa, duk surutun Mujah shima lokacin baza kaji shiba, zuwa can Nujah ya ajiye spoon d'in shi ya d'auki cup d'in da aka saka mishi zobo ya karb'a, ae kuwa kawai ji akayi ya tuntsire da dariya, da sauri Aunty ta dubeshi tace.

"Lafiya Mujah nah?".

Ajiye kofin yayi yace."Wallahi Aminiya ta iya zobo kunji dad'i kowa har tsakan kaina inji mumman kafi".😄

Dukkansu saida suka kwashe da dariya, Aunty takai mishi rankwashi tana kaji mun tsohun yaro, duk lokacin da santinka ya debe ka sai kace ummah tace meyi? Baba yana dariya yace.

"Dan Mujah wato zob'o yayi dad'i Kkodai don Aminiyar kace tayi?".

Duk da dakiyan Hamma amma saida ya daraa yace.

"Baba ni narasa wani irin wayo yaran nan take dashi wallahi".

Baba ma yana dariya yace. "Ae Mujah sai ya sayar dakai da wayon shi".

A haka aka kammalah cin abuncin sannan nida Gid'ad'o muka tattara kayan zuwa kitchen, sai bayan sungama kallon network news Hamma yayiwa baba da Aunty sallama ya wuce wurin maman shi.

" Ina kashiga umar?".

Inji mama da ta k'ura mishi ido yana shigowa, batare daya kalletaba ya nemi wuri ya zauna yace.

" Ina wurin Baba ne?".

Mtsss tsaki taja tace. "A gefen wancan sakarar ko?".

Ba tare da ta jira taji mezai ceba tace."Ga abinci akan dinning kaje kaci, ga dare yayi kazauna can kana shiririta".

Yana danna remote bai dubeta ba yace." Munci tare da Baba..... "

"Kan bala'i don wula'kanci kaima ta fara a surceka kenan? Toh wallahi daga yau bazai yiwu ba kada na kuma ji, kaida hidimanta baya ga banka amma shine yanxu kaima zaka zama kaman su Babagana? Yau isowarka amma baka zo kaci abinda nasaka aka girka makaba sai abinda jahilar matar Babaka kaje kaci jagwal-gwalonsu".

Baice komai domin shi bai iya tana magana yana yiba, saidai acikin zuciyarshi yana idan banda Mama keda masu aiki ke miki girki ina saki had'a da d'inshi da tsaftar shi da Wanda ita takeyi da hannunta? Shi sai yanxu ya gane dalilin da yasa Babagana koda wasa baya son cin abinci a side d'in su sai dai side d'in Aunty, shi babu abinda ya mishi dad'i irin ferfesun da zobon, don yana son yanayin girkin gargajiya, yaji kayan k'amshi yadda girkin Aunty yayi mishi dadi kaman a jama'are.

Side din su Hammah Umar shine daga ka shigo gate d'in gidan shine side d'in su a farko, shida Babagana.

Palour ne da d'akuna biyu kowanne da toilet d'in shi, amma tsabar tsoron Hammah Umar, Babagana bai cika zama a palon ba

Saboda tsananin tsaftar Hammah, shikuma Babagana baya son gyara sai dai ayi wanna a fita kawai.

Riyace rik'e da hannun Mujaheed ta rik'o su har jikin Motan su, inda driver yake jiransu yakaisu islamiya, Mujaheed sai surutu yake mun.

"Addah Riyah inace bazaki tafi ba ko?" Idan kin zauna zan saya miki ball kinji, zan saga miki gun me kadanki adda Riyah".

Itadai sai dariyanshi takeyi tana cewa. "To Amininah sai ka dawo ayi karatun sosai babu inda zanje".

Ta window Hammah yake kallon mu, muna had'a ido nayi Sauri na sake hannun Mujah na juya nayi gida, nikan haka kawai mutumin yake mun kwarjini.

Zuwan saurayin Addah Humairah daga kano, gaba d'aya gidan sai farin ciki sukeyi, domin su tsarin sune duk abinda nasu yake so suna so.

Bayan sunyi hira ne ya gaisa da Mummy sannan yake gayawa Addah ta fad'a a gida iyayenshi zasu zo sati na sama domin a saka musu rana.

Tunda ta gama school d'in yanzu, cikin murna tazo ta yiwa Mummy bayani bayan taraka Ahmed jikin Motan shi yatafi.

Babu komai inji Mummy. "Bari Daddyn Ku yadawo duk abinda ake ciki zakiji".

Hutun da Hamma yaxo dama na kwana Biyar ne, nasan cewar ranan asabar yazo ranan Sunday zai koma, daman Saturday Aunty tasaka ni na gyara kajin da tasayo guda goma.

Na agric domin muyiwa Hammah dambu nida mai mata aiki Innah Ladi, sannan ita kuma Aunty tana aikin mishi cake da cincin mai kwakwa, bawai ta tab'a yi mishi bane idan yaxo, amma da yake wannan zuwan nashi duk rannan girkinta yana biyo Baba suci abinci tare, kuma hakan yana mata dadi, don wata rana tayi alale da kunun gyad'a da safe, shima yayi dai-dai da Raman ya shigo, ba kad'an ba yaci alalen yasha kunun sosai da zai fita ya d'an duka yana rike da hanmu Mujaheed yace.

" Aunty idan kunun yayi saura a bawa Gid'ad'o ya kawo mun".

cikin Sauri Aunty tace.

" Akwai, dayawa ae Fatima tayi bari su zuba maka a flask sai sukawo".

"Riyah tashi kije ki zuba mishi kai kuma gidado ka kai mishi".

"Mummy yau Hammah zai dawo mezaki saka a dafah mishi?".

Cesar Zainab tana duban mamanta.

" Zee Hamman kinne mai ra'ayi idan yaga dama ko lek'omu yau d'in bazaiyi ba".

Toh ki kira kiji ko zaizo mana? Donni wallahi idan yaga dama bazai d'auki wayan ba, zaice yana kan hanya, kuma d'azu munyi magan.

" Hmmm Zainab kina da matsalah mutumin da zaki aura amma kike tsoronshi haka?, Idan anyi auren wallahi ina tausaya miki don ya gane kinfi son shine".

Cikin zunb'ura baki Zainab tace. "Toh ni yaya zanyi mutunne komai kayi zaice laifine, to basai na barshi da halinshiba, tun da ance bai tab'a cewa yana son wata ba a rayuwar shi saini ae na ciri tuta". 💃

Sakaryar yarinya kede idan da badan mun tashi tsayi da maman shiba ina zaice yana Sonki? Nidai tunda ya fad'a ae an wuce wurin, barima na tashi naje nafara shirin zuwanshi.

Har side d'in shi nida Gid'ad'o muka kai mishi sakon Aunty, a tsorace muke da kyar Gid'ad'o ya daure yayi sallama, sannan da Sauri na ajiye nawa roban nace don Allah Gid'ad'o ka Shiga mishi dashi wallahi tsoron shi nakeji, kafin Gid'ad'o yabud'e baki yamun magana, na juya da gudu nayi side d'in Aunty, dole haka Gid'ad'o ya d'auki roban ya shige Palon, har k'asa ya durk'usa ya gaida Hammah sannan yace.

" Gashi inji Aunty tace akawo maka".

" Ina Wanda ta gudun ce mata akayi ni dodo ne?".

Inji Hamma. Gid'ad'o sai zare ido yakeyi kaman yayi karya wa sarki yace. "Daman ta tayani d'auka ne".

"To kada ta k'ara zuwa mun side d'in nan idan bazata shigo ba".

Dariya Muke tayi nida Gid'ad'o, kowa yana dariyan kanshi.

Da safe wurin karfe 8:00 munafalon Aunty suna ta shirin tafiya islamiya, ni kuma ina sakawa Mujaheed sucks sai labari yake tabani babu tsattsayawa, sallama Hammah yayi ya shigo, da saurin su rige-rigen gaishe shi.

Har k'asa da inda Aunty take yaje ya zauna bayan ya gama amsa musu gaisuwan.

" Ina kwana nace mishi a nutse".

Ba tare daya kalleni ba yace "Lafiya". Sannan ya gaida Aunty, yama mata godiyan abinda ta aiko mishi, Aunty na had'a ki da wahala haka, toh nagode.

"Babu wani wahalah abu da duk aikin ma Riyah ce tayi". A hankali ya tashi yace.

"Toh Aunty nagode sai next month insha Allahu".

Tashi yayi ya fita yayi side d'in mamanshi.

*DAGA ALKALAMIN AUNTY NICE*✍🏻✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*

®🖋
*GASKIYA WRITERS*
*ASSOCIATION*✍🏻
{Gaskiya d'aya ce daga k'inta sai b'ata, burinmu mu fadakar da al'umma domin ribantar duniya da kuma lahira.}

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN KORFE*•🏇

Story and written
By
*AUNTY NICE*

*PAGE*5️⃣

Yusuf wai meye ka zauna kana ta dariyah ne? Nifah ban cika son abinda kakeyiba.

•• dariyah Yusuf yasakeyi, sannan yace aboki bakasan wani jagwal bane? Yarinyar nan da yake jakah ce, wai na turo iyayena, ae saina dannah ringing tone nace ana kirana, zamuyi maganan

later😄😄.

Allah ya shiryekah, toh idan kasan ba aurenta zakayiba toh meye na zuwa? Kaifa wlh kana da problem Yusuf!..... " Toh meye laifinta?.
Haba aboki bakace fan!, ni kawai bodyn tane ya debe ni, kuma sai akayi rashin sa'a, wai na turo😳 na aureta nakaita ina? ai ni mace fara dogowa mai gashi nakeso aboki, amma bakar mace ae na shiga uku.
Mtsss amma kana da problem, meye a jikin farar Wanda bakar babu? ae kasamu mace mai hips da boobs, kasamu mace mai shagwaba da yanga ae kagama riban aure, ballantana ta hada da tsaftah da iya girki, ga kwalliya, toh ai aboki kawuce wurin a wajen zaben mace, ni anawa kalan mace baya cikin choice dina ko fara ko wata baka, ko wata chocolate, ni kawai qualities din Dana zayyana maka sune abinda nakeso.

Haba aboki, toh meyasa kaso zainab? ae ita bata da hips bata da boobs, dogowace kawai, saidai yana da gashi ga iyah kwalliyah.

Hmmm zainab choice din mama ne, ita ta matsa na nemi zee, sannan ni kwalliyan zainab bai burgeni SBD ko yaushe English wears ta ke sakawa, ni kuma traditional kwalliya ne yake ban sha' awa, especially naga mace na saka dogon riga,.

Shiru Yusuf yayi zuwa wani lokaci sannan yace abokina kenan bayan ka auri zee zakasake wani auren kenan?.... " babu auren dazan sake, sbd ra'ayi na namace dayace kawai dai zainab tayi sa'a".

Chabb amma ko baka morewa rayuwar aure ba, ae ka auri matar da tayi dai-dai da tsarinka, shine jin dadin rayuwar auren.

Har tsawon wani lokaci babu Wanda yasake magana acikinsu, kowa da abinda yakeyi, Yusuf yana ta tabe-tabe a kan wayanshi, hamma kuma wanka yatashi yashiga bayan yagama shiryawa ya dubi Yusuf yace muje gidan su zee muyi dinner cos am felling hungry kuma bazan iya zuwa restaurant ba.

**********

Bayan iyayen Ahmed saurayin Adda humairah sunzo ansaka rana, Wanda an tsayar dashi nanda four months lokacin mun sake dawuwa Hutu, kowa a gidan kaga fuskarshi sai annurin murna kefita, a gidan ummi na ta kusan wuni don tare sukayi abincin karban bakin da 'yan uwan mummy Dana daddy.

Da yammah besty nah tazo gidan Aunty wurina, da gudu Nazo nayi hugging dinta, kaman munyi shekara bamu haduba, na kaita har cikin dakin Aunty suka gaisa Wanda lokacin aunty nah bata dade da dawowa daga kafin madaki ba domin duba Jikin bappah.

Dakin mu muka wuce ina rike da hannun ta, har bakin gado na ajiyeta sannan naje kitchen na debo mata cake da coke nadawo cikin dakin,  besty yyh Addah nah? Wato bata missing dina ma ko? Kema kikace mun zakizo tun last week amma shiru nayi fushi ae.

Haba besty wlh munje alkaleri ne last week, kuma wlh tun da safe naso zuwa amma Kinsan yau ankawo gaisuwan Addan ki, kuma ma sai kawai akasaka rana,  .... Da ihu na daka tsalle nace dagaske? Wayyo Addah nah zamu sha biki💃💃  "ita dai besty sai dariyah na takeyi, tace zamu sha biki kuma zamuyi mssn Din Adda wlh, ni har nafara jin wani iri wlh besty" .

Wlh hakane besty, ni yanxu zanji shiga gidanku baxai mun dadiba, amma bakomai zamuje kano mushana wlh, hiransu sukayitayi har aka kira magarib sannan suka tashi sukayi sallah, bayan sun idarne badariyah ta shiga kitchen ta debo musu abinci, Wanda gwaten doya akayi, kuma dama yawanci idan kaga sunyi tuwo to baba yana side din. Ana kirana ishaa nafisa suka shiga dakin aunty tamata sallama zata tafi, " haba nafi na dauka kwana zamuyi?" Aunty ae bantam baya ba, tana murmushi tace kawai zan koma sai wani lokacin, " toh kuje driver yakaiki ko,sanan ta mikawa riyyah 1k tace tabata.

Bayan ta rakata wurin da driver yake, tana mishi bayanin Aunty tace yakai nafisat kawai saiga mama da kawarta sun fito daga side din mama, daidai lokacin badariyyah ta budewa nafisat kofan shiga.

Kai dan talaka bai iya samun wuriba, bandake badariyyah kike ko bahijjah? Har Kinsan ki bude mota wa kawa, an samu na banza ko? Wlh kawata ina gaya miki jaye- jayen yaran talakawa bayida amfani, don gaba daya auren su masifah ne, " kawawar mama Wanda bata da nisa dasu tace ae hajiya da amiki kishiya da y'ar talakawa gwanda akawo miki y'ar minister, don ko ba komai za a kawo muku baki masu shiga manyan motoci, amma y'ar talaka saidai tazame muku kiyashi, kowani sshirgin ta janyo muku, gaskiya kawata kitashi ki tsaya,
Mtsss mama tajah tsaki tace gata baka sai bakar aniya,

Da sauri nayiwa besty sallama raina a bace nace kiyi hakuri besty sai kinganni gudu-gudu na juya nayi side din Aunty,  itama besty shiga tayi da sauri domin badon darajan Aunty ba dabazata shiga motanba, domin ranta yayi mugun baci, ita dama ta tsani ganin matar.

Yusuf ne kawai yaketa kai loman abincin, amma shi umar chakulawa kawai yakeyi ajima kadan kaji yayi tsaki don shi ya tsani abincin da akayi mishi hadi da spices dayawa , don kamshin abincin tayr mishi da zuciyq yake, kawai daurewa yake yana ci.

Bayan sungama ne suka karasa cikin palon, inda su zee suke zaune da mamanta, gefe daya suka zauna, suna Dan taba hira, zuwa wani lokaci sukayiwa Aunty falmata sallama suka fita, daidai lokacin suka hadu da babagana zai shigo.

Hammah an wuni lpy? " kallonsa yayi yace yayah ba wani Abu ko"?

Da sauri babagana yace ba komai, amma ran Friday zanje bch insha Allahu.

Da kyau hammah yace sannan ya juya yayi jikin motansu, shi kuma babagana ya juya yana gaisheda Yusuf, bayan sun gaisa ya wuce cikin palon.

Honey ni yaushe zakazo na musammanne muyi hira nifah har yanxu..... Shiru tayi sbd kallon da yake mata, " duk zuwan damakeyi bai mikiba? bakida problem, sanan ya bude motan ya zauna ko kallonta bai sakeyiba, fuskanta a daure ta juya ko sallama batayiwa Yusuf ba tayi cikin gidan.

Aboki meyasa kake yiwa yarinyar nan hakane? Cewar Yusuf.

Me namata?

Kaman bakasonta wlh, babu wani Dan concern wa mutum ko kadan. Idan baka sonta kagaya mata mana.

Wayace maka bana sonta? Idan bana sonta ae bazan aureta ba, kawai ni rawan kai ne bana so, kuma metake nafada? Ni bana son hayani wlh, .... "Hmmm kawai Yusuf yace yayi shiru.

Da murna babagana ya shiga palon mama yana sallama, da sauri yayi wurin dinning inda ya hangota zaune tana shan tea da meatpie, oyoyoyo banana ta bude mishi hannu ya fada, shima cikin murna da begen ganinta yace mumcy nah! Nayi mssn dinki,... " tana murmushi domin taji dadin ganinshi duk da ba lallai bane sukwana su wuni ba suyi fada ba, domin shi faransai ne tana yin ba dai-daiba zai gaya mata, bayada haka kuma duk taxi jin dadin zama dashi saboda yana tayata hirah donshi mai surutu ne, Wanda duo ciki tafi son umar amma basu saba dashiba saboda bayida magana kuma itama tanajin kunyan shi kadan,.

Mama inasu abdallah? Dan ya mutsa fuska tayi tace suna chan side din, wai don yau me girkinmu tayi tafiya wai sukuma bazasu sha tea ba, kuma har meatpie namasu, amma don jaraba kaman Wanda aka mallakesu sun tafi chan cin tuwo, " shima mikewa yayi yace gaskiyansu ae nima chan zani naci don yunwa nakeji, ko jiran mezatace baiyiba yayi gaba.

************

Da sallama ya Shiga side din Aunty, direct wurin dinning din ya wuce inda duk suke zaune, fuskar shi dauke da murmushi yaje ya rungume babanshi yace Baba nagudo, duk Palon dariya sukeyi saboda sanin abin dariyan babagana, sannan ya gaishe da babanshi, yana Jan kujera yana gaisheda da Aunty yace kai su twins mayun girki kunga tuwo Ku gaisuwa babu ko? Toh duk almajiranci zaku tafi, bai jira amsan suba yakaiwa khalifah rankwashi yace kaga acici jikan

dadah sai loma kakeyi.

Babane ya daure fuska yace kayi dataka uwarka, jadawo kenqn ko? Yana dariyah yace baba afuwa, sannan yajawo plet gabanshi yana zuba abinci bakinshi baiyi shiruba yace Aunty kice dole gidado yayita kifi-kifi da ido Ashe sakwarane bugun kato  kenan.

Aunty tana dariyah tace don Allah babagana nayi shiru kaci kawai, gashi tun kana zagin iyayenmu har ka dawo zagin naka iyayen, " lah Aunty ban zagi nawa ba😄.

Injiwa? Bayanzu kace bugun kato ba, bayan kuma ni mamankace nadaka, da Saudi ya rife bakinshi yana dariya, toh nayi shiru, kowa dariyanshi sannan sukaci gaba da cin abinci.

Har sun kusa gamawa ya sake dago idon shi sai akan badariyah, da sauri yayi ciki-ciki da iron shi domin yadda yaji zuciyarshi ta buga da sauri!" Aunty wannan riyyah ce?

Itace babagana.

.kaii amma ta girman , don na Dade bangantaba almost yrs2 fah!

Ahh laillai ka dade, inaga tunda taxo mana hutun gama primary ya ae bata sake zuwa ba, " jama' a idan kun koshine Ku tashi bana son ana cin abinci ana surutu. lowa sai yayi shiru sai kqran spoons kawai kakeji,.

Duk sainaji na takura saboda duk daga idona sainaga ya tsurah mun ido, kawai tashi nayi nace alhamdulillah.  Aunty ce tace riyyah har kin koshi?  Ehh kawai nace na kama hanyan daki, shima da Saudi ya juya yana bina da kallo, take zuciyqrshi ta sake bugawa, duk wanna kayan kawai yafada a zuciyanshi,  wannan idan takara girma  yayah za'ayi?  Allah kabani wannan kadarar ya fada a mine dinshi, duk kuma sai yaji ya koshi.

Tofah yayah mama zataji idan naji danta yana son jinin Auntyh?

*DAGA ALKALAMIN AUNTY NICE*
*BADARIYA*

®🖋
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION* ✍🏻

{Gaskiya d'aya ce daga k'inta sai b'ata, burinmu mu fadakar da al'umma domin ribantar duniya da kuma lahira.}

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN KARFE* 🏇

Story and written
By
*AUNTY NICE*😘

*PAGE*6️⃣

Banda juyi babu abunda babagana yakeyi akan gadon shi, akaro na babu iyaka ya sake duba agogon dakin yaga har karfe biyu na dare, ya kwanta tun 11:00pm amma yakasa bacci, shi wai meyake shirin faruwa ne dashi?
Wannan yarinya yayah ta keso ta hana shi baccine? Tashi yayi ya zauna yasaka duka hannun shi biyu ya tokare fuskan shi, babu abinda yakeyi sai lissafin ta yayah ma zai fara son y'ar uwar Aunty Wanda yasan babu yadda za'ayi mama ta amince mishi, " tsaki ya sake ja yace haka dai zata hakura don shi wallahi rainon ta zaiyi" sannan ya koma kan gadon ya kwanta.

" Riyah me zamuyi ne yau kam"? Inji Aunty, ... " Dan dariya kadan riyyah tayi tace Aunty dumame kawai zamuci.

Chabb in kin isa kenan inji gidado, yana turo bakinshi, bayan ya harari riyyah.

Duka dariya Aunty da Riyyah sukayi daman sun San babu abinda ya tsana irin dumame, .... " Riyyah tace ina wasa da kai ne?" Idan kana son cin Abu mai dadi kazo muje ka tayani,
Tashi tayi tana dariya, shima ya bita yana cewa ae dole ki yadda na fiki tunda ni namiji ne.
Aunty kada kai tayi tana dariyansu.

**********
" Toh ke falmata wani lokaci kike ga zamu tsayar da maganan auren? Inji Hajiya Zahra maman su hamma umar, " Adda ina ganin mubarshi zuwa December kinga lokacin kowa yana hutu kenan," " shikenan zan samu baban su yau idan ya shigo, sannan maganan hada kayan inaga sai mutura ita zainab din da yafannah su tafi dubai su hada ko? "Ehh hakane Allah ya nuna mana, inaga nima zan bisu sbd mu sayo kayanta na daki ma kawai," shikenan hakan yayi sai kinji ni.

" Banda murna babu abinda zainab ta keyi lokacin da Aunty kemata bayanin saka rana, " Toh Aunty kinsan fah hammah yace wai baya son programs dayawa, ni kuma wlh ina so, yyh za'ayi"?

Rabu dashi mukan duk abinda mukayi niyah zamuyi saidai shi kada yayi, kuma Wanda yakamata yazo dolen shi yazo, haka dai sukayita hiran yadda abubuwan zasu kasance, a karshe Aunty tace zatayi waya da fannah, su tsayar da ranan tafiyan su, fannah itace autarsu hajiya zahra ita tana aure a kaduna, kuma itama zuwa Dubai yakeyi sari.

Babagana ne ya shigo falon Aunty bakin shi dauke da sallama, dukkansu suka amsa mishi daga Auntyn har Riyyah Wanda suke kallon fin din India, su gidado kuma sunyi islamiyyah.

Wuri ya samu ya zauna yana gaisheda Aunty, idon shi yana kan Riyyah, itama gaishe shi tayi, sannan ta cigaba da kallonta.

Aunty kinji wai ansaka ranan  auren su hammah ko? " ehh wlh babagana haka babanku yake fada mun jiya" Allah ya nuna mana da rai da lpy.

Amma Aunty ae zakije Maiduguri lokacin ko? "Insha Allahu zanje, Kaine mah mai ma sauki na ko?"...." Yana dariya yace insha Allahu kuwa, a gidan Aunty yafannah zan sauke ki, don wlh ita bata da halinsu mama, zakiji dadin zama da ita"

Aunty tace kai babagana waya gaya maka itama hajiyan tana da matsalah babu komai ae, " gaskiya Aunty kema kinsan halin mama da Aunty falmata, saidai kawai ki Kara hakuri, amma dai zaki tafi da Riyyah ko? Don naga bata wayeba gara taje ta ga birni😄

Itama Auntyn dariya tayi tana kallon Riyyah da ta tura baki gaba tace haba babagana Riyyah fah Auntyn kace, kamanta takwarata ce?

Yana dariya yace kinga tana tura mun baki gaba ko? Ke budurwar kauye yar kafi, " kaima ae Dan kauyen ne inji Riyyah, me jama'are tafi kafi?.

Ita dai Aunty tashi tayi tana dariya tayi kitchen domin ta daura girki,

Shi kuma ganin Aunty ta bar falon sai ya tashi ya taho kusa da Riyyah ya zauna, " yace y'ar kauye bani labarin school dinku da kauyen Ku? ..... Hararan shi tayi tana murmushi tace nifah ba y'ar bauchi bace.

Toh bani labarin kawayen ki? Murguda baki tayi tace nifa kallo nakeyi, " murmushi yayi haka kawai yaji tasake shiga ranshi, yace nidai saikin bani shima cikin shagwaba yayi mata maganan. Hararanshi tayi tace nikan,..... "Shima yace nima nikan sai kingaya mun".

Dariya tayi tace kacika surutu, toh ni kawata dayace nafisa amma zaka iya kiranta feenah,....." Ke me kike kiranta"?

Ni besty nake kiranta, "nima besty zan kirata kenan inji babagana". .... Hararanshi tayi tace besty nace ni daya, kuma Adda hummairah itace best Adda nah,  dariya yayi saboda jin dadin yarintar ta yakeyi, " Addan mu dai da bestyn mu, saboda nima yanzu na zama bestyn Ku, kinga munzama y'an uku ko?

"Kaiii ae kai namiji ne, yanzu bazan yadda ba sai na tambayi besty, idan tace ta yadda shikenan idan taki kuma sai kayi hakuri,   " toh yanzu besty yaushe zamuyi magana da besty feenan?" "Sai ranan da tazo". Nidai ban yadda ba saidai mu kirata a waya kawai yanzu,  "toh ae bata da waya saidai na Adda hummairah".

Miko mata wayan yayi yace saka number Addan mun.

Tana fara ringing kuwa Adda ta dauka tayi sallama, cikin dariya Riyyah tace Adda nah!!😄 itama tana dariya tace baby nah! Wayan wa kika samu? Dariya Riyyah tayi tace na hammah babagana ne, Adda ina missing dinki, ina besty nah? Bari na kaimata cewar Adda hummy,.

" Hello besty! Yyh kike, wayan wakika samu? Da sauri babagana ya karbi wayan yace "Bestyn mu yayah kike?
😳zare ido feenah tayi tace besty kuma?" " shima dariya yayi ya kwaikwayeta yace ehh mana new besty Ku kayi, yayah kina lafiya?  Don Allah ina besty inji feenah, da sauri Riyyah ta mika hannu kasancewar a handsfree yake, ta karba sannan tabawa feenah labarin babagana, dukkansu dariya sukeyi, sannan feenah tace sun amince, shima dariya yayi sannan suka cigaba da hira duka su ukun, shidai sai biye su yake da shirmensu, suna ta bashi labarin bikin Addan su da za'ayi, shima sai kara tayasu shiriritan yakeyi, lokacin Aunty ta fito daga kitchen tana dariyan shirmensu tace " Hammansu amma bakada aiki, yanzu way'annan yara kake biyewa shirmensu ko, har kaima zakayi ashobin su? Yana dariya yace Aunty ae nima kawansune yana dariya yana duban fuskan Riyyah, shidai haka jawai yakejin dadin ranan irin ta yau.

"Aboki toh yanzu kai me kake gani zamu shiryah ne?"  Shirin me inji Umar, " kaifa kana da matsala umar kaman yayah shirin me? Bansaniba Dan rain in hankali, ...Hararan shi umar yayi yace toh banda kai mu matane da zakace shirin me mukeyi?

Hmmm duk abinka dai kasan zamuyi dinner sannan za muyi crossing of the sword.

Hahhhhh zakuyi dai amma nikan kucireni, hararanshi Yusuf yayi yaja tsaki yafuta yabarshi a dakin.

Har jikin mota Riyyah ta rako besty babagana tana rike da bocket din roba guda biya y'an kana da Aunty ta musu dambu shi daya hammah umar daya, mujah ma yana binsu a baya rike da roban cincin a hannunshi Wanda yasha kwakwa a ciki kaman wani cake cincin din yayi,.

Besty Allah ya kiyaye hanya, sannan ayi karatu da kyau tana dariya ta fada mishi, hararanta yayi yace kaman baki damu da tafiyana ba? " besty toh nima ae next week zan koma school, shiyasa nakeso kowama ya koma, " muguwa Ashe farin ciki kike? Toh Allah ya kara tunda kema tafiya zakiyi, shine baki gaya munba? Hira Kadan sukayi sannan ta juya sukayi gida, muja na rike da hannunta yana cewa, " nima binki zanyi idan zaki tafi, haba amini nah baka so na tafi kenan ko? Ehh mana ni banaso ki yafi nafiso na girma na aureki ko? Dariya tayi suna Shiga falo tace ae dama kai ne mijin Dan mujah nah!.

***********

Hammah kana gidane? Babagana ya kira hammah a waya, "ehh meya faru inji hammah umar,". Dama Aunty ce tabani sakon dambu da cincin tace nakawo maka.

Mikewa yayi ya zauna, sannan yace kazo ina gidan sannan ya ajiye way an, a ranshi yace kaman ta san ina tunanin danbum tan, gashi harda cincin, shikadai baisan lokacin dayayi murmushiba yace amma nifah Dan duniyane tunda matarnan tayi min abin duniya na dawo ko kiranta banyi a wayaba gashi yanzu ma ta sake yimun amma naji kunya wallahi.

Dai-dai lokacin Babagana ya shigo falon gidan umar, a kwance ya Ganshi kan three sitter, ya dafe goshin shi, sallama yayi ya nemi wuri yazauna yana gaishe da hamman, batare da yatashiba yace ya kabaro su mama? " lafiya kalau hammah duk suna gaisheka, harda Aunty ma tace a gaisheka, dago kai yayi yace yayah tana lafiya? Sannan idon shi yakai kan rubbern yace amma nagode, tashi Babagana yayi ya mika mishi sakonya koma ya zauna, budewa yayi yadan taba danbum dadinshi har tsakar kanshi yaji, a zuciyar shi yace lallai matar nan ta iya girki a rayuwarta, sannanya bude rubbern cincin din shima ya dauki daya ya saka abakinshi, juyowa yayi ya kalli Babagana yace matar nan tana da kirki kuma ta iya girki..
Wallahi kan hamma kuma gashi tabawa yaranta tarbiyyah ka ga yanda suke girmama kowa a gidan, gashi duk abinda mama ta ke musu wallahi duk Inda suka ganta da Sauri zasuje su gaisheta koda zata zagesu, kuma ko a fuskan su basu nunawa, ga ta koya musu aiki kaman ba yaran mai kudiba, yanzu fah duk danbum nan da cincin Besty ce tayi ita da Gidado.

Ways besty kuma? Inji Umar, .... Kama baki Babagana yayi yace sorry na mantane, Riyyah nake nufi, wannan yarinyar brother Aunty da taxo mata hutun nan,  kallonshi kawai Umar yakeyi cike da mamakinshi wai besty, me Babagana yake nufi?  Kodak son yarinyar yakeyi??.

Shidai Babagana tunda ya lura da baranbaraman da yayi kawai sai ya mike yace Hammah

nikan zan wuce sai next time, a gaida hammah Yusuf idan ya shigo, ko kallun shi Umar baiyiba ballantana ya amsa mishi, kawai tunani yakeyi yaushe ma Babagana yagama karatu ? Har zai fara soyayyah? Mtssss tsaki yajah ya tashi ya kwashe kayan yakai kitchen, yana jin haushin bai karbi number wayan Auntyn ba gashi Babagana ya tafi, kuma yana so yamata godiya. Kawai Baba zai kira ya hadusu da ita.

Da misalin karfe 8:00pm ya kira mamanshi suka gaisa sanna ya tambayeta babanshi? Yana can side din, tabashi amsa, cikin far in ciki dama haka yakeso yaji, sallama ya mata sannan yakira babanshi. Bayan sun gaisa take gayawa babanshi abinda Auntyn ta mishi, cikin farin ciki Baban yace kai lallai angode ga Auntyn taku ma Ku gaisa.

Kar ban wayan Aunty tayi tare da sallama, bayan sun gaisa ne yake mata godiya, " Lahh Hammansu meya aciki kanne kane suka ce zasu maka, ni ko leka suma banyiba, yana karamar murmushi yace wato Gidado baya son karatu sai aikin kitchen ko? Ina yake? Dariya Aunty tayi sannan ta mikawa Gidado wayan sai zare ido yakeyi ya Karna yana sallama, gaishe da Hamman yayi cike da ladabi, " kai kuma kitchen kawai make Shiga ko?  " Gidado yana shafa kai yace a' a kawai na taya Riyyah ce, Hammah shiru yayi can kuma yace toh nagode amma a maida hankali akan karatu ko? Sannan ya musu sallama ya ajiye wayan, kumawa yayi ya kwanta ya rufe ido yana tunanin maganganun Babagana.

*DAGA ALKALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*

®✍
*GASKIYA WRITER ASSOCIATION* ✍🏻
{Gaskiya d'aya ce daga kinta sai b'ata, burinmu mu fadakar da al'umma domin ribantar duniya da kuma lahira.}

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN KARFE*🏇🏻

Story and written
By
*AUNTY NICE*

*PAGE*7️⃣

A yaune muka koma makaranta nida besty, amma abun mamaki kullum muka koma sai munyi kuka, kaman y'an aji daya.

Sabbin dalibai muka gani Wanda wannan term dinne zuwansu school din na farko, kowa shirin kayan shi yake a loka, amma nida besty muna kwance sai kuka mukeyi.

Shigowar wata dalibace yasa na dago kaina, saboda yanda naji ansaka ihu a dakin ana Aisha trouble, tana dariya ta kalli wacce ta kiratan tace indo umar dama kema nan aka kawo ki?

Wlh kuwa trouble cewar Wanda aka kira da indon,..... Juyi mai suna trouble din tayi tace dama na gajji da day, da kyar na roki babanah ya barni aka kawo ni bording, "ihu suka sake sawa.

Wani room aka kaiki inji indo ta tambayi trouble? ....hmmm wai room 2 naji sunce, amma ni dazasu taimakeni ae da sun hadamu ko indiya, tana duban indon suna dariya.

Juyo tayi ta kallemu, tsabar neman rikici lokacin tafara ganinmu amma bai sakata tayi shakkan komai ba, tana kallona tace Burkina Faso suna wani country, wannan kayan ta kashin fa da aka zuba shi kaman kayan wanki? Ke kukan me kikeyi? Ta matso kusa dani.

Hararanta nayi nace waye me kayan ta kashin? ..... Ahhhh kada idon ki ya fado bar hararana ko nayi jifah dake ta window, inji Wanda aka kira da trouble din, " yi shiru kada ki kulata inji besty ta gayamun, daganan na juya na kwanta.

Trouble ina ruwankine, zaki fara jawo mana rikicin naki ko? Inji indon Wanda take ce mata India.

Nayi shiru Hindu ga rawa ga waka, wai dama nayi maganane don naga abun dadine ka ganka a school hakanma bording.

Wata senior ne dabata son surutu y'ar SS class tacewa trouble fita a dakinnan, sannan ta juya ta kalli indo tace last warning kada ki kara jawo mana y'an rikici dakinnan, kinji ko? Da sauri indo ta amsa, naji Aunty! " ita kuma trouble ta hararesu ta fita.

*****************

Washe gari da safe bayan an taso daga Assembly, kowa tayi class dinta, abin mamaki sai gashi duk sun hadu class daya daga Trouble, India, Nafisat, Badariyyah duk class daya suke a SS 1A.

Da wuri Riyyah ta zauna a sit din gaba, takama musu ita da bestyn ta, tana zama, su trouble suka zauna a bayansu.

Ran Riyyah baisoba suka zauna dasu Trouble amma babu yadda ta iya, don tafi son zaman gaba, a haka class master su ya shigo.

Hello Aunty yayah su Mujaheed? Inji Babagana da yake waya da Aunty, .. " lafiya qalau Hammansu yayah karatu?

Aunty ina labarin kawata, idan zakuji visit don Allah Aunty ki hadamu a waya.

Tana dariya tace insha Allahu muna zuwa zan hadaku, kuyita hiran ashobinku, tana fada tana dariya, shima dariyan yayi yace toh Aunty nagode sai anjuma.

Honey toh maganan kamun da zanyi, don Allah kazo mana, zanji kunya a wurin friends dina idan bakazoba.

Kallonta kawai Umar yakeyi hannun shi rike da cup yana shan juice da aka kawo mishi, zuwa can ya gajji da mitan data keyi, yace " haba mine! Meyasa kike da hayaniya ne? Wai programs har nawa zakiyi ne? Kinsan dai ko zanje daya zanje saboda haka ki zabe Wanda kike ga yafi cancanta naje, ya kura mata ido bayan yayi shiru da maganan.

Gaba daya fuskan Zainab a jagule yake, tana kallonshi kamantayi kuka tace, Honey zanyi kamu, shima yakamata ace kayi attending wurin, akwai Mother's night, shima yakamata kazo, akwai Dinner kuma, tafada tana lankwashe kai don ya yadda.

Kallonta ya tsaya yi, can yace haba mine, ae kema zaki gajji kafin agama, nidai daya zanje sai ki zaba, ni taron matan nan ba iyashi zanyiba.

Dai-dai lokacin Aunty fannah ta shigo palon, bayanta kuma Aunty Falmatace me biye da ita, da Sauri Zainab taje ta rungumeta tana kuka.

Doug me ya faru kike kuka? Inji Aunty fannah Wanda take dago fuskar ta da duka hannunta,

Aunty falmata ma da sauri ta karaso tana sweet heart meya faru?

Shidai kallon mamaki kawai yake musu yana zaune a inda yake, Wanda Ku daman gaisheda Aunty fannan bai samu yayiba.

Aunty wai Honey program daya kawai zaiyi attending, toh yyah yake so nayi da kunyan kawayena? Inji Zainab.

Jan hanjunta Aunty Fannah tayi suka koma kusa da Umar suka zauna, tana dariya tace " son meye kuma zakace program daya zakaje? Kada muyi haka dakai kaji?.

Ajiyan zuciya yayi yana rike da haban shi yace amma Aunty kema biye mata zakiyi? Ina laifin zanje guda dayan ma? Gaskiya Anuty programs din sunyi yawa, gashi a bauchi ma friends dina dina sun matsa har biyu zasuyi, ga Dinner ga Sword Crossing. Gaskiya itama ta rage wani a ciki, ya fada tare da daure fuskanshi.

Dariya sosai Aunty Fannah tayi, tace inaga gidannan dole na dinga kai ziyara saboda ganin irin zaman da za ayi.

Toh yanzu na raba gardama, tunda zakayi Dinner da crossing of the sword, toh itama zata rage programs din yazama biyu, tana kallon zainab da ta zaro ido tace kema Doug kamu kawai zakiyi da mothers night, Dinner din ki barshi saboda can ma akwai wani dinner.

Kaima son sai kazo program biyun.

Haba Fannah ya zakice tayi biyu? Bayan ita da friends dinta sun tsara ukun, shi maizasa ba zakice ya daure ya hallaci duka ukun ba, cewar Aunty Falmata.

Gaskiya Yayah Falmata babu ruwanki a cikin magannan mu, nifah dukan y'ay'a nane ina da right na ce musu suyi ko su bari, saboda haka a nawa adalcin haka yayi.

Saboda shi dama yace daya zaije kuma nace biyu nakeso yaje, kinga yayi min musu ne? Idan Doug tana son har ukun toh tayi amma kada tayi tunanin angon zaije na ukun fakad na gama magana.

Gaba daya palon shiru kakeji don dama Aunty fannah idan tace haka za'ayi babu wacce zata canjata.

Itace karamarsu amma duk tafiso zafi ga fadin gaskiya, shiyasa ko iyayensune ma sunfi ji da ita, kuma ko irin halin mama da Aunty Falmata na son kanso da yaransu toh ita bata da wannan halin, don ita ko zuwa bch tayi sai ta Shiga side din Auntyn mu, don ita bata da mugun zuciya, gata a dauki yaran y'an uwanta kaman nata,  ita Allah da daya yabata itama mai suna Faisal.

******************

Trouble ce ta tashi ta tsaya a gaban class dinsu, tana kokkoyon tafiyan maths teacher su, gaba daya class din dariya akeyi.

Babu teacher da zai fita trouble bata kokkoyeshi ba, babu Wanda bata iya maganan shi da tafiyanshi ba.

Zuwa lokacin daga in har besty babu yadda muka iya da trouble duk mun saba da ita don kullum sai ta so room dinmu.

Hatta seniors din dakinmu idan bata shigo ba, zasuce indiya ta kirata, ko baka son dariya dole sai kayi, don idan baka fahimcetaba a farko zaka dauka masifaffiyace, amma idan kun zauna zaka gane ta iya zama da mutane, ita dai bakinta ne ba ya shiru ga Neman tsokana, yanzu harta da wanki da zuwa wanka, da yawo a cikin school kusan duka mu hudun tare mukeyi, wayyo Allahn mu rana daddayane ba a dukanmu saboda trouble, amma babu yadda muka iya da ita.

Haka kawai Allah yasa mata kauna a ranta, gata da juriyar aiki, ko waki zamuyi saitace Fati y'ar lukuta ki Dibo ruwa kawai zamu miki, don kullum mukazo wanki sainayi mitan hannuna.

Akwai wata rana muna zaune akan window dakinmu, kawai saiga wata senior tazo wucewa gata muguwace kitchen prefect, irin masu duwawu mai tsinin nanne, da kyar take juyashi, ga trouble bata iya magana a hankaliba, kawai said ji mukayi tace shankalele, amma wannan duwawu kaman kofato, wazai aureta?

Bamu rufe baki da dariyan da mukeyi ba, mukaji tace don ubanku duk ko zo nan, ae bansan lokacin danasaka kukaba, saboda nasan senior Ai lere babu sauki a wajen duka, don yau said mun fadi yaren garinmu.

Muna zuwa mukayi nildown tun kafin tace muyi, wayyo Allah na kawai nake fadi don na tuna wani dukan da ta taba mana duk saboda rikicin trouble,.

Aunty don Allah kiyi hakury inji besty da tafara kuka, ... .. " Hakurin yaci uban uwarshi takai mata rankwashi, ae  tunin na kara volume din nawa kukan, tace Ku tashi kubiyoni, tayi hanyar hostel dinsu damu.

Ranan no Fatima Riyyah naci kwakwa don yana cikin ranan dabazan Lance dasshiba, seniors

sun kai shida kowa da irin horon da tamana, daya tace dama tana cike damu, akwai ranan ta shiga hostel dinmu taga muna kallonta muna dariya ita dai kawai anbata hakuri be rannan, amma yau saita huce.

Muna dawowa hostel sai kuka mukeyi, duk da cewa trouble sai kayi da gaske take kukan duka amma yau tayi.

Muna shiga hostel na juyo nace daga yau kidena zuwa wurinmu, bakijin magana kullum mune dukan teachers mune na seniors, toh na gajji ni karatu aka turoni, ba Neman shan duka ba, na juya nayi room dinmu banjira me zatace ba.

Yau ne ranan visiting day, tun safe mukayi wanka muka shiryah, kowa tana daukin zata ga y'an gida, kada ko dauka fushinmu da trouble yayi tsayi? ae zuwa dare sai a ta leko dakinmu, bayan mundawo a night freb, tace y'ar duma-duma,saida safe, sannan ta fita da gudu tayi dakinsu, dukkanmu dakin saida mukayi dariya.

Zuwa yamma saiga  su, Aunty da Mummy sunzo muna tare da Addah humaira, Hammah walid ne ya kawo su, da guru nazo na rungumi Addah nah sannan na rungume mummy, na dawo qurin Aunty ina kallon idonta yanda take murnan ganina.

Rungume Hammah nayi saboda na kwana biyu bamu haduba, nace Hammah oyoyoh INA Abbah nah da ummi nah? Kawai sai mukaii kukan mujaheed Wanda besty take rike da hannunshi, kowa ya kalleshi ana tambayanshi meyasa meshi?

Ba Aunty Riyyah bace bata kalleniba, kuma nine mijinta!   " dukansu dariya suka saka, tazo da Sauri ta daga shi sama tana haba swit heart dina, kai na musamman zan daga ka dama.

Sai lokacin mujah ya saaake fusknshi yana dariya.

Bayan mun gaishe su ne, besty tana kwance a jikin mummy ni kuma INA jikin Adda humairah nah.

Sai Aunty tace bari na kira bestyn ku, yace idan munzo na hadaku dashi, Adda ce tayi dariya tace ya hadu da wahala wlh, AUNTY tace baya gani ta fada  tana dariya tana Kokarin Koran wayan shi.

Dai-Dai lokacin Babagana suna tare da Hammah Umar da Yusuf a Palin Hammah Umar saboda bai ji dadiba, shi kuma yaje duba shi, lokacin wayan Babagana ta fara ringing.

Yana dauka yaji muryan Aunty, da Sauri yana fara'a yace Nigeria sai Aunty. Itama dariyan tayi

tace Dan rigima yayah karatu?

Alhamdullillah ya amsa, sannan tace mishi ga su bestynka!  Yana dariya yace y'an kanzo ba.

Sannan ta mikawa Riyyah wayan , sallama yaji tayi, yana dariya yace Besty nah! Nayi msdn dinki dosai- sosai, yafada yana dariya, duk ya manta ysna gaban Hamman shi ne, hiranshi kawai yakeyi dasu idan yayi da wannan, wanna ta karba, bai San lokacin da ya kwashe da dariya don jin bayanin da besty feenah take mishi na punishment din da suka sha.

Da tsawa yaji ance mishi tashi kaje kayi shirmen a waje, kana magana da jariran yarah kaman sa'o'in ka, yana hararan Babagana, shi kuma da sauri yafita  a Palon yana mamakin masifan Hamma Umar.

Yusuf ne ya Juyo yace haba aboki ? Yaron nan yana maka kokari amma Baka gani? Toh don Allah idan da budurwar shi yakeyi fah? Ka kyauta kenan?

Tsaki Hammah yaja yace shi yasani ya samu yarinya karama duk tabi ta rikita shi, naga yanda zaiyi ko karatu baigama ba, ko kuma sai kuma yayi shiru shi kadai yake huci.

Shidai Yusuf kallon shi kawai yake don bai fahimci Inda  ya dosa ba.

Nima tsayawa nayi ina kallon shi, ina nazarin shi, kaddai shi ma basin Aunty yakeyi ba tsakani da Allah?

Muje zuwa ju jasance da alakalamin Aunty Nice ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*

®☄
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION* ✍🏻
{Gaskiya d'aya ce daga kinta sai b'ata, burinmu mu fadakar da al'umma domin ribantar duniya da kuma lahira.}

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN KARFE* 🏇🏾

Story and written
By
*AUNTY NICE* 😘

*PAGE*8️⃣

Ajiyan zuciya kawai Hamma Umar yayi, ya koma ya kwanta, shidai Yusuf kallon shi kawai yakeyi, a ranshi yana fadin, " wato wannnan bazaka tab'a gane inda ya dosa ba ko?"

Har zuwa wani lokaci babu wanda ya sake wa wani magana a cikinsu, duk sunyi shiru kowa da abinda yake ranshi.

Zuwa can sai Babagana ya shigo, idon shi akan Hamman shi, ya risina ya mika mishi wayan yace Hammah ga Aunty zata gaisa da kai.

Hello! Aunty kuna lafiya? A dayan bangaren Aunty ke amsa mishi da lafiya, sannan take tambayanshi yayah yakara ji da jikinshi?
"Da sauki ya amsa mata, sannnan yadan tambayeta su Gidado, sai sukayi sallama ya kashe wayan, ya mikawa Babagana". Shima Babagana sallama ya musu ya tashi ya fita a gidan.

Lokaci babu wuya har yau su Riyyah sun dawo Hutu gida, ga bikin Addah humairah saura sati daya, dama hutun 3wks ake badawa a first term.

Riyyah tana shiga gidan taga Hammah sadiq, da gudu taje ta rungume shi tana murnan ganin abokin fadanta.

Shima dariya yayi yace " Riya baka danginta farare" andawo za'a cinye mana food, kallon shi tayi ta mumguda mishi baki tace da dinta ma Ummi ma bakarce ehee, yana dariya yace kaji wawiya, ummin y'ar uwarkice? Mahaifiyar kice, amma duk danginki farare ne, yanayi yana dariya.

Taho autana ki rabu dashi "inji ummi" aidai duk kinfisu kyau, kuma har sugama zaben matar aure, bazasu samu irin autana ba.

" Haba ummi kidaina hura mata kunne, wannan bakar"?

*************

Bayan naci abinci  na yi wanka na kwanta, bani na tashi ba saida akayi Azahar na tashi.

Bayan nayi sallan la'asar nacewa ummi nah zanje Gidan su besty naga kayan ashobinmu, toh kawai tace mun, nakama hanya sai gidan su besty.

Ranan Thursday akayi kamun Adda humairah a multipurpose, zokaganmu yadda mukayi kyau nida besty nah, kayanmu iri daya da nasu umaimah, amma nida besty colour namu purple and yellow, nasu kuma pitch, munyi kyau sai kai komo mukeyi a wurin.

Amaryah tasha kyau, duk inda tayi muna mara mata baya har aka tashi taro, washe gari Friday akayi walimah Wanda malama Juwairy tamana wa'azi mai tsayawa a rai, shima haka taro ya tashi lafiya.

Ranan Saturday aka daura auren Adda nah da angonta Ahmed, ana sallan la'asar aka kama hanyan kano, muna motan Aunty nida besty, kallon besty nayi kasa-kasa nace besty kiga besty yaki zuwa ko?

Itama kasa-kasa tace mun kimishi uzuri kinsan Dan makaranta ne, shiru nayi ban sake ce mata komai ba, a haka har muka isa garin kano,  gidan iyayen mijin mukaje a Rijiyar zaki. Ana ta murna da shewan ankawo amaryah.

Da dare mukayi shirin dinner, dukkan mu gown maroon muka saka nida besty, da su Adda Hafsat, kada kaso kaga kyaun da mukayi, dama a farko na gaya muku y'ay'an mummy  y'an gayune, kuma duk a Dubai ta sayo mana kayan, gaskiya abikin Adda ankashe kudi, don da mukaje gidan yadda tsarin yake sai yabaka sha'awa, kuma da ga gani ankashe kudi a gidan saidai addu'an Allah yabasu zaman lafiya.

Rannan Sunday wujajen karfe 11:00 muka baro kano, kowanmu yayi kuka, tunba ma ni Adda nah ba, Ranan duk wani murnan ayi bikin Adda nah dana keyi, Ranan sainaji kaman dama ba ayibaa, kuka kam munsha shi, Allah sarki Addanmu mai sonmu, haka dai mukadawo bauchi jiki a sanyaye.

Lokacin babu wuya yau har an Shiga  satin bikin Hammah umar dama tsakani Dana Adda two weeks ne, Aunty ce ta shigo gidanmu da la'asar suna hira da ummi nah, take ce mata Adda Halima zamuje Maiduguri tare dasu Riyyah,ummah Da Addan bauchi ma zasuje, bansan ko kema zakije ba?

Ummi ta dan yi dariya tace, haba Fatima yanzu keda y'ar ki sai kin rokeni da ki dauke ta zuwa biki? Dasu umman duka zakuje ko? Cewar Ummi nah tana kallon Aunty, Allah yasa kada Hajiya Zahra ta muku wulakanci.

"Wallahi tamana wulaknciya da wuwa zamuyi, nida banyi niyyan zuwa ba, amma Alhaji ne yace mutafi harda su Adda Aisha, amma wallahi don ta ita kam bata isaba.
" hakuri zakiyi Auntyn su, baka biye ta mutun, nima don ranan jumma'a zamuje da mummyn su kano kallon dakin amarya ne da na biku, amma bazataji dadi ba idan taga ban bita ba".

Ba ko mai Adda Halimah kuje kawai, nida yaran ma ya isah ae, dama yabamu babbar motan shi muje a sake.

****************

Ranan Thursday tunda gari ya waye muka kama hanya, gaban motan Gidado ne zaune, sai sit din tsakiya kuma, Aunty ce da umma da Goggon Bauchi, mujaheed yana cinyan Aunty, baya kuma nida besty ne da khalifah .

Tafiyan tamana dadi, don tunda muka Shiga bakin Gidado bai rufu ba, sai nemana da magana yakeyi umma na karba mun, waishi dole saidai yazama yayah ni kanwa, tunda yafini tsayi, har aka isa bakinmu baiyi shiru ba.

Muna isa Aunty takira Babagana, yace driver ya wuce damu gidan Aunty Fannah, duk jikinmu a gajjiye muka isa gidan.

Dai-Dai lokacin shima Babagana ya iso gidan, a tare muka fito daga motan, mukayi cikin gidan, inda muka tarar da Aunty Fannah da y'an aikinta, sai haba-haba take damu kaman danginta,kai matar nan akwai mutunci wallahi, daki daya takai mu, amma dakin hade yake da palonshi, cikin dakin gadone babban a ciki sai katifu kusan guda uku da aka ajiyesu.

Sallah muka idar muna zaune saiga Aunty Fannah da y'an aikinta sun shigo da abinci, samun wuri tayi tana gaishe dasu ummah kaman iyayenta, sannan ta mika hannu wa mujah tace "kai kan auta kamanku daya dash Abdallah, ana cikin haka Babagana ya shigo yace " Aunty idan kunci abinci Gidado yazo mutafi dashi, don su Abdullah ma suna can, sai ya hadu dasu suyi komai tare saboda nan bazai sakeba".

Hmmm wannan na matanka gara ka daga mana shi a cikinmu, dama ya damemu, "charab khalifah yayi yace Hammah nima wurinsu Hamma Abdullah zanje". Yana dariya yace Allah sarki

damo sarkin hakuri inji Babagana yace tare zamu tafi kada kaji komai.

Aunty Fannah tace yauwa Auntyn su idan kungama Ku huta sai dare ne program din idan yaso, Babagana zaizo sai kutafi wurin, sannan duk abinda kukeso masu aikin nan zasu kawo, don Allah hajiya Ku sake, ta na kallon Goggon bauchi da fara'a a fuskarta , sannan ta mana sallama ta fita.

Kai matar nan tasan mutunci wallahi cewar Goghon bauchi bayan fitan su, don tare suka fita dasu Gidado, kowa saida ya tifah albarkacin bakinshi a cikinsu, nidai na dale kan gado na kwanta abuna.

Muna sallan ishaa muka shiga wanka kowa tana shiryawa, domin ance babu African time, Wani atamfah Red muka saka nida besty nah, style din na gown ne yayi masifar fito damu, sannan muka daura dankwalin kaman daurin amare yayi kyau sosai, wayyo zo kuga yaddah Aunty nah tayi kyau acikin wani arnen less ash colour da pitch ajiki, ta yafa wani pitch gyale, sai ka dauka matar wani Governor ne, kai mai kyau ya more kallonta kawai nakeyi duk inda ta juya.

Babagana ne suka shigo tare dasu Abdullah da sauri Mujaheed yaje ya rungumi Abdullah yana oyoyo hammah nah, ya rike hannun shi sukayi Palo, gaba daya idon Babagana a kaina yake, har mantawa yakeyi dasu Aunty, hararanshi nayi na juya  da kai na gefe.

Aunty kiga besty sai harara nah take tayi, tun dakuka zo bata gaisheni ba! ......."Toh wa ya isa ya shiga tsakanin Aminai inji Aunty tana dariya ta fita zuwa inda zasu shiga Motan, kowa saida ya fita a dakin akabar su biyu shida ita, hararanshi nasakeyi nace bani hanya na wuce, yana dariya yace haba besty laifin me nayi ne? Bance komai ba nasa kai na fita.

Wurin kamun muka isa, wurin babu masaka tsinke, matane y'an gaske a wurin, kowa tana wance bani wuri don gayu, gefe daya Hajiya falmata ne da kawayenta, dayan side din kuma y'an uwan angone a zaune a wurin, da sauri Aunty Fannah ta taso tamana jagora har wurin dazamu zauna.

Gefe daya Babagana yaja mu nida besty muka zauna, yawanci wurin duk y'an uwanshine na wurin Mama,a haka muka gaisa dasu,  " yauwa besty wai menayiwa besty take fushi dani ne?" Tana dariya tace wai Dan bakazo bikin Adda bah.

Hana my sweet besty! ae saiki tambayeni mai ya faru? Bawai fushi zakiyi da bestyn ki ba, cewar Babagana yana langabe mun kai, dukkanmu dariya mukayi.

Zan bashi amsa mukaji DJ yana maganan shigowan amaryah da ango, gaba daya Hall din aka

maida kallo Kansu, wakan shuwa Arab aka saka musu suna shigowa abokai da kawaye na binsu a baya, Aunty Fannah ce ta mike tare da wasu cousins dinsu sukaje suna musu spray, har inda suka sauna, a lokacin Babagana ma ya bisu, saini da besty aka Bari a wurin, gaba daya hall din ya kachame.

Lojacin da Babagana ya dawo wurinmu, sai akayi dace Hammah Umar yana binshi da ido, kawai idon mu ya hadu danashi, tsabar mamaki baisan dalilin dayasa ya bude bakin shiba, da sauri ya juya gefen Yusuf Wanda yake side dinshi ta dama, yace " Aboki kaji fitina a wurin yaron nan, sai da ya kawo jaririyar nan?"

" Wani yaro cewar Yusuf" can kuma shima idon shi ya sauka akammu lokacin ina kallon Babagana daya kariso yana taka rawa, ina dariya nace ..... "Kai besty! Bakajin kunya ko?.

Woow Yusuf yace " Aboki wannan ae dole ta tafi da hankalin yaro, Babban ma ae bai tsirabah". " Gaskiya abokina duk da ina son farar mace, amma wannan ae kadarace,". Dama ni nafara ganinta, "Cikin Jan tsaki Hammah Umar ya juyad da kanshi yace, bakada problem.

Nima nace Hammah bakada problem, ina ruwanka da hidiman da bata kaba?.

*DAGA ALKALAMIN AUNTY NICE* 😘
*BADARIYA*

®✍
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION* ✍🏻
{Gaskiya d'aya ce daga kinta sai b'ata, burinmu mu fadakar da al'umma domin ribantar duniya da kuma lahira.}

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN KARFE* 🏇

Story and written
By
*AUNTY NICE* 😘

*PAGE*9️⃣

Duk abinda sukeyi idon Hammah nakansu, baza a jima ba sai kaji yayi tsaki shi kad'ai shi.

MC ne yayi sanarwan ana so aga dangin ango a fili, kafin kace wani abu sai ga Family an fito filin rawa, harda cousins d'insu y'an jama'are, zuka ga zuk'a-zuk'an kyawawan mata a familyn, ba jama'are ba, ba Maiduguri ba.

Besty ne yace "kutashi muje fili".

kallon shi nayi nace "Nikan bana rawa besty".
Sai naji yace  ehh ko bakya yi fito muje kiyi mun liki".Besty Feenah ke kam zamuyi rawa ko?"
Tana dariya tace rawa kai besty, sanann ta mik'e tana kallona.

Babu yadda na'iya na mik'e, shi kuma ya bud'e purse d'in hannu na ya zuba mun kudin liki a ciki, sannan muka wuce filin rawan.

Wata cousin d'in suce tazo kusa da Besty tana wani rawa a gaban shi tana zolayan shi kanin ango, amana lik'i, tana nan kaman zata b'alle don sirintaka, yake kawai yamata ya shareta, haka ta cigaba da rawanta, shi kuma yafara bin bayan besty suna rawa.
A haka suna rawa nafara mishi lik'i face d'ina d'auke da smiling, shima haka ya zuba mun ido kaman zai janyeni ya keji, abun sha'awan kuma ina lik'i amma bansan ina juya jikina ba a hankali kaman ina rawan y'an shuwaa, Wanda ya burge mutane dayawa a wurin.

Duk inda nayi idon Aunty nah dasu Ummah na kaina, Aunty nah fuskarta d'auke da murmushi, ita kuma Goggon Bauchi zuciyarta yana mata fari duk lokacin data ganni, a ranta tace Allah yasa burinta ya cika, mu had'a kanmu da HAIDAR.

Da sauri Gidado yazo yana ta d'aukan mu photo da wayanshi, itama Aunty Fanna haka kawai taji ranta na kauna na, kuma haka kawai take jin dad'in a ranta na alaman da take gani kaman d'an ta m sona yakeyi, da  sauri ta tashi tazo tana mana lik'i, ko takan sauran bata bi ba, hankalinta yana kaina da besty, ganin haka yasa Auntyn mu ma fitowa tana mana lik'i babu k'ak'kautawa, gaba d'aya sai filin ya kachame, kud'in hannu nane ya kare, najuya zan koma na zauna, charaff sai naji hannun besty ya rik'o nawa, zuciya na naji ya yanke amma shi ko a jikin shi, sai murmushi dayake mun, tsorona kada mutane su ganmu, amma dana ga kowa hidimanshi yakeyi babu Wanda ya lura damu, sai mutsu-mutsu nakeyi akan ya sakeni amma fir yak'i.

Kaman ance na daga kaina na dubi Hammah Umar, sai ganin wani banzan kallo yake mun kaman idon shi zasu fad'o k'asa, bansan wani irin k'arfi bane yazo mun, a d'ari na k'wace hannu na, na juya wurin zaman mu kaman zan fad'i k'asa, numfashi na da sauri yake tahowa.

Besty ce ta biyoni inda nake sai haki takeyi, tana murna tace "Besty kid'an yamun dad'i, kaman kada a daina".

Hammah Umar yayi tsaki yafi sau ba iyaka, har saida Zainab ta maida hankali kan shi tace "Honey me ya faru?".

Ko kallonta bai yiba shid'ai kawai ji yakeyi kaman ya tashi ya bar taron, a zuciyan shi yana fad'in.

"in banda sakarci, ina Babagana ina mace at this age? Yaron da ko karatu baigama ba, meyake nufi?".

Mtsss ya sake Jan tsaki.

Da sauri Yusuf ya juyo ya kalle shi, yana mamakin dalilin d'aure fuskan abokinshin, shida ake auren shi ae ya kamata yafi kowa farin ciki a wurin.
Amma saboda sanin halin abokin shi sai baiche komai ba, ya maida hankalin shi inda y'an matan keta rawa, yana harin wacce zai zab'a shidai yana son fara mai tsayin gashi.

Ba' a tashi taron ba har wurin karfe 11:00 sannan aka koma gida, kowa jikinshi ya gajji, banda bacci babu abinda nake so, a haka mukayi wanka babu wani hira kowa ta nemi wurin kwanciya ta kwanta, Aunty ne kawai da Goggon Bauchi suke taba hiransu.

Washe gari da misalin karfe sha d'aya muka gama shirinmu, driver ya kaimu gidan Aunty Falmata, a can muka had'u da Aunty Fannah da murnanta takaimu d'akin Aunty Falmata, ni tun tashin mu banga Aunty Fannah a gidan ba, kasancewar uwar biki ko zama bata samun yi a gida.

Fuska adan sake Aunty Falmata ta karb'e mu, saboda duk da tana taya Mama kishi akan Aunty mu toh nata da sauk'i, saboda ita macece mai son kanta dayawa, itadai damuwarta data yaranta shine damuwa naka sai dai don zumunci kawai.

Bayan an gaggaisa ne, Aunty Fannah tace" kozo nakai ku inda Ummanmu take da sister ta, don zakufi sakewa a can". fuskarta d'auke da murmushi.

A d'akin da aka kira Ummunsu na ciki, a can muka samu Gidado da d'an ta Faisal a kwance a kan gado hannunsu d'auke da waya suna ta game, shikowa Khalifah ya kwantar da kanshi a jikin Gidado sai kallon su yakeyi.

Sallama mukayi muka nemi wurin zama muka zauna, bayan an gaggaisa cikin farin ciki Umman su ta amsa mana, ta nuna jin dadinta akan zuwan su Aunty da y'an uwanta, cikin

zolaya take cewa Aunty uwar masu gida wannan kyakkyawar diyar fah? Idonta a kaina, bata kiran sunan Fatima saboda sunan surukuwar tace, kuma sunan Mama kenan, y'ar ta ta fari.

Aunty ce ta dube ni tana murmushi tace "d'iya ta ce ta wurin yayah na Babban, kuma takwarata ce, Faitma amma muna mata alkunya da *BADARIYA* .".

"Masha Allah" y'ar uwar Ummansu .ama tace, duk idon su yana kaina, can ummansu tace tun jiya a wurin kamun yarinyar tamun kyau, har nayi sha'awanta wa maigida na, nace lallai-lallai zanyi kamu wa angona, duk dai dama naga kaman sun riga sun had'a Kansu.

Murmushi Aunty da su Umman mu sukayi sukace Allah ya zab'a abinda yafi alkhairi.

"Amma sabone kawai da sukayi itada Hamman su Babaganan". cewar Auntyn mu data ke dariya tana kallona.

Aiko abin zaimun dadi inji Immansu, zanso naga Maigida na yasamu wannan nutsatsiyar yarinyar taku, gata mai kyau da ita, dai-dai lokacin Hammmah Umar ya shigo, kuma maganan tana karshe duk a kunnen shi suke.

Hararan Umman yayi sannan ya nemi wurin zama a kusa dasu Faisal, sannan ya gaishe da kowa a d'akin fuskarshi a d'aure.

Muma gaishe shi mukayi Wanda da ky'ar ya bud'e baki ya amsa, hararanshi ummansu tayi tace.

"Mugun Boss ranar aurenka ma bazaka sake fuskar kaba?". Mtsss taja tsaki taci gaba da cewa.

"Shiyasa ni bamu shiri dakai, Donni ko gidanka bazanje ba, kai bak'in hali kana d'aure fuska baka son mutane, ita kuma matar ka, bakin hali da raina mutane, Sam bata ganin girman babbah, shiyasa ni bazanje gidankuba, fatana Maigida ya samu wannna nitsatstsiyar yarinyar mai mutunci naje gidansu". tana nunani da yatsanta.

Kowa saida ya k'washe da dariya a d'akin banda ni da Hammah Umar, ni gaba d'aya ji nayi garin ya fita mun a raina kasancewar magananr da naji Ummansu tana yi akai na da besty, ita bata San shi k'awana bane ko?.

Shi kuma Hammah haushin watse shi da tayi a gaban mu yakeyi da kuma shishigin da takeyi nawani zata had'a aurenmu da Babagana, toh ina ruwanta? ya fad'a a zuciyanshi.

Mtsss yaja tsaki yace "Kina da problem, meya hanaki zama a naki gidan?".

Hararan shi tayi tace "Toh shugaban y'an bak'in hali, ni ba anan na kwana ba, a gidan mijina

mai son mutane na kwana, kuma shi yabani izinin Nazo na wuri, da y'an uwana Dana shi anan din, ehhe malam shiyasa nace banda gidanka kai kam".

k'anwar ta ta amsa mata " Haba zakije mana idan firituwar tashi ta haihu ki musu zaman biki ae" .

Duk su Aunty dai dariyansu sukeyi, daga k'arshe sallama yayiwa su Aunty fuskarshi a d'aure yana hararan Ummansu, hannunshi rik'e dana Mujaheed suka kama hanyar waje.

Dai-Dai lokacin na d'ago ido na naga ko ya fita, tsautsayi shima ya juyo muka had'a ido, as mugun hararan daya mun saida naji zufah yazo mun, da sauri na sake sauke kaina.

A na kiran magarib muka koma gidan Aunty Fannah don muyi sallah muyi shirin mother's night, a yammacin ranan kuma Baban su Gidado ya iso da y'an jama'are da kuma friends d'inshi, Wanda masaukinsu na musamman ne, Baban Zainab ya tanadar musu.

Bayan mun shiryah ne, muka fito muda su Aunty muka wuce wurin program d'in.

Washe gari ranan Saturday aka d'aura aure, ana d'aura wa aka d'auki amaryah da wasu danginta, da kuma dukkan k'awaye a jirgi, BABA ma a jirgi ya taho, mukan tun kafin a d'aura aure tun wurin 7:00 muka kama hanyar bauchi don a can za'ayi bud'an kai, wuraren 5:00.

Direct gidan Aunty muka k'arasa da muka isa, kowa jikinshi a gajiye, babu Wanda ya lura damu nida besty muka sulale mukayi gidanmu, don wallahi mun gajji.

A gida muka samu Mummy tana jiran Ummi nah su wuce gidan biki, "Ku kuma muna shirun zuwa mai yakawo Ku?".

Inji mummy.
Mungajji ne mummy zamu huta, tunda akwai dinner da dare sai muje, kwanciya zamuyi na gayawa mummy.

Hararana Ummi tayi "tace anci sa'a ma dakikaje can d'in ae".

***************

Bamu muka koma gidan Aunty ba sai  around 7:00 na dare, lokacin da muka isa, a baking gate muka had'u da Hammah da Abokanshi, duk da gidan ta ko'ina haskene, amma nayi mamakin danaji Yusuf yace jaririyar Hannah, da badan idon shi akaina take ba, banyi tsammanin dani yakeba, kuma naga bansan shiba.

Yana dariya ya k'araso inda muke, saiji nayi yace "Queen of Beauty's ya kike?".
 Jikina har rawa yakeyi muka amsa mishi, yana dariya yace " baki sanniba ko?, Toh nine Babban aminin ango, kin gani nafi k'arfin abokima, na sanki ne tun awaya, ranan danaji kuna waya da Babagana. Sai rannan Thursday kuma naganku tare dashi a wurin kamu".

Sai lokacin hankalina ya kwanta na d'auka ya tsayar damu yace yana sona ne, don ni natsani ace ana son a tun ban girma ba, besty ta sake gaisheshi cikin sakin fuska, sannan tace "Ashe kaima yayanmu ne?".

"Kwarai kuwa". Ya amsa mata, yace kuma yayan dazai tsaro akan ku ba, ya fad'a yana dariya" sannan yace kubani number wayanku.  Lokacin yana fito da wayar shi cikin aljihun shi

Besty ne tace mishi ae bama rik'e waya sai mun gama makaranta, bamu dashi.

Kama bakinshi yayi yana cewa duk wannan zuk'a -zuk'an y'an matan basu da waya? Fuskar d'auke da dariyan tsokana.

Bansan lokacin Dana kwashe da dariyaba don duk da bana son magana, amma mutumin nan yabani dariya, kaman ya Dad'e da sanin mu, ina dariya nace ae bamu girmaba ballantana a kiramu a waya ko besty? Ina kallon Besty da itama dariyan shi takeyi.

Da k'arfi ya kwashe da dariya yace.

 "amma zan so na dinga hira daku wallahi, don duk zakusa mutum nishadi, Ashe da gaske kudin jarirai ne?".

Zaro ido nayi nace "jarirai kuma?, Bakasan nuna SS class ba?  nan da 2yrs zamu gama sai a bamu waya, muma lokacin mun girma".

 Gashi Idan ina magana ina juya idona, hakan ba k'aramin burgeshi yayiba, ya bud'e baki zaiyi magana kawai sai mukaji muryan Hammah ya daka mana tsawa "kai Ku wuce cikin gi......".

 Bai k'arasa bama, mukayi hanyar cikin gidan da gudu.

Matsuwa Hammah yayi kusa da Yusuf, yace "Amma aboki kana zubar mana da girma kaima, a

gaban yaran nan, wai me kake ce musu be?kana ta dariya agaban jarirai".

Hararan shi Yusuf yayi yace "baza kaji abinda muka fad'a ba d'an gulma kawai, tunda jarirai ne, ina ruwanka da jin irin Hiran da mukayi da su".

"Kai kasani" inji Hammah yana hararan shi yace. "kazo muje muji da friends d'in mu kafin a fita wurin dinnern nan".

Babu ruwanka dani, ka wani kore mun abokan hirana, inajin dad'in hira dasu, da d'inta ma idan anje wurin dinner baka isa ka koresu ba, hiranmu zamu sha dasu.

Hmmm kawai Hammah yace yana hararanshi ya wuce cikin Palon shi na gidan.

Mu kuma muna fad'awa d'akin Aunty sai dariya mukeyi mu kadai, kowa kallon mu yakeyi, Aunty tace.

"Don Allah Ku wuce d'akin Gidado kuje Ku shiryah tun dazu nake dakon Ku iso, kunzo kunata shirme wa mutane".

Muna dariya muka wuce d'akin Gidado domin mu shiryah.

Nima Aunty nice nace ya kamata na koma gida nayi wanka na shiryah, domin na turara jikinah da turaren Maiduguri da Aunty Fannah tasanmu, domin na kwaso mana irin badakalan da za'ayi a wurin dinner, Donna lek'a d'akin Babagana naga sai rawa yake yana shiryawa daga gani yayi niyyan burge besty, ga d'ayan gefen, Yusuf sai cewa yake aboki wani Shiri zanyi na burge jaririyar nan?

Ko kula shi Hammah baiyiba.

*Kucigaba dabin alkalamin Aunty nice*😘✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*

®🖋
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION*✍🏻
{Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar duniya da

kuma lahira.}

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN KARFE* 🏇

Story and written
By
*AUNTY NICE*😘

*PAGE*1️⃣0️⃣

Hall ɗin da za'ayi dinner ya cika maƙill da ƴan'uwa da abokan arziki, gefe guda iyayen amarya da angone mata a zaune.

Kowa ka gani sai shan ƙamshi takeyi, tanaji kaman babu wacce ta fita haɗuwa, can na hango Aunty da mummy suna zaune, gefen su kuma sister hauwa ce a gefen su, wato ƙawar Aunty ce office ɗinsu ɗaya, babu abinda yake raba sister hauwa da Aunty domin nasu yazo ɗaya, gefensu kuma ni da besty nane a zaune da kuma Adda hafsat da Adda umaimah kowar mu taci kalan nata gayun, mudai still anko mukayi da besty na, wata material ce mai shegen ɗaukan ido Red and black muka saka, sai ɗaukan ido mukeyi.

Kowani sit table ne da sit ɗin mutane takwas, wurin mu yazama akwai sauran sit ɗin mutum ɗaya, ɗayan gefen wasu ƴan jama'are ne zaune kyawawa kaman zubin larabawa don baƙaramin kyau suka mun ba,
Tunda suka zauna idona yake kansu, domin baƙaramin kyau suka munba, sunanan su shidah a zaune can sai ga sauran mata guda uku sun shigo, kowacce tanaji da kyaunta da gayunta.

Kai tsaye sukazo wurinmu suna kallon Aunty suna dariya, kaga manya matar babban yayah inji wacce ta fisu girman tana zolayan Aunty.

wuri ta samu a wurinmu ta zauna suna gaisawa dasu Aunty cikin murna, sauran ma suka gaisheta suka koma ɗayan sit ɗin suka zauna, ganin haka sauranma suka taso ɗaɗɗaya Suka gaishesu, ita kuma wanda ta fara zuwa wurinsun wanda naga suna kama da Baba ta nemi wuri ta zauna kusa da su Aunty.

juyawa nayi zan duba ɗayan side ɗin kawai sai idon mu ya haɗu da Besty Babagana, ɗaga mun gira ɗaya yayi yana murmushi, wani irin kyau besty yamun, wanda bansan lokacin dana maida

masa martanin murmushinba, kuma lokaci ɗaya naji kunya ya kamani sbd idon daya sake kashe mun.

Muna cikin haka sai naji MC yana sanar da isowar amaryah da ango, gaba ɗaya hall ɗin ya ɗauki wani kiɗa mai daɗin gaske.

Ango yasha wata ash shaddah da hula ash, ba karamin kyau yayiba ga yasa hannu ɗaya cikin aljihun shi, sai wani takun fadī yake yi, itama amaryah tayi masifar kyau cikin wani ash dogon riga da silver head da takalmi, bayansu kuma abokan ango ne da amaryah, tunda suka shigo kaman ance Yusuf ga Riyyah, gaba ɗaya idonshi ɓa kaina, yana bina dani kayatattan murmushi yana ta girgiza kanshi, irin alaman nayi kyau ba ƙaryah, da sauri ɓa juyad da kaina, don ni dai yana mun girma a ido nah.

Besty da sauran ƴan familyn sune suke ta liƙi wa ango da amaryah har sit ɗinsu suka rakasu.

Bayan sun zauna ne MC ya fara bayanin barka da zuwa wa ango da amaryah, sannan ya ƙira Aunty Fannah yace ta buɗe taro da addu'a, bayan tayi addu'a ta koma, aka ƙira babban abokin ango wata Yusuf yazo yabada tarihin ango,
Cikin takun ƙasaita ya fito ya bada tarihin ango, a ƙarshe ya jefo tsokana waa ango, inda yake bada labari wa amaryah ta dage da hidimah saboda kada wataran taji yace mata jaririya, yana fadī yana kallon idona yana dariya, gaba ɗaya hall ɗin aka kwashe da dariya, shi kuma Hammah banda hararan shi babu abinda yakeyi.

Daga nan ƙawar amaryah ta taso ta bada tarihin amaryah ta koma ta zauna, bayan hall ɗin ya ɗauki tafi.

MC ne ya ƙara ɗan bayani akan ango da amaryah na raha, sannan aka kira friends ɗin amaryah su fito filin rawa, bayan firowarsu gaba ɗaya filin ya kachame da liƙi, duk yadda amaryah taso tashi, ango ya hanata.

Daga baya aka ƙira amaryah da ango a fili, amaryah sai rawan kai takeyi, amma ango ko gezau baiyiba.
Anata ƙiransu ango yayi shiru bai tashiba, Yusuf sai magana ƙasa -ƙasa yake mishi amma bai kula shiba, har saida Aunty Fannah tazo dai-dai kunnen shi tace idan baka tashiba ranka zai ɓaci, jin haka baiko ɓata lokaciba ya miƙe hannun shi riƙe dana Zainab suka fito filin rawan.

Tunda suka tsayah ya saka hannu ɗaya a aljihu, ɗaya kuma ya rike hannun Zainab, ita kam sai rawa takeyi, shi kuma ta ƙura mata ido.

Besty ne yazo wajen da muke zaune yace besty zo muje muyi liƙi, babu ydda na iya saboda Aunty tana mun kallin na tashi naje, riƙo hannun besty feenah nayi muka miƙe tare, dama Aunty ta bawa kowanmu 5k.

Besty da rawa ya isah gaban amarya da ango yana liƙa musu kuɗi, ido na kanshi, cikin zuciyata nace gaskiya besty yana da kyau gashi komai yayu burgeni yakeyi.

Haka mukaje gaban su muka fara musu liƙi, tunda mukaje idon Hammah yana kaina, ni kuma nakasa mishi liƙi illah nayi wa amaryah nayi wa besty da besty feenah, Yusuf ne ya taso da sauri yayi kanmu a take ɓare bunch yana mana liƙi, kawai sai ganin Hammah mukayi ya kama hannun amaryah sun fita a filin, besty da Yusuf suka bi bayan shi, suna mishi liƙi har wurin zamansu sannan suka juya wurin zamansu, MC kaman zai fasa hall ɗin da karaɗi tun fitowar Yusuf yake cewa ga babban aminin ango ga babban ƙanin ango ƙaƙatsara-ƙaka, kai jama'a abawa jiga-jigan taron bikin fili, kowan su cikin burgewa ya koma wurin zaman shi.

Yusuf ne ya sunkuyo dai-dai kunnen Hammah yace" Aboki gaskiya jaririyar nan tana da kyau, zankaɗaziya kenan, ashe gaskiyar ka da kace mace choculate mai hips da boobs tafi kowacce mace qulity, yau kan na yaddah, domin data tashi Kaga yadda hips ɗinta suke juyawa Kuwa? Wannnan idan tazama cikakkiya yayah mutum zaiji?"   wayyo Allah ina wuta Hammah ya jefah yusuf.
   Wani banzn kallo y bishi da shi kaman zi kifah mishi maari, yace "ashe haka kake baɓsniba? Idan banda nema ka zubar mana da ƙima a idon yaran nan, tunda na fita baka tasoba saida jariran nan suka fito sannan ka tashi ko kunya babu ka fito, yana hararan yusuf yana maganan".

Dariya Yusuf yayi, "yace inajin daɗin kalman jariran nan a bakinka, amma ina tsirata maka wani abu, ya faɗa yana miƙewa daga sunkuyun da yayi akan Hammah yana dariya".

Tsaki Hammah yayi yana sake duban inda ɓake zaune, wanda shidai bai san meyasa ba daga ya ganni a wuri sai yaji idonshi baya iya barin kallona, ko dan irin colourn dana ke dashi ne ohuu.

Filin aka bawa iyaye su fito, babu kunya saiga su mama dasu Aunty Falmata da ƙawayensu  a cikin fili, ansaja musu waƙan uwa sai taka rawa sukeyi.

Aunty ce suka miƙe tare da wnnn ƴar'uwar su baban da Mummy daa sister Hauw sukayi filin rawaan domin suyi manni, a lokacin kuma ango da amaryah suka fito domin yi liƙi waa Iyayensu.

Besty ne yazo ya tashe mu, badan nasoba na bishi mukayi filin rawan, munaa cikin liƙi, can ƙasa-ƙasa kawaai naji an riƙe hannu na irin riƙon da ba kowa bane zai iya lura.

A hankali na sunkuyar da idona naabi hannun da ya rikeni daaa kallo, babu tantama hannun Hammah Umar ne, ɗago idona nayi da sauri na kalle shi amma ko kallon inda nake baiyiba.

Ƙoƙarin kwace hannu na nayi amma nakasa, hararah na yayi ba tare daya sake hannuna ba ya ke kallon amaryar shi, yana ta duka mata murmushi, itama murmushin take mishi.

Kuka ne kawai banyi ba dana kasa ƙwace hannuna, duk abinda mukeyi idon Yusuf na kallonmu, da dabara ya matsu kusa damu, dai-dai kunnen Hammah yace "kana tsoron jaririyar tamu ta faɗi ne? babu komai barta zamu kula da ita nida Babagana, don wallahi mun damu da ita, gata ƴar duma-duma yoghout kenan, yana magana bakinshi ɗauke da wani ɗan iskan murmushi."

Da sauri Hammah ya saki hannunah yanaji kaman zuciyar zata faɗo, wai mai ɗan iskan nan yake nufi da wani wai ƴar duma-duma, toh mai yagani ajikin ta? Baisan lokacin dayaji yayi tsakida ƙarfi ba, wanda har saida Aunty Fannah ta dube shi.

 Samun an sake mun hannu da wuri nayi sit ɗinmu na zauna, zuciyata yana ta bugawa, besty ne ta iso inda nake, tace "besty kawai sai naga kin tafi kin barni?" Hmmm kawai na iya cewa nayi shiru da baki nah.

Bayan sunje sun zauna ne, akace kowa yaje yayi saving kanshi, nidai ko kaɗan bazan iya cin komaiba, don babu abinda nakeso irin naga na kwanta a gida, abin ya dameni donji nake kaman har yanzu hannun mu yana haɗe, duk jikina rawa yakeyi.

Aunty ne ta ƙira sunana tace "tashi ko ɗebo abincin mana, ko so kuke mu debo muku? Tana miƙewa da ga zaunen da take", Aunty kaina ne yake mun ciwo, naji bakinah yana faɗi.
  Kallo  nah tayi tace "hala gajjiyan hanya ne, da kuma hayaniya, sannan ta wuce suka tafi dasu mummy, besty tace " bari na ɗebo miki kinji besty nah".

Besty Babagana Kawai na gani a kaina ɗauje da pilet da juice a hannunshi, gefe ne ya zauna yana cewa, " sorry my dear besty! wai kanki ke ciwo? Sorry na kawo miki kice mu gudu gida, yana Sauke mun murmushi ƴana ajiye pilet ɗin.

Daga inda muke zauna idona ya sauƙa akan na Mama, banda hararana da takeyi kaman idonta zai faɗo, da sauri na sauƙe kaina ƙasa don daga inda nake ina ganin wani tsaki da ta ta jah, lokaci ɗaya naji kaman zazzaɓin gaskiyan naso ya rufeni.

Kaman ance na sake duban Hammah, shima still hararah na yakeyi, jinayi duk taron ya fita kaina, muna haka harsu Aunty suka dawo, tukun ya miƙe ya bar wurin..

Muna isah gida batare danayi wanka ba kawai na cire kayana na kwanta, duk mitan da besty ta keyi ban kulataba, da ƙyar na samu baccu ya ɗaukeni, tunani nah!   Mena musu suke hararah nah?.

Da safe da wuri muka tashi mukaje ɗakin Aunty muka chanjah bedsheet sannan muka fara gyaran ɗakin, besty kuma toilet ta shiga take wankewa.

Karfe goma aka fara tafiya wurin crossing of the sword. Ba'a sun raina naje wurinba saboda Tsoron haɗuwa da mama nakeji, Shaddah muka saka nida besty wata gown mai masifar kyau.

Duk inda nasan idon mama ko Hammah zasu ganni ban tsayaba, duk yadda besty yayi dani haka ya bar ni.

Ana tashi a wurin mukabi motan Aunty, su Adda hafsat kuma suka bi mummy.

Wuni ranan akayi da yammah kuma za'ayi buɗan kai, ni duk hidiman ma ya hau kaina, gidanmu kawai nake son tafiya.

Babu yaddah na iya haka muka shiryah cikin skirt da riga na atamfah nida besty muka fita wurin, muna zaune akan kujera wanda aka tsara wurin kaman za'ayi walimah.

Duk yaddah besty tayi muzauna a layin farko ƙinayi najata layi na biyu muka zauna, a haka amaryah da ƙawayenta suka fito, shima ango da abokanshi suka iso wurin a tare.

Ango ne yafara tashi ya buɗe fuskar amaryah wanda tasha ado da wani atamfan super wax mai stones a jiki, bayan ya mata liƙi ya zauna, sai ƴan'uwa suka fara fitowa ɗayabayan ɗaya suna musu liƙi, gefen ango Yusuf ne zaune shi yake tara mishi.

Aunty ce suka miƙe itada ummi nah da Goggon bauchi da mummy suka fita filin sukati nasu, murmushi Hammah yayi ƙasa-ƙasa yacewa Aunty "nagode"...... Murmushi Kawai  tayi suka juya wurin zamansu, sannan tace nafisah tashi kija wannan Kuran kuje kuyi musu manni.

Babu yaddah na iya haka muka tashi mukaje wurin, kaman zan faɗi nakeji, duk sai naji skirt ɗin yana harɗe ni ba don komai ba, sai don tunda muka tashi, idon Hammah yake kaina,  da kyar na usa inda suke, buɗe jakana nayi nafara yuwa amaryah, gaba ɗaya nakasa yiwa  Ango, besty kawai takeyi musu.

Saijin muryan Yusuf nayi yana cewa"ƙawayena kuna lafiya? Besty ce kawai take ta iya amsa mishi, da lafiya, sai charab naji muryanshi yasake cewa" ke ƴar jaririyar ƙanwata ba zaki mannawa ango bane sai yaƙare?"  cikin fargaba na matsu kusa da shi wanda gaba ɗaya turaren shi ya gauraye wurin.

Haka na daure ina manna mishi, kasa-ƙasa naji yace mun saida kuɗin ya ƙare zaki mun?ɗago kaina nayi na dube shi, amma abun mamaki baya kallona,
 Muryan yusuf naji yana ce mun"Baby da dare zamuyi sallama daku fah, don gove zan yafi, kinji?" ɗaga kai na mushi alaman naji, sannan na juya nayi wurin zaman mu.

Shiko Yusuf sai dariyan shi kawai yakeyi, saboda jin Hammah ya mutstsine shi a cinyan shi da ƙarfi.

Haka taron ya watse lafiya, bayan munyi sallan ishaa, muna cin abinci Gidaɗi ya shigo yace"ke ƴar ƙanwata kuje inji abokin Hammah Umar ɗinnan, inaga kunyi kasuwa fah," yana faɗa yana dariyan shaƙiyanci, ɗaukan abu a gefe na nayi na jefe shi, waye ƙanwarka? Kajimun yaroh!.

A faalon su Hammah muka same shi a zaune, dukkan mu ƙasa muka zuna muna gaishe shi, cikin sake fuska yake amsa mana, shiko Hamman banda danna wayanshi babu abinda yakeyi, muna gaishe shima ko kulamu baiyiba ballantana ya amsa.

Can sai ya tashi yayi cikin bedroom ɗinshi, shi kuma Yusuf ya cigaba da janmu da hira, babu ɓata lokaci muka sake muna ta bashi amsan tambayan mu da yakeyi, labarin school besty ke ta bashi nidai ban da murmushi babu abinda nakeyi.
Can sai yake tambaynmu waye saurayin mu? Dariya besty tayi tace ae bamu gama school ba, kuma ba aure zamuyi yanxu ba sai mun girma, juyowa yayi yana dariya yana kallona , yace " ƴar jaririyar baby kefah wanene saurayin naki?" Rufe bakina nayi, ina dariya nace " ni kan banida shi".

Dariya yake mun yace toh kice nayi kamu kenan? Yana kallon besty yace " Besty ina zaki bani ƙawarki?" Tana dariya cikin farin ciki tace amma zaka jira sai ta girma fah! Don sai munyi karatu, idam kajira zan baka ita, ta faɗa tana dariya itama, rufe fuskana nayi gaba ɗaya.

Yana ta dariyan kunyan da nakeji kuma haka kawai yaji abin yana burgeshi, wato auren yarinya fah zai bada ma'anah, yana kallina yace zan jirata mana , amma sai ta amsa mun da bakinta, tambayana suke yi babu kakkautawa,niko sai ƙaraƙunshe kaina nakeyi a cikin gyale nah.

Hammh ne ya fito kallon mu ya keyi, ganin duk bamu lura dashi ba ƴace, ke!! zonan, a tsorace na juyu ina ganinshi , tsawa ya daka mun wanda bani Kaɗai ba, hattah besty saida ta razana ta miƙe tsaye, ahiko Yusuf ko gezau baiyiba kallon mu kawai yakeyi yana murmushi.

Da sauri na karasa kusa da shi, nace gani Hammah lokaci ɗaya naji idona ya ciko da hawaye, kallona yayi na wani lokaci sannan ya juya cikin ɗakin, da sauri na bishi.

Ina shiga naji ya jawo hannuna kaman zan faɗa jikinshi, amma na daure na tsaya da kyau ina duban shi, kallon idona kawai yakeyi yakasa furta komai sai ajiyan zuciya yakeyi dasauri. Can yace ƴaushe kika girma har kike biyewa maza su ɓata miki rayuwa?Karatu zakiyi ko soyayyah?

Jijjiga mishi kaina kawai nayi na kasa magana, sannn naji yana cewa"ko kina so na faɗawa Abban ki aure kike So? Hawaye naji ya zubu mun a kan fuskana.

Kallonshi nayi nace " nifa nace mishi karatu zanyi, saina girma nayi auren" lokacin harna fara sheshsheƙan kuka.

Jinayi ya damƙe hannu nah da ƙarfi, yayi ƙasa da muryah yace "kina son shi ne?"

Nifah ban girma ba, bansan ya akeyin son ba, ..... Baisan lokacin da murmushi ya kufce mishi ba, yace " bakisan yayah ake soyayyah ba kuma kikeyi da Babagana?

Zaro ido nayi ina kallon shi, nace shima fah bamu soyayyah  kawai beatyn mune.

Ƙara damƙe hannu na yayi wanda har saida naji zafin hakan, sannan yace "shi baice yana sonki ba"? ... Ehhh kawai na iya ce mishi, ajiyan zuciyan shi kawai naji, sannan ya ce kija ƙawarki kuje ku kwanta ,yusuf ƙarya yakeyi ba sonki yakeyi ba, don shi farar mace babba yake so, kinga ke kuma yarinya ce kuma ke  Ba fara  bace, ɗaga mishi kaina ɓayi alaman na fahimce shi, sanna ya sake ni yace kada ki gayawa kowa kinji! Toh kawai na gaya mishi sannan ya sake hannu na, da sauri na juya na fita a ɗakin , da sauri besty ma ta biyoni, nima binsu nayi naji yayah ake ciki.

*KUCI GABA DA BIN ALƘALAMIN AUNTY NICE*✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*

®✍
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION*✍🏻
{Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar duniya da kuma lahira.}

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN KARFW* 🏇

Story and written
By
*AUNTY NICE* 😘

*PAGE*1️⃣1️⃣

Da sauri na hau kan gadon mu, lokaci guda naji kuka yazo mun tunani nah kada fah Hamma yace zai fayawa Abba nah, don Hammah walid yace kada ɓa haɗa kaeatu da soyayyah.

Duk irin tambayan sa besty ta mun bance mata komai ba, saidai nayi shiru sa kukan.

Da safe bayan mun taya Aunty da masu mata aiki gyaran gidan, mukaje muka karyah,sannan mukaje mukayi wanka.

Ɗakin Aunty nayi bayan n tayata gyaaran kayan da takeyi ne, nace mata "Aunty yau zamu koma gida, idona na kallon ƙasa"

Kallo na Aunty tayi sannan tace ''amma zaku kai zuwa yamma ko"?

Insha Allahu Aunty nafaɗa ina shigar mata da wasu freshner zuwa toilet, da ido tabi ni, batajin daɗin tafiyan dana ce zanyi.

Wuraren Ƙarfe biyar mukayi shirin tafiya, banda mita babu abinda Gidaɗo yakeyi, wai daga gama biki zamu tafi, ko gidan amaryah ba muje ba.

Ko kula shi banyi ba, sai sai duk inda nayi yana bina yana damuna wai muje ya rakamu gidan, Hamma Umar muga yadda gidan yayi mugun kyau.

Babu inda zanje ƙaninah! ...... Kutt waye ƙanin naki? Inji Gidaɗo yana hararah na, dai-dai lokacin mukaji ana sallama cikin palon.

Hammah Umar ne da Yusuf suka shigo, nidai tunda suka shigo naji jikina ya fara rawa.

Gaisawa suka farayi da Aunty, sannan nida besty muka gaishe su, Gidaɗo da kusan wuni sukayi a gidan shi ma, saida ya sake gaishe shi.

Fito da jakan kayan mu mukayi, "Tafiyan zakuyi inji Gidaɗo" yana hararah nah.

Aunty ce cikin dariya tace, "Gidaɗo kai baka so ta tafi kuma kana mata rashin kunya, ka raina ta ko"?

Duk kansu dariya sukeyi, amma banda Hammah da ko kallon su baiyi ba, Yusuf ne yace, su besty har za'a koma school ne?

Aunty mun wuce sai anyi hutu, mungode sosai cewar besty tana kallon Gidaɗo tana dariya.

Ƙani nah bazaka rakamu bane, na faɗa ina kallon Gidaɗo ina dariya, Hararah na ya sakeyi, yace "bazan rakaku ba"

Babu sallama ne? Yusuf ya faɗa yana mikewa domin yi musu rakiya, ko alamar tashi a wurin Hammah ballantana ya mana Allah ya tsare hanya.

A jikin motan Yusuf ya tsaya yana tambayan mu, "toh sai yaushe kuma baby nah? gashi zaki tafi amma yayanki bai barmu munyi cikakkiyar sallama ba, tun safe naso zuwa amma yaki barina"

Jin shi kawai nakeyi amma inajin zuciyata kaman zai dare biyu, wato yama raina mun hankali kenan, wai yaso yazo hmmm kuji daɗin baki.

Yusuf ganin bazan amsa mishi ba, kawai sai ya miƙawa besty wani envilope yace gashi babu yawa, da ƙyar tasa hannu ta karba, driver yaja motan muka tafi.

Bayan mun koma makaranta da sati shidah, Wata rana mun fito evening freb, gefe nah troble ce ke riƙe da wani kara a hannunta, har zamu wuce gaban wani hostel, sai ta hango wata ƙawar mu ana ƙiranta Asmau inuwa, gefenta kuma wasu prefect ne a zaune  a gaban hostel ɗin.

Akwai ɗaya da ake ƙiranta seniour findiga.

Kawai sai jin trouble nayi tace asma inuwa! asma'u ta ɗago mata hannu, kawai saaaiji mukayi tace yayah amaryar babanki chilliga ƴar findiga? Kawai bamu ankaraba sai muka kwashe da dariya, daga mu har asma'un, don mun san maman asma'u ce kawai matar gidan.

Dariyan da bamu gama ba kawai naji seniour findinga tace "duk kan ku kuzo nan don ubanku, yau sai kunyi bayanin yaren garinku."

Nill-down mukayi, gefen ta kuma akwai wata ana ce mata seniour Duguri, ita ce ta kalli Findinga tace " friend kici uban yarinyar nan, ita kaɗai sauran basu da rashin kunya, itace hatsabibiyar.

Kawai abin mamaki saiji nayi trouble tace " seniour don Allah ki bata haƙuri, kinga ni ɗin ma ƴar duguri no lover ne, wallahi rashin farin jini ne yasa aka kawo ni nan" tana faɗa tana matse hawaye.

Wani irin rubdugun duka kawai ake sauƙewa trouble, wanda bamu ake duka bama saida mukayi kuka, sannan bamu tsirah ba muma sai da aka mana namu na warning ɗin dariyan da mukeyi.

Da ƙyar muka wuce hostel ɗinmu dukkan mu kuka makeyi, a hanya nace amma trouble ban yafe miki ba, kawai tsabar kin saba da shan duka kowan mu ma so kike kimai da mu jakuna ko? Allah zai saka mun nikan.

Washe gari a class tunda na shigo na ɗaure fuskana, naƙi yiwa kowa magana, don ma jada trouble taga fuska tace zata mun magana.

Muna haka maths teacher mu Mr Friday ya shigo, mugun gaske ne, gashi baya jin hausa.

Allah yaso mu duk muna gane maths amma trouble inda matar ta kada mijin kenan, ko kaɗan bata ganewa, can sai yafara ɗaga mutane zuwa jikin black bord yana quation.

Charab sai ya nuna trouble, ƙasa-ƙasa najiyota tana cewa "zanyi mafaninka kuwa".

Gaban board ɗin taje ta tsaya, sai ƙyafta ido takeyi, Mr Friday ya tambayeta ta rubuta mishi almighty formular, kawai sai ji nayi tace, yes my name is Aishatu Inuwa.

Gaba ɗaya class ɗin muka kwashe da dariya, don mun gane ta nuna mishi bata san me yace bane, buɗe ido yayi yace mata get out! Sai kawai ta je ta rufe ƙofan class ɗin ta dawo ta tsaya mishi, darita class ɗin ya saaake kachamewa.

Tambayan class monita yayi normal kowa ta ke? Trouble ta ƙyabta mata ido tayi alaman tace ba normal bace.

Monita ta razana da Mr Friday kawai se ce mishi tayi ae Trouble bata jin turancine, kallon troble yayi ya cigaba da abin da yakeyi, mukan clasa ɗin banda dariya babu abinda mukeyi. A haka ya fita ya barta, don shi tunanin shi ba normal take ba.

*************** Babu wuya a wurin Allah yau ne muke gama rubuta jarabawar mu na SS 3 second term, kuma daga hutun da zamu dawo zamuyi SSCE.

A wannan lokacin Adda Humairah ta haifi yaronta mai suna Ishaq amma muna ƙiranshi ammar, Hammah ma Zainab ta haifi yaronta mai sunan Baba wato Nuhu amma ana ƙiran shi Nabil.

Haka zalika besty yana service a lagos yama kusa gamawa, Hammah walid yana service a kaduna, Hammah khaliƙ yana jigawa.

Kuma a lokacin Yayah Kamal ance mana yazo lokacin muna school, yana law schooƙ ɗinshi a Abujah.

Adda Hafsa da Adda umaimah an kawo gaisuwan auren su, daya ke wani abokin Ahmed mijin Adda humairah ne keson ta, ita kuma Adda umaima wani cousin ɗin sune ɗan alkaleri ya ke sonta.

Wannan haɗin auren babu wanda baiyiwa daɗi ba, duk da ance bayanzu bane amma mukan munji daɗi.

Mun dawo wurin ƙarfe goma na safe, ina shigowa gidan mu na faɗa jikin Ummi nah ina murna, saijin muryan Hammah Sadiq nayi yana cewa Riyyah baƙa danginta farare.

Ummi kin ganshi ko?  Na faɗa ina turo baki gaba, shima turo bakin yayi yace toh kin dawo ko? Zaki fara damun Ummi nah, ko? Hmmm kaji shi wai Umminshi ƙato da kai na faɗa ina shigewa ɗakin ummi nah.

Dawuwa nayi da wuri nace Hammah yayah naga anyi gini ta waje, aure zakayi ne? Na tambaya ina dariyan zolaya.

Shima dariyan yayi ya zauna gefen ummin mu, yana cewa " yaushe nama Riyyah? ae saina ƙara girma ko Ummin mu?" ya faɗa yana duban Ummi yana dariya.

"Zakaji dashi dai cewar Ummi" sannan ta dubeni tace jeki cire uniform ɗin kiyi wanka kizo na baki labari, da sauri na shige ɗaki don cire uniform.

Dama tun farko nagaya muku tsarin gidan mu, ɗakuna biyu ne kawai a jere sai banɗaki guda biyu a jere, ta ɗayan ɓarin kuma kitchen ne sai wani ƙarain ɗaki kusa da shi.

Toh bayan su Hamma sun fara girmane, sai aka basu ɗaki ɗayan, ɗayan kuma nasu Ummi da Abba nah.

Bayan Hammah ya gama secondry sai ya koma gidan Goggon bauchi wurin Hammah khalil, domin sunfi sakewa a can akwai wdataccen ɗakuna.

Toh wannan ƙaramin ɗakin Hamnah Sadiq sai ya mayar nashi, ɗayƴan ɗakin kuma yazama na Ummi nah, wanda a ciki nake kwana, ɗayan kuma ya zama na Abban mu.

Hammah Sadiq irin masu ƙulafucin Uwane, shi a rayuwar shi baya iya nesa da ita kullum suna tare, har ana tsokanan so, so da ƙauna. Sannn Hammah mai neman na kanshi ne soasai yana dawuwa a school zaije wani gidan block yana aiki a wurin, da kuɗin ya ke biyan kuɗin makaranta kuma yake tarawa a ciki.

Bayan naci abinci na matso kusa da Ummi nace "Ummin Sadiq bani bayani" ranƙwashi ta Kaimun, muna dariya dukkan mu don na kwaikwayi bakin ƴan unguwar mune, sannan tace .

" kinga wannan filin gaban mun? Toh dama Abban ju ya daɗe da saya, kuma burin shi ya gina kafin su Hamman ki su girma, amma Allah bai nufah ba, yanzu wani kuɗin shine, da wanda Hammanki yake tarawa, da kuma Abban ki ɗayan da Auntyn ki suka haɗa aka gina wannan palon da ɗakuna biyu kwanne da toilet ɗin shi, kuma na zamani.

Kinga har kujeru Auntyn tasaka mana da gadaje, palon da ɗakin kusa da cikin gidan na Abban ki kenan, sannan wanda yake gaban varandan na su Hammanki ne, don yafi girma ma, duk da Hammanki babban kan nasan ba zuwa zaiyi ba.

Kuma wani abin daɗin, wannan ɗan gidan mijin Auntyn ki wata rana sunzo da Auntyn ki, ya samu ana aikin ginin, toh shima ya mana albishi ɗin zaiyi renoveting namu side ɗin, za'a haɗe mun ɗakuna biyun su zama room and parlo, da toilet ɗinsu, ke har madai anzo an duba wuraren, yabar jomai a hannun Auntyn ki.

Duk bayanin cikin farin ciki Ummi nah take mun, da sauri nace mata " Hammah Babagana?" ...... Bashiba yayan nashi wanda yanxo ya koma Abujah, wanda kukaje bikin shi maiduguri, tana kallona.

Gaba nane naji ya faɗi, domin ni harna manta dashi a rayuwata.

Hmm kawai nace, sannan Hammah ya riko hannu na yace Black tashi muje ki ga side ɗin yayi kyau.

Muna shiga naga yaddah wurin yayi kyau, ae bansan lokacin dana tuntsire da dariya ba.

Hammah kaga gidanmu irin na ƴan gayu? Na faɗa ina dariya, ahima dariyan yakeyi, don ganin naji daɗi.

Dole naji daɗi wurine duk anasake tyles ga rober silling, ga wani white pent hakanma mai maiƙo, gaba ɗaya wurin ya haska.

Daɗin ma sai dana shifa palon naga ƙaton plasma a manne da bango, da sauri ɓa juya ina kallon Hammah ina wani zare ido.

Dariya yayi ya riƙo hannu na yace, wannan duk aikin Hammanki Babba ne, shida Hammah khalil da kuɗinsu na service suka saya dubu ɗari fah my sis, ya faɗa yana jin daɗi.

Hawaye ne bansan na meye ba suka zubo mun a ido nah, yayi dai-dai da shigowan Abban mu, da sauri naje na rungume shi kawai saiji nati na fashe da kuka.

Ummi ce a bayan Abban mu, tace haba autan Abba yayah zakiyi kuka bayan murna zakiji ƴan uwanki sunyi abun kirki da iyayenki!.

Kallon Abba nah nayi idona ɗauke da hawaye nace toh Abbah nah ni banida abinda zan muku kuji daɗi.

Dariya yakeyi yana buga kafaɗa na yace haba ƴar uwarta jinin jikina, ai kece zaki mun komai nan gaba, donke zaki kaimu makkah insha Allah, bansan lokacin dana kwashe sa dariyaba don daɗi, nace "Abbah na ko su Hammah sunce zasu kaika kada kaje, kajira nagama karatu nayi kuɗi sai na kaiku kaida Ummin Sadiq, na faɗa ina dariya.

Shima dariyar yayi yace hakane ƴar'uwata, Ummi ce tayi charab tace "lallai ma saidai kajira takai ka, nikn Sadiqu nane zai kaini ko? tana duban sadiq da yake dariyan shirmena.

Baki isa ba ae inji Abba yace " dole ki haƙura sai ƴar'uwata ce zata kaimu, ni kuma sai daɗi nakeji ina kara shiga jikin Abba nah, a rayuwa ta ina son Abba nah sannan ina jin wani irin tausayinshi a raina.

Abba nah talaka ne, amma ya riƙe talaucin shi, kuma dai-dai gwargwado yana kula da mu, gashi yanzu bawani samu yake yiba a sana'ar shi, yawanci ma yafi zama a shagon da ake aiki, da yake ya iya aiki sosai.

A rayuwata ina son iyayena ina kuma tausaya musu, ga Allah ya bani yayu wanda ban isa ince ga wanda yafi sona ba, haka zalika, ƴan uwan Abbah na da ƴaƴan su, suna matuƙar ƙauna ta, Ummi na ita kaɗai mahaifiyarta  ta haifa sai ta rasu, shiyasa yawancin zamanta wurin goggon tane, wato umman kafi, wataran idan na Kwanta  sai nayi tunanin mutuwa, yanzu kenan watara nah, zamu iya rabuwa? Kawai sai na fara kuka.

Ban shiga gidan su besty ba, sai bayan kwana uku shima ta shigo ne tana ta mun mira ban shiga ba, kuma yayah Kamal ta dawo jiya da dare, babu yadda na iyah haka na bita muka shiga

A palo muka samu duka ƴan gidan daga yaran har iyayen, Daddy na da bai cika zama ba yau yana nan, suna murnan dawowan Kamal, wanda zai fara law school.

Gaishe da Daddy da Mummy nayi, suka amsaaa cikin farin ciki da ganinah.

Sannan na juya gun yayah Kamal wanda ya mun kuri da ido kaman bai sanni ba, har ƙasa na tsuguna nace "yayah kadawo lafiya? Yayah karatu?.

A fusge ya amsa mun, wanda gaba ɗaya na lura jaman hankalin shi ya tafi wani wuri, sannan na juya nagaida su Adda hafsa ina tsokanan su amareh.

"kuma kuna kusa inji Adda umaimah" tana dariyan mu, da sauri nace mata "Adda mukan ae bamu girma ba, sai kunyi yara uku-uku tukun a fara zancen mu" nafaɗa ina dariya nida besty.

Mummy ce tace a'a ban yadda ba auta na, har sukayi yarah uku kan ai kuma kuna shirin yin nabiyu, yadda kuka cika idon nan ina zanbarku? Tafaɗa kowa yana mana dariya.

Shidai tayh kamal baice komai ba, banda murmushi da yakeyi, amma gaba ɗaya idon shi yana kaina, har besty taja hannu na mukayi ɗakinsu.

Ranan saturɗay wanda yayi daidai da satin mu ɗaya a gida, muka shirya nida besty zamuje gidan Goggon bauchi domin mugaisheta, da misalun ƙarfe sha biyu na rana muka tafi, domin sai dare mu dawo.

A can muka haɗu da Hammah Sadiq da Hammah Bappah a falon goggo suna haɗa mata TV Stand, a wurin muka zauna muna ta hira dasu, ɗayake daga Sadiq ɗin har Bappan halin su ɗaya ne na tsokana, babu inɗa zasu ganni basu zolayeni ba, kamar kakarsu.

A haka  Goggo ta fito daga ɗakinta hannunta rike da cup tana shan abu a ciki.

wuri ta samu ta zauna tana me ƴar'uwata ta muku kuke zolayar ta?

Muna dariya nida beaty muka tsuguna muka gaisheta, bayan ta amsa ne, tace mun kuje side ɗin Hammankiku gaishe shi, jiya yazo shi, da sauri na tashi nace "Goggo nakai 2yrs banga Hammah ba fah, na faɗa ina nufan hanyan fita a palon, besty na bina a baya".

A zaune muka same shi a palon shi yana breakfast, innalillahi na faɗa a zuciyata don ganin wani irin fari da kyau da  Hammah ya ƙara.

Har ƙasa muka tsuguna muka gaisheshi, yana tambaynmu yayah su Abbah? Cikin nutsuwa da Kamala yake mana maganan.

A nutse muma muke bashi amsa, sannan ya juya ta jalli besty, yace " yayah ma sunanki?".......... Gaba ɗaya naga besty  ta ruɗe kaman zata dungura tace Nafeesat!.

Maida idon shi ya sakeyi yana kallonta ,can yace  ajin ku nawa? Jiki na rawa ta sake ce mishi bana zamuyi candy.

Ya ɗau lokaci bai ce komai ba, yana shan tea ɗin shi, sai can yace me zaku karanta?

Jiki na rawa ta taɓa ni alaman ni nayi magana, amma kawai saiji nayi yace "da ke nakeyi nafisatu".

Ina gani tsugonon ya gagari besty, jawai neman wurin zama tayi kawai naga ta zauna, bakinta yana in ina tace " Dama computer muke so mu karanta."

Bashi zakuyi ba naji muryan shi yana faɗa, ɗago kanmu mu kayi muna kallon shi, saiji mukayi yace ku cika school of nursing.

Sannan yace ku tashi kuje zan samu su Abban, da sauri muka fito, besty kaman zata dungura ƙasa don sauri.

Muna fita muka kalli juna muka kwashe da dariya, besty tace "ikon God inji ƙawar mu Troublem, kiji mun tsabar Kwarjini da zai halaka mu?"

Dariya nayi, nace ae naga duk kin ruɗe ko maiyasa haka ohoo, itama dariya tayi, tace ktau nagani da class kawai, kwashewa muka sakeyi da dariya, nace ko dai za'ayi ƴar gida -gida ne?

Hmmm kawai tace, sannan muka shiga wurin Goggo inda muka samu su Hammah sun fita wai.

Goggo sai murna takeyi tanata tambaya nah ina dai kun haɗu da Hamman naku? Amsa mata ɓati ehh Goggo har ma ya tambayemu wace makaranta zamuyi?

Da saurinta tace ina dai kin gaya mishi abin sa kike so? Zunɓuru baki nayi nace Goggo munce mishi computer muke so amma yace School of Nursing zamuje, Goggo ce tace babu komai bari ya shigo zan sa shi yabarki a inda kike so kinji auta!

Da sauri Besty tace a'a Goggo kibar shi kawai da wanda ya zaɓa mana nan, inaga zaifi mana ma alkhairi.

Da sauri na kalleta ina mamakin abinda tace, amma bance Komaiba, a gidan Goggo muka wuni har bayan magarib mukace zamu tafi, nan Goggo ta ƙira Hammah Haidar tace yazo ya maida mu gida, duk a tsorace nake da shi, amma ira Goggo kaman tayi yayah takeji, dama ita haka take duk ranan dana zo gidanta kaman ta lashe ni takeji.

Washe gari ranan sunday muka shiryah zuwa gidan Aunty, inda na shiga wurin besty around 11:00 nace tazo muje, a palon na samu yayah Kamal yana kallo gefen shi su Adda Umaima ne.

Tashi yayi yace kuzo na rage muku ganya dama zanyi dass park ne, tashi mukayi da sauri muka bi bayanshi har wurin motan shi mai masifar kyau.

Muna parking a cikin gidan Aunty, Yayah Kamal yace muje muce yana gaishe da Auntyn, muna fitowa a motan yayi dai-dai da fitowan Hammah Umar a side ɗin Maman shi, gaba ɗaya idon shi yana kanmu, ya kalleni ya kalli Yayah kamal.

Da sauri na shiga side ɗin Aunty, nagaya mata da Yayah Kamal muke tafe, tura mu tayi tace muce ya shigo su gaisa tana ta murna don ta daɗe basu haɗuba.

Palon ya shigo bayan sun gaisa ya tashi yayi hanya waje, yana cemana what time zai dawo ya ɗauke mu? Besty ne tace after anyi sallan ishaa.

Yana fitowa suka sake haɗuwa da Hammah Umar wanda zai shiga motan shi su fita da zainab, kallon banza  kowansu yayiwa kowa, wanda idan zaka kashe su basu san juna bama.

Toh ƙaƙatsara ƙaƙa, idan baku gajji ba kuci gaba da bin alƙalamin .

*AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*

®☄
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION* ✍🏻
{Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar duniya da kuma lahira.}

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN KARFE* 🏇

Story and written
By
*AUNTY NICE* 😘

*Page*1️⃣2️⃣

Aunty mai zamu dafah? Na tambayi  Aunty muna wuce wa kitchen nida besty, "ku dafah mana abu mai daɗi kawai auta" ta faɗa tana dariya.

Bayan mun shiga kitchen ne, na tambayi besty, "me kike gani zamu dafah?" ..... Kawai muyi tuwo miyan egusi da zoɓo inji besty, hararanta nayi cikin wasa nace " ke kam mayyar tuwo ce wallahi".

Tana dariya tace bazaki gane bane beaty, idan akace miki tuwo da miya mai daɗi ai kin wuce wurin, kawai shi zamuyi besty ta faɗa tana dariyan jin daɗi.

Wurin 2:00 muka gama da kitchen banda ƙamshin miyan egusi babu abinda yake tashi.

Dinning mukaje muka jera, ga zoɓon yayi sanyi, yasha abarba da cocumber ga ƙamshin chittah da kananfari  yana tashi, bayan mun jera muka wuce ɗaki don tin sallah, muka bar Aunty a palon sai albarka take saka mana.

Mujaheed ne ya shigo yace mun besty kizo inji Aunty, ya juya da gudu yana dariya, dariya nayi nace ja'iri wai yaji kunya.

A kan dinning na samesu daga Baban, Auntyn har yaran suna cin abinci, gefen Baban naga Hammah Umar ya ɗaure fuska gam yana jefa loman tuwa a bakin shi.

Matsowa nayi na gaishe da Baban, cikin laadabi, fuskar shi ɗauke da fara'a ya dube ni yace "wato kika ƙi zuwa mana hutu ko? baki zuwa a hakan zan aurar da ke wa Mujaheed ɗin? Ya faɗa yana kallon muja yana dariya," gefe ɗaya shima Mujaheed ɗin dariyan yakeyi yana rufe idon shi, a dole yaaji kunya.

Murmushi  nayi ina  duban Mujah, shi kuma Gidaɗo kaman jirah yakeyi, yace dama kuma nine alwalinta Baba, ya faɗa yana mun dariyan neman tsokana, kallon shi nayi ina hararan shi, nace " kaji yaron nan! ni sa'ar kace?"

Baba ne yake dariyan  faɗan mu na kullum da Gidaɗo yace " ni wanene babbah a cikin ku ne kam?"

Baba ni ce yayarshi amma ya raina ni, shima da sauri yace "Baba ae tunda nine namiji na zama yayanta, kuma Abba yace nine zan zama alwalinta"

Toh babban magana inji Baba da yake daariyan hararan Gidaɗo da nakeyi, yace ahhh lallai Gidaɗo yanzu na yadda kaine yayaantaa, tun da har alwalanci zaka mataa, ya faɗa yaan dariyan mu, itama Auntyn dariyan mu takeyi.

Shidai Hammah bai saka mana baki ba a maganan mu, abinci shi kawai ya ke ci, saboda har sun kusa gama ci ya shigo, shima Khalifah ko uffan bai ce ba, sai kallon mu kawai yakeyi

ɗayavbayan ɗayƴa.

Baba ne yace "Fatima gaskiya girkin nan yayi daɗi shi yasa nace a ƙiraki nayi godiya, don munyi missing girkin ki sosai, ga Gidaɗo ya raina ki, gashi da nayi niyyaan naa haɗaku aure, amma naga ba zaiyi miki biyayyah ba, Baba ya faɗa yana dariyan abinda zaije yazo, ...... "Chabbb wannan ɗan ƴaaaaron" na faɗa ina hararan Gidaɗo da yake mun dariyan shaƙiyanci, shima cewa yayi haba yrinya kinyi wa kanki da kin samu ɗan handsome y faɗa yan mun gwalo.

Kawai saaaijin Khalifah mukayi yace "wane kai yaro, Haammah Babagana yace mun shi zai auri Adda Riyyah, kuma ya ban amananta na dinga kula mishi da ita, kafin wani yace yana sonta, kuma muna waya da shi tun da ya tafi lagos in bashi information akan ta," ya faɗa yana kallon Baban, sannan yaa cigaba da kallon Baban shi yace " ɗazu ma munyi waya, na gayaa mishi ta zo, kuma yace mun idan bai aure ta ba zai iya mutuwa Baba, shiyasa kullum idan nayi sallah ina addu'an, Allah yasa suyi aure."

Gaba ɗaya palon shiru wurin yayi baka jin komai sai ƙarn TV, hattah Hammah Umar saida ya dakata da cin abincin ya ƙurawa Khalifah ido, a zuciyar shi yasan gaskiya yaron ya faɗa, don babu shiririta kwata-kwata a rayuwar yaron, don ya daɗe da sanin halin su ɗay da khalifah, nutsuwar su da rashin sun maganan su ɗaya, shi kuma Gidaɗo da Babagana halinsu ɗaya, surutun su da son mutanen su ɗaya, don idan basu gidan sai kasan basu nan.

Gaba ɗaya ji yayi abincin ya fita mishi a rai, yama rasa tunanin me zai fara.

Itaa kanta Aunty saida taji gabanta ya faɗi, duk da ta daɗe da fahimtan Babagana yana son takwaranta, amma ganin har anzo wannan lokacin bai furta ba, saita cire abun a ranta, don haar ga Allah tana son shi, amma bata jin zata iya barin ƴar ɗan'uwanta tayi surkunta da Mama, shiyasa suka shirya ita da Goggo Aisha akan Hammah Haidar kawai ya nemeta.

Duk da Ummah bata goyi bayansi ba, don tace subar Riyyah ta zaɓi mijin daya mata, idan Baababaganan Alkhairi ni mama bata isa komai ba, idan kuma an saaka Haidar ya aure ta basu son juna fah? Nan ma an ɓat zumunci.

Shima Baba saida yaji wani iri sanin halin Mama, da kuma sanin haƙuri irin na Fatima, amma chan cikin ranshi abun ya mishi daɗi sosai, don kullum ya ga yarinyar sai a ranshi yace dama Gidaɗo babba ne mana, daya haɗa su auren zumunci, amma ga abinda Allah ya shiryah, insha Allahu zaiyi iya yinshi yaga Mama bata kawo mishi matsalah ba, kuma zai nemi Babagana yaƙara jin gaskiyan bayanin.

Duk saida naji kunta ya Kamani, irin kallon danaga kowa yana mun, ina jin tsoron Maman su besty, amma kullum cikin raina sai naji dama ace idan na tashi aure besty ne mijina, haka kawai naji daɗi a raina tun ban tabbatar da abin ba, kuma ni idan har zan auri besty babu ruwa na da

masifar maman shi, nidai kawai bazan raina taba, kuma idan har zata bari wannan ɗan farin ɗan nata ya aure ni ae tagama mun komai, Nifa gaskita ni *FATIMA* tun asali Allah ya samun son farin miji, tashi nayi da sauri na wuce ɗakin Aunty,bwurin Besty nah.

Baba ne cikin farin ciki ya juyo wurin Hammah yace " kaga ƙaninka ko? Wato shi Fatima yake so kuma yayi shiru bai faɗa ba? abin yamun daɗi wallahi Umar, don Fatima ɗiyace da kowani uba zai so yaga ɗanshi ya haɗa zuriya da ita, saidai matsalan Maman ko nake tunani".

Shiru Hammah yayi har zuwa wani lokaci kaman bazai ce komai ba, har Aunty taji wani iri da maganan Maman su da Baban su yyi agaban shi.

Baba idan Allah ya nufah Babagana mijin tane, toh Mama ba abinda zata hana, saidai shawara ɗaya yakamata shi Babaganan ya nemi haɗin kan yarinyar, idan ta amince saika samu manyanta, inaga hakan zaifi, ita kuma Mama kabar ni da ita, bai sake cewa komai ba ya tashi yayi hanyar waje.

Baba cikin farin ciki ya dubi Auntyƴ yace "Fatima ina mamakin hali irin na Zahra, amma sai Allah ya bata yara masu hangen nesa, wallahi duk yaranta basuyi halinta ba, ya faɗa fuskan shi ɗauke da farin ciki.

Hmmm Baban su kenan, ae halinka suka gado, sannan itama Maman su ka mata uzuri baka ga iyayenta nasu halin dabanba, ƴar uwarta Fanna kaman ba ciki daya suka fito ba, kawai kamata addu'a Allah yasa ta gyara.

Palon shi ya shiga inda ya samu Zainab kwance tana kallon wani series, Harara ya watsa mata yace "kimgyara mun palone da zakizo kiyi baƙeƙe?" Cikin Rangwaɗa ta tashi tana matsowa kusan shi tana cewa haba honey? Hayanin Nabil ne ya dawo dani nan, Kallo nake son yi.

Malama  don Allah fita ki bani wuri nima bana son hayaniya yau, kallon shi tayi taga babu wasa, kawai sai ta kwashi shirginta ta fita kafin ya sauƙe akanta.

Mtsss yaja tsaki, yace ƙazama kawai baki iya gyara ba sai ɓatawa, amma idan akace kallone kinfi kowa iyawa.

Ɗaki ya wuce ya kwanta, gaba ɗaya shi yarasa tunanin da zaiyi, yarinyar nan ba ƴar'uwar shiba amma yafi so yaga rayuwar ta tayi kyau, Karatu yake so yaga tayi ba soyayyah ba, bata ga ita

kaɗaice mace a familyn su, amma tana su tayi wasa da damanta, juyi ya sakeyi a fili ya furta Ƴar jaririya, sai kuma ya ce Babagana, shi kaɗan shi yaji yana magana.

*************

A ɗaki faɗawa nayi kan Besty da take kwance tana kallon pics a wayan Aunty, photon Hammah Haidar ta ƙurawa ido kaman zatayi hawaye tana kallon shi.

A razane ta tashi tana cewa " Besty me ya faru?"...... Dariya na kwashe da shi na rungumeta, ina buga bayanta nace Besty burina zai cika, ita ma dariyan tasamu kanta dayi tace bani bayani nasha ƙawar Trouble, dariya mukayi gaba ɗayan mu.

Kwashe jomai nayi na bata labari cikin farin -ciki, itama murma ta tayƴani da shi, sannan tace Besty Allah yasa auren mu yazo lokaci ɗayƴa, ina dariya nace Amin Besty nah, kema Allah ya kawo miki.

" Besty nima Allah ya kawu mun sai dai addu'an Allah yasa ya soni yadda naji ina son shi"

Da sauri na dube ta nace Besty Wanene? Labarin rashin baccin da tayi daren jita saboda tunanin Hamma Haidar ta bani, wani irin masifaffen daɗi naji, nace Besty idan Allah ya yarda Hammah Haidar mijinki ne, don naga irin kallonki da jiya yakeyi a sace, nasan shima ya rallah farar fata, ga ƙugu zallah, gaba ɗayƴa daruya muka kwashe dukkan mu cikin jin daɗi.

Yayah Kamal ne yazo wurin ƙarfe 8:30 na dare, har palon Aunty ya shigo anan ya same mu muna ta hira dasu Gidaɗo dasu mujah nawa, bayan sun gaisa ne da Aunty, muka mata sallama, tana kallona cikin zolaya tace, wato nati niyyah wannan karon bazan kwana mata ba ko? Ina darita nace Aunty ae idan muka gama  a nan zanyi hutu, har saina dai-daita miki hankalin wannan yaron, ina duban Gidaɗo ina dariya, shima dariyan yayi yace "doƙe na ae matar yayah, na isa nace wani abu ki cire mun kwano na a gidan ki?" Hmm kawai nace nayi hanyar waje, da sauri Yayah Kamal ya dubi Gidaɗo baice komai ba Ya juya yabi bayan mu bayan ya sakeyi wa Aunry sallama.

Baba ne ya ƙira Hammah Babagana bayan sun gaisa yake ce mishi, an kawo gaisuwan aure ƙawarka ma, har Abban ta ya bani daman bayadda da ita ma.

"Riyyah ko wa Baba? Babagana ya tambayi Baban shi cikin razana.

Dama kana da wata ƙawa ce bayan ita? Cewar Baba, "shiyasa nace ni zan fara maka albishir don na san zakafi kowa farin ciki.

Nafi kowa baƙin ciki dai Baba, yaji maganan ta fito abakinshi batare da ya shiryah ba, Baba kasan fir how long nakai ina jinta a raina?  Ae bani da wani buri irin naga tagama School saina tun Kareta da maganan aure, donni nafiso tayi karatu ma a gidana, nidai Baba kawai kaje kace an fasa basu ita, kaima ɗanka yana aonta kuma idan bai aureta ba mutuwa zaiyi, duk magana Besty yakeyi ba cikin nutsuwar shi ba, don ya ma manta da yaah matsayin Baban yake a gunshi.

Baba cikin darita yace "dole na naje na rushe wancan maganan na kafa na ɗana don kada ya mutu akan soyayyah.

Amma kuma Babagana idan Mamanka taƙi amincewa kuma fah? Bayan na bawa wa ƴancan haƙuri, yayah za'ayi?.

Baba kace mata idan taƙi ɗanta mutuwa zaiyi gara ma ta saduda, don wallahi ban san irin sonda nake mata ba, don har yafi ƙarfi nah, ya faɗa kaman zaiyiwa Baban shi kuka.

Baba ji yayi jikin yayi sanyi, a ranshi yace wannan zafin soyayyah yaron shi ya gado shine, haka yayi wa dukka matan shi, Umar ne kawai baiga yana da zafin soyaayyah ba.

Kada kaji komai cewar Baba, kaidai ka nemi haɗin kan yarinya kawai, kabar mun komai a hannu nah.

Ranan wedsday tun da safe muke shirin zuwa Alkaleri, wanda  yaya Kamal ne zai kaimu, zucitana kuma cike da murna, don labarin da zan bawa Besty, don jiya bayan ishaa Hammah Haidar yazo gidanmu, kuma ya tambayeni ina ne gidan  su ƙawata? Bayan na bashi bayani akanta, sai ya tambayeni na bashi digit na ta, amma sai nace mishi bamu rike waya sai mun gama school imji Abba.

Kaɗa kanshi yayi yace ba komai, hakan dai-dai ne, amma ki gaya mata kada ta chanja shawara school of nursing nake so kuje.

Muna shiga Alkaleri direct family house ɗinsu mukayi, wasu kyawawan ƴan mata ne masu kama da Besty su biyu suka zo mana oyoyo, yaran masu masifan sun mutane, ɗaya sunan ta Haƙilah

ɗayan kuma Fauziya, kaman su Lashe mu haka sukeji muka shiga har ɗakin maman su wacce suke ce mata Hajiya, itama fara ce mai kyaun gaske kaman ƴanmatan.

*DAGA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*

®☄
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION*✍🏻
_{Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar duniya da kuma lahira.}_

🎐G•W•A🎐
_*GASKIYA DOKIN KARFE* 🏇_

Story and written
By
*AUNTY NICE* 😘

*PAGE* 13

Hajiyan ma da farin ciki ta tarbe mu, tana tambayan mu mutane gidan yayah muka baro su? "amsa mata muakayi da lafiya, suna gaisheta" sannan muka wuce ɗakin su Haƙilah, Fauziyyah ce riƙe da hannun besty kaman ta lashe ta don murna.

Har sai naji sun burgeni, dama nima ina da cousin mace mana, ko kuma sister mace, abin duk sai yaban sha'awa.

Bakin gado muka zauna, sannan Haƙilah tace wa fauziyyah "sis jeki kawo musu abin sha mana, sannan ki kaiwa Yayah Kamal ma,yana falon Hajiya".

Bayan Fauziyyah ta dawo da trey a hannun tane, ta nemi wuri ta zauna kusa dani, tace " Bestyn besty kunzo lafiya?" tana kallona fuskanta ɗauke da murmushi, nima murmushinne ɗauke a fuskana nace " lafiya qalau cwityn Besty na faɗa ina kallonta da murmushi ɗauke a fuskata".

Hirane ya kachame tsakaninsu, inda naji Haƙilah tana gayawa Besty, maganan haɗa auren su da za'ayi dasu Umaimah nan da ƙarshen shekara.

Dama Haƙilah sa'o'i suke da Adda Hafsa, akwai ƙaninta kuma Mubaarak wanda shine sa'an Umaimah, ita kuma besty da Fauziyyah.

Fauziyyah ce tace, " muma fah ashobi zamuyi ɗan gaske ko Feenah?" tana tambayan Besty, gaba ɗay daai hiran ya koma na maganan auren.

Can saai nagaa Fauzy ta tashi "tace bari na duba Yayah Kamal, bata jira mun ce komai ba da fita abunta da sauri" .

A palon Hajiya ta samu Yayah Kamal suna kallo da Hajiya jifa-jifah sun ɗan taaɓa hira akan karatun Mubaraq daya tafi maleshia.

Gefen shi ta zauna, tana ɗauke da murmushi ta dube shi tace "Yayah Kamal mun bar ka kai da Hajiya ko? ta faɗa tana murmushi", shima murmushin yakeyi yace No ba komai, muna tare da Hajiya ae.

Zama tayi aka cigaba da hiran da ita, can mukaji shiru, sai Haƙilah tace mutafi palon Hajiyan muma, haka muka ɗunguma sai can, inda muka same su zaune suna kallo, muma mukayi joining ɗinsu ana kallon ana hira.

Duk ɗaga idon da zanyi sai mun haɗa ido da Yayaa Kamal, duk sai naji na tsargu, ita kuma Fauzy duk hiranta sai ta sakaa Yayh a ciki, haka yake biyeta suna kallon suna hiran, tashi Hajiyan taayi ta barmu.

Azahar tana yi muka shiga ɗakin Hajiya domin muyi sallah, Fauzy tana idarwa sai ta ɗaga hannu saama, tace "Ya ALLAH kabaani miji haɗaɗɗe kamili, fari mai kyau da aji kaman Yayaah Kamal, taa faɗa tana kwashewa da dariya".

Muma kwashewa da dariyan mukayi, Haƙilah tace "zama kiyi bayani yarinya, gara ma ki fito kiyi bayani, don inda wani taimako kisamu muyi miki," tafaɗa tana dariyanta, Besty ma dariyan tayi, tace "lallai tuwo na mai na za ayi, abinko zai bada kala, mai surutu da mai shiru, ta faɗa tana dariyan Fauzy".

Haka sukaita tsokananta, nidai sai murmushi nake musu, Hajiya ce ta ƙwala musu ƙira tace su fito suci abinci.

Muna fitowa palon muka samu Yayaah Kamal yana cin abincin shi hankali kwance, idon shi kuma na kan TV yana kallo, amma duk bayan wasu ƴan mintuna sai ya ɗaga kai ya kalleni, duk naji ni a takure abincin ma saiji nayi ya gagare ni ci.

Hajiya ce ta dube ni tace "me zan gani Badariyyah? wai har kinci abincin kenan? gaskiya ban yadda ba ki maida hankali kici abinci".

Ɗan murmushi nayi na dubi Hajiya nace "naci ae Hajiya, kuma na rigah na ƙoshi ae" kaman ance na dubi inda yake, kawai sai idon mu suka sake haɗuwa, alama yamun dana ci abincin, amma ban saurare shiba kawai na cigaba da kallo nah.

"Yayah Kamal kai yaushe naka auren?" cewar Fauzy data ƙura mishi ido, kallon ta kawai yayi, sannan yayi murmushi yace "nabaki kwangilah ki sama mun" ya faɗa idon shi still yana kaina fuskar shi ɗauke da wane cool smile.

Toh Yaya Kamal insha Allahu zan sama maka mata mai kyau da hankali, kuma ƴar gidan mutunci, kuma kasan wani abu ne yayah? Ta faɗa tana tashi kumawa kusa da shi ta zauna, yace "sai kin faɗa".

"yayah zan sama maka wacce zata ɗebe maka kewa a gidanka, ta haifah maka kyawawan yara farare sol" kallonta yayi yace "Toh ni ce miki nayi dole fara nakeso? Bakiga ni fari bane, ae kawai kisama mun nai hankali, wanda bata da rawan kai, kuma ke zakije mun hiran"  dukkaan su palon dariya suke musu, banda ni dana sunkuyar da kaina ƙasa.

Bayan munyi sallan la'asar ne, muka fita zagaya dangin su domin gaishe su, Fauzy ce agaaban motan saai zuba takeyi mu kuma muna baya nida Besty da Haƙilah dai dariyan su mukeyi.

Duk gidan da mukaje sai an tsokani Fauzy da Besty kan cewa daga su Haƙilah fah sai su, dariyan su kawai muke tayi, haka muka zaga gidajen, wajajen 5:30  muka kama hanyan Bauchi.

Bayan sallan ishaa sai ga Yayah Kamal ya shigo gidanmu da sallama, palon Ummi yaje ya zauna, bayan sun gaisa yake tambayanta "Ummi ina Riyyah"? "tana palon Abbansu ta gaya mishi".

Ina zaune da dogon riga  mai roba, da hulan shi irin wanda ake ɗinkasu da yadin hijab ya shigo ya sameni muna kallo nida Hammah Sadiq, kujera ya samu ya zauna, Hammah ya gaishe shi, nima gaishe shi nayi sai palon ya ɗauki shiru saboda kallon daya ɗauke mana hankali gaba ɗaya na *TARKON ƘAUNA* Wanda tashan Arewa 24 suke haskawa, shima biye mu yayi yana kallon bawai don ya fahimci kan film ɗinba.

Bayan mun gama ne,ya dubeni "yace ɗauko hijabin ki, ki rakani wani wuri," da sauri na tashi na shige cikin gida, ɗakin Ummi naje na gaya mata Yayah Kamal yace nazo na rakashi wani wuri, kaɗa kai kawai tayi ta cigaba da cin abincinta, bayam na fito ne, da hijabina har ƙasa mai ɗinkin pocket hand, Ummi ta kalleni tace "FATIMA ki kula da kanki fah" insha Allahu na amsa mata, sannan na fita har inda mottan Yayah Kamal yake na shiga na zauna.

Tafiya mukeyi batare da yace min uffan ba, bamu muka tsayah ba, sai a gaban *TREEFUL N* bai ce mun komai ba ya buɗe motan ya shige cikin restaurant ɗin, jumawa kaɗan nagan shi ya fito hannun shi ɗauke da ledan su wurin leda uku, bayan motan ya buɗe ya zuba, sannan ya shigo mukayi gaba.

Bamu tsaya a ko'ina ba sai Bauchi clup nan ma shi kaɗai ya fita ya shiga, jumawa kaɗan ya fito da leda a hannunshi, shima bayan sit ɗin ya ajiye, sannan muka wuce, a gaban city crown ya tsaya nan m shi kaɗan shi ya shiga, nidai sai kallon ikon Allah nakeyi, ledodi kusan huɗu ya fito dasu sannan yaja muka kaama hanyan gida.

Riyyah! Naji sautin muryanshi ya ƙirani,  batare dana amsa ba na ɗago na dube shi, shima wannan karon kallona ya keyi, naga kallon yaƙi ƙarewa, kuma baice komai ba, dole na ƙasa-ƙasa na amsa mishi da "na'am", sannan ya kawar da kanshi gefe yace ɗazu kinƙi cin abinci , ko me yasa?

Batare dana kalle shiba nace " kawai naji na ƙoshi ne".

"ƙarya kike yi, ido nah kike tsoro, ko bahaka ba"? Ya faɗa yana tsaida motan a gefen titi, "Yayah ba haka bane kawai dai na ƙoshi ne " na faɗa ido na yana kan cinyana ina wasa da hannuna.

"Toh idan ba haka bane yanzu ki kalleni, kice ba hakan bane", "nidai kasan bazan iya ba, amma ka yadda na ƙoshine kawai".

Murmushi yayi mai sauti, sannan yace "ga dai abincin na saamo miki, saboda ina binki bashi, kinje gidanmu bakici ba," dariya nayi nace"Yayah ae basai ka biyani ba, nima ae gidanmu ne, da babaka wahalar da kanakaba".

"Hmmm wahala ne don na kula davƴar'uwata? ae ni daza a amince daga yau nine mai miki dukkan hidiman ki, abincinki, Suturan ki, makarantanki, ke da dukkan ɗawainiyar ki, ya faɗa fuskanshi ɗauke dabdariyan tsokana".

Nima dariyan nayi nace mishi" Yayah dama kana magana ne?" Wani irin kallo ya mun wanda idan ba wurin Babagana ba bana ganin irinshi, duk sai yasaka naji kunyan shi kaman na nutse ƙasan motan,".

Dariya kaɗan yayi ya ce " baki san ina magana ba ko? Toh yau kinga alama, amma a gaban ki kaɗai zan dingayi, kin amince?" murmushi nayi na dube shi nace" mutafi gida kada dare yayi kaji".

Tada motan yayi yana ta murmushi, sanan yace "kinji ƙawar ku wai zata sama mun mata, toh ke meye shawaraki?"  kallon shi nayi nace mishi "Ni shawarata ita kawai na zaɓa maka, kaga tuwo na maina, kuma zaku dace sosai,"  ....... Shiru yayi har na ɗauka bazai sake magana ba, don har mun karyo ƙofar gidanmu, sanann naji yace "Hakan kike ga ya miki? Idan ni kuma bata mun ba fah? Wa zaki bani?"

Shiru nayi nace " toh ae bansan irin wacce kake so ba" " itan tasani ne?" ya rambayeni da sauri, juya kaina nayi alaman a'a, " toh wa zaki zaɓa mun? ya sake tambaya nah.

Kawai nidai naga kun dace, na sake faɗa mishi, harara na yayi yace "toh ni banga dacewan ba, amma na hango inda zanfi dacewan".

Kallon shi nayi nace "dama kana da wacce kake so kenan? Yayah amma kuma naga kaman Fauzy tana sonka, dabadan kana da wata ba, dani a ganinah kawai zaku dace", kallona yayi yace " ita ta gaya miki tana sona"?

Darita yabani saboda tambayan da yayi kuma yana hararah nah, murmusawa nayi ina kallon shi sannan nace " bata gaya mun ba, amma naga alama", unwwm kawai yace yana duba nah, sannan yace " alaman nata kawai kika iya ganewa, don kindamu da ita, amma ni ko oho baki damu da ki gane wa nake so ba?"

Yayah Kaga Baba ya shiga gida bari naje, " kin kauce wa zan cen ko?  naji ya jefo mun tambayan",  bance komai ba na buɗe motan na fito, Shima  Fitowan yayi, ya tsaya kusa dani, bazaki ɗauki ledan bane ko ni kike jira na ɗauko miki? Ya tambaya.

Ban bashi amsa ba na kama hanyan shiga gidan mu ina mishi dariya, nace " kafara duty ka na kula da friend ɗin matan ka daga yau, na faɗa ina dariya nayi shigewa na cikin gidan.

Dariya yayi ya kaɗa kanshi sannan ya ɗauko mun nawa ledojin ya bar nasu a motan, ya biyo bayana har palon, inda ya same mu duka harda su Ummi, kallonah yayi yace ga kayanki, sannan ya juya yayiwa su Ummi sallama ya fita.

Washe gari Baba ne, naga yazo wurin Abba na, naga sun shiga palo, bansan me suke taattaunawa ba, kallon Aunty nice nayi nace, don Allah je kiji me suke faɗa, da sauri Aunty nice ta tashi ta shifa palon, shiru-shiru banji ta fito ba duk haushin ta yakamani, shiyasa zan jira ta fito sai muji me yake tafe da Baban.

*DAGA ALƘALAMIN AUNTY NICE*
✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*

✍®
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION*✍🏻
{Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma da domin riban duniya da kuma lahira.}

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN ƘARFE*🏇

Story and written
By
*AUNTY NICE*😘

*PAGE*1️⃣4️⃣

{Hmmmm nasan dayawa nason jin meye ake tattaunawa tsakanin Abba da Baba, toh babu ruwan Aunty Nice, baza aji a bakinta yanzu ba, wannan page ɗin naki ne, Juwairy Ahmadu Yari Bauchi}

Da yammah Besty ta shigo mana domin muje muyi shooping domin kumaawan mu school yazo, don ranan sunday zamu koma.

Muna zaune muna ta rubuta abinda zamu saya, saboda Yayaah Kamal ne yace mu rubuta zaizo ya kaimu da yammah.

Gaskiya Besty bazamu saka da Pad ba, na gayawa besty inata hararan ta, saboda naga dariya takeyi, kuma tayi niyyan sai ta rubuta, "toh ban dake Besty ae Yaya Kamal yasan dole mun fara period zuwa yanzu, mu da muke jin ƙanshin aure, ta faɗa tana ta dariyan neman magana".

"Nidai baki isa ba wallahi Besty, na saake gaya mata, idan kuma kin dage zan turawa Hammah Haidar cewa ni dake muna so yasaya mana brezia saboda zamu koma school, kuma kinsan gobe friday naji Goggo tace zai zo, ihuuu Besty ta saka tace "Besty na tuba wallahi baxan rubuta ba," ta faɗa tana ɓoye kanta akan kujera, dariya naketa mata don nasamu maganinta.

Kallo na tayi tace "Besty har zamu koma school Besty Babagana baizo ba?" ɗan turo baki na nayi nace " bai damu dani bane ae daya zo ya faɗi abinda ke ranshi, kinga nima hankalina zaifi kwanciya, gashi rannan Baban shi yazo, naso naji mai ya kawo shi amma Aunty nice tace bataji mai suke cewa ba", "kar ki damu Besty ina ga komai yazo ƙarshe ne dole ya zauna ya ƙarisa, kehh! Besty ban miki gulma ba, ta faɗa tana leƙa hantan kitchen domin ganin ko mama tana jin mu"

Yimun Besty na faɗa ina kallon ta, Hmmm "Besty kinji ashe da gaske Fauzy son Yayah Kamal takeyi? Hmm jiya Babanta yazo ya samu Daddy wai yana so idan anyi auren su Adda, ayi na Yayah da Fauzy, domin ya tambayeta tace Yaya takeso, amma Besty kinsan wani abu?" ta faɗa tana kallona, jijjiga mata kai nayi alama ban sani ba.

Toh da aka gayawa Yayah Kaamal sai cewa yayi shi yana da wacce ya keso, amma Daddy yace bazai iya cewa ɗan'uwan shi a'a ba, saboda haka ya haɗa duka ya aura, Besty wallahi tun jiya Yayah yake ta ɗaure fuska".

Shiru nayi ina kallon Besty, chan nace "nikan Besty banga laifin Fauzy ba, gata da kyau da son mutane! Na faɗa ina kallon Besty".

Hmmm wallahi kam Besty, muma haka muka faɗa muda su Adda umaimah, don har su Adda

muka ƙira muka basu labari, kowa yaji daɗin hakan, don wallahi yaran suna da kirki, amma mummy cewa tayi abar shi ya zaɓa, idan Fauzy ce fine, idan kuma akwai wacce ya keso abar shi."

Uhmmm Besty hiranmu bazai ƙareba, tashi muje mu same shi, gara muyi mugama, shi kuma Allh ya zaɓa mishi wacce tafi  zama alkhairi.

A palo muka samu Mummy da Yayah Kamal, a zaune suna ta hira, har ƙasa na durƙusa na gaisheta, da murmushi ɗauke a fuskanta ta amsa tana zolayan mu, student za'a koma cin gari, ta faɗa tana dariyan mu.

Gefen Yayah Kamal na dawo ina gaishe shi, amsawa yayi kaman baya son gaisuwan, a hankali na koma gefen Besty na zauna, Besty ce "Yayah mun gama tana miƙa mishi paper".

Tashi kawai yayi batare daya karɓa ba, yacewa mummy sai mun dawo, muma bayan shi mukabi muna ma Mummy sallama.

Kasuwan wunti muka je, acan mukayi ta shiga shago muna saƴayyah, a wani shagon provision Yayah ya bamu mamaki don karɓan list ɗin yayi duk abinda muka rubuta saida ya ƙara mana, can mukaji ya cewa mai shagon ya miƙo mishi Pad guda Shida, kallon juna mukayi, muna zarewa juna ido, " wallahi dabadan tare muka shiga gidan ba, kuma banga Yayah ya kula Besty ba, toh da zance ita ta faɗa.

Daga wurin wajen shoes mukaje ya saya mana sandal, sannan muka shiga wani shago, muna zama yace wa mai shagon "kabawa yaran nan innerwears size ɗinsu, kowa set shidah, sannan ya tashi ya ɗauko wasu Towel Irin manyan nan guda biyu ɗaya pink ɗaya yellow, sannan ya ɗauko wasu rigunan bacci guda bibbiyu, mudai pant da bra mai shagon ya miƙo mana, da sauri na turawa Besty ina mat alman ita ta ɗauka mana, tashi yayi ya fita ya bar mu.

Tunda muka dawo, muka zubewa Mummy Kayan namu a palo, sai albarka ta ke ta saka mishi, shidai baice komai ba sai daddan na wayan shi yakeyi.

Ranan Saturday da dare muna zaune a palo, nida Ummi da Hammah Sadiq, muna kallo mukaji sallaman Hammah Haidar, ɗagowa nayi da sauri na kalleshi, lokacin yana neman wurin zama, bayan ya gaida Ummi ne, sai Hammah Sadiq ma ya gaishe shi.

Gaishe shi nayi, bayan ya aaamsa na tashi na kawo mishi zubo da cincin ɗinmu da Ummi ta mana naa makaranta, hira sukeyi shidah Ummi inda ta ke tambayan shi  jikin Bappah, " da sauƙi Ummi kinsan jikin girma, ɗazu munje nida  Abbah na, munje mun duba jikin, amma da saauƙi," " toh Allah ya bashi lafiya cewar Ummi".

Zuwa wani lokaci, Hammah yaayi sallama wa Ummi sannaan yaace a gaida Abba idan ya dawo, duk da ya barshi a kafin madaki, akan shi sai gobe ya dawo, hanyan waje yayi, yana cemun ke Riyyah zo mana, sannan ya sa kai ya fita, nima tashi nayi na bi bayan shi.

Hammah Sadiq ne ya dawo kusa da Ummi ya zauna yace "Ummi nikan maganin farin jini kika bawa ɗiyar taki, ni baki ban ba?" ranƙwashi Ummi ta kai mishi tace "nikan kakarka ce? Ta faɗa tana dariyanshi" shima dariyan yayi yace" toh Ummi baki lura da kowa yazo gidannan sai ya ƙira ɗiyarki ba, yanzu ga Hammah Haidar, last week haka Yaya Kamaal yazo ya ɗauke ta, yayi mata shooping kaman wata Quean, ga wananɓɗan gidan Auntyn da yazo yayi miki gyaran gidannan, ga ƙanin shi, ni Abubakar Sadiq yayaah zamuyi?" ya faɗa yana dariyan Ummi data ƙura mishi ido tana kallon yadda yake zaro ido kaman tsuhuwa ta so tsegumi, Ummi ce tace mishi " ce maka akayi duk sonta sukeyi? Kacika mita Sadiq, ta faɗa tana dariya,".

Jikin motan Hammah Haidar naje na tsaya, shikuma yana cikin motan, tambaya na yayi " gobe zaku koma school ko?" ehh insha Allahu na amsa mishi, sannan ya cigaba da cewa Riyyah ku dage kuyi karatu bana son shiririta, ina so naga reault ɗinku yayi kyau, saboda na sama muku school of nursing, kinga kuma sai kun maida hankali wurin karatu, ina fata dai baku kula samari?"  da sauri na amsa mishi da ehh Hammah bamu kula ƙowa wallahi, sannan yace naje na Ƙira Besty su gaisa, ae kaman jira nakeyi na tafi da sauri zuwa gidan su.

Rungumeta nayi, bayan na gaida Mummy nabita har kitchen nace "Besty kizo ku gaisa da Hammah Haaidar yace na ƙira ki ku gaisa, da sauri ta riƙe hannu na tace " Wayyo Besty tsoro nakeji," nace toh yi zamanki kada kije, ni kinga tafiya ta na faɗa ina juyawa, da sauri ta riƙoni tace bari na sa powder da ɗan turare.

A jikin motan muka tsaya nace "Hammah ga Bestyn" Juyowa yayi yace ta buɗe gaban motan ta shigo, ni kuma yace na buɗe bayan motan na ɗauka mana shooping ɗin daya mana na school ɓa shiga da shi gida.

Da sauri na buɗe bayan naga wasu kwalaye guda uku, na ɗauki ɗaya nakai, kafin na dawo na ɗauki sauran.

Besty ce zaune gaban motan ta kasa cewa uffan, Shima sai daddana wayanshi yakeyii bai kulata ba,  ina shiga palon na ajiye kwalin na riƙe haɓa nace "Ummi ba mita ba, ba tsegumi ba, kinsan Hammah Haidar son Besty ya keyi na faɗa ina dariya" itama ɗauke da murna tace kai haba? amma ko da abu yayi kyau, sannan nace " bari na kwaso kayan na zo, fita nayi na jido sauran kwalayen, a na ƙarshen ne, na matso kusa da Hammah nace, Hammah mungode Allah ya ƙara buɗi, ɗaga mun hannu kawai yayi yace a maidah hankali dai a karatu, nace toh mungode, sannan nayi cikin gida.

Ke baki iya gaisuwa bako? Hammah ya tafi Besty, sai lokacin ta tuna bata gaishe shi ba, ita dai mutumin nan kwarjni yake mata, kayi haƙuri ta furta, sannan ta gaida shi, ƙin amsawa yayi, har saida tace Hamma kayi haƙuri tsoro nakeji ni, na manta ban gaishe kaba.

Kallonta yayi, wanda itama ta juyo ta kalleshi, gaba ɗaya ji tayi kaman zata sume a zaune, wai ita me takeji ne akan wannan mutumin? Ko dai kyaun shi ne yaayi mata yawa? da sauri ta sun kuyar da kanta ƙasa, Murmushi yayi mai sauti sannan yace "Nida nakeso muzama kawaye kuma kike jin tsoro na? Ɗagowa tayi tana kallonshi, shima kallonta yayi ya kashe mata ido ɗaya, da sauri ta sunkuyar da kanta tana murmushi.

Nafisat ya ƙirata, ɗagiwa tayi tana kallon shi, shima ita yake kallo, sannan yace " nasan duk da ƙarancin shekaranku ki kin fahimci dalilin ƙiranki danayi ko? Sannan ya cigaba, Nafisa tun raanan dana ganki naji kin kwanta mun a raina, kuma har jiya na faɗawa parent dina, akan su nema mun izinin zuwa wajenki, shine naga ya kamata kafin suzo ki sani, domin kada kiji abin wani iri, sannan kuma na tabbatar kina ra'ayina," shiru yayi na zuwa wani lokaci sannan ya cigaba " yayah kin amince nabturo su ko akwai wanda kikayi wa alkawari?"

Da ƙyar naji bakina ya buɗu sanann nace "nikan banyi alkawari da kowa ba, amma kuma Hammah ae ni yarinya ce, ba ayi auren su Adda bama, kada ace ni tun ina tarinya za'amun aure.

Kallon ta yayi yace" ni ba aure nace miki ba, ae dai yafi mutunci iyayenki su san dani akann suga ina zuwa qurin ƴar su ko?" ya faɗa ya na karya mun wuya, " ehh nagane nace mishi, snnan nace toh ae Hammah Walid yace kada yagan mu da kowa sai mun gama school,".

Dariya yayi yace toh naji ahima zan nemi izini a Wurin Shi kenan?, amm Nafisah! yacigaba ɗa maganan shi, ina fata dai kin bani izini ko?

Sun kuyar da kaina nayi kan cinya na, sannan nace mishi ehh.

Toh naji na gode my dear, amma akwai wani abu, idan har kin amince dani toh ki saka a ranki babu kula wani, don ni ina da kishi, sannan kuma kada kiga Riyyah Friend ɗinki ce, idan nayi hira dake ki bata labari, toh bana so, don kinga ƙanwata ce ke kuma kinzam Addan ta ko? Kuma babu daɗi ki faɗi siirin mijin ki ƙo?.

Ɗaga kanta tayi alaman ta amince, saaannan sukayi sallama ya ƙara bata shwara akan karatunta, gidan mu ta shigo, da sauri na tashi na rungumeta ina besty kayan mu har sun mana yawa.

Buɗewa mukayi muna ta farin ciki, sannan Hammah Sadiq yace mana wallahi sai kun ɗiba mun wani abu kafin ku tafi, Ummi ce ta kalle shi tace Babba na ƙotalo kadaiji kunya, dariya muka mishi nace Hammah zo mu raka Besty dare yayi kuma ina tsoron hanya ni kaɗai.

Tashi yayi yace muje kubani labarin samarin naku a hanya, Ummi ce tace kadai ji kunya wallahi, tafaɗa tana mishi dariya haka muka fita zuwa raka Besty gida.

*KU KASANCE DA ALKALAMIN AUNTY NICE* 😘
*BADARIYA*

✍️®
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION* ✍🏻
{Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin riban duniya da kuma lahira.}

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN ƘARFE* 🏇

Story and written
By
*AUNTY NICE* 😘

*WANNAN LITTAFI GABA ƊAYAN SHI SADAUKARWA NE GAREKI MISS ZERKS, ALHERI

ALLAH YA KAI MIKI*

{ *MUM SAYYEED WANNAN SHAFIN NAKINE, AUNTY NICE NAJIN DAƊIN YABAWAN KI, ALLAH YA BAR ƘAUNA*}

*PAGE*1️⃣5️⃣

Da safe Yaya Kamal ya tafi Abuja,mu kuma bamu tafi ba sai da yamma, Mummy ce da Adda Umaimah suka mai da mu.

A kwana a tashi babu wuya a wurin ubangiji, yau saura kwana uku mu fara weac, gaba ɗaya hankalinmu ba a kwance yake ba, hatta Trouble da bata da burin cigaba da karatu, itama ta dage, duk da a lokacin har ankawo sadakinta, muna gamawa za'ayi aurenta.

Yauce ranan da zamuyi final paper mu na NECO domin tunin mun gama WEAC, ranan murna kaman zai mana yaya,bayan munfito daga Hall ne muka ɗunguma Hostel.

Allah sarki sabo turken wawa, wato wasu an rabu dasu kenan har abada, wata kuma baka san ta ina zaku haɗu ba?, abin tausayi dayawa sai kuka akeyi.

Akwai wasu suna SS 2 class, ana ƙiransu,
Umma Saleh Jos
Lami Garba (Pulako)
Azumi Tanko Bauchi
Tine Turaki,
Ranan nayi kukan rabuwa dasu, wanda har gobe idan na tuna su nakanji wani iri, gara Tine Turaki ina haɗuwa dasu, amma saauran har yau, duk inda suke ina musu fatan alkhairi.

Driver ne yazo ɗaukan mu, ido na yadawo kaman jan gauta haka muka shiga motan muna jin wani iri a ran mu.

Muna tsayawa na wuce gidan mu, Ummi ce ta tsaya kallona wani iri, can tace "Ke kuma me ya faru naga idonki wani iri?, bakida lafiyane?".

Hawaye naji ya zubo mun, sannn na ƙarasa kusa da ita nace" Ummi na mundawo".  Idona yana kan zubar da hawayen,tsaki tayi tace "amma kinji haushi wallahi, keda zakiyi murna kingama lafiya, sannan kiyi fatan sakamako mai kyau, amma sai kina kuka".

"Ummi wasu ƙawayenmu fa an rabu kenan har abada".shine kawai nake kuka sabon da akayi.

 Abba ne ya fito daga ɗakin shi yace "Fatima an dawo lafiya?". Sannan ya dubi Ummi yace "haba ae sabo ake kokawa ba mutuwa ba, yanzu rayuwa da sukayi ɗaki ɗaya, wurin karatu tare, wurin cin abinci tare, lokaci ɗaya a rabu ae ko zaka koka mana".

Haka dai Abbah nah yayi ta rarrashi na, har na shiga nayi wanka, nazo na sake gaishe su, kallon Ummi nayi nace "Ummi ina Hammah Sadiq?".

 "Yana school, tun last week ya tafi shida Bappah". cigaba da hiranmu mukayi.

Satin mu ɗaya da dawowa aka saka date ɗin auren su Adda, nan da sati shidda, a nan muka samu labarin Hammah Haidar ya turo an nema mishi izinin zuwa wurin Besty.

A ɗayan gefen ma, Daddy ya nemawa YayaKamal auren Fauzy kuma an bashi, Mummy babu yaddah ta iya, haka tayi ta lallaɓin Yayah,  ƙaarshe yace mataa shi ni yakeso, hankalin ta ya tashi, domin tasan Baba ya nema wa Babagana aure nah a wurin Bappah daga can kafi, kuma ance mishi an bashi.

Da wannan dalilin ta kwantar wa Yayah Kamal da hankali, sannaan ta nuna mishi babu komai ya nemi Fauzyn ita ma ba laifi, gashi ta samu tarbiya, a haka rai babu daɗi ya koma Abuja ba tare da yaje inda Fauzyn ta ke ba.

Da dare muna palon Abba muna cin abinci muna kallo, daga ni sai Ummi nah da Abba nah.

Hammah Haidar ya shigo bakin shi ɗauke da sallama, bayan sun gaisaa ne, Ummi tace na kawo mishi abinci, da sauri yace "abarshi kawai ya ƙoshi".

Bayan mungama cin abincin ne, yace na zo mu fita zuwa gidan su Besty, babu wanda yace mana komai, muka fita zuwa gidan.

Besty ne ta shigo gidan mu bayan tafiyan Hammah, ɗaki taja ni muka yi ɗaki, wani shegen waya ta fito mun nagani a cikin kwalin shi, dukkan mu murna mukeyi.

sannan tace "Besty nazo mu biyu ya kawo mana, amma sai ce mun yayi kema saurayin ki zai saya miki". ta faɗa tana dariya nima dariyan nayi, sannan nace.

"Bestýni yaya zanyi ranan da Besty ya fara zuwa hira?".

"Ɗamewa zakiyi yaddah nima na ɗame, gashi Dr na yace next week su Hammah Walid zasuyi passing out, kuma inaga tare ne da Besty."

Kallonta nayi nace "Besty Yaya kikeyi a gaban Hamma"?.

Dariya tayi tace "lallai ma yarinyar nan baki da kunya, yayan naki kike so kiji sirrinshi? Toh ki bari idan na nemi permission a wurinki sai na dinga gaya miki, amma yanzu kam ae da sauranki yarinya". ta faɗa tana dariya.

Tunda muka samu wayan Besty muka haukace mishi, wataran wuni guda zaiyi a wurina ina charting da ƙawayenmu, har sai Hammah ya kira wataran nake tafiya da sauri nakai mata.

Kaman yau ina kwance a palon Ummi nah ina ta karanta wani book na wata jaruma *NABILAH RABI'U ZANGO* wato *BANI BANE* inajin daɗin book ɗin, don duk hiran da Ummi takeyi da baƙon da tayi a tsakar gida bana jinsu.

Kawai sallama naji an shigo palon, kuma muryan da ko a mafarkine zan shaidah shi, da sauri na tashi zaune, gashi kaina babu ɗan kwali, duk gashina ya kwanta a gadon bayana, kallona yakeyi kaman bai taɓa ganin halittan ɗan Adam ba, gaishe shi nakeyi, amma bai amsa ba kawai samun wuri yayi ya zauna, har zuwa lokacin bai daina kallo na ba, duk sai naji na tsargu.

Miƙo hannun shi yayi da nufin na bashi wayan, da saauri na miƙa mishi, yana duba wayan yace.

"waya saya miki?" .

"bana wa bane". na bashi amsa.

sannan na cigaba da kallon shi, ina mamakin zuwan shi gidan mu, kuma har palon Ummi nah.

Kaman daga sama naji ya sake jeho mun tambaya "wayan saurayin ki ne, ko nawa"?.

Kaman na fellah da gudu na keji, amma haka na daure na bashi amsa da cewa "Wayan Besty

ne".

"waya saya mata"?.

Sake jero mun tambayan yana kallona, a ɗan tsorace nace "Hammah Haidar ne, ba kowa bane". ya takura ni sai Hammah Umar, wanda nayi mamakin ganin shi.

Shi zai aure ta ko? ya sake jeho mun tambayan, " ehh"kawai na iya ce mishi nayi shiru.

Dai-dai lokacin Ummi ta shigo, tana mun faɗan ko ruwa bazan bashi bane?

Tashi nayi na wuce jikin friedge ɗin Ummi na buɗe,na ɗauko zoɓo a gora da yake Ummi bata yadda ta zauna babu zoɓo ba, na haɗa da ruwa na kawo mishi, sannan na miƙe nayi cikin ɗakin Ummi.

Inajin su, suna ta hira kaman su daɗe da sanin juna, can naji yace "Walid wannan satin zasu dawo ae, don munyi waya da shi jiya," haka akayi inji Ummi, sannan yace mata zai koma gida, don gobe zai wuce Abujan, dama yazo duba jikin kakanshine, a jama'are, daga nan ya miƙe yana cewa Ummi ina Fatiman take ne?ɗaga labulen ɗakin Ummi tayi tace na fito Hamman mu zai tafi.

Hijab nasaka akan dogon rigan material ɗin da ke jikina, kama labulen nayi ina kallonshi, batare daya kalleni ba yace fito ki rakani, ba musu na fito na sanarwa Ummi, sannan muka wuce wurin motan shi.

Dai-dai shagon Abbakar Waziri muka tsaya, anan ya fita ya barni cikin motan, bayan wani lokaci ya dawo hannun shi ɗauke da leda, ya buɗe motan ya shiga, muka kama hanyar gida.

A ƙofar gidan mu, muka tsaya, nasaka hannu zan buɗe naji shi a rufe, juyowa nayi ina kallonshi, shima kallo na yakeyi, dole na sunkuyar da kaina ƙasa, ɗora mun ledan yayi akan cinya na, sannan ya ɗora mun wayan Besty ma, bece komai ba ya buɗe mun ƙofan.

Gaba ɗaya naji na kasa fita a motan, sai zuwa wani lokaci naji yace "ko na tafi da kene?".

Da sauri na buɗe motan saannn na juyo wurin shi nace "nagode Hammah, Allah ya ƙara buɗi".

sannan na fita nayi cikin gidan mu.

Har na shiga yana zaune bai tafi ba, wanda bansn meyake jira ba, har zuwa wani lokaci tukun naga ya tafi, ina shiga na faɗa jikin Ummi na ina murna, nace "Ummi nah kiga Hammah ya saya mun handset"  ita ma tana murna tace kai Hamman nan akwai kirki wallahi, shi baya gajjiya hidima dai, shikenan wayar Nafisatu ya huta.

Da sauri nayi  gidan su Besty na kai mata wayan tagani, dukkan mu murna mukeyi, Mummy ce tace "wato Umar ya fanshi Ƙaninshi ko?" ta faɗa tana dariyan murna, muma dariyan mukayi.

Ranan da Besty ya dawo, sukayi babu daɗi tsakanin shi da Mama don tace mishi idan har baibi umurninta ya haƙura dani ba toh zata yafe shi a cikin yƴaƴanta, duk da Baba da iyayenta sun tsayar mata amma bata haƙuara ba, shidai Babagana rantsuwa yayi akan yana sona ,haka ya fita a side ɗin ran su duka a ɓace.

Zuwa dare kuwa yazo gidan mu, inda suka haɗu da Abba na a waje, don tare suka shigo gidan, palo Abba yakai shi, sannan ya shigo yace " na shiryah naje Babagana yana palon shi".

A kunyace na shigo palon, duk wani sabon mu dashi yau sai naji babu, tsabar kunyan shi kawai nakeji, a haka nazo na zauna a kunyace.

Beauty nah, naji ya kirani da shi, sannan ya gyara zaman shi ya ɗan fito wajen kujeran yana duba nah, Beauty nah!  kinji yadda Ƙawancen mu ya rikiɗe ya koma soyayyah mai zafi ko?".

"Wallahi Besty tin ranan dana fara ganinki nace Allah ya kawo mun irin matan danake, fatan samu, amma sai na bawa kaina haƙuri nace bari na barki ki ƙara girma, kinga cikin hukunci Allah kuma zaki zama rabo nah".

Ɓoye kaina nayi a cinya nah ina mai jin daɗi a raina , yau gani ga Babagana a matsayin masoya kuma yana mun hiran soyayyah,.

Wayan hannu nah da nake wasa dashi ya kallah, sannan ya buɗe baki yace .

"kai! kai! kai!, Wannan wayan fah Beauty?".

Ina ɗan murmushi na kalle shi nace "Hammah Umar neya saya mun". shima fuskan shi ɗauke da murmushi Yace gaskiya Hammah Umar masoyinane , wato har abinda nakeso shima yana so? Allah ya bar mun Hammah na, don shi kaɗai nakeji ko bayan raina zai kula mun da Family nah.

Kallon shi nayi nace "Amin, kaima ae kanaa sonshi, shiyasa shima yake ji da kai, gashi nima har ya shafeni.

Kallo na ya keyi kaman bai sanni ba, can sai yace

" Beauty ina fata kin aminci da Beatyn ko?".

sunkuyar da kaina nayi ina murmushi mai ɗauke da kunya , na kasa cemishi koma, sai wasa da wayana da nakeyi.

Hannu yasa ya karɓi wayan, sannan yasaka mun number shi, yayi saving da HUSBY, yayi flashing nashi wayan, bayan yayi ɗan dube duben shi ya miƙo mun yana ɗan smilling.

*KUKASANCE DA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*

🖋®
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION*✍🏻
{Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin riban duniya da kuma lahira.}

🎐G•W•A🎐

*GASKIYA DOKIN ƘARFE*🏇

Story and written
By
*AUNTY NICE*😘

*WANNAN LITTAFI GABA ƊAYAN SHI SADAUKARWA NE GAREKI, MISS XERKS*

{ *WANNAN SHAFIN KYAUTACE GAREKU IYAYEN GIDA NA,UMMU HANASH ( ƳAR ƘAUYE), DA UMMU NABIL, ALLAH YA BIYAKU DA ƘOƘARIN DA KUKEYI A KAINA, NAGODE MUKU SOSAI*

*PAGE* 16

Mun daɗe a haka kaman bazai sake magana ba, chan kuma sai naji yace "Beauty! Gobe in Allah ya kaimu zanje Lagos, akwai wani interview da zanyi, don Allah kimawa mijinki Addu'a".

Ido na yana kanshi nace ,"insha Allahu zanyi, amma yaushe zaka dawo"?

Uhmmm kawai kimun addu'a, inaga zanyi sati ɗaya,.

Zuwa wani lokaci na raka shi har jikin motan shi, bayan yayi sallama wa Abba nah da Ummi nah, a jikin motan yake nuna mun motan da Baban shi ya canja mishi, bayan ya dawo, murna na mishi sannan mukayi sallama.

Tunda Besty na ya mun waya ya isa lafiya, bamu saake waya ba sai bayan sallan ishaa, inda yake sanar mun da gobe ƙarfe tara zasuyi.

Addu'a na mishi alƙawarin daren yau zan tashi nayi, yana wata irin dariyan daban gane kanta ba, yace "Beauty kinsan dariyan me nakeyi kuwa yanzu"?

Girgiza kaina nayi kaman yana ganina, sannan nace"sai ka faɗa my besty!"

Ɗan dariya yayi mai sauti sannan yace "ɗazu a airpot muka haɗu da Yusuf aminin Hammah

Umar, shida matar shi, kinsan me yace"?

batare dana ce komai ba ya cigaba da dariyan shi yana mun bayani "tambayan farko ke yafara tambaya na, nace mishi ae an bani ke".

shine fah ya riƙe bakinshi yana mamaki, wai amma ya mun murna don samun first class mata irin ki sai antona, ga hipps ga komai, amma shi ya kwaso wata kamar walƙiya, bayan saida Hammah yagaya mishi qualities ɗin macan gaske, amma yayi taurin kai.

Kinsan abin dariyan? Nima dariyan nakeyi tun banji mai zaice ba, yana dariya yace "Beauty duk maganan da mukeyi fah matar tana gefen mu kaɗan, sai wani rausay takeyi kamar wata catoon".

Gaba ɗaya dariya muka kama yi da Besty, sannan nace "Besty baka tsoron nima rana ɗaya kawai na rame, na dawo kaman ita? na faɗa ina mishi dariyan ihun da yayi da ƙarfi".

Yana dariya yace "amma zan baki horo saboda tunanin da kikayi, wato fata ki keyi na shiga gararin damuwa ko? To ƙwalelenki, nan gani na bari, hakanan zakiga Beauty na ƴar duma-duma, ya faɗa yana mun dariya".

Besty yana son tsokana a rayuwar shi, ga baya fushi, sai dariya yake ta saka ni, har saida naji na sake da shi, sannan yace Beauty Hammah mabtausayin shi nakeyi, saboda idan kinga sirangalin Zainab kaman na catoon, gashi yana bala'in son mace ƴar duma-duma.

***************

Ranan da Besty zai dawo, yasaka ni dole naje gidan su wirin Auntyƴ, wai dole sai ni zan mishi abincin taryan shi, babu ƴadda na iya tun safe nayiwa Ummi sallama, akan zanje gidan Aunty kuma sai gobe na dawo.

Ina zuwa mukayi karo da ɗan mujaheed ɗina zasu tafi sch, don sammako nayi zuwa gidan, dav sauri yakama hannu na, yana tambayana " Adda Riyyah anan zaki kwana?".
Amsa mishi nayi da ehh, sannan ya fita yana ta murna, shi kuma, Khalifah murmushi kawai yakeyi yana kallona, har yaje bakin ƙofa tukun yace "Adda ayiwa Hamma Babagana delicious, idan mun dawo zamu lasa, ya fita yana ɗan murmushi.

Kama baki nayi ina mamakin yaya akayi yasan me yakawo ni? Saijin muryan ɗan rikicin nan

nayi yana cewa" amaryan Hammah yayah zamu dawo mu sameki ne?".

Hararan shi nayi na wuce ɗakin Aunty ban kula shi ba, ganin tana bacci yasa na fito na barta, don nasan halan tana off ne, ko kuma dutyn yammaj take da shi.

Kitchen na wuce, na duba komai naga akwai abin da nakeso, ban ɓata lokaciba na fara shirya abinda nakeso, don nasan bazai wuce 11:am ba zai iso, don a Abuja wurin Hammah ya kwana, kuma jirgin safe ƴa kawo shi kano.

Ƙamshin girke-girke dana keyi ni ya shigo da Baba, don a side ɗin yake, yayi tunanin Aunty ce ke haɗa mishi gara, Aunty ma abinda ya fito da ita kenan.

A palo suka haɗu da Baba, inɗa yake tambayanta "dama Fatima bake baceva kitchen ɗin"?

Itama cikin mamaki tace "nima ƙamahi ne ya fito dani", a lokacin na fito don jin muryansu, har ƙasa na sunkuya ina gaiahe su.

Baba ne yace " ashe chief coke ce tazo take haɗa mana danasha, ya faɗa yana kallon Aunty".

Ake haɗawa ɗanka dai, inji Aunty ta faɗa tana dariyan Baba da yake zare ido yana dubanta, kai tsaye kitchen ɗin ya biyo ta yana faɗin " amma dai Fatima nima za'a sammun, albarkacin ɗan nawa ko?"

Ya faɗa suna buɗe abin dana shiryah shida Aunty, "dolen suma inji Aunty, tunda suka zo gidanka suka mana fin ƙarfi ae dole mu ɗan taɓa muji," ta faɗa tana dariya.

Nidai banda kunyan Baba babu abinda nakeyi.

Bayan Besty na ya iso ne, na fito mishi da komai kan dinning, Aunty da Baba kuma sun koma side ɗinshi sun barni.

Besty sai santi yake zubawa, ni kuma nayi kwalliya kaman zanje gidan biki, sai dariya nake ta yi mishi, yana cin abincin yana ta ƙarawa, nidai sai dariyan shi kawai nakeyi, narasa wani irin so nake mishi, wanda komai yayi burgeni ya keyi.

Muna hiran mu yana cin abincinshi hankali kwance, sai ya dube ni yace "Beauty yanzu fa watarana a gidanmu, da yaranmu, zakina mana girki mai daɗi muna ci tare ko?" bai gama rufe bakin shiba kawai mukaji muryan Mama akan mu, tana cewa "Ƙarya kakeyi Baba na, badai wannan baƙar yarinya mai baƙin aniyan bace zata haifah maka ƴaran, har kayi tunanin cin abinci da ita, insha Allahu kaida auren wannan  baƙar jarabar saidai bayan raina, amma dana bari jinin Fatima ya haɗu danawa wallahi gwara naga gawanka a gabana, ta faɗa tana ƙara sowa inda muke.

Da sauri dukkan mu muka miƙe tsaye, Babagana yana kallonta yace "Haba Mama? Me Aunty da zuriyanta suka miki ne? Shin kintaɓa zama na rana ɗaya kika fahimci Aunty kuwa? Wallahi mace ce mai kirki, idan kin kwantar da hankalinki wallahi zaku zauna lafiya, don nasan Aunty̌ bata da problem ɗin komai".

Ya faɗa idon shi na cikowa da hawaye, sannan yace "Mama idan baki bar furucin sai bayan ranki ba, ko kuma kiga gawata ba, toh nidai bana fatan saboda aure na kibar duniya ba, amma ina tsoron miki kiga gawata a gabanki, Mama ranan zakiyi kukan da babu mai iya rarrashinki".

Sannan ya ƙara matsawa kusa da ita idon shi na zubar da hawaye yace "Duk duniya babu abinda nakeso sama da ke Mama na, baza kuma kisani cewa duk yaranki babu mai sonki ba iri na, sai ranan da akace miki babu ni a rayuwanki.

Ya juya ya kalle Baba da Aunty da tunda aka fara hayaniyan suka fito da sauri, sannan ya juya ya kalli yadda nake kuka, ya kaɗa Kanshi ya fita a palon.

Amma duk da haka Mama saida ta juta ta kalleni a wulaƙance tace "Allah kaɗai yasan irin sheggen suddabarun da kukayiwa ɗana, keda talakawan iyayen ki kwaɗayayyu, tsawa Baba ya daka mata, sannan ya nuna mata hanyan waje, yace " Fita kibani wuri babbar banza kawai, banda hauka mutunci bai taɓa shigo dake side ɗin ƙanwar kiba, sai tashi hankali? Shima akan wacce ɗan ki zai aura? Wallahi Zahra ina mai tabbatar miki zakiji kunya nan bada daɗewa ba.

Sannan ya juya yayi ɗakinshi, ita kuma ta harare mu tayi tsaki ta fita, Aunty ce tazo ta kama hannu na muka wuce ɗakinta, rarrashi na tayi-tayi tana bani baki, sannan ta roƙeni daka da na faɗawa kowa agidanmu.

Amsa mata nayi da kai, sanann na kwanta a gadon ta nayi shiru ina ajiyan zuciya, Aunty tace " auta dama kindai na kuka, gara ma kisaba da halinta, tunda ɗanta zaki aura, dama abinda muka guje miki kenan tun farko, amma Umma tace a barki da zaɓinki.

Bayan sallan ishaa, lokacin Baba ya koma side ɗin Mama, muna zaune a palo saiga Besty ya shigo cikin wasu ƙananun kaya, masu masifan kyau, three quater ce ash, da kuma armless red colour, kai gaskiya Besty b ƙaramin kyaukkyawa bane.

Gefen Khalifah yaje ya zauna yana gaishe da Aunty, cikin fara'a taa amsa mishi kaman babu abinda ya faru, sannan dukkanmu muka gaiahe shi, kallona yayi, yace "Aunty meyasa kija bar mun Beauty na tayi kuka? Har idon ta sukayi jaa, ya faɗa yana dariya, kaman bashi bane ɗazu yake zibar da hawaye kaman ba namiji ba.

Ɗagowa da kanta  Aunty tayi tana murmushi, idonbta akaina tace "Raguwa ce ae Babagana, in

bahaka ba ,meye dan matar dazata zama surkuwarki ta miki faɗa zakiyi kuka?  ae koyon haƙuri kawai yakamata tayi, har zuwa lokacin da Mama zata fahimci komai".

Kallon Aunty yayi kaman zaiyi kuka sannan yace "Aunty kinaga Mama akwai lokacin da zata fahimci gaskiya? Har itama ta tayani son abinda nake so?".

Ƙwarai makuwa, "Aunty tacigaba da mishi bayani, "ae Babagana duk ranan da kukayi aure, har Allah ya kawo rabo, toh mama zata haƙura itama ta tayaka son iyalinka, ae babu abinda yake tabbata sai ikon Allah, kawai ku ƙara Addu'a, insha Allahu zaku ga haske."

Kallona yayi ya kashe mun ido ɗaya, nidai ƙara sunkuyar da kaina nayi bance mishi komai ba.

Aunty ce ta tashi tayi hanyar ɗakinta, alama tabarmu ne mu sake, shima tashi yayi yace "zo muje kan dinning kada Gidaɗo ya dinga jin hiran Auntyn shi, ya faɗa yana wucewa wajen dinning ɗin.

Gidaɗo ne yana murmushi yacewa Hamman shi "tadai ci darajan kane kawai hammah, amma ae ƙanwata ce, sannan yabini da harara yana cewa, ke tashi mana bana son yanga, kibi shi kada ki shanya mana Yayah, Hararanshi nayi na tashi, Khalifah sai murmushi kawai yake  yi.

Hira mukayi har wajen 11:00 sannan ya wuce side ɗinsu.

Soyayyah tsakanin Hammaj Haidar da Besty har mamaki yake bani, don ko gidanmu sai da ta rage shigowa, wai kunya, dukbda Ummi tana cemata su iyayenta nr ba surukai ba, amma fir taƙi.

Abin mamakin ma ƴadda yake nuna mata love, don duk after two weeks sai yazo bauchi, gashi ko yayah zanyi bazata taɓa cemun ga hiran da sukayi ba, wai ita Aunty nace kada naji sirrinsu.

Soyayyar Besty na aƙwai shiga rai, don irin maza masu nacin soyayyah ne, kullum sai ƴazo gidan mu, kuma a rana ban san adadin wayan da mukeyi ba.

Har Ummi mita takeyi wai duk kuɗin shi a ƙiran wayan zai kare, amma mudai kaman zuga mu akeyi.

Wannan satin ne Yayah kamal zai zo. Kuma a lokacin su Adda Hafsat sukai ta zuga Mummy akan  sai yaje Alkaleri wurin Fauzy.

Bayan sallan ishaa ne Besty yazo, kuma a ranan Ummi tace ya shiga ya gaida Mumy don kullum sai tayi mitan baya shigowa a haɗa zumunci, don ae ni Ƴar gidan tace dama.

Haka na raka Besty gidan, ya tsaya a waje kafin na sanarwa Mummy ya zo, faɗa Mummy ta fara mun akan miyasa na barshi a waje maza na tashi nace ya shigo.

Besty ce ta wuce da sauri tayi waje, tare suka shigo ita da Besty, bayan sun gaisa ne,mummy take tambayanshi mutanen gida da kuma na maiduguri.

Cikin sakin jiki kaman ɗan gidan yake mata bayanin suna lafiya, nidai sai kunya nakeji amma shi kan ko ajikin shi, sai wani hiran su sukeyi shida Besty da  su Adda, kaman sun daɗe da sanin shi, gaban shi kuma cake ne da maltina wanda BestyƳ ta kawo mishi.

Ƴanaci ana hira kaman yana palon gidan su, nidai babu abinda nake iya cewa, Mummy abin nema ya samu sai labari kawai akeyi.

Saijin buɗe kofan kawai naji anyi ɗauke da sallama a hankali, gabana sai da naji ya faɗi, don jin Muryan Yaya Kamal, a hankali ya shigo, kai tsaye gefen Mummyn shi yaje ƴa zauna.

Hankalinta ne ya dawo kanshi, tana kallon shi da murmushi tace "My dear ga Babagana wanda zai auri sister ka Riyyah".

Juyiwa yayi ya dube ni fuskarshi kaman an mishi albishir da mutuwar sa tazo, gaba nane kawai naji ya sake faɗuwa , da suri na kalli Aunty Nice da take shirin guduwa a palon, Ina jin kaman nima na rufah mata baya, shiko Beaty sai kallon sa yakeyi fuskar shi ɗauke da murmushi.

Ko yayah za ayi irin wannan gaisuwan?  Bari mujira muga ikon Allah.

*KU KASANCE DA ALKALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*

®☄

*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION* ✍🏻
{Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar duniya da kuma lahira.}

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN KARFE* 🏇🏽

Story and written
By
*AUNTY NICE* 😘

~Wattpad@GaskiyaWritersAsso.~

*WANNAN LITTAFI SADAUKARWA NE, GA MISS XERKS.*

_Wannan shafi na baki shi kyauta *MAMAN ZAINAB* daga *XUMUNT@ NOVELL@* inajin daɗin comment ɗinki, nagode sosai😘._

*PAGE* 17

*__________📖* Shiru Yayah Kamal yayi yana duba wayanshi, kaman baiji mai Mummy tace ba.

Besty da fuskan shi ɗauke da murmushi,  ya dubi Kamal yace "Abokina barka da yau tare da miƙa mishi hannu, domin su gaisa".

Tashi Yayah Kamal yayi kaman bai ganshi ba, yayi hanyar kitchen, duk kanmu saida mukaji kaman mu nitse a ƙasa.

Abin mamaki sai Besty ya dubi Adda Umaimah, still fuskan shi ɗauke da murmushi, yace "Adda inaga wani a waje ya ɓatawa abokina raine, don muma muna da irin shi a gidanmu, ya faɗa yana dariya".

Mummy ce ta fara dariyan yaƙe tace, "shi ae haka yake, wai idan ranshi ya ɓaci sai yaƙi kula mu, yanzu hala shida wacce zai aura ce, haka yake duk ranan da ta ɓata mishi rai, sai ya ɗauka wa shi kaɗai mata sukeyi, gashi yana sonta kaman babu gobe", ta faɗa tana kallon hanyar kitchen ɗin tana dariya.

Gaba ɗayan mu, mun gane Mummy tayi haka ne don kada Besty ya ɗauka da wani abu.

Ko ya gane, ko bai gane ba, sai cewa yayi "Mummy ae haka babban yayanmu yake, idan wani ya ɓata mishi, toh duk gidan ya shafesu har abokanshi, ya faɗa yana dariya".

Dai-dai lokacin Yayah Kamal ya fito a kitchen, hannunshi riƙe da cup ɗin tea, bai kalli kowa ba yayi hanyar waje.

Babu wuya a wurin Allah, ya Mummy da Adda Hummairah suka dawo a Dubai wurin sayayyar kayan ɗakin su Adda Umaimah.

Bauchi suka taho, saboda haka ranan , Ammar kamar zamu lashe shi, daga na gudu da shi gidan mu, can zaka ga Besty taxo, hankalina na tafiya wani wuri zata ɗauke shi tayi gida.

Haka nima zan bita na mata masifah, sannan na ɗauko shi na dawo, Ummi sai masifah take mana, akaan muna wahaladda shi, ita kam Adda Hummy da Mummy ko su kula mu, sai aikin ware kayan sukeyi, wanda Aunty ma tun safe suka zo itada sister Mummy suke tayasu.

Lokacin bikin sauran 3weeks, Adda Hafsat da Adda Umaimah basu wani zama a gida kullum sai sun fita, wannan karon muma zamu haɗa musu ƙauyawa Day.

Ni FATIMA BADARIYYAH kullum mamakin soyayyar Besty da Hammah Haidar nakeyi, yau mabshi yazo ya kaimu gidan ƙawayen mu, da muke kai musu IV da kuma ashobi.

Har gidan Aisha Trouble ya kaaimu wacce take unguwar Railway bauchi, last month akayi bikin Trouble, wato muna gama school da 3weeks.

Ranan monday da muka shiga week ɗin bikin su Adda, Hammah ya kawo mana wasu arnakun material kowa ɗaɗɗaya da kuma lace wanda aka mana gown mai masifar kyau, gaba ɗaya ƙasan ƙace ɗinne aka saka a gaban rigan, sannan aka zuba mishi arnakun stones.

Gashi mummy ta mana ɗinkuna kaman babu gobe, shima ganin haka Hammah walid ya saya mana wasu takalma da jakansu kowan mu kala ɗaɗɗaya, akowanne yakai 15k, a wurin Mummy ya saya.

Week ɗin da za'a fara bikin kuma Besty ya samu appointment letter ɗinshi a inda yayi interview Wato FORTH AUTHORITY  branch ɗinsu dake lagos.

Saboda haka ranan saturday yazo ya mana sallama, duk sai naji babu daɗi, don za'ayi bikin baya nan, da zai tafi ya bani mint na 50K yace muyi haƙiri babu yawa, nabawa Besty 20K na ɗauki 30k na liƙi wa amare, kaman zanyi kuka na rakashi jikin motanshi ya tafi.

Haka aka fara hidiman biki, domin haddah na Haƙilan alkaleri za'ayi, saboda haka sai suka haɗa venue ɗinsu wuri ɗaya.

Ranan Wednesday  mukayi ƙauyawa day a hara ban gidan su Besty, kuma abin ya ƙayatar don har mai kiɗan ƙwaryah Aunty ladidi matar mayana Bauchi ta ɗauko mana daga Alkaleri, kunsan Aunty ladidi da sun hidimah gashi bikin ƴar gaaban goshinta wato Haƙilah, kuma dama su Familyn su, idan kagansu da cousins ɗinsu kaman ciki ɗaya suka fito.

Domin ita Aunty ladidin tayi insisting  a young duka  programs ɗin tare a Bauchin saboda zai fi musu sauƙi.

Ranan Thursday kuma akayi Dinner a zaranda, muna shiga Hall ɗin na riƙe hannun Besty nace, " Gaskiya Aunty ladidi tayi ƙoƙari, Besty kiga yadda wurin nan ya ƙayatu kaman ba bauchi ba?" Murmushi Besty tayi tana kaɗa kanta, bata sonyin magana saboda yadda Hammah Haidar yayi kane-kane, a gefenta.

sit wuri ɗaya Hammah yakaita suka zauna, nida Fauzy sai gulmansu muke tayi, sannan na riƙo hannun Fauzy nace "gara su, zo muje mu samawa friends ɗinmu wurin zamaa, gacan Trouble dasu indo umar.

Sit na nunawa su trouble  suka zauna, tana ta mana iya shege, wai "yara kuna su ku falle ku iso mu ko?hmm toh indai yaran novel kuke matari, zai sameku har ya ishe ku, don naga wancan zabiyar sai wani rangwaɗa take agaban wancan zabgegen, toh kimata albishir da zatayi bayani, idan taji shi a tsakar kanta".

Riƙo hannun Fauzy nayi na jata da sauri nace, "Fauzy zo muguda kada wannan ƴar barikin ta ɓata mu".

Dariya trouble tayi tace, "Zamaki ɗame yarinya mai duma-duma," duka wurin suka saka dariya, nima dariyan nayi muka barsu.

anyi Dinner lafiya angama lafiya, Amare sun kyau, muma munsha kyau, cikin lace ɗinmu da Hammah yamana muka saka, gaskiya munyi kyau sosai.

Ranan Friday akayi Walimah a Multi-purpose, Inda mukayi shigan dogayen riguna, wanda Mummy ta kawo mana daga Dubai, nawai Red na Besty Blue, Fauzy kuma baƙi,bbu ƙaryah munyi kyu kaman aa ɗauke mu, duk da haka, hankalin Fauzy ba akwance yake ba, saboda yadda Yayah Kamal yana wani shareta.

Allah sarki su Adda,tunda gari ya waye suka kasa sukuni, duk inda Adda Hafsat tayi zakaga Adda Umaimah, kowa ya gansu sai ya tausaya musu, don irin sabon da sukayi da juna.

Da misalin ƙarfe 10:00 aka ɗaura auren su,  Kowa yana ta hada-hadan tafiya kano, Mummy tace a ƙira mata Yayah kamal, bayan yazo ne duk muna ɗakin nata sai tace mishi.

"Kamal ka ɗauki Fauzy da Ummita" ƴar sister ta wanda itama baifi da 1yr muka fita ba, don itama SS3 zata shiga, tace "katafi kano da su, ku kuma Nafisa da Riyyah a nan zaku zauna da Umaima".

Babu yadda ya iya, yace "toh naji Mummy sai su Shiryah da wuri," sannan ya fita a ɗakin, jin cewa mu banda mu zuwa kano kai Addah Hafsat, don Aunty ce dasu Ummi nah zasu kaita, sai sauran dangi, nidai tsarin yamun, amma Besty ba haka taso ba, taso ta tafi kano saboda Hammah.

Ƙarfe 12 akaa fito da Adda Hafsat, Adda Umaimah na riƙe da hannun ta kuka takeyi na ɗaga hankali, kaman sun rabu kenan, itama Adda Hafsan tana rungume  da ita tana kuka, a haka suka shiga ɗakin Mummy, dama daga palon Daddy suka fito, Adda Hummy na bayansu ita da Aunty ladidi, itama kuka takeyi hannunta riƙe da Nabil.

A ɗakin Mummy dukkan su jikinta suka faɗa suna kuka, Mummy ce take buga bayansu cikin dauriya tace, "Haba ƴan biyun Mummy? Wayace muku wannan ranan kuka zakuyi? Bayan kun rabu da Mummy da Daddy lafiya? Muna farin ciki yau zamu kaiku gidanku lafiya, babu komai kuyi shiru, Allah ya albarkaci rayuwar aurenku, Allah yabaku zuri'a masu albarka da biyayyah irinku.

Farin cikina yau na aurar daku lafiya, Allah ya ƙara haɗa mun kanku yadda kuka taso kaman ƴan biyu, haka nakeao ku ɗaure har ƙarshen rayuwarku, ke Umaimah bayan gari ɗaya muke, jullum zaki na ganina idan kinso, ke kuma Hafsat ga ƴar'uwarki kuma wacce take miki mazaunin uwa, Hummairah kuna gari ɗaya, don Allah kuyi haƙuri kuyi shiru, saboda yau wace rana ce acikin ranakun da bazan iya mantawa da itaba, yaran danake ganinsu naji sanyi a raina, yaran ɗa suke mun biyyayah da duk abinda nakeso, yau zasu yi nisa dani, alokacin Mummy ta fara kuka,wanda duk ɗakin sai da aka rayata.

Don maganan gaskiya duk yaran Mummy babu wanda ta shaƙu dasu irin su Addah, don babu inda zatayi baka gansu gefen taba, abin tausayi gashi yau rana ɗaya duk zasu barta.

A haka Daddy ya leƙo yanata faɗa su fito da Hafsat kada suyi yammah.

Bayan an fita da Hafsat, sai mu wanda zamu zauna a bauchi domin cigaba da hidiman wuni, domin daga Umaimah har Haƙilah a bauchi zasu zauna.

Adda Hummy ita tabi ƴan tafiya kano, inda Aunty Ladidi zata zauna anan damu, duk da anbar kukan amma ni har yanzu wani iri nakeji a raina, a haka nafita zuwa gidanmu don na huta.

Nima Aunty nice nace bari dai na huta sai jumawa.

*KUKASANCE DA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*

®✍
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION* ✍🏻
{Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu gaɗakar da al'umma domin ribantar duniya da kuma lahira.}

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN ƘARFE* 🏇

Story and written
By
*AUNTY NICE* 😘

Wattpad@GaskiyaWritersAsso.

*WANNAN LITTAFI SADAUKARWA NE GA MISS XERKS*

*PAGE* 18

Wannnan shafin sadaukar wa gareku, Masoyaana, na hannun dama nah *AISHA ALTO*& *MAI

DAMBU*

__________📖Duk da hutawa nake so nayi amma zuciyata taƙi hutawa da tunani, a zuciya na ina ayya na yanzu Mummy dake da yara mata har uku, amma take cikin damuwa da tafiyan su Adda, toh Ummi nah ita yayah zatayi idan nima nayi auren?.

Sake juyawa nayi ɗayan hannu, a zuciyata ina jin ba daɗi yadda Yaya Kamal yake yiwa Fauzy, domin gaskiya idan nice ita bazan iya cigaba da son shi ba.

Toh ni ɗin meye nafi Fauzyn da zai so ni sama da ita? Bayan ita farace gata ƴar'uwar shi, sake juyawa nayi gefe ɗaya ina jin babu daɗi a raina, saboda yadda take nuna mun tana sona.

Wayata ce ta ɗauki wani sarewan india mai daɗi, ina murmushin jin daɗi na ɗauki wayan don na san mai ƙiran.

"Hello Besty na faɗa ina tashi zaune" can ƙasa-kasa da muryah naji shi yana ce mun, "My dear nikan na gajji da rashin ganinki, nifa gaskiya zaɓ dawo ya faɗa da muryan shagwaɓa".

Ina dariyan shi saboda yadda yake ta mun shagwaɓa kaman ahine macen nace, "haba Bestyn Beauti! yayah za'ayi ace kadawo kabar aikin da nake alfaharin miji na jarumi ne, ya tafi neman halal ɗin da zai riƙe ni, toh idan kace ka gajji, ni kuma nace meke nan?.

Shiru yayi kaman bazai ce komai ba, can kuma yace, "Beauty nah!" sannan ya sake shiru yana sauke numfashi kaman bazai sake cewa komai ba, can kuma saaai naji ya sake ajiyan zuciya sannan yace,
"Beauty toh nikan amana auren mana don Allah, nifah gaskiya kisani ina takura sosai".

Ɓoye kaina nayi cikin bargo kaman ana gani nah, inata dariyan shi ƙasa-ƙasa, ni wallahi mamakin Besty nakeyi na yawan shagwaɓan shin nan.

"Beauty kinyi shiru idan baki ce komai bafa zanyi kuka", ya faɗa yana wani irin murya kaman ɗan 5yrs.

Haƙuri mana Bestyn Beauty, kaga nima zaka sakani kukan kuma babu mai lallashi na, don Ummi nah ta tafi kano, na faɗa nima da muryan kukan.

"Haba Beauty kashe ni zakiyi ne?nikan gaskiya zan ƙira Baba na gaya mishi kawai a mana auren, kinsan sun bani gida mai 2 bedroom ae ya ishe mu ko?"

Haka mukayi ta hiran har zuwa bayan sallan la'asar, sannan mukayi sallama na tashi na yi wanka.

Tunda na shiga haraban gidan na haɗu da Besty zata zo nema na, hararah na take tayi tana cewa, "ke wai ina kikaje ina ta nemanki? Kinsan kuma zamuje gidan Haƙilah ko?.

Hararan ta nayi na buɗe motan bance mata komai ba na zauna, bayan munje gidan Haƙilah wuraren ƙarfe shida mukayi gidan Adda Umaimah, gaskiya gidajen amaren yayi Kyau.

Muna gidan Adda Umaimah har wurin 9:30pm, tukun ango da abokan shi sukazo, muna cikin ɗaki nida Besty Hammah Haidar ya ƙirata akan mu fito, haka muka fita ko sallama bamuyi da Addah ba.

A mota sai hiransu suke kaman zasu lashe kansu don so, har mukaje bauchi clup ya saya mana hanta, bayan mun iso nabar su a motan suna sallama, ni kuma na ɗauki ledan naman nayi cikin gida, a palo na samu Mummy zaune da wasu daga cikin dangi suna ta hira.

Gaishe su nayi sannan na wuce ɗakin Besty, wanka na shiga tare da yin alwala, ina fitowa naga Besty ta haɗa mana tea sannan ta buɗe ledan hantan ta fara ci.

Towel ne ɗaure a jikina nazo na zauna ina mata masifah muna cin naman, ko kula ni batayi ba, ta cigaba da cin naman tana ɗan wani dariyan isknci, muna gama ci na tashi na kuskure baki na, ko kulata banyi ba nasaka kayan bacci na na kwanta.

************

Hammah Haidar ne ya kawo mana form na school of nursing muka cika, sannan yace mana mu shiryah nan da 2weeks za'ayi interview.

Yau gaba ɗaya gidan mu mun tashi da farin cikin samum aikin Hammah Walid da Hammah Khalil, dayake Computer suka karanta dukkansu lecturing suka samu a Federal Poly Bauchi.

Ranan da yammah sai ga Aunty tazo, haka sukayi ta hira da Ummi na ƙin shan maganin Bappah, har zuwa bayan ishaa tana gidan mu, daga nan ta tashi bayan na shiryah kayana, din tun jiya tace mun zatazo mutafi gidanta nayi hutu har sai na samu admission.

Muna fita muka wuce gidan Goggon Bauchi, acan naji Goggo tana gayawa Aunty cewa, "Fatima kinji ɗanki kam wai dole sai anje maganan neman auren shi? Kuma don fitina wai da wuri yake so a saka date."

Dariya Aunty tayi sannan tace, "babu wani abu ae Adda Aisha, shima Babaganan haka naji yanata damun Baban shi akan a je a saka mishi rana, yaran ne dai basu da haƙuri, kawai ki barshi aje a saka ɗin babu komai".

"Hmmm Fatima naga yaushe iyayen yarinyar nan suka yi biki har biyu? Sannan yazo da zancen a sake ta kura su? Gaskiya ya ɗan kara haƙuri ko makarantar ne ma ta fara".

Dariya Auntyn tayi tana miƙewa tsaye tace "Adda ki bar shi zamuyi magana da shi", sannaan mukayi sallama muka fita.

Ranan Thursday tunda asuba na tashi da ciwon mara kaman zan mutu, domin ni idan zanyi period kaman wata mai labour, ina kwance naji Baba yana cewa Aunty Mama ba lafiya yanzu suka fita zuwa asibiti.

"Subuhanallahi jikin ne kuma ya sake tashi?" hmm kawai yace  yana duba wayan shi, nidai ina kwance akan kujera ina jinsu, can yace" Zahra bata kiyaye ciwon ta, kullum zaki ganta tana ciye-ciyen kayan zaƙi, ima mata maganan amma da girmanta bataji" ya cigaba da neman wayan.

Aunty ce tace " dasu Abdallah suka tafi ne"? Ɗaga mata ki yayi ƴa fara amsa wayanshi, inaji nagane da Hammah yakeyi don naji ya tambaye shi ina mai fashin matan nan yake? Yana dariya yace "ka gaya mishi ya taho uwargidan shi da yake saya mata   sweet ciwon ciwon ta ya tashu, tana asibiti saboda rashin iya cefanen shi, daga ganin haka Aunty ta fara musu dariya

tana "Baban su inaga har da kishi kakeyi da maigidan namu" bayan yagama wayan ya dubi Aunty yace "Me yasamu Fatima naganta kwance"?   Kallo na tayi sannan tace, "wai cikinta ke ciwo, amma dai tasha magani, yanzu Baban su zamu iya dafa mata abinci ae ko"?

Yana kallonta yace "Allah ya miki albarka Fatima, ku dafa mata idan yaso sai Abdallah yazo  ya kaiku, ko kuma kawai ma kuje da kanku".

Da rana Aunty dasu Gidaɗo sukaje duba Mama, ni kuma nacewa Aunty tabarni sai za'aje kaiwan abincin dare.

Ni aka bari na mata abincin daren tuwon acca  da miyan kuɓewa nayi, Aunty ta ɗauke mu muka tafi asibitin.

Acan muka samu su Abdallah da Hammah Umar da akace wurin magarib ya iso tare da matar shi, fuskar shi a haɗe kaman bai taɓa dariya ba, ashe dabi suke tayi da Zainab akan yace ta kwana da Mama amma firr tace matar da ta gansu tare suka kwana mana, ita yayah zatayi ta kwana a asibiti, suna haka muka shiga.

Ɗakin duk shiru sukayi babu mai cewa komai, don duk zuciyarsu babu daɗi, ita matar uta takeyiwa Mama abinci gidan ta babu nisa da gidan su, ita tace tabar yarah ƙanana babu mai kwana dasu, amma idan wuni ne babu komai zatayi amma a samu mai kwana ita kuma da safe sai ta dawo.

Mama kenan yau garanan baƙin halinki na ƙin dangi, yau da ace kina shiri dasu ace garin bauchi kaf da yaje cike da ƴan'uwan Baba arasa me kwana da ke?Allah ya sauwaƙa.

Baba ne ya buɗe ƙofan suka shigi tare da Abdulrahman, gaishe shi muka sake yi yana kallon Hammah yace yaya, "Sojaa an saamu mai kwanan ne?"

Hararan Zainab yayi sannan yace, "Baba ga Zainab ae sai su kwana, Mama watake dashi sama Zainab? Shiyasa na taho da ita.

Kuka kawai mukaji ta saka tana cewa, "nikan Baba ban iya kwanan asibiti ba, tsoro yake bani"' kowan mu kallonta  ya tsaya yi ana mamakinta, su Twins kuma banda hararanta babu abinda sukeyi, Hammah ko kallunta baiyi ba, Baba nema cikin murmushi yace, "Toh ae babu komai sojaa sai ka barta ae, su Abdallah sai su kwana da ita".

Aunty ce tace, "haba yayah za'ayi haka, babu komai tunda kunce gobe Hajiya zata iso, ni saina kwana tunda dama off nakeyi, tunda dai kwana ɗaya ɓe babu komai, ta dubi Baba tace kawai aɗauko mun kayan sallah nah.

Cike da farin ciki Baba yace toh angode Fatima, sannan ya kalli Hammah yace kamaida wife ɗinkan gida dasu Fatima, udan yaso sai ka karɓo ma Auntyn ku abinda zata buƙata ko?.

Batare da yace komai ba ya juya yayi hanyar waje, muma muka bishi nida Mujah tun da anbar su Gidaɗi dama agida, Aunty ce ta biyo bayan mu tana ƙirga  mun abinda zan ɗauka mata, da kuma abinda zan girka na break-fast na gida da kuma na asibiti.

Acan ɗakin kuma Abdallah sarkin zuciya sai tsaki kawai yake ja, Babane ya Kalle shi yace, "Mazaje yyah akayi ne? Babu wani abu ae kasan ƴar masu kuɗi ne bata saba irin wannan rayuwar ba, ya faɗa yana dariya".

Itama kanta Mama ranta a ɓace yake din dai babu yadda ta iyane.

Muna isah bakin gate, Baba mai towan Mama ta sauƙa tana godiyan kuɗin motan da Hamma ya bata na zuwa asibiti da safe, yana ƙara jaddada mata don Allah ta fito da wuri, mu juma a ka buɗe gate ya shiga damu.

Ina palo ina ta roƙan Gidaɗo ya miƙawa Hammah kayan Aunty sai iskanci yake mun yana cewa, "kaji mun yarinya ke baki da ƙafah ne ko kuma kin raina ni?" yana rufe baki Hammah yana shigowa palon, hannu ya miƙa mun ya karɓi kayan sannan yace, "Da safe idan kin haɗa break-faat na gida, ki bar shi duka anan side ɗin, zamu shio nan muyi".

Ba tare daya jira yaji mai zance ba, kawai ƴa juya ya fita, nidai kallon shi kawai nakeyi ina mamakin ikon shi, ga wani ƙamshi daya bar mana a cikin palon.

*KU KASANCE DA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*

®☄

*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION* ✍🏻
{Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin rubantar duniya da kuma lahira.}

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN ƘARFE* 🏇

Story and written
By
*AUNTY NICE*😘

Wattpad@GaskiyaWritersAsso.

*WANNAN LITTAFI SADAUKARWA NE GA MISS XERKS*

*PAGE* 19

Wannan shafin nabaki shi kyauta *MUMMY* *NA UMMU ASMA'U NOVEL* Allah yabar zumunci.

*____________* 📖Juyawa nayi ina kallin Gidaɗo da yake mani dariya, hararan shi nayi nace

"Bakana mun dariya ba kasani tare zamu haɗa komai inji Aunty, ehhhe yaro garama ka kwana da sanin haka", na juya nayi hanyar ɗaki ban saurari dariyan dayake ta mun ba.

Tunda Asuba da nayi sallah ban koma bacci ba, kitchen na shiga na fara haɗa break-fast, alale mai ɗauke da hanta nayi wa Mama, sannan na soya doya da ƙwai na gida, nazo nayi peppesoup ɗin kayan ciki.

Nasan kullum Aunty sai tayi Tea mai kayan ƙamshi, nima ban fasa ba na haɗa hadda shi, sannan na haɗawa Mama kunun alkama.

Bayan naga komai ya kammalu na juya na harari Gidaɗo nace, "sai kaje ka kwanta ae, don duk wanda ya ganka zaiyi tunanin wani abun kirki kake tayani, bayan daga fere doya babu abinda kamun," harara na shima yayi sannan yace, "yarinya ki maida hankalinki fah! bani na tayaki ƙulla alalen ba?" sannan ya ɗauki cooler ya zuba alale guda uku a ciki ya ɗaura a saman fridge, yana hararah na yace, "idan ban adana ba nasani ba zaki ajiye mun ba, bayan na gama shan wahalan yinshi" ya juya ya fita yana mun dariya.

Ɗakin Aunty naje gyara na haɗa turaren wuta ta kowa wuri, daga palor, ɗaki, toilet duk na zuba, idan kaji side ɗin Aunty yadda ya kama ƙamshin turaren borno, ko side ɗin Mama ba yayi.

Wanka na shiga nayi, sannan nayiwa Mujaheed muna shiryawa wurin ƙarfe 8:00 saiga Aunty ta shigo ɗakin.

Da murna Mujah yaje ya rungumeta, ina tahowa wurinta na gaisheta, "Ƴan mata na duk ke kikayi wannan aikin? Gaskiya Babagana zai more da mace mai ƙoƙari ga tsabta," ta faɗa tana duba na da dariya a fuskanta.

Nima dariyan nayi nace, "Aunty yayah jikin Maman? Da sauƙi ta amsa rana ƙarasa bakin gadon, sannan tace, "mai tayata wunin ae har tazo shiyasa na taho, idan yaso keda su Gidaɗo kwaje anjuma ku gaisheta, don na bawa driver abincinta ya tafi mata dashi".

Tana gama faɗi ta wuce toilet don yin wanka, bayan ta fito ne ta samu har na wuce ɗayan ɗakin, zama tayi ta shiryah kaman wata ƴan mata, gown ta saka na wani material, sannan ta fito zuwa dinning.

Muna zaune a dinning sai ga Baba dasu Hammah sun shigo, hannun Abdallah ɗauke da Nabil, wuri kowan su ya zauna, mu kumaa muka gaishe da Baba dasu Hammah.

Aunty ce ta karɓi Nabeel tana tambayan Hammah " ina Maman shi kuma, ko bata tashi bane" bayan ya gaisheta ne yake cemata, "ae bata ma san gari ya waye ba, wanka ma Abdurrahman ne ya mishi".

"Gajjiya ne ya ke damun ta", inji Aunty da ta maida hankalinta kan cin abincinta, kowa ma shiru yayi yana cin abinci.

Baba ne ya tashi yana kallon su Abdallah da su Gidaɗo yace, "Boys ku tashi muje mu duba Maman ku ko"? Duk kansu suka bishi, daga ni sai Aunty da Hammah aka bari a palon.

Aunty ce ta dube ni tace, "Riyyah ki ɗauki doyan ki kaiwa Zainab side ɗin Mama kada ta tashi bata san a nan yake ba"! "Babu inda za a kai mata Aunty, matar da bata san ta tashi ta girka bane za a bata? ae yadda ta nuna mun ban isa da ita ba akn uwata wallahi zata gane ƙuranta, tamanta ko bata aure ni ba Mama ae uwartace" ya faɗa kaman zai yi yayah don haushi.

"Haba Hammansu ae bazaka biye ta taba, yanzu kam ae komai ya wuce, kuma idan ba abata abinci ba ae baƙuwa ce yayah zatayi?"

"Rabu da ita Aunty, idan ta gama baccin asaran zata girkawa kanta" ya faɗa yana jin haushin matar ta shi, nidai tashi nayi zan wuce ɗaki, amma sai naji muryan Aunty tace, "kwanciya zakiyi ne?" nace mata "ehh" sai ta miƙo mun Nabeel tace, "inaga yaron nan yayi sanyi hala baccin zaiyi, kuje tare ku kwanta, in yaso idan za aje kai abincin dare sai kije ko?"

Da yammah kusan sallan magarib Umman su Mama suka iso daga maiduguri ita da Maman Zainab, alokacin itama Zainab ɗin tana asibitin, amma abin mamaki Mama sai nak nak take da ita, kaman ba itace jiya taƙi zama da ita ba, bayan su Umma sunzo ne ɗakin ya sake kachamewa da hayani.

Wuraren 7:30 bayan munyi sallan ishaa, Hammah ya shigo yace, "Mu fito da abincin ya kaimu asibitin, har mota Gidaɗo suka kai abincin, sannan nida Aunty muka shiga motan domin zuwa dubiya, haka na daure na zauna a gaban motan ba don na so ba.

Muna shiga ɗakin nayi arba da idon Maman Zainab dake ɗauke da Nabeel a kan cinyanta sai zuba takeyi, Umman su kuma rana gefe tana sallah.

Bayan sun gaisa da Aunty ne kaman bata son magana don yanga, Auntyn na tambayan ta yyah hanya?  haka a dakile ta amsa kaman bata so, nima gaisheta nayi sannan na gaishe da Mama da tunda muka shigo take mun wani irin kallo na ƙasƙanci.

Zainab ko ɗago kai batayi ba, ballantana kayi runanin zata gaishe da Aunty, ganin haka nima ko ta kanta ban biba.

Umma ce bayan ta idar da sallah naji tana cewa, " Wanake gani kaman kishiyata?" Tana dariya tana matsuwa inda muke, da sauri Aunty ta gaishe ta fuskanta ɗauke da murmushi ta amsa, sannan nima na gaisheta cike da ƙaunar dattijiyar, cihaba tayi da tsokana, " Ina wancan ragwaɓaɓɓen maigidan namu? Ko bai iso bane shi? Ta faɗa tana mun dariya.

Charr mukaji muryan Mama tana cewa, "In ban da ke Umma ina zaki ga Babanah? ae tunda aka bashi yaci baya iya tunawa da ni, don ko kirana baiyiba, " ....."Subhanallahi haba ke kuwa, ashe kina kwance a gadon asibiti ma bazaki bar zuciyarki ta huta da rashin hankali ba?wani irin magana ne kikeyi irin haka?" inji Umma da take watse Mama.

"Mama wa yace miki angayawa Babagana? Baba yace kada a gaya mishi saboda yaushe ya fara aikin kuma suga yana yawan ɗaukan escuse, don Allah ki dena haka", Hammah yana faɗa ranshi a ɓace.

"Toh Ubana mari na zakayi ne?" inji Mama da take hararan shi, ae dama kai ma inaga an mallake ka tunda har za'a hana matar ka abinci kai abaka amma baka ce komai ba, duk zuciyarku an lashe," ta faɗa numfashinta na wani iri.

Maman Zainab ce ta ɗago kanta tana wa Aunty wani irin kallo, sannan ta juya ta kalli Mama tace, "Haba Yayah Zaurah yanzu da ranki ake nema a wulaƙanta mun ɗiya ƙwaya ɗaya da Allah ya bani? Ni kinga duk wani kishinku na shirme bai dame ni ba, amma kada ki sake ki bari a wulaƙanta mun ɗitata, don sam bazan ɗauka ba ko kaɗan yawwa" ta faɗa tana hararan Hammah, kama baki kawai Umma tayi tana kallon su ranta a ɓace, can ta juya ta kalli Hammah ranta a ɓace tace.

" Ɗauki Aunty ka da matar ɗan'uwanka ka mai dasu gida su huta, sannan ta juya kan Mama tace, amma kinji kunya wallahi, dubi kiga irin hidiman da matar nan takeyi akan ki da ƴaƴanki amma baki gode mata ba?, sannan ta juya kan Aunty Falmata tace ke kan kullum akan mugun

son kanki kike abin kunya, wato idan ba ke da ƴarki ba, baki san kowa ba? Sannan damuwar kowa bata ɗameki ba sai taki dana ƴarki? Toh wallahi na sake jin muryar ɗayanku a daren nan zaku mayar dani inda na fito ,kuma nayi mummunan saɓa muku manyan banza kawai, wannan halinku bansan inda kuka gaje shiba, wallahi inda kukayi banbanci da ƴar'uwarku kenan, Allah ya shirye ku".

Sannan ta dawu kallon Zainab tace, "ke kam halinki na son jikinki da rashin kunya da baki ganin kowa abakin komai shi zai kaiki ya baro ki, don dai kam Umar baiyi sa'a ba, ta juya gun Hammah tace, Umaru kullum nayi sallah ina maka addu'an Allah ya baka mace ta gari, don kaima kaji daɗin rayuwar aure, don halinka kam bakayi dace da matar ƙwarai ba.

Harara Zainab take mata a ɓoye don duk iskancinta bata isa tayiwa Ummah ba, don Umma a tsaye take akan ƴaƴanta, tayi ma mana ta gani ko Aunty Fannah zata bar ta, don daga ita har uwarta basuisa ba tanaji ita dasu.

Haƙuri Umma ta fara bawa Aunty, amma Aunty cikin murmushi tace "babu komai Umma," ta miƙe tana cewa, " Mukan mun wuce Allah yabata lafiya ku kuma Allah ya huta gajjiya," Umma ce kawai ta amsa mata , amma daga Mama har Aunty Falmata basu amsaba don ko kallun mu basu sakeyi ba.

Hammah ne ya jalli ma Mama yace, " Mama saida safe Allah ya kara sauki, sannan ya kalli Zainab yace ki wuce mutafi kuma ki tabbatar gobe ke zaki musu abincin breakfast, don bazaku ci mutuncin mutane ba kuma su tashi su muku abu babu godiya, ya faɗa yana ɗaukan nabeel da yayi bacci acinyan Maman Zainab, Umma tace "dolen tama ae tunda rayuwar aure ta keyi bawai zaman jin daɗi ba"

Gaba ɗaya daga Mama har Aunty Faƙmata basu ji daɗin daren ba, don kusan raba dare Umma tayi tana zagin su kaman ta cinye su, kuma adaren ta ƙira Aunty Fannah ta zaƴyene mata komai, itama kaman tayi ihu don haushin halin yayunta da takeji, sai masufah takeyi tana cewa, "ae an bar Zainab ne take abunda taga dama, shidai Umar gaskiya baiyi dace ba, shiyasa take murna da zaɓin da Babagana yayi.

A Mota banda tsaki babu abinda Hammah ya keyi can yace, "Aunty daga gobe kada ki sake girka komai, Zainab zatayi kowani lokaci akai musu, idan yaso da dare sai taje ta gaishe su, tunda bata san mutunciba har zata iya kai kara don bata da kunya."

" Haba Umar ae baza ayi haka ba, ita kan ae yarinya ce babu komai zamuyi kwana nawa ne za a sallame su? Kawai babu wani abu".

Hararan Zainab ya juya yana yi sanan yace, " wannan tsohuwar sakaliyar ce za'ce mata yarinya? Ki barta kawai Aunty tayi",ya faɗa yana shiga gate ɗin gidan, ita ko Zainab yana ce mata tsohuwa ta fashe da kuka gashi babu halin tace mishi uffan, don bata isa ba.

Ni Aunty Nice ban san lokacin da dariya ya suɓuce mun ba, "wai tsohuwa har ta tsufah ne? Yamanta lokacin da yake cewa Yusuf su Riyyah jarirai ne? Sai kuma nayi shiru ina tunanin yaka mata naje gidan Yusuf fah, fita nayi a motan na barsu su kadai, fita nayi waje  mota nabgani a waje nace ya kama na shiga na roƙe shI ya kaini gidan Yusuf ko ba kuɗin mota, don nasan ɗan isubulle yana ganina zai biya kodan yaji ya labarin ƴan jarirai.

*KASANCE DA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*

✍️®
*GASKIYA WRITERS ASSICIATION* ✍🏻
{Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar duniya da kuma lahira.}

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN KARFE* 🏇🏽

Story and written

By
*AUNTY NICE* 😘

Wattpad@GaskiyaWritersAsso.

*WANNAN LITTAFI SADAUKARWA NE WA MUSS XERKS*

*PAGE* 20

*SAHIBA* ( *UMMI YAWALE BABA* ) ƴar uwata Aminiyata, wannan Ishafin naki ne ke kaɗai na dadaukar miki, Alherin Allah ya isar miki.

*___________*📖 Malali shine sunan unguwan da Yusuf suke zaune da matar shi Aishatu, babu matsalah Yusuf yayi dacen mata mai kirki da sauƙin kai, gashi tana da tsaftah da sauƙin kai.

Duk da ayanzu Yusuf haɗuwar shi da Hammah yayi ƙaranci, amma basu fasa communicating ta waya ba kusan kullum, gashi Yusuf har Abujah ya kai Aisha, amma da yake Zainab bata da kirki kuma bason mutane take da shi ba, sai sabon nasu yaƙiyi yuwa, don tunda suka dawo tace, "My dear gaskiya bazamu sake zuwa wurin wannan mata mai ji da kan nan ba, don wallahi baka ga yadda ta mun ba, ko kaɗan banji daɗi ba".

Dariya Yusuf yayi yace, "kuna da matsalah ko mata wallahi, mudai ba zamu fasa zumuncin mu ba, kodai da yake kuna da jin rai sai ku haƙura", ya faɗa yana kallonta da dariya a fuskanshi.

"Haba my dear! ae bai kamata kamun wannan shaidan ba kuwa, kasan hali na
ni ban iya wulaƙanta ɗan Adam va, da mai kuɗi da talaka duk ɗaya ne a wurinah, kawai dai inaga bata samu home training bane" ta faɗa kaman zatayi kuka.

Sorry my happiness wasa nake miki, ni ko nafi kowa sanin wacece ke? nasan ba halinki bane wulaƙanci shi yasa nake ƙara sonki baby nah, ita ma idan bata gyara ba, nasan Umar zai gyarata very soon.

A haka suka dawo kaduna suka cigaba da rayuwar su, suna six month da aure cikinta ya ɗan fara fitowa, kuma a wannan lokacin Yusuf ya lura da irin cikan da Aisha ta keyi, har ga Allah yaji daɗi cikin zuciyar shi, don shima yanzu ƴar cikakkan mace tana burge shi.

Da gari ya waye Aunty bata wani jira sai Zainab tayi break-fast ba, tashin nah tayi muka shiga kitchen muka haɗa komai, daga na asibiti har na gida, kafin 7:30 mun gama komai.

Bayan driver yakai su Gidaɗo sch ne, Aunty ma tayi shirin fita office tana tsaye a dinning tana mun bayanin abinda zanyi na rana, hannun ta ɗauke da tea cup tana shanye sauran tea ɗinta, bayan mun haɗa komai na asibiti tace, "driver yana dawuwa ki bashi ya kai musu, amma kada kije kinji auta".

Amsa mata da "ehh naji" kawai nayi, muna haka sai mukaji Hammah yana sallama ya shigo.

Aunty ya gayar sannan nima na gaishe shi, Aunty ce ta nuna mishi break-fast ɗin ƴan asibiti, sannan ta nuna mishi na cikin cooler tace ya ɗiba a wurin, su Abdallah kuma nasu yana kitchen dana Baban su.

Kallon Aunty yayi yace, "Hmmm wallahi Aunty da kin barta ta haɗa musu idan yaso suga ranan ku, amma yarinya babu abinda ta iya kaman ba mace ba" ya ja tsaki ya ɗauki basket ɗaya yace, "Aunty bari na kai musu idan na dawo na karya".

Hanyar fita yayi Aunty tace, "na bishi da flask da ɗayan basket ɗin, tunda shi ya ɗauki basket ɗaya da babban flask ɗin.

Har mota naje na saka mishi, ko kallona baiyi ba ya shiga ya fita.

Aunty ma office ta wuce aka barni daga ni sai mai mata sharah da wanke-wanke, ɗaki na wuce don nayi wanka na huta.

Sai wajajen 10:00 su Abdallah suka shigo suna breakfast, inajinsu amma ban fito ba, sai can naji Abdurrahman yana mun sallama.

Tashi nayi naje bakin ƙofan, sai na ganshi da Nabeel ya miƙo min shi yace, "Hammah yace ga kayan shi ki mishi wanka ya zauna a wurinki, Maman yaron zata je asibiti ne".

Karɓan yaron nayi inama Abdurrahman yayah jikin mama? Sannan muka koma ɗakin na rufe.

Gado muka koma muka kwanta nida Nabil kafin kace yayah har munyi bacci, sai wajen 12:00 na tashi na yiwa Nabeel wanka, na kaishi palo na kunna mishi catoon bayan na bashi Boobo na Mujaheed,  yana mun hwalamniyan maganan shi ina dariya nayi kitchen.

Gwaten wake mai hanta na ɗaura na Mama, sannan na gida kuma Rice and Stew,  na leƙa Nabeel ya fi a ƙirga yana ta kallin shi, duk lekawan danayi sai ya mun dariya, nima na mishi na koma kitchen ɗin.

Wurin 12:30 naji yana ta dariya, da sauri na fita don nasan time ɗinbda wowan Mujaheed ne, amma kawai sai mukayi ido biyu da Hammah yana ta mishi wasa, juyawa nayi na koma, bai daɗeba Mujaheed ya dawo, har kitchen ya biyoni yana, "Adda na dawo" kallon shi nayi nace, "toh ɗan Mujah na kana jin yinwa ne"?

Dariya yayi yace, "Boobo zan sha Adda", je ka ɗauka Besty nah, dauka yayi ya fita da gudu yayi palo.

Ana kiran sallan Azahar na gama komai na fito palon na samu duk Hammah yaja su mosque.

Ɗaki na shiga nayi sallah bayan na fito ne na same su dukkan su a dinning suna cin abinci haɗa na asibiti nayi a basket na fito da shi palon, ina kallon Gidaɗo nace, "idan ka gama kabawa driver ya kai kaji ƙaninah".

Harara na yayi baice komai saboda ganin idon Hammah a wurin, da sauri Nabeel ya sauƙa akan cinyan Daddyn shi ya biyoni yana ta mun gwalamniya, riƙe hannunshi nayi muka wuce ɗakin Aunty.

*______________*

Yau su Abba na da wasu daga cikin Bappah nen Hammah Haidar suka je neman auren Besty, kuma akayi sa'a dama iyayen su na Alkaleri sunce a saka auren farkon shekara da zamu shiga, idan yaso sai a haɗa dana Yayah Kamal da Fauxy.

Jin wannan labarin Besty ya ɗaga hankalin shi, akan shima sai an tura nashi maganan neman auren, babu yaddah Baba baiyi da shi ba akan ya bari ya shekara yana aikin amma yaƙi yadda.

Bayan 2wks ƴan'uwan Baba daga Jama'are suka zo neman aure nah, babu ɓata lokaci Baba ya saka musu rana ɗaya dana su Hammah Haidar, wanan kuma dama Shawaran su Goggo ne don abin zaifi musu sauƙi.

Ranan Besty kaman zai cinyeni don tsaban nuna mun soyayyah, sannan ya mun alƙawarun zuwa wani satin, kusan raba dare mukayi munabta hirah da Besty na, nima farin-ciki na keji idan nayi magana da shi.

Mama ce har palon Aunty yau ma ta shigo tayi bala'i, ko kallonta Aunty nah batayi ba ballantana ta tanka mata, haka tagama zage-zagenta ta bar wurin, nidai ina kitchen tunda naji muryanta ban fito ba har ta tafi.

Jikina yana rawa na fito na zauna gefen Aunty nace, "Aunty nikan gida zan tafi, tsoron matar nan nakeyi, kada wataran tazo baki nan, ta mun shegen duka".

Duk yadda ran Aunty ya ɓaci, amma bata san lokacin da tayi dariya ba tace, "Riyyah Allah ya shirye ki da tsoron nan naki, rannan da aka kawo ki a matsayin surukarta yayah zakiyi? Gara ma ki daina irin wannan tsoron naki". Ta faɗa tana shigewa ɗakinta.

Mamace ta kira Besty tace, "Wallahi Baba nah idan baka janye maganan auren yarinyar nan ba zamu haɗa ƙafan wando ɗaya dakai a gidan nan, kuma duk abinda kakeyi ka taho wannan satin, akwai ƴar ƙawata kazo ka ganta don babu abinda wannan ƴar matsiyatan zata nuna mata , banda kai me zakayi da ƴar talakawa gata baƙa.

Besty ƙiran Hammah yayi ya gaya mishi duk yadda sukayi da Mama yana kuka, yana cewa, "Hammah yanzu yayah zanyi da ita? office baza su barni ba, kuma tace sai nazo."

Shiru Hammah yayi can yace, "ka zauna kada ka taho zan neme ta," daga nan ya kashe wayan,

Mama ya kira, bayan sun gaisa yace.

"Mama maganan auren Babagana don Allah bana so ki sake cewa komai, sannan maganan zuwan shi bazai samu dama ba saboda office, don Alllah Mama in banda abinki ba albarka zaki saka musu ba? Amma kullum kina ɗaga hankalinki akan matar da bata taɓa nufin ki da kowani sharri ba ? Haba Mama yaƴah kike so na dinga ji acinkin raina? ace Mamana ce Kullum ake samun matsalah da ita? Gaskiya idan har kina son kwanciyar hankalina ki daina bana so Mama."

Kuka Mama ta fara tana cewa haba "Hamman su kana ga anmun adalci? Kawai ina zamana da miji na yaje ya ƙaro mun wata kishiya, yanzu kuma duk da rashin adalcin da aka mun kake so na yadda ɗana ya auri zuriyan su?" ta faɗa tana ƙara sautin kukanta.

Daga inda Hammah yake yayi murmushi cikin zuciyar shi yace, "kai mata wato su duk girman su basu son maganan kishiya? Meye aciki tunda ya hallatah ayi ɗin, amma ko kaɗan basu girma da ƙin kishiya".

A fili kuma yace, "Mama nah kiyi haƙuri Baba nasan bai kyauta miki ba ko kaɗan, amma yanzu ki bari ayi auren Babagana da yariyar na, kada ki sake ɗaga hankalinki nake so, amma idan kika ɗaga hankalin ki bazan ji daɗi ba, kinji Mama nah".

Shiru tayi can tace, "naji amma ka gaya mishi ya rage rawan kannan da yakeyi, kuma kace mishi yaci albarkacin kane, amma ya Sani babu bakina a maganan auren, kuma kada yazo mun da maganan komai na auren shi."

"Hakan ma yayi Mama nah, Allah ya bar mana ke first luv", ya faɗa yana dariya abunda ban taɓaji yanayi da wani ba aduniya idan bada Maman shi ba, itama dariyan dole tayi tace, " ina maigidan da Maman shi? Yaushe zaka zo ne?"

Yace "ƙarshe wani watan Mama, don ƙarshen Watan nan zan je zaria na duba twins ɗinki don zanyi wani course na 1month a can, ina gamawa zan taho Bauchi naganki Mama nah.

Dariyan tayi tace sai kazo sannan sukayi sallama.

Aunty ce suka haɗu dukkansu a Kafin-Madaki wurin su Bappah, inda suke shawaran yadda zasuyi  bikin yaransu har biyu, Aunty so take ayi mun komai na girma saboda Mama.

Inda ta kawo shawaran idan Mummy zataje Dubai zasu bada kuɗin su domin yimun sayyayah na acan na kayan ɗaki, duk kansu suka yadda da shawaran.

Bappah ne ya ɗauko takaddun filin gonayen shi guda biyu yace, "gashi a sayar a saya mata gado wannan gudumawa nane, saboda babu abinda zan mata da ya wuce haka.

Abba ne yace, "Bappah da kabarshi ae zamuyi abinda ya sauwaƙa a tsakanin mu".

Hararan Abba Baba yayi yace, "saboda nine bare acikinku ko? Toh inga wanda yace a'a acikin ku kuga yadda zanyi da mutum, ba tsawon rai bane yakawo ni har yanzu? Wanake da shi yanzu sama da Fatima acikin ku?"

✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*

✍®
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION* ✍🏻
{Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar duniya da kuma lahira.}

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN KARFE* 🏇

Story and written
By
*AUNTY NICE* 😘

Wattpad@GaskiyaWritersAsso.

*WANNAN LITTAFI SADAUKARWA NE WA MISS XERKS*

_Wannan shafin baki ɗayansa sadaukarwa ne gareku Wattpad fans namu na *Gaskiya WritersAssociation*, musamman user 1686532 da FateeMaiturare, ina godiya sosai a gareku da yanda kuke bibiyar wannan novel nawa, tare da bamu votes yanda ya kamata,anq tare kudai kuci gaba bibiyata ni kuma ina killing naku da jin daɗi😅,one love wattpadian😍🤝._

*PAGE* 21

*___________📖* Gaba ɗayan su jikin su yayi sanyi, cikin nuna jin daɗi Goggon Bauchi tace, "Hakane Baffah"

tasa hannu ta karɓi takaddun tana cewa,

" Allah ya biyaka da abunda kake mana da mafificiyar Aljannan shi Baffanmu, insha'Allahu duk yadda kake so haka za'ayi".

Kowa ya nuna jin daɗinshi a ɗakin, sannan Umma ta ce tabada shanunta guda biyu ɗaya Abba na yayi nashi hidiman ɗaya kuma Goggo, haka aka gama taro lafiya suka dawo bauchi.

Admission ɗinmu yana fitowa aka mana Registration, juma Hammah Haidar yace a cikin school zamu zauna don zamu fi maida hankalinmu a kan karatun.

Nidai ranan kaman zan mutu don haushi, ina samun Aunty da maganan itama ta goyi bayan Hammah haka nayi haƙuri nayi shiru, don ita kam Besty bata da matsalah don duk abinda Hammah yace dai-dai ne a wurinta.

Komai babu wuya a wurin Allah, ranan da zamu tafi cikin makarantar, ranan aka aiko Adda Hummy ta haihu ɗa namiji wannan karon ma, kowa saida yayi mamaki don ba'a lura da cikin ba da tazo biki.

Babu yadda muka iya haka muka tafi school, don Hammah yace ko suna kada wani ya tafi da mu, mu maida hankali a karatun mu yake so, Allah sarki Besty nah sarkin haƙuri da mukayi waya ina ta mishi rikicin ni Hammah Haidar ya takurani kaman shine zai aureni yana ta saka mun dokoki.

Shidai dariya kawai yayi yace, " Beauty nah kada ki damu Hammah gata yake muku kinji, kiyi haƙuri kuyi karatun ku insha Allahu kuna hutu zan kaiku har kanon kuga Baby'n"

haka yayita rarrashina ina botsarewa, ita kuma Besty gyaran ɗakinmu ta keyi bata kulani ba, bayan ta gama ta buge ƙafa na ta wuce toilet don tayi wanka, dayake da yamma muka iso ana fara ƙiran sallah mukayi sallama da Besty.

Ranan Friday da yayi dai-dai da watanmu biyu a school ɗin muka shiga gida yin weekend, wanda shine karonmu na biyu da Hammah ya barmu zuwa.

Haka zalika a wannan week ɗin Besty na yazo, dadî kaman zai kashe ni, bayan munyi sallan isha'i yazo hira, a palon Abba muka zauna muna ta hiran mu har wurin 9:30 ya mun sallama zai tafi, jikin motanshi na rakoshi muka sake tsaya wa har sai da 10 yayi tukun mukayi sallah ma zuciyar mu cike da ƙaunan junan mu.

Yana tafiya ina ta kallon shi har yabar layin unguwarmu, na juya kenan zan shiga gida naga Yayah Kamal ya fito daga gidanmu, abin yabani mamaki sosai don bansan yana gari bama.

Gaishe shi nayi ya tsira mun ido bai amsa ba, ganin haka sai na ratse ta gefen shi zan wuce, da sauri ya tare hanya yana kallon idona yace,

"Riyyah wannan yaron kika zaɓa sama dani ko? Me yasa bazaki amince dani ba Riyyah?"

jinayi yabani tausayi daga yanayin yadda yake magana, a hankali na matso kusa dashi kaina a ƙasa nace.

"Yayah Kamal kasan dai daba don mun haɗu da Babagana ba, kuma ba ayi maganan Fauzy ba da babu abinda zaisa bazan amince da kaiba domin kyawun halayenka dana iyayenka da kuma kyawun nasabanka, ka cire ma maganan Babagana, wallahi koda na amsa mishi idan babu maganan Fauziyyah to zan amince da kai na barshi, koda yaya tsawon ƙaunar shi yake kuwa a raina, don sau ɗari kafimun kowa wallahi.",

"amma ina ƙara baka haƙuri idan da gaske son da kake mun ya kai so, to na roƙeka ka maida shi kan Fauziyyah kanuna mata asalin son da kake mun to zanji daɗin hakan fiye da komai."

Kallona ya tsaya yanayi ya cije lips ɗinshi na ƙasa wanda har naji tsoro kada yaji ciwo, kaman ba zaiyi magana ba can naji yace.

"Naji daɗin abinda kika ce mun, kuma abinda na fahimta nine nayi rashin hanzari bawai kuma don baki sona ba, Allah ne bai ƙaddari hakan ba a tsakanin mu, sannan kisaka a ranki Riyyah duk duniya babu mai sonki sama dani, kuma zan miki proving hakan nabin umurninki, nayi haƙuri dake badon zan taɓa daina sonki ba, sai don nuna miki irin son da nake miki, zan auri Fauziyyah na nuna mata so da gata a dalilin sonda nake miki, kuma na miki alƙawarin ɗaukaka darajanta sama dana sauran matan duniya a idona saboda ke."

ya faɗa idon shi na kawo ƙwalla.

Gaba ɗaya nima sai naji banji daɗi ba don wallahi kodan darajan ƴan'uwanshi da ɗawainiyar da iyayenshi suka mini a rayuwa dana aminta dashi nabar Besty, amma kasancewar shigowar Fauziyyah rayuwar shi kaɗaine zai saka na barshi, amma nasan Yaya Kamal mijine na nunawa sa'a, ban iya nace mishi komai ba saboda kukan da yazomini, bin gefen shi nayi na shige gida, wanda shima bai hanani ba, matsawa yayi na wuce shima ya wuce gidan su.

Gaba ɗaya weekend ɗin babu wani karatun da mukayi sai ɓarza soyayyanmu da mukayi tayi nida Besty, a lokacin na yadda da maganan Hammah Haidar na babu wani karatu da zamuyi na kirki a gida, domin ranan saturday gidan Adda Umaimah mukaje da gidan Haƙilah, babu abinda muka tsinana wa kanmu sai yawo da soyayyah.

Ranan Sunday Driver ne ya maida mu, kasancewar daga Besty har Yayah Kamal da safe suka tafi, bayan sun mana shooping ɗan gaske.

A ɗaki muna kwance Besty tace mun, "Besty kinsan naso da mukaje weekend mu duba yaya jikin Trouble, don kinji sau biyu tana kwanciya a asibiti?"

ta faɗa tana kallona, nima kallon ta nayi nace,

"ba auren bane ai, yau ace kana da ciki gobe ace haihuwa jibi ace baka da lafiya, ni wallahi Besty har tsoro nakeji".

Dariya tayi tace, "nikan ina so Besty, ban ƙi ace yau ma za akaini wa Hammah na ba, don a matse nake da son kasancewa da shi"

ido na ƙura mata bakina a buɗe nace,

"lallai Besty bakida kunya, yanzu namiji babba kaman Hammah kike buri kiga kin kasance da shi? nifa dama kullum mamaki kike ban yayah zaki iya da shi?"

Dariya tayi ta kalleni tace, " dabadan ke yarinya bace dana gaya miki yadda zanyi dashi,to amma idan nayi hakan ban kyauta mishi ba, don na buɗe sirrinshi a gaban ƙanwar Shine kuma

ban kyautaba,"

ta faɗa tana wani ɗaura hannu akan zuciyanta,Tana ta dariyan iskanci.

Tsaki naja nace, "Besty amma wallahi kin rainani ai baki isa don zaki auri Yayah naba kice mun yarinya, don duk abinda kike tunani Hamma'n naki zai miki ina mai baki tabbacin Besty na sai ya fishi"

na faɗa ina tashi zan fita a ɗakin, ita kuma ihuu ta saka tana cewa, " wallahi yarinya kinyi ƙaryah don abinda Hammah na zai mun ko za'a ɗaure Besty ba zai iyaba"

ta faɗa tana faɗawa kan gado tana kiran sunan Hammah tana ta dariyan iskanci, hararanta nayi na fita a ɗakin, don inna biyeta sai mu lalace a haka.

Soyayyah tsakanin Yayah Kamal da Fauzy sai kankama yakeyi, don inaji wataran ta kira Besty tana ta bata labari, don har tace yanzu yace bazata tafi ATBU ba, don wai shi bazai iya juran tana wani wuri shima yana wani wurin ba, saboda haka Abuja zataje tayi karatunta, abin mamaki sai naji wani irin daɗi a raina, wato ashe da gaske yana sona da har zai iya mai da Ƙiyayyanshi akanta ya koma soyayyah.

Ranan wednesday bayan mun fito a lectures wanda wata mata mai tsananin take ɗaukanmu ana kiranta Mummy Boo, duk kanmu yayi zafi babu abinda nake so irin najini kwance a kan gado, gashi muna da test ɗinta gobe, kallon Besty nayi nace,

"yakamata daga anyi sallan isha mu fito muyi karatu".

Wajen 5:00 daidai zamu shiga Hostel ɗinmu sai naji muryan wata tana kirana "Sis Riyyah!"

Da sauri na juya ina kallonta, ƙarasowa tayi inda nake tace, "Kije Mummy Boo na ƙiranki a

office ɗinta"

da sauri na juya nayi office ɗin.
Ina zuwa bakin office ɗin naji ƙamshin wani turare da na sani yana busoni, bakina ɗauke da sallama na shiga office ɗin bayan ta amsa mun.

Wani irin yankewan zuciya naji kaman zanyi fitsari a jikina dana yi arba da mutumin dayake zaune a office ɗin, ni narasa wani irin kwarjini yake mun a rayuwata, duk inda naganshi sai naji wannan mummunan faɗuwar gaban, a zuciyata nace, _shi kuma lafiya na ganshi a school ɗinmu?_.

Nima dai Aunty nice nayi mamakin ganin shi a office ɗin, to me yakawo shi? Bari dai muji damai yazo.

*KU KASANCEVDA ALKALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
2019published.
*BADARIYA*

✍®
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION* ✍🏻
{Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar duniya da kuma lahira.}

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN KARFE* 🏇

Story and written
By
*AUNTY NICE* 😘

*WANNAN LITTAFI SADAUKARWA NE GAREKI MISS XERKS*

_Haƙika anyi rashin Babban mutum, mai haƙuri, son mutane da cigabansu. *BAPPAH HAKIMI* ina ta'aziya wa masaratan Misau da dukkan legal community, Allah ya masa Rahama ya gafarta masa zunubansa._

*PAGE* 22

*___________📖* Gaba ɗaya ji nayi ƙafana kaman baza su iya ɗauka na ba, muryan Mummy Boo naji tana ce mun,

"ki ƙara so mana, ba Yayan ki bane ba?"

Dole na jawo ƙafana na ƙaraso cikin office ɗin, har ƙasa na sunkuya na gaisheta, sannan na gaisheda Hammah Umar wanda duk naji muryana yana rawa.

Mummy Boo ce ta tashi tace, "Toh Sojaa bari na barku ku gaisa, amma kada ya wuce 30mnt, ina jiranka a wajen can"

ta fita tana cewa na zauna akan kujeran.

Juyowa yayi ya kafa mun mayun idanun shi wanda bansan lokacin da na buɗe baki na sake gaishe shi ba.

Batare da ya amsa mun ba ya jeho mun tambaya, " baki da number nane a wayanki? baki damu da kiji Yayah muke ciki ba ko?"

Jijjiga mishi kaina nayi alaman ba haka bane, harara na yayi yace, " hala bakinki yana ciwo ko?"

buɗe baki nayi nace, "bani da number ne Hammah".

Miƙo hannu yayi ya karɓi wayana ya saka number shi, sannan yace,

" daga yau ina samun ƙiran ki na gaisuwa, sannan duk wani abu da kike buƙata ban ɗauke miki ba, ki kira ki gaya mun"

shiru yayi yana ta dube-dube cikin wayan har zuwa wani lokaci sanann ya ɗago ido ya dube ni yace,

"Fatimah! Naso ace kiyi karatunki ki gama successefully kafin ki shigo da maganan aure, amma sai kika watsa mun ƙasa a ido kika biyewa wannan yaron mai rawan kan, wai kema aure kike so, bakiga kinyi ƙarama ba? Me zaki ɗauka a rayuwar aure?"

Ban iya ba shi amsa ba sai sunkuyar da kaina ƙasa da nayi ina wasa da hannu na, shima ƙura mun ido yayi wanda har jikina sai da naji yana rawa, shi ɗaya naji yayi a jiyar zuciya sannan yace,

"Fatima bana so kibiye wa soyayyah ki kasa maida hankali a karatu, don ke har yanzu bakiyi wayon da zaki fahimci so na gaskiya ba, kuma zaiyi wuya a age ɗinki ganzu ki gane menene soyayya" ,

"Amma da zaki mun alfarma ɗaya ki dakatar da maganan auren nan sai kin gama karatunki, da ni kuma zan miki alƙawarin wani muhimmin abu mai daraja a rayuwarki, wanda har ki ƙarasa rayuwarki a cikin farin-ciki"

ya faɗa yana ƙura mun ido.

Ɗaguwa nayi ina son satan kallon shi, amma cikin tsautsayi sai idon mu ya haɗu wuri guda, da sauri na sun kuyar da kaina kasa, ban iya bashi amsan komai ba.

"ki buɗe baki kimun magana, saboda akwai abu masu muhimmanci da suka sa ni shigowa cikin school ɗinku, kuma ya kamata kibani haɗin kai mutattauna kinji"

Batare dana shirya ba nasamu bakina da furta,

"amm..umm Hammah...."

sai kuma naji na kasa iya cewa komai, nidai wallahi da yasan yadda yake mun kwarjini da bai zo inda nake ba.

Ta suwa yayi ya zo har inda nake ya tsuguna.

Jin shi kusa dani ya saka ni ɗago kaina na sauƙe mishi ido na akanshi wanda ban san dalili ba nakasa ɗaga ido ba akanshi.

Shima kallo na yakeyi amma abin mamaki duk girman idonshi sai na gansu ƙanana, kuma gaba ɗaya cikin idon nashi kaman da hawaye a ciki, wanda ganin hakan ya sani kasa ɗauke ido na a kanshi ƙasa-ƙasa da murya naji yace,

"Fatima yaya kike jin son Babagana a ranki? Kinajin zaki iya rayuwa idan ba tare da shi ba? Kin

taɓa ji akwai ranan da soyayyan Babagana ya hana ki ci,ya hanaki bacci, ya hana ki iya jin daɗin rayuwa da kuwa?"

Juya mishi kaina nayi alaman a'a.

A hankali naji yasaka hannun shi duka biyu ya riƙo nawa hannun, kuma har zuwa lokacin idon shi yana kaina kuma ɗauke da wannan ruwan hawayen da ban gane irin shi ba, don har lokacin banga ya zubo ƙasa ba.

wanda dalilin hakan yasa na kasa ɗauke ido na akanshi, saidai duban hannun mu dana ga ya haɗa su wuri ɗaya kuma ya ƙura mun idon shi.

A hankali ya runtse idon shi, ya kuma sake buɗe su akaina yace,

"Fatima akwai wanda yake miki irin wannan son, baya iya bacci mai daɗi, baya iya jin ɗan-ɗanon abinci saidai yaci kawai, ya daɗe da daina jin daɗin rayuwa cikin jin daɗi saboda shine mutumin da yafi kowa sonki a rayuwar shi, kuma shine mutumin dana so kiyi haƙuri ki ƙara girma domin ku kasance tare, wanda hatta mahaifinki yayi na'am da shi sama da kowa da kike so, amma duk kika watsar da wannan mutumin kika ɗauki wanda ƙuruciya ke ɗiban shi, kuma wanda mahaifiyar shi baza tayi na'am da keba"

"Toh ai Hammah ni bansan shiba"

na faɗa gaba ɗaya jikina yana rawa, wanda nayi imani da Allah yana ji ajikinshi yadda jikina yake rawan.

"Fatima to ki maida hankali kinji shawaran dana baki ne? Ba son zuciyarki kawai kika bi ba?"

"Toh Hammah kayi haƙuri kaji, nasan ai zaka fi son Babagana akan shi ai?"

Matsamun yatsu na yayi da ƙarfi, wanda har sai dana jasu amma na kasa ƙwacewa, yana duba na yace.

"Tabbas nafi son Babagana akan shi, amma shi kuma nafi yaƙinin shi zai fi riƙeki saboda yafi ɗan'uwa na sonki, kuma shi bazaki samu matsala da mahaifiyar shi ba" ,

"Fatima gobe zan tafi libyah wani kashe tarzoma da zamu tafiyi har tsawon shekara 1, nasani zuwa lokacin za'ayi bikin ku, abinda ya kawoni shine na gaya miki irin son da mutumin yake miki, wanda is too late amma yaka mata ki sani, kuma duk wani abu da kike so kada kiji shakkan ƙirana ki gaya mun" ,

"Idan na isa zan ƙiraki da number na nacan"

ya miƙe ya tsaya amma har lokacin hannu na na cikin nashi wanda na rasa dalilin hakan.

A hankali ya sake ni, sannan ya miƙo mun wani laida ɗauke da wani turare iri ɗaya guda biyar a ciki yace ,

"Wannan shine turaren da nake amfani dasu wanda na daɗe da sanin kinfi kowa son ƙamshin shi, ki riƙe ki dinga amfani da shi, kuma ban amince kibawa kowa ya shafa ba, ke kaɗai nake so kiyi amfani da shi."

ya juya yayi hanyan waje yace, "nabarki lafiya kuma ki kula da kanki"

Har yasa hannu zai buɗe ƙofan ya fita nasamu bakina da cewa, "Hammah!"

ban iya ƙara cewa komai ba, shiru nayi saboda babu dalili kawai na samu kaina da yin kuka mai cin rai wanda banso ya fito ba, don bani da dalilin yin shi.

Ta kowa yayi ya dawo gaba na yana murmushi yace, "me kike so ki tambayeni? Faɗi abin da ke ranki kinji my cweet in-law"

ya faɗa fuskanshi ɗauke da murmushi.

Kallonshi nayi kaman zan saka kuka nace,

"Baka gaya mun mutumin ba? Kuma kace zaka tafi kayi 1yr baka dawo ba".

Yana murmushi yana Kallo na yace, "babu amfanin kisan wanene mutumin tunda auren wani zakiyi, babu amfanin sanin shi, damuwan Kawai dama kisan akwai wanda zai rayuwa da soyayyarki kuma har ya mutu da ita, tafiyana kuma kin damu da shi ne"?

Ɗaga kaina nayi alaman na damu.

"To kimun addu'a Allah ya dawo wa Zainab da mijinta lafiya, Allah ya dawo wa Mama da ɗanta lafiya, Babagana kuma Allah ya dawo mishi da ɗan'uwan shi lafiya"

ya faɗa yana juyawa ya fita a office ɗin.

Tunda nake rayuwa ban taɓa samun kaina awani yanayi marar daɗi ba irin wannan satin da Hammah yazo, gaba ɗaya bana fahimtan abinda yake mun daɗi a raina, don ko waya Besty ya mun baya gane kaina, haka itama Besty duk yadda tayi dani ban ce mata komai ba.

Haka kawai naji a raina da ace iyaye na zasu fahimce ni, to dana yadda da wanda Hammah yake son na aura, amma kuma idan nayi wani tunani sai naji a raina to zan iya son wani a duniyan nan bayan Besty?.

Babu yadda Besty batayi dani ba na fito muje na gaisa da Hammah Haidar da yazo wurinta, amma firr naƙi nace mata, "kije ki ni karatu na zanyi".

"Hmmm kaman da gaske wai karatu zakiyi, da ace bansan ki bane da sai ki gaya mun haka, ni nakasa gane ina kika dosa wallahi, gaba ɗaya kin ɗaga mana hankali daga ni har Besty da sabon halayen da kika tsira yanzu, ke ba karatu ba, ke ba hira da Beauty ba, na rasa abinda yake damun ki wallahi"?

Tsaki taja ta fita nidai ban ko Kulata ba, naja wayana ina so na ƙira Ummi nah amma nakasa, sai kallon wayan nake kaman ance nayi ta Kallonshi.

Ringing ɗin wayan ne ya dawo dani daga tunanin da natafi wanda bansan me nake tunani ba, baƙon number nagani kuma gaban shi da plus, kaman bazan ɗauka ba amma wata zuciyar kuma tace ki ɗauka kawai.

Sallama nayi bayan na kara wayan a kunnena, abin mamaki daga ɗayan gefen ma sai jin muryan da ban yi tsammani  a wannan lokacin ba.

cikin hanzari na tashi  zauna bakina na samu da ambatan sunan shi,

"Hamma Umarrr!" sai kuma nayi shiru na kasa gaishe shi.

Sautin murmushin shi wanda har inaji sannan yace, "Kina mamaki ne? Toh kidaina, yaya karatu and wannan ƙawarkin? Kuna lafiya ko?"

"lafiya ƙalau Hammah, ka isa lafiya? Hammah baka ƙirani ba sai yau? ina ta damuwa yayah ka isa wurin, duk hankali na a tashe Hammah"

na faɗa muryana kaman zanyi mishi kuka, wanda maganan gaskiya abinda ya tayar mun hankali kenan a wanan kwanakin wanda har aka kasa gane kaina.

Tunda yace mun wurin Kwantar da tarzoma ne, kuma banji ya ƙiraba, kawai na rasa me yake mun daɗi.

Sautin dariyan shi naji wanda ban taɓa gani ba koji yayi yace, "haba ƴan mata kada kizama raguwa mana, ba komai na isa lafiya wasu abubuwane suka sha kanmu, amma yanzu Alhamdulillah"

Ajiyan zuciya nayi nace, "Hammah na girmane?"

"Kaman yayah kin girmah"?

Haka kawai na samu kaina da ƙarfin gwiwan bashi amsa nace,

"Hammah ba kai kace mu jarirai bane"

na faɗa ina dariyar da nima ban cika yin shiba.

Daga inda yake yasa hannu ya dafe kanshi yana dariya ƙasa-ƙasa idon shi a rufe yace,

"Toh yaya zanyi dake tunda kince aure zakiyi ai nasan kin girman kenan ko?"

shima ya sake jeho mun tambaya.

Kaman yana gani na cikin shagwaɓa nake buga ƙafa na ajikin gado ina mishi kukan ƙarya wanda bansan ya akayi nake mishi ba nace,

"Hammah na nikan ban girma ba, har yanzu ni Baby ce fah"

Lokaci guda yaji kanshi kaman yana juyawa wai *BABY* sunan da yaji ya fito daga bakinta ya tuna mishi da abubuwa dayawa, a hankali yace,

"Babyn Hammah kiyi shiru na yadda baki girma ba har yanzu ke Baby ce, shike nan anbar wa Hammah kukan?"

Zuciyana naji yana bugawa da sauri domin jin yanayin voice ɗinshi, dolena na buɗe ido na domin haka Kawai nakasa iya buɗe ido na tunda na ɗauki wayan, abin haushi kawai sai naga Besty tsaye akaina ta rike haɓa tana kallo na, ban san lokacin da bakina ya furta "Besty!"

Shi kuma a ɗayan ɓangaren Hammah yayi mamakin jin kalman Besty, a tunanin shi Babagana nake nufi, da sauri shima ya buɗe idon shi domin tambayan ina inane?.

Charabb suka haɗa ido da Yusuf dake tsaye kanshi cike da mamakin dawa abokin shi ke waya har yake lumshe ido kuma yake dariya?.

"Aboki dawa kake waya haka? Kodai kafara soyayyah da watace bayan matar ka?"

hararan shi Hammah yayi yace, "Wani irin soyayyah kuma? Matar da ƙanina zai aura ne zanyi soyayyah da ita?"

Wani kallo Yusuf yake mishi wanda shi kanshi Hamman sai a wannan lokacin ya lura da ɓaran ɓaraman da yayi, bai iya sake cewa komai ba ya wuce toilet ya bar Yusuf da mamaki ya sake rufeshi, wani irin matar da ƙaninshi zai aura, Riyyah yake nufi? toh me hakan yake nufi da har yau abokin shi ke lumshe ido yana waya cikin nutsuwa koma yana ambatan Baby?

A gefen su Riyyah ma tashi tayi cikin tsarguwa tace, "Besty har kindawo ne? Hammah Umar ɗin har ya tafi ne?"

"Hammah Haidar ne ya tafi ba Hammah Umar ba, wato tsabar Besty ya ɗauke miki hankali shine kike ambatan ɗan 'uwanki da sunan ɗan'uwan wanda Zaki aura?" ,

"Besty dama ku munafukai ne keda Besty, Yabi ya ɗaga mun hankali na ƙarya wai baya gane kanki bayan hiran ku na soyayya kukeyi har da rufe ido? Wanda koni da Hammanki bama iya wanna soyayyan".

Tashi nayi na zauna ina kallonta nace, "soyayyaah kuma? Nida Hammah Umar ne fa ba Besty ba, kuma yaya zanyi soyayya da ɗan'uwan wanda zan aura?" ,

"Kawai yaƙira ne yaji yaya muke har kema ya tambayeni"

na faɗa kaman wata marar gaskiya na tashi na fita a ɗakin.

Bina da kallo tayi ɗauke da mamakin wai da Hammah nake wayan, bayan yadda tazo ta sameni

babu wanda  bazaice da wanda na shekara goma da soyayya ba nake wayan.

Juyo wa Besty tayi cikin mamaki tace, "Aunty Nice kiji wani kayan kulle kai"?

Nima Aunty Nice cikin al'ajabi nake kallon Besty nace, "kodai yana yiwa ɗan'uwan shi hirane?"

Amma bari zan binciko mana wurin miss zerks, don ta san harkan Soyayya zata iya banbanta mana, soyayya ce ko kuma taya ɗan'uwa ne?

_Haƙika anyi rashin Babban mutum, mai haƙuri, son mutane da cigabansu. *BAPPAH HAKIMI* ina ta'aziya wa masaratan Misau da dukkan legal community, Allah ya  masa Rahama ya gafarta masa zunubansa._

*KU KASANCE DA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
2019published.
*BADARIYA*

🖋®
*GASKIYA WRITERS ASSOCIARION*✍🏻
{Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da kuma lahira.}

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN KARFE* 🏇

Story and written
By
*AUNTY NICE*😘

Wattpad@GaskiyaWritersAsso.

*WANNAN LITTAFI SADAUKARWA NE GAREKI MISS XERKS*

*PAGE* 23

*____________*📖 Tun ranan da Hammah ya kirani bai sake ƙirana ba, amma duk da rashin kiran shi sai na maida hankali na akan karatuna, kuma kullum sau babu adadi muna waya da Besty nah.

Akwana a tashi babu wuya wurin Allah yau saura 1week mu fara jarabawa, gaba ɗaya hankalinmu ya koma kan karatu, don hatta su Hammah Haidar da Besty sun sarara mana da yawan ƙira, sudai burinsu mu fito da sakamako mai kyau.

Ranan wednesday muka gama jarabawar mu, kowanmu kagani ya faɗa saboda damuwan karatu.

Da wurin ƙarfe ɗaya drivern Mummy yazo ɗaukan mu, muna ta ɗauki da murna muka isa gida.

Ranan kam munyi barcin huce gajjiya, don nidai da ƙyar da akayi sallan la'asar na tashi nayi sallah, kuma sai zuwa lokacin naci abinci.

Bayan nagama cin abincin ina zaune a gefen Ummi na ina yanke farce take ce mun,

"Auta kinga irin kayan abincin da Yayan Babagana ya kawo mana kuwa? lokacin da zai tafi wancan ƙasan, ga kuma kuɗi har million ɗaya yabawa Abbanki yace baya so ko iyayen shi suji, wai Abbanki ya saya miki gado da shi, kai mutumin nan ɗan albarka ne sam baiyi halin uwarshi ba".

Tsayawa nayi da cin abinci ina kallon Ummin mu, fuskana ɗauke da mamaki sannan nace, "Ummi ni dama yana zuwa wurin Abba ne? Wancan karon ma kunce mun shi yayi gyaran side ɗinki".

"Zuwa kai" inji Ummi sannan ta cigaba da mun bayani, "auta ai yafi mai neman naki zuwa gidan nan, mutumin da idan yazo sai su wuce awa biyu zuwa uku shida Abbanki, gashi duk yanda Abbanki yayi yaron nan sai ya taimaka mishi, don yanzu gaba ɗaya karatun Sadiq shi yake biya".

Ummi tana gama mun wannan bayanin ta tashi ta shige kitchen domin ɗaura abincin dare, don tace yau na huta zatayi.

Duk jikina a sanyaye dajin bayanin da Ummi ta mun, ɗaukan wayana nayi na ƙurawa number shi ido ina mamakin abinda ya hana shi ƙirana.

Can na ce, " Ummi to da yatafi kuma suna waya da Abban"?

Fitowa tayi daga kitchen ɗin hannunta ɗauke da rober ta miƙo mun kuɓewa na yanka mata, ta nemi wuri a gefe tana gyaran kifi tace mun,

"Jiya ma ai ya kira Abbanki sun daɗe suna magana, har maganan dawowan ki yau naji suna yi, ai yaron ɗan albarka ne sose"

Satinmu uku da dawowa gida hutu wanda yayi dai-dai da saura sati ɗaya mu koma school, da yamma Mummy da Adda Hummy suka shigo garin Bauchi wanda suka taho da sayayyan da sukayi na auren mu, kuma da kayan auren Yaya Kamal da aka haɗo a can.

Washe gari da safe Adda ta ƙirani akan mu harhaɗa kayan a jakakkunan su, kusan set biyu ko

wanne mai biyar, wayyo kaya kam ba'a maganan yawansu da kyaunsu.

Da yake Adda Hafsat ma ta biyo su da suka sauƙa a kanon, acan kuma Adda Umaimah ma tazo, saidai tunda ta zo take kwance a ɗakin Mummy babu abinda ta ke iya tsinanawa saboda wani irin laulayi mai wahala ta keyi, Adda Hafsat ce ba za kace ma tana da wani ciki ba, kuma a lokacin ma ya kai 4month zuwa 5, amma kaman babu komai, haka mukai ta shirya kayan.

A store kuma Mummy ce da masu aiki taje nuna musu inda zasu sauƙe namu sayayyan.

Bayan mungama saka kayan ne muna ta hiran kyan kayan saiga Yayah Kamal ya shigo palon, wanda ban taɓa tunanin yazo garin ba, ashe tare da su Mummy yazo.

Adda Hummy ce ta kalle shi tana dariya tace, "ango zo kaga irin bajintar da Mummyn ka ta maka, don alama ya nuna Mummy ashe rufah-rufah take mana, yanzu ne na fahimci tafi ƙaunar ka akan mu, don komai ta ɗaga sai tace zaiyi kyau da matar ɗana"

ta faɗa tana dariya wanda dukkansu palon dariya sukeyi.

Shima cikin takun shi na barazana ya shigo ya zauna face ɗinshi ɗauke da murmushi yana duban Mummy yace,

"Mummy ai nasan bata da wanda ya wani cikin ƴaƴanta tun ba yau ba, kallon ku kawai na keyi ana wani cewa wai Umaima da Hafsat ne gwanayenta, ni kuma nasan ba haka bane ko Mummy nah" Ya faɗa yana dafa kafaɗanta.

Dariya tayi tace, " hakane yaro na, don nafi gadara da kai, sukuma na gidan wasu ne, kai kuma da kai da matar ka da yaranka duk iko nane, sai yadda nayi da ku" ta faɗa tana buɗe mishi kayan.

Kallo yakeyi yana murmushi ya dubi Adda yace, "kaman kinsan yanzu daga wurin Fauzy nake, tana gaya mun wai best colour ɗinta Blue ne, gashi ko duk yawancin kayan mai Blue kuka saka, nasan zataji daɗi wallahi, Adda mun goggode fa da ɗawainiya".

_Hmmm ko kallona fa baiyi ba_, na faɗa a zuciyana Lokaci guda sai naji abin bai mun daɗi ba, tashi nayi nace, "Mummy bari naje gida zan taya Ummi aiki".

"Okay Auta sannunku da aiki" Mummy ta faɗa fuskan ta ɗauke da farin ciki, haka na fita ko jiran Besty banyi ta mun rakiya ba na fita na bar gidan.

*****

Ranan saturday aka kai kayan Fauzy Alkaleri, mu kuma sunday muka koma school, duk yadda naga Yayah Kamal yana so ya ritsani sai na kauce wa wurin don bazan iya ɗaukan raini ba.

Bayan mun koma ne muna kwance nida Besty take cemun,  " ashe Besty ya tambayeki best colour ɗinki dasu size ɗinki ki kaƙi gaya mishi? amma kin ban kunya har saida ya tambayeni? Kenan inaga idan anyi auren ni zan dinga gaya mishi irin cefanen da kike so ko?" ta faɗa tana harara na.

Tashi nayi na zauna ina dubanta nace, "Besty fa bayida kunya ne, cemun fa yayi wai gaya mun size ɗin bra ɗinki dasu pant, ni kuma na kashe wayan, to ke idan Hammah ya tambayeki zaki iya faɗa mishi ne"?

Kallo na takeyi sheƙeƙe sannan tace, "na yaushe? Ni ai har mun wuce wurin domin Aunty har ta fara haɗa kayan, colours ɗin dana keso na gaya mishi, ni hatta irin night wears dana keso na tura mishi, ke har turo mun yake yi ina zaɓa".

Ta sake kallo na dana buɗe baki ina kallon ta tace, "idan ma zaki ɗame to ki ɗame, don namiji duk yadda ka mayar mishi da kanka haka zai bika, idan kika maida kanki local haka zai ɗauke ki, idan kika nuna mishi ke mace ce haka zai ɗauke ki, ni yanzu hatta kayan daya ke sakawa ni nake zaɓa mishi bari kiji bayani yarinya."

Haka na bita da kallo ina mamakin wayewa irin na Besty, tana hararana tace, "gara ma ki gyara don wannan surakarkin idan baki riƙe mijinki ba tun yanzu, zuwa zatai tana miki chefane naga alama"

Nima Aunty nice nace, " Hakane fa rayuwan da gaske, don mazan yanzu duk yadda kike haka zasu biki, Mata gara mu gyara don shi rayuwa da miji ɗan kissa ne, bawai ki cuce shi shine kissa ba, a'a wannan mugunta ne da zalunci, amma kisan right ɗinki da Kuma yadda zaki zauna dashi lafiya shawaranku ɗaya ai shine jin daɗin"

*KU KASANCE TARE DA ALƘALAMIN AUNTY NICE A SHAFI NA GABA* ✍🏻✍🏻✍🏻
2019.
*BADARIYA*

✍®
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION*
{Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da kuma lahira.}

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN ƘARFE* 🏇

Story and written
By
*AUNTY NICE* 😘

*WANNAN LITTAFI SADAUKAR NE GAREKI MISS XERKS*

*{Ina Gwanar wasu don ni ga tawa Gwanar, Alal haƙiƙa INAWURO, Gaskiya Writers wannan shafin kyauta Aunty Nice ta baki domin jin daɗin irin comment ɗinki, kisani kina cikin ran Aunty Nice dare da rana*}

*PAGE* 24

*___________*📖 Bayan mun fito daga lectures ne Mummy ta ƙira wayan Besty take cemata, "Auta an turo daga gidan su Haidar ranan Friday zasu kawo kayanki fa" Mummy ta faɗa tana dariya.

Bestyn ma dariyan takamayi tana, "kai Mummy ai nasani, tun last week ya gaya mun shine nace ya bari sai ranan Friday, idan yaso saturday sai mu shigo mugani".

Nidai kallon Besty kawai nake ina mamakinta, bayan sun gama wayan ne ta juya tana kallona tace,

"Besty ran Friday fa zasu kai kaya, mukuma saturday sai mu shiga ko?"

"Duk yadda kikace Hakima haka za'ayi"

na faɗa ina dubanta sai wani kauɗi ta keyi tana ta waƙoƙinta.

Ranan Saturday muka shiga gari babu inda muka tsaya sai gidansu Besty, gudu-gudu muka shiga gidan a palo muka haɗu da Mummy zata fita.

Kallonta Besty ta keyi tace, "Mummy ina zakije kuma? bayan munzo."

"Zanje mu duba Umaimah ne ɗazu wai suka dawo a asibiti, yanzu zamuje nida Ummin ku, ku shiga kawai sai mun dawo ku sai kuje".

Tana fita muka rufe ƙofan gida muka wuce ɗakin Mummy, muna shiga mukaci karo da akwatuna set biyu, ɗaya pink ɗaya kuma wani orange mai kyaun gaske.

Kallon Besty nayi saboda mamakinta nakeyi, duk colours ɗin jakakkunan da take so nagani a kwance, ita kaɗanta ta kwashe da dariya tace, "I Luv U Hammah my Luv".

Ƙiran wayan shi tayi muna buɗe kayan, duk abinda ya mata kyau sai ta bashi labarin abun, nidai sai mamakin shi nakeyi, don jin irin dariyan  da yakeyi kaman bashiba,  ita kuma sai kwaɗa shi takeyi na irin ƙoƙarin daya yi kaman wata tsohuwar mata, shi kuma sai wani wage baki yakeyi.

Nidai rabuwa nayi da ita kawai nake ta kallon kayan, jakan kayan bacci muka buɗe, abin mamaki kawai sai naji muryan Besty tana cewa,

 "My luv kaga wannan red nighty dana tura maka? Kaga kyaun da yayi kuwa?"  ta faɗa tana wani rawan jin daɗi.

Biyeta kawai yakeyi suna zuba chaftan su.

Muna gama gani muka hau gadon Mummy muna ta bayanin yadda kayan yayi kyau, Besty tana ta faɗa mun irin ɗinkunan da zamuyi.

Kallona nayi tace, "Besty yanzu yaushe kukayi za'a kawo naki saboda 3month kaman yau ne, gara mu fara maganan ɗinkuna"

Muna cikin hiranmu mukaji tsayuwar motan Mummy, da sauri muka fito Besty ta buɗe ƙofan muka tarye su, Ummi ce a bayan Mummy suka shigo palon.

Hira akayi akan ciwon Adda Umaimah, Mummy tana cewa,

 "harda raki fa a ciwon Umaima, don wallahi halinsu ɗaya da Addan su Humairah wurin raki".

Saida akayi sallan magarib tukun nida Ummi muka wuce gidanmu, inda muka samu Hammah Walid da Hammah Bappah sunzo ga Hammah Sadiq ma, gaba ɗaya sai naji daɗi a raina domin rabon danaga Hammah Walid na daɗe.

Muna sallan isha'i na ɗauka mana abinci zuwa palon waje,  anaci anata hira can sai Hammah Walid yace mun,

"jiya munyi waya da Umar yake cemun me kuke shiryawa ne ta fanninki? amma bance mishi komai ba saboda wannan mu yakamata mu miki duk abinda kike so ko Autan Ummi?".

Nidai murmushi kawai nayi ina kallon Ummi, bance komai ba, shima dariya kawai yayi ya cigaba da cin abincin shi.

Washe gari mukaje gidan Adda Umaimah muka duba jikinta, tunda mukaje ta saka mu aikin gyare-gyaren gidan, bamu muka gamaba sai da akayi sallan azahar muka dawo gida.

Ana sallan magarib Hammah Walid suka mayar damu school bayan sun mana shooping shida Hammah Bappah, wanda shirun shi har yafi na Hammah Walid.

Muna hira da dare wurin 9:00pm sai naji ƙiran Besty, bayan mun gaisa yake tambayana, "don Allah Besty ki faɗa mun wasu colours jaka kike so, don gobe Aunty Fannah zasu ƙarasa sayayyan su, tun ɗazo take tambayana wallahi".

Ina dariya ƙasa-ƙasa nace, "Besty toh purple nakeso"

 shima dariyan yakeyi yace, "ni kuma nace a haɗa da Navy Blue, don kinsan Hammah nah 2ml ya turo mun yace na haɗa miki kaya na kece raini."

"Besty gaskiya Hammah yana ji damu sosai,muma yakamata mu bishi da addu'a"

 ya faɗa yana nuna jin daɗin shi.

Har 11:00 muka kai muna ta shan hiran mu, muna sallama na tashi na shiga toilet nayi wanka na ɗauro alwalah, bayan na dawo ina saka kayan bacci naji wayana yana kuka, da sauri na ɗauki wayan abin mamaki sai sunan Hammah Umar na gani akai, da sauri na juya ina kallon Besty data yafe acikin gadonta ta shige net tana ta waya da Hammah Haidar bata san me na keyi bama.

Ina ɗauka na haye kan gadona ina masa sallama, dukkan mu mukayi shiru babu wanda yace wa kowa komai, sai can naje yace,

"Babyn Hammah me kikeyi bakiyi bacci ba har yanzu?"

a jiyan zuciya nayi sannan nace mishi,

"Muna waya ne da Besty shiyasa ban kwantaba"

na faɗa batare da nayi tunanin komai ba, shiru yayi har zuwa wani lokaci sannan yace,

"ashe hiran luv kikeyi? to bani labari me yafaru"?.

Gaba ɗaya sai naji kunya yakamani, kuma lokaci guda naji wani farinciki ya lulluɓe ni.

"Hammah baka ƙirana"

na faɗa ina mishi muryan kuka.

Shima muryana ya kwaikwaya yace, " Babyn Hammah kema baki taɓa ƙiran Hamman kiba, kawai kin manta dani"

dariya na farayi ina cewa, "kaine fa kamanta dani, bayan kana ƙiran kowa nine baka ƙira".

Muryan shi naji yana cewa, "wa nake ƙira kikaji?"

" hmmm kaji Hammah bayan Ummi tace mun kana ƙiran Abba, kuma Hammah Walid ma yace mun kana ƙiranshi"

na faɗa ina mishi shagwaɓan da bansan na iya shiba.

Dariya yayi yace, "Baby problem, to su basu ce miki suna ƙirana bane? amma ke shiru kawai kika ƙi ƙirana duk kin manta dani ko"?.

Ban fahimci komai ba kawai sai nace, "Nifa Hammah kullum tunaninka nakeyi har kasa bacci nakeyi, gashi lokacin muna karatun exams, ina ta tunanin ko yayah kake? Hankali na bai kwantaba har saida muka dawo gida  Ummi tace mun kunyi waya da Abbah na tukun hankalina ya kwanta."

Murya can kasa naji yace,

" Babyn Hammah kema kina missing ɗina sosai ko?"

Rufe ido na nayi da sauri nace, "Ehh mana Hammah, kaman zan tambayi Besty fah"

"toh meyasa baki kirani ba"?

Shiru nayi sai can nace,

"ina jin tsoro ne"

"tsoron me kuma zakiji bayan Hammanki zakiji lafiyan shi, ni ai fushi nayi da ke"

ya faɗa yana muryan irin shagwaɓaɓɓun yaran nan.

Dariya nayi nace , " to ai ban san me zance bane".

Shima dariyan yayi yace, " ai sai ki ce.............

Da sauri ni Aunty Nice jiki na na rawa na matso don jin me zai ce mata, inaji na juya na kalli Besty da take ta kallon ta tana riƙe da haɓa, don mamaki takeyi, nima sai na riƙe haɓa don jin abinda Hammah ya faɗa.

*KU KASANCE DA ALƘALAMIN AUNTY NICE, DOMIM JIN ABINDA HAMMAH YAKE FAƊI*
✍🏻✍🏻✍🏻
*typing🤳.*

*BADARIYA*

®✍
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION* ✍🏻
_{Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da kuma lahira.}_

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN ƘARFE* 🏇

Story and written
By
*AUNTY NICE* 😘

*WANNAN LITTAFI SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS.*

*PAGE* 25

*__________📖* Sai kuma yayi shiru yana dariya, "sai nace me Hammah"?

"Babu komai Yaya exams? Ina fata dai Babagana ya barki kinyi karatu sosai ko?"

Dariya nayi cikin jin kunya nace, "ya bar ni sosai ma"

shima dariyan yayi sannan yamun sallama yace na gaida Besty Feenah ta.

"Kinaji ko Fannah ban yadda aje wani haɗa kayan nan ba, domin auren nan fa idan ina numfashi bayin shi za'ayi ba, gara ma kada ku wahalar da kanku"

Mama ta faɗa kaman zata fasa wayan ta samu Aunty Fannah da take gaya mata maganan tafiyanta Dubai haɗa kayan Babagana dani.

"Hmmm" kawai Aunty Fannah tace zuwa can ta buɗi baki tace,

"amma dai kinsan bazan ƙi zuwa aikan da Yaya yace naje ba ko?"

Mamace cikin wani tunzuran tace, "Inace dalili na yazama Yayan na ki ko? To ni nace babu wanda ya isa ya sakani haɗa zuriya dasu Fatima gara ma kiji da kyau Fannah"

sannan Mama ta kashe wayan gabaki ɗaya.

Aunty Fannah bin wayan tayi da kallo tana mai mamakin halin ƴar'uwarta ta, can kuma sai ta ƙira Aunty Falmata tana gaya mata yadda sukayi da Mama.

"Rabu da ita Fannah ai yaranta ne bana wani ba, idan taƙi ya auri wannan yarinyar ai zai auro wacce bata sani ba, ni fitinar Yaya Zahra ya ishe ni, nidai ina tsorata mata taje ta mutu ayi babu ita"

ta faɗa tana jan tsaki.

Aunty Fannah haka ta ajiye wayan ko ajikinta ita dai babu wanda ya isa ya hanata zuwa haɗa kayan nan.

Da yamma muna zaune da Ummi nah a ƙofar kitchen ina tayata aikin abinci dare, sai take bani labarin abinda Mama taje har side ɗin Aunty tamata akan maganan auren mu da Besty.

Ina kallon Ummi da mamaki ɗauke a fuskana nace, "Ummi kuma Aunty ta barta bata gayawa Baban ba? wallahi tama samu an barta ne take abinda taga dama"

"hmmm kedai bari, ai ƴan uwanshi daga jama'are suka ɗauki mataki akai, inaga har wannan sister shi dake aure a Abujan nan tazo anyi babu daɗi da ita, dama lokacin tana gari, kuma Kakansu yace idan ta ƙara shiga side ɗin Auntyn ku, toh tabbas shi Baban su ya sauwaƙe mata, hmm anyi abu fa babu daɗi wallahi, ni har auren ya fita mun a raina auta"

Jikina a sanyaye nace "hmmm" kawai, dai-dai lokacin mukaji sallaman su Besty da Fauzy, suna shigowa da murna nake tarbansu, bayan sun gaida Ummi naja su muka wuce palon Ummi nah.

Friedge na buɗe na basu zoɓo mai sanyi, na zauna ina kallon Fauzy yadda take ta bawa Besty

labarin telan da Aunty Fatima'n su ta bashi ɗinkinta a Abuja ya mata, tana cewa,

"hmmm sis Kinga wasu gown daya sauƙe mun? Wayyo telan ya haɗu wallahi, dama Hammanki ya yadda akai miki naki ma can wallahi"

ta faɗa tana ɗaukan cup dana zuba mata zoɓo a ciki.

Besty tace, " to sis yaya zanyi? Sweet Hamma na yace kano zai kai mun, akwai wata mata da take da wurin ɗinki a kano, wurin ya haɗu, don har yaje yayi boocking zai kaimata, kuma Adda ma dana gaya mata tace wurin har daga Abuja ake kawo mata ɗinki domin haɗuwan shi, kinga ai ban isa nace wa Husby na a'a ba ko?"

ta faɗa tana wani rausayar da kai gefe kaman tana gabanshi, hannu Fauzy ta kawo muka tafa tana cewa,

"Wai Besty'n Sis zakuyi fama da wannan yauƙi da iyayin matar Yayankun"

ta faɗa tana riƙe hannu na, sannan ta jeho mun tambayan ni kuma idan an kawo nawa kayan ina zan kai ɗinki?.

nidai har ga Allah ina magana ne amma bansan ina yanga a magana naba, amma babu hali nayi magana sai mutane sunce ina yanga, kawai dai inaga a jinina yake, kallon ta nayi nace, "duk yadda Besty nah ya ce, haka zanyi".

shewa suka saka suna tafa hannu, Fauzy tana kwai-kwayon yadda nake magana, ita kuma Besty tana ce mata, "indai kwai-kwayon Besty nane zaki gaji don ni har na saba da yanganta"

nidai hararan su kawai nayi, na canja mana yanayin hiran namu, wanda duk na shirye-shiryen auren mu ne.

Batare da Aunty Fannah ta damu da masifar da Mama take mata ba, suka tafi Dubai tare da Aunty Falmata wanda itama tazo dai-dai da lokacin zuwan ta sari, sai suka tafi tare.

Ranan sunday jirginsu ya sauƙa a ƙasar mu tana Nigeria mai girma da daraja cike da nasararori.

Zuwa laraba Babagana ya sauƙa a garin kaduna gidan Aunty Fannah domin yaga irin sayayyar da Aunty ta mishi, domin yasan idan suka isa bauchi bayida ikon ganin su.

Lokacin da Aunty ta fito mai da kayan kasa magana yayi, sai kaɗa kai kawai yakeyi yana zaune kusa da ita.

Kallonta yayi yace, "Aunty yaya set ɗin akwatin naga sun ƙaru?  Ba da kince set biyu za'ayi ba, kuma naga har set uku?"

Tana dariya ta buɗe mishi wani set mai colourn Navy blue tace,

"wannan shine kuɗin da kabani to ga kayan dana saka a ciki"

bayan sun gama ganin wannan kayan wanda ko shi aka kaiwa mace to ya ishe ta nunawa sa'a, sai ta buɗe wanda yake Ash tace,

"wannan kuma kuɗin da Babanka yabani ne yace na haɗa maka nashi gudumawan"

ta rufe ta buɗe Purple ɗin tace, "Wannan shine na ɗan'uwanka wanda ina can ya ƙara aiko mun wasu kuɗin domin a saya maku kaya masu matuƙar kyau da burgewa"

Baki ya buɗe yana mamakin wani irin kuɗi Hamman shi ya bayar haka? wanda gaba ɗaya babu kayan daya kai na cikin wannan set ɗin kyau, sannan sai wasu guda biyu, ɗaya baƙi ta buɗe

tace,

"wannan kayan uwa da danginta ne, wannan kuma kayan uba da dangin shi ne, wannan kuma ni na haɗa wa ɗana nawa gudumawan"

ta faɗa tana buɗe mishi yana kallo.

Rungumeta yayi yana,
" wayyo my best mum, me zance miki Mumcy nah?"

Tana dariya tace," addu'a da kuma biyayya, nidai fatana Babana duk yadda Mamanka zatayi kada ka yadda ka kamata rashin kunya ko kuma kabari matarka ta raina ta, don uwa uwace ko yaya halinta yake kaji my son".

Idon shi yana kan kayan yace, " insha Allahu Mumcy wallahi bani da wani buri irin naga na kyautatawa Mama wallahi, kuma insha'Allahu zanyi haƙuri da komai dazai faru na mata biyayya, har sai ranan da zata fahimci gaskiya"

Haka sukayita hiransu wanda washe gari yabi jirgi ya koma lagos.

Aunty Fannah ce ta ƙira mahaifiyar su Ummah ta gaya mata ya kamata ta taho bauchi domin a kawo kayan tana nan, domin ganin idonta zai sa Mama ta bar wani bala'in, haka suka saka rana Umma zata taho washe gari kuma Aunty Fannah ta taho da kayan.

Aunty ce ta shigo gidan mu yau da yamma ita da Goggon Bauchi don su duba Abba nah da baiji daɗin jikin shi ba, kwana biyu yayi fama da zazzabi.

Suna zaune naji Aunty tana basu labarin jiya Aunty Fannah ta taho da kayan aure na, hauka ne

kawai Mama bata musu ba agidan har saida Ummanta tace zata tsine mata tukun tayi shiru.

Aunty tana dariya tana kallon Goggo tace, "ni Adda abinda yaban dariya ma, sai cewa take irin wannan kuɗi da ɗanta ya kashe wai asiri muka mishi, amma daga gani ba'a hayyacin shi yake ba, idan kinganta kaman mahaukaciya ƴan aiki sai leƙowa suke suna ganinta".

Tsaki Goggo tayi tace,  "Zata sha mamaki kuwa sai tayi kuka da idon ta don Babagana sai ya haukace akan son Auta"

ta faɗa tana jan tsaki don ita haushin matar take ji sosai.

Abba ne ya dube su yace, "Don Allah ku rabu da su kodan Albarkancin son da ƴaƴanta sukeyiwa jininku, wannan ma kaɗai ya isa mai hankali tunani, ita babu abinda ta tsana a rayuwarta irin Fatima da ƴan'uwanta, sai gashi ƴaƴanta kuma duk suna son Fatima da zuriyarta tun suna ƴan yara, wanda har takai suna son haɗa jini da ita, toh meya saura? Kuma son da ɗan'uwan shi Babaganan yake mana da ita Autan inaga koshi mai auranta baya mana, saboda haka aniyarta ya bita mu munyiwa ɗiyarmu tarbiya mai kyau wanda zata riƙe aurenta da daraja babu asiri, kuma zata mata biyayyan da ko ɗan cikinta bai mata ba insha Allahu"

Aunty tace, " insha'Allahu ai tama fara gani ina cewa surukuwarta ta matsayin ƴa take mata amma ta kasa mata biyayya, zama da ita ma taƙi yi babu yanda bata yiba su zauna amma firr taƙi kuma uwarta ta goyi bayanta, duk da shi Umar ɗin yace ta zauna a nan wurin Mahaifiyar tashi amma suka ɗaga hankalinsu sai da Babansu ya saka baki ta tafi wurin uwarta, amma jiya da tazo da kakasu kaman zata cinyeta ta manta duk laifin da ta mata."

Goggon Bauchi tace, "ni wallahi ƙiyayyar da takeyiwa Auta shi yake damuna gata da haƙuri haka zata je tayi ta mata halin iyayen miji" ta faɗa tana nuna ɓacin ranta a fili.

Abba ne yake dariyan su yace, "haba Aisha ai babu abinda zai faru insha'Allahu, kudai kawai kuyi Addu'a wa ɗiyarku kusaka haƙuri a zuciyarku, don kowacce mace da irin jarabawarta, wata ta rasa miji na gari wata tayi rashi dace da uwar miji, wata da ƙannen miji, kowa dai da yanda yake zuwa mata, sai da kawai Addu'a"

Ita dai Ummi nah sai aikinta kawai ta keyi bata ce ko uffan ba, har saida Aunty tace mata,

"ke kam wallahi Ummin su halinki sai ke, ace duk hankalin mu atashe da yanayin da Auta zata samu kanta amma ke ko ajikinki? Ko kula mu bazakiyi ba?"

ta faɗa tana kallon Ummi nah da take fitowa daga kitchen.

Dariya Ummi tayi tace, "toh ni meye nawa aciki bayan ga kunan, kuma ma yadda nayi imani da Allah yadda bata ci galaba akanki ba to haka akan Auta ma babu abinda zai faru da hukuncin Allah, wanda tun bata zo duniya ba bakinmu yake ɗauke da addu'a akansu, yanzu kuma da muke tare dasu kullum addu'a ne tsakani mu dasu, insha'Allahu Auta idan ta riƙe mijinta tsakani da Allah da ƴan'uwanshi daku iyayenta inaga bata da Matsala, ƙiyayyar uwar miji ko ba kanta farau ba, don wata ko sanin wanda ɗanta zai aura bata yiba amma ƙiyayyarta ke zuciyar ta, kawai addu'a zamu mata Allah ya dai-daita tsakaninsu".

Ta faɗa tana wucewa palo inda nake zaune na ke ɗura mata zoɓo a goruna.

Abba ne yayi dariya yace, "kinji damo sarkin haƙuri, Babu komai Aisha da Fatima kutaya mu da Addu'a kawai"

haka suka gama hiran su Aunty ta ɗauki Goggo domin ta kaita gidanta ,ni kuma take zolayana wai nafara surkunta naki zuwa mata hutu, haka dai muka rakata ina ta dariya bance nata komai ba.

Besty ne yake cemun idan an kawo kayan da sati zaizo bauchi insha'Allahu don ya daɗe bai ganni ba , nima kuma naji daɗin hakan da yace mun don saura kwana goma sha ɗaya mu koma school.

Bari muda kace su muga kawo kayan ko yaya za'ayi, domin dai Mama tayi alwashin babu mai kai wannan tulin kayan, don tace kona Umar ai bai kai haka yawa ba don kawai kowa baya bin bayanta, amma gashi duk alamu ya nuna asiri Iyayen yarinya su kayiwa ɗanta hatta da iyayenta akan baƙar yariya.

_KU KASANCE DANI AUNTY NICE DOMIN CIGABA DA JIN YADDA ZATA KAYA TSAKANIN MAMA DA MASU KAI KAYA._

```KARKU MANTA DAN ALLAH KU DANNA ƘARAMIN TAURARON DAKE ƘASA, TA HAKAME ZAKU NUNA MIN ZALLAR SOYAYYARKU.```
comment nd share plsss.

*DAGA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
2019
*typing✍🏻°•°*

*BADARIYA*
```

®☄️
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION* ✍🏻
_{Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da kuma lahira.}_

🎐G•W•A🎐
_*GASKIYA DOKIN ƘARFE*_ 🏇🏽

Story and written
By
*AUNTY NICE* 😘

_*WANNAN LITTAFI GABA ƊAYA SADAUKARWA NE WA MISS XERKS.*_

*PAGE* 26--27

*___________📖* Tunda garin Allah ya waye Mama take ta musu hali amma daga Aunty Fannah har Baba babu wanda ya kula ta, gara ma Aunty Falmata tace,

"Yaya abinda kike mana fa tun zuwan mu jiya kinga babu dole ni sai nai wucewata , dama lagos zanje duba kaya na da suka iso, saboda kai kayan nan ne yasa ka na haƙura, amma tun jiya sai gaya mana magana kikeyi, gaskiya ni babu dole a wurina idan baki bar ɗan naki yayi aure da wanda yake so ba, ke zaki zauna da shi?"

ta faɗa tana hararan Mama.

Umma ce ta dube su tace, "kada na sake jin muryan ɗaya daga cikin ku idan ba alkhairi zaku faɗa ba".

ta juya ta cigaba da wuridinta inda Nabeel da yake kwance kan cinyar Aunty Fannah.

Aunty tun wurin ƙarfe takwas na safe ta taho gidanmu domin su haɗu akan aikin taryen baƙin, duk da komai ma sun bayar ne ayi musu, samosa ne da cake Besty da Adda Umaima da Aunty Ladidi sukeyi a gidan su Besty, wanda nima tun safe na shiga gidan.

Ƙarfe ɗaya na azahar su Hajiya Addayo ƙanwar Baba suka iso daga Jama'are su uku, ita da babbar ƴarta da kuma wata cousin ɗinsu matar chairman ɗin jama'are, babu wani karɓa na arziki da Mama ta musu sai wani sauƙe musu baƙar magana da takeyi.

Ganin haka Baba yasaka Aunty Fannah ta rakasu side ɗin Aunty inda su Gidaɗo suke zaune shida Khalifah suna ta kallo a palon Auntyn.

Da murna Gidaɗo ya karɓe su ya wuce dasu can palon Aunty, ita kuma Aunty Fannah ta koma ta haɗo musu abinci ta kawo musu side ɗin, inda ta samu Baba yana zaune cikin su sai hira sukeyi.

yana tambayan su yaya jikin babbar Addan su wanda take fama da diabities.

Ana sallan la'asar ƴan gidan wazirin jama'are su biyu suka iso a wata arniyan mota kaman wani jirgin ƙasa, sai sauƙe ƙamshin turare kawai sukeyi, ko gefen Mama basuje ba saboda sunyi waya da Hajiya Addayo ta gaya musu inda suke, bayan sun gama gaisuwan yaushe gamo n Aunty Fannah tace,

"su fito su wuce kai kayan"

inda babu ɓata lokaci suka wuce.

Duk yadda nayi da Besty akan mu zauna nida ita agidan amma firrr taƙi tayi wuce wanta gidanmu ita dasu Adda, babu yadda na iya dole muka cigaba da wayanmu nida Besty kaman zamu lashe junan mu don so.

Tunda aka shiga gidanmu Zainab take ta wani yatsine-yatsine irin gidan bai mata ba, babu wanda ya damu da ita, dama suma ƴan'uwan Baba ko gaishe su batayi ba haka suma ko cikanki babu wanda yace mata.

Bayan an gama buɗe kaya ne sai Aunty kece mata, "Zainab ina kika baro mana maigidan namu? Ko dan yau yaga mata iri-iri ne ya hanashi zuwa inda nake?".

Aunty ta faɗa tana dariya.

Ita dai Zainab ɗan yamutsa fuska tayi kaman mai jin warin kashi tace, "yayi bacci ne shiyasa na bar shi wurin Mama".

Ganin abinda tayi sai Hajiya Addayo tacewa Aunty, "ai kawai Fatima wannan mijin ki barshi wa Zahra, ke kuma kiyi fatan matar Babagana tana shiga ta sulluɓo mana namu maigidan wanda ya iya gaisuwa da cefane, don nasan zai iya damu dukanmu, ba irin wanan da bai iya gaisuwa bama ballantana aje ga maganan chefane ba".

Ta faɗa tana duban Aunty.

Aunty Fannah ce tace,

"haba Addayo ai ni nariga ku na wurin Babana domin har mun tsayar idan an haifa mun mijin ni zan yaye abina ma, saboda haka ku kuji da Nabil duk kan ku".

ta faɗa tana maida jakan gabanta tana rufewa.

Gaba ɗaya dariya sukayi suna cewa,

"lallai wannan tun baizo duniya ba matan sun mishi yawa, shidai Nabil yayi bandaro".

haka suka gama rahar su Aunty Falmata ko ƙala bata ce musu ba har sukayi sallama.

Kaya ba kaɗan ba su Goggo suka basu na tukwici wanda har saida sukayi maganan abin yayi yawa.

Aunty tace musu, "babu komai ai haka al'ada yake".

suka rakosu har jikin mota kowa cike da farin ciki.

Suna tafiya Besty taƙirani akan nazo da sauri naga tulin kayana, amma dajin abinda tace kawai sai na kashe wayana ban saurare ta ba har saida Aunty ta ƙirani da kanta tukun na fito.

Kayane kaman an buɗe shago a baje a palon Abba nah, kowa sai faɗin albarkacin bakin shi kawai yakeyi daga yanayin kyaunsu har yawansu abin burgewane.

Hajiya Addayo suna komawa motan su ya wuce dasu jama'are ko takan Mama basu bi ba.

Da Gari yawaye daga Aunty Fannah har Aunty Falmata suka wuce, inda Umma tace, "ita sai Falmata ta dawo sai su wuce".

Babu yadda Zainab ta iya dole ta zauna har sai Mamanta ta dawo su wuce acewarta.

Umma kuma da Besty dama sun shirya babu inda zataje har sai yazo yaga yadda ta kaye mishi shi da Mama.

Bayan kwana uku da kawo kaya saiga Besty da Aisha Trouble niƙi-niƙi da cikinta sun shigo gidanmu da yamma, haka na tarbe su har ɗakin Ummi nah, ina ta kallon trouble yadda cikinta

yayi ƙato kaman bana fari ba.

Hararana tayi bayan sun gaishe da Ummi, ita kuma ta fita tabarmu, samun wuri nayi na zauna ina cewa, "trouble haka kika zama?........"

Itama tana harara na tace,

" kuma kaman yau ne idan kuka ci karo da yaren novel duk zakuyi bayani, ina da ƙarya kuke mun sai kunga ƙarshen paper da biro ko? To yanzu kam zaku haɗu da biron a ɗakin auren Ku".

ta faɗa tana mana dariya.

Kallonta nayi nace,

"haba mukan ai jarirai ne, idan munje zasu ƙyale mu har sai mun gama karatu ko Besty?"

na juya akalan maganan nawa kan Besty.

"Hala haka kukayi keda Besty'n ki, domin dukkan ku yarane babu abinda kuka sani, amma nikan Hamma na a matse yake, babu wani ɓata lokaci zai fara buɗe mun babin falle-falle, ni kuma ina hadda babu sanya".

ta faɗa ko dariya babu a fuskarta.

Trouble ne takai mata hannu suka tafa tace, " kina basu assignment Feenah gara ki ɗauki babin babu wasa, ita kuma tsageriyar barta tayi ta nuƙu-nuƙu muna ganinta mun san komai ƙyaleta mukayi".

tashi Besty tayi tacewa trouble, "rabu da ita muje kiga kayan, don wanan har saita fiki iya shege a babin"

.

Tun da akayi magarib Hammah Sadiq ya iso Bauchi ranan daɗi kaman zan yi yaya, dama mun daɗe bamu haɗu ba gashi nayi missing ɗin zolayan shi kwana biyu, aikuwa yana zuwa muka fara faɗa, inda ya dage wai sai ya ɗauki turare ɗaya akayan, ni kuma nace bai isa ba, ita dai Ummi ko kula mu batayi ba, haka mukayi tayi, dole a ƙarshe nace zan bashi wani turare mai daɗi tukun ya yadda.

Ranan Friday wurin ƙarfe goma da rabi Besty ya iso bauchi, babu inda ya tsaya sai ƙofar gidan mu, babu yadda na iya haka na fita wurin shi, don nayi-nayi ya shigo yace a'a gida zai wuce kawai ya iso ya fara ganin face ɗinane farko, yayi wani irin ƙiba da fari gaba ɗaya sai naga kaman ba Bestyn dana sani bane, duk kunyan shi ya ishe ni, Haka yamun sallama bayan mun gaisa akan zuwa dare zai dawo.

Wurin Baba ya fara zuwa suka gaisa, tukun ya shigo side ɗin Mama, inda ya tarar da Umma da Mama da Zainab a palon suna breakfast, gudu -gudu ya shigo ya rungume Mama yana, "Mama na nayi missing ɗinki sosai".

Tureshi tayi iya ƙarfinta duk idonta ya rufe ta manta ma da Umma na zaune wurin tace, "tashi a jikina ni babu abinda yayi saura tsakani na dakai, tunda bani da daraja na uwa a idon ka kaje na yafe musu kai, ni tunda ka dage sai ka auri yarinyar nan, na cire ka acikin ƴaƴana"

Salati Umma ta saka sannan ta dubeta tace, "lallai Uwar masu gida ke kika isa da haka, wato duk irin biyayyan da yaran nan suke miki amma kika iya buɗe baki kice kin yafe shi cikin yaranki?",

"To ke kuma nace miki me?  Bayan tunda aka fara maganan auren anan nake jan hankalinki akan kibar shiga al'amarin aure, domin shi abune da Allah kaɗai yake haɗa shi amma ke ko narana ɗaya bakiyi mun biyayya ba?" ,

"To kema daga yau na yafe ki a cikin ƴaƴana tunda ni har abanda bani da darajan da zaki iya haƙura da wani abun akan ƴaƴanki."

Kuka Mama ta keyi kaman ranta zai fita da sauri ta riƙe Umma tana cewa ta yafe mata, ita kuma Umma kallon Besty tayi tace, " maigida na kayi haƙuri da halin mahaifiyarka, kuma kasaka driver yanzu ya maida ni maiduguri don bazan iya cigaba da zama da ita ba".

Ta kowa yayi a hankali ya riƙe Maman shi yana kallon yadda take kuka yace, " Mama na duk duniya bani da abinda zan iya haɗaki da shi ballantana mace da zan iya canjata sau babu adadi ke kuma fa? Kiyi haƙuri ni bazan so ki shiga wani hali na rayuwa ba akan maganan aure na, har abada Mama albarkan ki nake nema bawai na saɓa miki ba, wallahi nayi imani da Allah duk cikin ƴaƴanki bazaki samu wanda yake miki irin son dana ke miki ba, amma kin kasa fahimtan hakan Mumcy nah, daga yau idan ni acikin ki na fito kuma nake neman naga ma dake lafiya, wanda aljanna ta yake ƙarƙashin ki, to na haƙura da maganan auren Riyyah, ki yafe mun Mama na ɓata miki dana daɗe inayi".

Umma ce tayi murmushi tana kallon shi tace, "Allah ya maka albarka duniya da lahira yadda kayiwa mahaifiyarka biyyaya wanda ita kuma ta kasa yiwa tata mahaifiyar, ina maka fatan kagama da duniya lafiya Babagana".

Sannan ta kalli Mama tace, " ni bazan miki baki ba, amma wannan aure da kika hana insha'Allahu sai kin zubar da hawayen ki".

Ta juya zata shiga ɗaki kawai sukaji muryan Baba yana cewa, " yadda ɗanki ya miki biyayya ina mishi fatan gamawa da duniya lafiya, amma ke kuma yadda kika kasa yima naki mahaifiyar biyayya da kumani mijinki da aljannanarki yake ƙarƙashina, to kije gida bazan iya rayuwa dake ba har sai kin amince da auren ɗanki, kuma har sai kin saka mishi albarka".

ya sake labulen ya juya yafita yabarsu.

DAN ALLAH KARKU MANTA DA DANNA VOTE.

share and comments.

*KU KASANCE DA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*typing*

*BADARIYA*

®☄
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION* ✍🏻
{Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da kuma lahira.}

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN ƘARFE* 🏇

Story and written
By
*AUNTY NICE* 😘

Wattpad@GaskiyaWritersAsso.

*_WANNAN LITTAFI SADAUKARWA NE WA MISS XERKS_*

*PAGE* 28 --29

*_____________*📖Mama tana jin abin da Baba ya faɗa ta saka hannu aka tana ihu, tana cewa, "Umma kinga abinda Babanah ya jamun ko?" Umma ta harare ta tace, "yaushe zuciyar ki zata yi laushi ne? Kikajawa kanki dai, nidai wallahi idan ba zaki gyara tsakaninki da mijinki da ƴaƴan ki ba toh babu abinda zai sake haɗa ni da ke", ta sa kai ta shige ɗakin domim haɗa kayanta.

Zainab dai ɗaukan ɗanta da ya tashi sakamakon ihun da Mama tayi tana jan tsaki ta shige ɗakin Mama ta bar su a wurin.

Ɗakin Mama tabi Umma tana kuka tana ce mata, "Umma ki bashi haƙuri don Allah, da girma nah wani zaman gida kuma zanje nayi?" juyowa Umma tayi tana kallonta tace, "girmana kike so ya zube a idon mijinki? Ke dana haifeki kika kasa yimun biyayyah, sai mijinki kike tunanin ya mun?"

"wallahi Umma nabi Allah nabi mijina, indai akan auran wannan baƙar jarabar ce nawa auren zai ƙare, toh na haƙura suje can suyi auren su, amma don Allah Umma kiba shi haƙuri".

Haɗa kayanta ta cigaba dayai batace komai ba, bayan ta gama ta ɗaga waya ta kira Babagana da tunda Baban shi ya fita shima ya bi bayan Baban.

Babu ɓata lokaci Babagana ya shigo ɗakin har lokacin idon na zubar da hawayen abinda ya faru a gidan, har bakin gadon yaje ya zauna, amma abin yayi magana kawai sai ya fashe musu da kuka iya karfin shi

Jikin Ummu duk yayi sanyi taji batajin daɗin zuciyarta ko kaɗan, ita dai Allah yasa ka mata son Babagana a ranta kaman ɗan da ta haifah takeji ba jika ba, ɗaura hannu tayi akan kafaɗan shi tace, "maigida na ka kwanyar da hankalinka insha Allahu duk abinda yayi farko zaiyi ƙarshe, babu abinda bazai zo ya wuce ba sai ikon Allah, kayi haƙuri me kake ao na maka?"

Yana kukan yace "Umma kada ki tafi yanzu, kibari gidan ya canja yanayi, kinga yanzu Baba nabashi haƙuri amma yaƙi yadda, ni kuma bazan taɓa yafewa kaina ba idan ta sanadi na, auren iyayena ya samu matsala, don Allah kiba shi haƙuri" ya faɗa yana kwantar da kanshi a kafaɗan Umma wanda yaji ciwon kai kaman ana sara ishi wuƙa akan.

Shiru Umma tayi tana ta buga mishi bayan shi kaman ƙaramin yaro, suna haka har aka kira sallan magarib, kallon shi Umma tayi tace, "kaje masallaci idan kayi salla kamun magana da Baban naku" ta faɗa tana miƙewa hanyar toilet.

Yana fita a ɗakin Mama ma ta wuce nata ɗakin inda ta samu Zainab zaune tana sawa Nabeel pampams, ko kallon inda Maman take batayi ba, ita ma Maman wucewa toilet tayi domin tayi alwalah.

Har misalin ƙarfe tara da rabi banga Besty yazo ba, nidai kawai jin hiran da Hammah Sadiq kawai nake ba wai don ina fahimta ba, nasan iɗan zaizo ana idar da sallan ishaa yake tahowa, amma shiru har yanzu.

Palon Ummi na tashi naje, wani zuciyar tace toh meya hana shi zuwa? Ko wani abu ne ya faru? Kai da wani abun ne ya faru da Aunty ta ƙira ta sanar, kawai dai hala gajjiyane, na saka hakan a raina.

Saida su Besty suka idar da sallah tukun suka shigo side ɗin Mama, sallama sukayi a ɗakin da Umma take sanan ta basu izinin shiga, wuri Baba ya samu ya zauna, Besty kuma ya juya zai fita Umma ta ƙira shi tace ya nemi wuri ya zauna.

Bayan sun gaisa ne ɗakin ya ɗauki shiru na wani lokacin, Umma nebta fara magana inda ta ke duban Baba tace.

"Alhaji nidai a matsayina na uwa a gareku babu abinda zance maka saidai nace ku ƙara haƙuri da mahaifiyarsu, domin nasan iya haƙuri kana yi da ita, domin ita kuma haka Allah yayi ta mace ce wanda bata san gaskiya ba, kuma ta ɗaurawa kanta baƙin kishi da bazai kaita ko ina ba.

Maganan ta koma gida kayi haƙuri badon batayi laifi ba a'a, kayi haƙuri saboda darajan yaran da ke tsakanin ku, sai maganan auren Maigida kuma babu magana a fasa shi don ba ita ta haife muba, da ita nata yaran zasu mata biyayyah ita kuma ta kasa yimana, ballantana kai mijinta da kafi komai daraja a idonta.

Abu ɗaya zuwa biyu nakeso da kai Alhaji, yadda ka taso da maganan auren ayi shi, na biyu kuma kada kowa ya sake ɗaurata akan maganan auren sannan kuma sauran kabar ni nida ita.

Ta juya kan Besty tace, "Maigida ka kwantar da hankalin ka babu abinda bakinta zai maka, tunda bawai ka na shirin aikata mummunan abu bane, kuma idan ka koma kan aikin ka bana so

kasake zuwa sai satin auren, wanda bana so ya wuce nan da wata biyu, ina fatan hakan ya muku ko?"

Baba ne yayi ajiyan zuciya sanann yace, " insha Allahu hakan yayi kuma kema ina mai ƙara baki haƙuri da abinda ya faru a gabanki wanda banso hakan ba ko kaɗan, amma nayi hakan ne saboda ta fahimci kuskuren da takeyi," haka suka ci faba da tattauna matsalolin har zuwa shaɗaya na dare, sannan sukayi wa juna sallama kowa ya wuce inda yafi wayo.

Lokacin da aka idar da sallan Asuba bayan gari ya fara haske, dama tun ajiyan Umma tayiwa Baba maganan komawan ta maiduguri kuma ya fahimceta da abinda take nufi, suka bari akan ƙarfe takwas driver zaizo ya wuce da ita.

Tun wajen 7:00 Besty ya shigo ɗakin Umma shima cikin shirin shi na komawa lagos, wanda da yayi niyyan sai washe gari sunday ya tafi, amma gaba ɗaya bayajin daɗin komai, gara ya koma can ya samu kaɗaici ko zuciyar shi zata huce.

Suna gaisawa da shi kenan Mama ta shigo ɗakin jikin ta ɗauke da hijabinta na sallah, ƙarasawa yayi har inda take ya tsuguna a gabanta ya gaishe ta cikin nutsuwa, batare da ta dubi inda yake ba ta amsa ciki-ciki, sannan ta dawo da hankalinta kan Umma tace.

"Umma antashi lafiya?" itama Umman ganin abin da tayiwa Besty ya ƙona mata rai, itama ciki-ciki ta amsa mata ba tare data dube taba, gaba ɗaya ta maida hankalinta akan Besty.

"Maigida yaya naganka cikin shirin tafiya?"  kan sauƙe yana kallon capet dake shimfiɗe a ɗakin yace, "Umma tafiyan ne ya taso, shiyasa kawai zan koma yau".

Umma tana kallon shi lokaci ɗaya taji idonta ya ciko da hawaye, ƙarasawa tayi har inda yake zaune dafa shi tayi tace, "kayi haƙuri kuma ka ƙara dagewa da addu'a, domin duk bawan da yayi imani da ƙaddara mai kyau da marar kyau to yaga ma samun ribar rayuwa duniya da lahira."

Ɗagowa yayi idon shi cike da hawaye yana kallon Umma, kaman zaice wani abu kuma sai yayi shiru ya sunkuyar da kanshi, dai-dai lokacin wayan shi ya shiga kiɗa yana neman agaji.

Ɗauka yayi tunda yace, "hello" sai kuma ya kasa magana ya rufe idonshi hawaye yana zuba a idon shi, a ɗayan ɓangaren kuma aka cigaba da faɗin "hello Babagana ko bakaji nane? Wani abu ya faru ne?kayi magana mana" aka faɗa hankali a tashe.

Yana fara magana kuka yazo mishi batare da ya damu ya tsayar da kukan ba ya cigaba da maganan, "hammah babu abinda ya faru", sai kuma yayi shiru ya miƙawa Umma wayan, shi kuma ya sunkuyar da kanshi ƙasa yana kuka mai cin rai.

Umma ce ina jinta bayan sun gaisa duk abinda ya faru tabawa Hammah Umar labari, har tana ƙari da bayani ita ma daga yau tafita a hidiman Mama da yaranta, ta faɗa rana ahare hawayen tausayin Besty.

Bayan sun gama wayan ta miƙawa Besty wayan, sallama sukayi da Hammah inda yace mishi ya kwantar da hankalin shi tun da yaga tuƙi zaiyi kada yaje wani abu ya faru dashi, ya kara jan kunnen shi da ya tafi a hankali cikin nutsuwa idan ya isa lafiya za suyi waya.

Tashi yayi yama Umma sallama ya ajiye mata 20k, sanann ya dawo inda Mama take ya tsuguna yace.

Mama ni zan koma sai an kwana biyu, sannan don Allah Mama ina ƙara baki haƙuri, duk abinda na miki na ɓatanci kiyi hakuri ki yafe mun, addu'anki nake nema Mama nah, ya ajiye Mata 50k ya tashi yayi hanyar fita har yaje bakin ƙofa ƴaji bata ce mishi komai ba sai yaja ya tsaya yana share hawayen shi, ya juya ya fita.

Baba ne ya shigo bayan tafiyan Babagana yace wa Umma ta fito ga driver a waje,  Haka ta tashi ta fita ko kallon inda Mama take batayi ba tasaka kanta tayi waje , duk da yada Mama take magiyan tayi haƙuri Umma bata kula taba, Gefen Aunty taje sukayi sallama, ta ɗauki wani roban Humrah da kulakcam tabawa Auntyʹtace ta aika mun ɗaya ta ɗauki ɗaya.

Nidai kawai ranan ban san wani irin bacci nayi ba, don wurin goma na ƙira shi bai ɗauki wayana ba, dana sake ƙira sai naji wayan akashe, haka na haƙura na kwanta raina babu daɗi.

Washe gari Besty ta dameni muje gidan Adda Umaima  daga nan mu wuce Kasuwa muyi shooping, haka firr na mata ƙaryan bana jin daɗi, taje kawai ita kaɗai ta mana, babu yadda ta iya haka tabarni ta tafi.

Nima gani yadda Besty Riyyah takeyi yasa naji bana jin daɗi a raina, nima gara kawai na wuce gida nayi wanka don yau jumma'a ne, amma nima zuciyata babu daɗi.

*BARKA DA JUMMA'A, KU KASANCE DANI AUNTY NICE DA ALKALAMI NA DOMIN JIN YADDA ZA TA KAYA*✍🏻✍🏻✍🏻
*typing*

*BADARIYA*

®☄
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION* ✍🏻
{Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da kuma lahira.}

🎐G•W`A🎐
*GASKIYA DOKIN KARFE* 🏇

Story and written
By
*AUNTY NICE* 😘

Wattpad@GaskiyaWritersAsso.

*WANNAN LITTAFI SADAUKAR WA NE ZUWA GAREKIMISS XERKS*

*PAGE* 30--31

*___________*📖Babagana yana isa lagos ya shiga gidan da yake, har zuwa lokacin zuciyar shi zafi rake mishi, kasa yin komai yayi ya hau gado ya kwanta.

Idon shi yana kallon saman ɗakin ya dafe goshin shi da ɗayan hannun shi, yana ta ayyana abubuwa a ranshi game da rayuwanshi da Mama, sai yaji ƙaran wayan shi.

Kaman baxai ɗauka ba, wani zuciyar ya saka shi ya ɗauka, ganin sunan Hammah Umar ne ajikin screen ɗin ya saka shi tashi  zaune.

"Hello Hamma!" cewar Besty wanda daga jin muryan shi kasan akwai rauni a cikin muryan, Hammah ne yake tambayan shi yanda ya baro gida da kuma isowan shi lafiya, sannan yace mishi.

"Babagana ina so kayi haƙuri ka cire abinda Mama ta maka a zuciyarka, domin ita uwa haƙuri ake dayita akowani lokaci, domin a samu a rabu dasu lafiya".

Lumshe ido Besty yayi yana jin wani irin sanyi a zuciyar shi, domin a rayuwa ya daɗe yana so yaga Hamman shi yana shiga al'amuranshi, gashi yau ɗaya yaji zuciyar shi ya fara sanyi domin jin dadin da Hammah ya yi na nuna damuwan shi a kanshi.

Lokaci ɗaya yaji bakinshi ya buɗe yana cewa, "Hammah ni da nace ko na haƙura da auren Riyyah ce"?........ "kull naji kana faɗin haka Babagana, ita ae matsayinta na uwa kamata biyayyah a rayuwa ba wai ance idan tana so ka kauce hanya ka biye mata kuyi ɓarna ba, a'a ba haka ake nufi ba, kawai ku zauna lafiya har Allah ya rabaku lafiya, amma shi maganan aure babu wannan tunda bawai an sameta da wani na kasu bane wanda yakai a ƙi aurenta."

Babagana yaji zuciyar shi tayi sanyi, suka cigaba da hiransu kaman dama sun shaƙu, Hammah yana ta ƙwantar mishi da hankali, har zuwa wani lokaci sukayi sallama.

Sai a sannan Besty yaji ƙarfin gwaiwan ya nemeni a waya.

Inajin ƙiran da kaman bazan ɗauka ba, amma sai wani zuciyar ya danne ni na ɗauka, ina ɗauka ko magana banyi ba nati shiru kawai.

Dariya yayi sanan yace, "Beauty nah, nayi laifi ko"?  Murguɗa baki nayi kaman yana kallo na nace, "Da akayi me kuma?".

"Beauty don Allah kiyi haƙuri wallahi wani abu ne ya sha mun kai, har zuwa dare ban samu

kaina ba, da Asuba kuma aka neme ni a Office duk hankalina a tashe  na tafi babu shiri".

Hmmm kawai nace ba tare dana tanka ko kalma ɗaya ba, haka yayita rarrashina ina jinshi, a ƙarshe ya mun sallama, ajiye wayan mukayi amma sai na samu kaina da jin daɗi saboda ko ba komai nasan lafiyan shi qalau.

Ranan sunday muka koma school, bayan mun koma ne Besty ke tambayana yayah mukayi da Besty akan maganan ɗinki?

"kawai Aunty tace na bari akwai wata ƙawarta a kaduna da sukayi zata aika mata wasu, sannan kuma Hammah Haidar yace a aika mishi zai baiwa telan da zata miki".

Haka muka cigaba da hiran mu, kuma na kwantar da hankali na domin muyi karatu a nutse, domin yanzu muna second semester ne, aji 2 zamu tafi.

A kano gidan Adda Humaira suna tare da Adda Hafsat sun baje a palo suna ta shan rake, Adda Hafsa ce ta taho musu dashi daga asibiti inda yau taje tayi bucking antenatal, wanda zuwa wannan time ɗin cikinta ya shiga six month, tana mitan bikin mu za ayi shi lokacin haihuwar tane.

Adda Hummy nata mata dariya tace, "gashi babu yadda za'ayi na jiraki, domin dai kinga bikin ƴar ɗakina zan tafi," sunayi suna dariya, sai Adda take cewa Hafsat, "Hafsat kinsan wai nima cikine dani kusan 2mnth"? Ta faɗa tanabya mutsa fuska, murna Hafsat tayi tana cewa, "Adda ae wallahi naji daɗi da hakan, domin wanann sakalcin da Ammar yakeyi yayi yawa, Allah yasa ki haifa mana baby girl".

Yau tunda muka tashi nake ta shirin tafiya gida saboda Aunty tace nazo mu cire kayan da zata bada ɗinkin, kallaon Besty nayi nace, "kefa ƴan mata bazaki tashi mu tafi bane, har sai yammah yayi mana bamu tafiba"?  Tana ihu ta tashi ta ɗauki himar tace, "jaraba mutafi kada ki cinyeni nama ɗanye.

A gidan muka samu Aunty da Ummi suna cin abinci suna hira, muma zuwa nayi na ɗebo mana bayan mun gaisa dasu, muna gama cin abincin Aunty tace mutashi muje mu cire kayan.

Nidai kaman a dasani a wajen, sai kallon su kawai nakeyi, daga Aunty sai Besty ne suke tafitar da kayan, nida Ummi kam sai ido, haka suka cire inajin su suna ta bayani wannan a mishi gown zaifi kyau wannan skirt and blouse, haka dai suke tayi ina jin su.

Aunty ce ta kalleni tace, "kinsan Hamman ku yayi rashin lafiya kuwa?"   gaba nane naji ƴa faɗi kaman zanyi fitsari a jikina saboda irin faɗuwar gaban da naji, girgiza kaina nayi nace mata, "banjiba wallahi, don ko Besty bai gaya mun ha"

"Toh dai yakamata ku gaishe shi, domin irin wannan hidama da yakeyi da ko, kuma gwara kudinga kyautata mishi".

Ummi tace "ai ko baiyi hidima dasu ba wanda yafika kan ai dole su mutunta shi, ballan tana irin abinda yake mana agidan nan, ni wataran har gani nakeyi kaman ke kika haife shi Fatima am".

Aunty tayi dariya tace, "Umar kam al'amarinshi abin duba wane gaskiya akwai dattaku a hidimanshi yadda kika san tare suka zo duniya da *_MISS XERKS_* wurin karamci, nidai wallahi Adda saidai nace sam barka, bani ba ba ƴaƴa naba ba dangina ba, ko ɗan dana haifah Albarka."

Haka suka cigaba da hiransu mu kuma muka wuce gidan su Besty, don bamu so mukai magrib bamu koma school ba.

Muna shiga muka samu Mummy da Yaya Kamal a palo suna zaune yana shan kankana da aka saka shi cikin wani plet mai kyaun gaske.

Gefen Mummy mukaje da sauri muna gaisheta, da murna take amsa mana tana cewa,

"ƴan mata zuwa babu notice"?

Muna dariya Besty tace "Aunty ce tace muzo mu fitar da kayan Besty wanda za'a tafi dasu ɗinki, shiyasa kika ganmu kaman sauƙan aradu, ta faɗa tana ɗaukan kankanan gaban Mummy tana sha".

Da sauri Yayah Kamal ya dube ni sannan yace, "kudai shegen rawan kai, kayan ma sai kunzo don rashin kunya, Aunty ita baxa ta iya cire wa bane sai kunzo? Ku tashi na maida ku school ɗin," ya faɗa yana miƙewa tsaye.

Har gate ɗin school ɗinmu ya kaimu, kowan mu godiya muka mishi, mun buɗe zamu fita yace tsaya Riyyah!

tsayawa nayi da buɗe ƙofan ina kallonshi, itama Besty sai ta tsaya, kallonta yayi yana mata wani mugun kallo sannan yace,

"ko sunanki yaxama Riyyah ne?" da sauri ta wuce cikin school tana cewa, "Allah ya kiyaƴe hanya mungode Yayah agaida Fauxy."

Hararanta yayi sanan ya juyo kaina yace, "wato tunda kika yanke duk wani alaƙa dake tsakanin mu ko waya bazaki neme ni muna gaisawa ba? Shike nan kina so ki yanke duk wani dangantaka a tsakani na dake?"

Sun kuyar da kai na nayi ina wasa da zoben hannu na nace, "ban isa ba Yayah kawai dai naga bai kamata na dinga shige maka ba, saboda kada ayi tunanin akwai wani abu tsakanin mu, kaga ita kanta Fauxy idan taji zatayi zargin wani abu".

Shiru yayi yana kallo na can yace, "toh ga auren yana ta matsowa me kike so namiki? wanda zai saki yadda ni yanzu na ɗauke ki ƙanwace mafi soyuwa a wajena,"

ya faɗa yana duba na ta gefen ido wanda kaman baizai kalleni ba, amma kuma kallon yake yi, wanda aka sarin kallon shi kenan sai ya kalle ka kaman baya son kallon.

"ni duk abinda kamun zan so shi yayah" na faɗa bayan naƙi kallon face ɗinshi.

Shikenan jeki kada ƴar gulman nan tayi mita, zan duba naga abinda yafi cancanta dake.

Dariya nayi na rufe mushi murfin motan na wuce cikin school.

Ina shiga ɗakin Besty ta taso tace, "me yace miki Besty"?

Na harareta nace "gulma na cinki, dama saida Yaƴa ya faɗa, ashe ko yafini sanin halinki, toh ni babu abinda yace mun, wanda kike tsammani kawai ya tambayi abinda muke so ne ni dake na auren mu don ya saya mana."

"Allah sarki Yayah Kamal wallahi tausayi yake bani, don idan ya ganki wani birkicewa yakeyi, saboda son daya ke miki ba kaɗan bane, ashe tun kina yarinya ya taɓa gaƴawa Adda Hummyƴ amma bata ɗauki abin serious ba" ta faɗa tana zama a bakin gado.

Nima zama nayi gefenta nace "banda sharri wani irin ruɗewa zai yi sai kace wani yaro".

Kallo na tayi tace, "hmm bazaki gane bane, kawai shi Yaya kinsan koman shi a nutse ya keyi shi yasa baza a gane ba, amma ko Mummy kwanaki saida tace idan ya ganki rasa abunyi yakeyi, ga kishin ki dayakeyi har tausayi yake bata, kawai babu yadda ta iya ne.

Lokaci guda naji jikina yayi sanyi, don koni na fahimci haka duk irin nutsuwan shi idan ya ganni har manta abinda zaiyi yakeyi wataran, don ko yau ma na lura ana fara maganan kayana ya katse magana akan mu tashi yakai mu.

"Allah sarki Yaya Kamal wallahi Besty koni wataran nakanyi tunanin cewa da ace babu maganan Besty, kuma da ace iyaye basu shiga maganan da wuriba, babu abinda zai hanani auren Yayah Kamal.

Don na daɗe ina sha'awan auren nami irinshi, domin Gaskiya akwai nitsuwa da sanyin hali a alamuranshi duk da zafin shi tunda sai an taɓo shi, toh amma abinda Allah yayi babu mai canjawa."

Toh yaya za ayi cewar Bestyƴ sannan nace, "amma idan Mama tace bani auren ɗanta halan sai muyi da Yayan" na faɗa ina dariya.

Maka mun duka Besty tayi tana cewa bayan kin ɓata komai kin haɗa shi da Fauzy,
yayah kike so muyi da ita?

🎐

Saidai idan ayi da Hammah shi mai class ɗin nan, don shima irin Yayah Kamal ne, har ma yafi Yayah Kamal class, don wallahi Besty da nayi mugun miki sha'awan gayen nan kawai sai naji kince aure zayi.

amma ni kullum hasaso ku nakeyi da shi, gaki ƴar duma-duma yar choculete dake, ga yanga da sun gayu,shi kuma ɗan fari dogo ɗan siriri dashi," tafaɗa tana dariya.

Duka na kwaɗa mata nace, "amma bakida mutunci, wallahi idan kika sake faɗa sai na haɗaki da Besty don yasan irin zaman da zaiyi dake."

Tana dariya tace to ƙarya nayi? Kinsan dai Hamman nan ya haɗu over, kawai dai don Beatyƴ ya riga ne, amma hmmm kedai kawai ayi shiru, don idan ana sallah ba a magana".

Nima nace toh kowa dai saidai yayi shiru, tunda Besty ya riga sai kowa tayi haƙuri, Hammah mezaiyi da jaririya tunda ya samu Zainab.

*KU KASANCE DA ALƘALAMIN AUNTY NICE*✍🏻✍🏻✍🏻
🔘 *BADARIYA* 🔘
*1442H/2019M*

®☄
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION* ✍🏻
{Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da kuma lahira.}

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN KARFE* 🏇🏽

Story and written
By
*AUNTY NICE* ✍🏻

*WANNAN BOOK SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS*

Wattpad@GaskiyaWritersAsso.

*PAGE* 32---33

*__________*📖Dariya nayi ina kaɗa kaina don jin abinda Besty ta faɗa, ina kallonta una dariya nace, "kinsan dai yanzu yazama surukina saboda haka ki daina haɗani da shi, bakima lura da wani abu ba Besty" na faɗa ina ƙara sautin dariya na.

Kallona ta tsaya yi, ina kan dariya na cigaba da ce mata, "ae idan jin lura da haɗuwar Hammah Umar sai kace omer na film ɗin tarkon ƙauna, inaga baki taɓa lura da kamnnin su ba ko"?

Tsalle ta daka ta faɗo kaina tana dariya, wanda har saida ta bani tsoro tace, "Besty wallahi hakane, kullum saina yita tunanin da wa yake kama ashe ke kan kinsan kayanki, Besty har yanayin tsayin su, da ɗaure fuskansu iri ɗaya, sai yau na ƙara yadda, kai amma munyi miaainh wallahi" ta faɗa tana sunɓuro bakinta gaba.

Hararanta nayi nace, "mekike nufi da munyi missing? Besty na ma har ƴafishi kyau, kawai tsayi zai nunawa Besty don wallahi kama sukeyi, Besty mai fara'a da son mutane ma" na faɗa ina ture ta daga jikina.

Har kasa ta faɗo tana dariya tace, "gara ma na daina damuwa da kyaun su don babu wanda

yafi Hamma Haidar ɗina" ta faɗa tana juya ikebenta.

Haka mukayita muhawara kowa tana cewa na ta yafi haɗuwa, har muka gama abinda zamuyi.

Tunda Besty ya koma kullum sai ya ƙira Mama amma bata ɗaukan wayan shi, haka babu yadda ya iya saidai ya tura mata txt.

sukuma sauran gidajen kowa shirye-shirye yakeyi, amma gidan Mama babu abinda take shiryawa, saidai Baba yasanar da AuntyƳFanna akan ta tsaya akan komai.

Ranan da muka gama exams muka dawo gida, inda zamuyi hutun kusan wata uku, a lokacin kuma auren mu saura 3wks.

Tunda muka dawo aka hanamu yawo, kusan kullum Aunty sai tazo gidanmu, ana tamana shiri kaman daga kanmu amare sun ƙare.

Mummy takanas ta ɗauko mana wata mata daga maiduguri wacce ake cemata Aunty Yagana tana ta mana gyaran amare.

Ga wani dilke da ake mana dama mun tare gidan Mummy ne aka ware mana ɗaki guda,nidai sai dare nake zuwa gidan mu na kwana wurin Ummi na.

Idan kunga jikina sai ka rantse da Allah irin matan baƙaƙen larabawan nan ne, domin wani colour nane ya ƙara fitowa yayi kyau, dama ga jikina duk gashi ne akwance, wanda suka ƙara maida jikina yayi kyau.

Kullum Besty ta kalleni sai tace, "kai Besty kina da wani irin fitinannen kyau, gaskiya Besty ya mure, kinga yadda kika canja kuwa? .

nidai dariya kawai nake mata, don nasan babu ƙarya nayi kyau saida goɗiya wa Allah subahanahu wata'ala.

Ana saura sati ɗaya Adda Hummy da Adda Hafsat suka zo, wanda ko kaɗan baxaka ga Adda Hafsat kace cikinta ya shiga watan haihuwa ba, domin ƴa baje a jikinta ne, sai uban ɗuwaiwaya da tayi, amma kuma duk inda ta zauna da ƙyar take tashi.

Murna kaman zamuyi yayah don ganin su Adda, itama sai ɗauki takeyi na ganin mu, duk unda mukayi sai kaji tana cewa, "Masha Allah da amaren mu, Allah dai ya sa abokanan zamankune".

Koɓkuma sai kaji tace, "Allah sarki Kamal ɗina ashe barabun mu bane Riyyah, amma wallahi ƴa daɗe yana sonta Mummy, dubi irin kyaun da mukayi rashi."

Nidai kunya kawai ta ke sakani naji, haka kawai naji inajin kunyanta daga ita har Mummyn, duk da ita Mummyƴ cewa takewa Allaj bai haɗa rabonsu ba Hummairah yyh za'ayi?.

Wani irin soyayyah da shaƙuwa ne ya ƙara ƙaruwa tsakanin mu da Besty, kullum ji muke kaman mu cinye junan mu, idan muna waya wataran har sai chajina ya ƙare.

Haka kuma tun ranan Hammah Umar ke tausayin Besty, kullum sai ya kira shi ya kwantar mishi da hankali.

Haka Mama ma bai barta ba Kullum cikin yi mata nasiha yakeyi, amma ko ajikinta kaman ba ita ba.

Haka Aunty Fanna ta iso ranan monday da za'a fara bikin tare da su Umma da Aunty Falmata, kuma Baba yace kada wata acikinsu ta saurari Mama.

Ga kuma sisters ɗinshi su Hajiya Addayo tun ranan wednesday suma suka iso, don haka Baba yasa Aunty shiga cikin su domin su yi hidiman komai tare, babu yadda Auntyƴ ta iya dole take tsayawa akan komai.

Ranan Wednesday da yamma Besty ya iso, ranan kuma su Abdallah ma suka iso tunda rana, dukkan su a palon Mama suka haɗu dasu Auntyƴ Fannah anata hira ga Umma kaman ta lashe shi takeyi.

Ga tausayin shi da takeji ganin duk ya rame, kuma tasan damuwar Maman shi yasaka a ranshi.

Tana kallon shi tace, " maigidana duk ka rame, ko tunanin barina kakeyi"? Ta faɗa tana dariya.

Tashi yayi yana dariya dai-dai lokacin Mama ta fito palon, idon shi yana kallon ta ƴadda ta dube shi ta juyar da kanta alaman bata son ganin shi.

Ganin hakan da tayi yasa shi ƙarasawa gabanta yana mata rawanshi da yake mata da, yana juya kanshi yana, "Sharen hawayena kiji tausayi raina"har gabanta ya ƙarisa ya durƙusa yana cigaba da wakanshi, "nazo ki dube ni, afuwarki na nema, Mama kiyafemun, kada ahaka muyi bankwana."

dukkansu ƴan palon suka kwashe da dariya banda shi da Mama daya tsura mata ido hawaye yana xuba mishi.

abin mamaki da kaman da wasa yakeyi cikin raha, amma kuma sai zuciyar shi ta karye ya kwantar da kanshi kan cinyanta yana zubar da hawaye, ita kanta Maman kasa tureshi tayi yadda da tayi niyyah, kawai kallon shi takeyi yadda yake sheshsheƙan kukan a kan cinyanta.

Haka kawai Umma ta samu kanta da fara zubar da hawayen ya dubi Mama tace, "Idan kina da rabon shiriya Allah ya shiryeki" ta faɗa ta tashi tayi hanyan ɗakin da aka sauke su.

Har sai da aka ƙira sallan magarib tukun Mama ta saka hannu ta ture kanshi a hankali tayi ɗakinta, yana binta da kallo har ta shige, tukun ya miƙe yayi side ɗinshi domin yayi alwala.

Ana sallah ishaa suka fito tare da Baba dasu Abdallah daga mosque, Baba na riƙe da hannun Mujaheed sukayi side ɗin Aunty domin su ci abinci.

A palon Aunty bayan sunci abincin ya fice da dabara, yayi gidanmu.

Ina kwance akan cinyan Ummi, Hammah Sadiq yana ta mitan wai ana sakaltani wallahi dayawa, Umman kafi tana ce mishi idan ba ayi munba wa za'ayiwa? Kaidai sadiƙu halinka saikai, kwana nawa ne ma ta tafi tabar muku Ummin ku kaɗai.

tashi nayi na zauna nace, "kuma ko na tafi babu shi babu hawa kan cinyan Ummi nah, saidai duk ranan dana zo na hau kan cinyana ko Ummi nah", na faɗa ina kallon Ummi.

"ku kuka sani" kawai Ummi tace mana, a haka naji ƙiran Besty yana shigo mun, ina ɗaga nace, "My heart! My noroul qalbi! My cwit darling! Ka iso ne? Na faɗa ina jiran jin abinda Hamma Sadiq zaice.

ae kuwa ban rufe bakinaba ya jefeni da pillow kan kujeeun yana cewa, "wallahi yarinyar nan dani takeyi, don ta rainani", Ummi da Umma sai dariyan shi sukeyi.

nima ina dariyan shi na fita da gudu nayi akin Ummi nah domin na shiryah na fita gun Besty nah.

Motan na buɗe ina kallon shi batare dana shiga ba, sjima kallona yakeyi fuskan shi ɗauke da smilling, ganin na tsaya yasaka shi cewa, "ko nazo na ɗauke kine my queen?"

Murguɗa baki nayi nace, "Besty auren dole za'a maka kawani rame?" yana dariya yace, "auren so za amun ki da Noroul qalbi nah! My heart ɗinah! My.... Bai karisa ba na rufe mishi motan ina dariya.

Fitowa yayi yana dariya ya tsaya agabana yana kallona, ni kuma nayi sauri na rufe ido na nace, "wallahi Hammah Sadiq ne ya dame ni shine nake tsokanan shi, kada ka ɗauka rashin kunya ne".

Shima yana dariya yace "waya isa yace rashin kunya?wannan ae shine so da ƙaunan,danake burin ya ɗaure har ƙarshen rayuwar mu" ya faɗa yana matsuwa kusa dani.

Inajin sautin numfashin shi kusa dani, yasani ɗagowa da sauri na kalle shi, shima kallona yakeyi amma narasa wani irin kallo ya kemum, kawai saina sake maida kaina ƙasa.

"Beauty wani irin kyau kika ƙara? anya bazan dinga ɓoyeki ba kuwa? Ya ɗaga hannu shi sama yana Allah na gode maka da kabani kamila kuma saliha kyaukyawa acikin matan duniya, Allah ka kara  mun ƙaunarta a zuciyata, kabamu zaman lafiya har ƙarshen rayuwata."

Ya dawo da kallon shi kaina, sanan yace mun,"Beauty duk duniya babu abinda nakeso sama da Mama na, da Babana, kinsan si waye kuma"?

Ina kallon shi na jijjiga mishi kai alaman a'a.

"Beauty ina miki wani so wanda bansan yaya zan kwatanta miki ba, kuma nakan rasa wana fi so tsakaninki da Hammah Nah.

Beauty ina so duk duniya idan kincire iyayenki da ƴan'uwanki, kada kiso kowa sama da Mama da Hammah na, kiyi haƙuri da kowani ƙiyayyah da Mama zata miki nasani akwai ƙarshen shi,

saboda nayi imani da Allah idan har ita ta haifeni, kuma duk sonda yake tsakanin uwa da ɗanta yana yawo ajininmu, jikina yana bani wataran sai taso abinda nake so, kuma koda bayan raina ne."

Ina kallonshi nace, "Besty kada kasaka shakku akaina, domin tsakani da Allah nake sonka, kuma insha Allahu zan so Mama da dukkan wani wanda ya dangaceka, sannan kuma zan mata biyayyah tamkar Ummi na, kada kadamu da kin da take mun, insha Allahu wataran zai koma tarihi".

"Alhamdulillah" ya faɗa yana kallina sanan yace "ina Bestyn mu da anginta? anata shirye-shirye ko"?

Ina daiya nace, "tana ta rawan kai dai" .

shima dariyan yayi yana kallona ƴace, "Beauty nifa bazanyi wani dinner ba fa abikina, Kawai zamuyi recieption ne idan mun dawo daga ɗaurin aure, sai kuma da yamma za'ayi buɗan kai shima Aunty Fannah ce ta matsa, saidai kiyi haƙuri bikina ba irin na Hammah bane babu event dayawa".

Ina kallon shi nace, "Besty ae hakan ma yafi wallahi, nima da badan Besty ba ae da walimah kawai zanyi, don ni bana son event daya wa a biki, duk da dai ma kamu kawai zamuyi, sai waliman da zamuyi gobe."

Shiru yayi yana kallon ƙafan shi, nima kaman ance na zuba mishi ido, haka na tsaya inata kallonshi, a zuciyana nace, "dama Besty haka yake da gashin gira da na ido dayawa? toh ni banga wani abu da Hammah zai gwada mishi a kyau ba, saidai kawai tsayin da ake cewa Hammah ya fiso da farin fatan shi."

Ɗago da idon shi yayi wanda ban ankara ba ya kamani ina kallonshi, da sauri na juyadda kaina yaana dariya yace, "kalli abinki ƴan mata na, idan ba ki kalleni ba wa zaki kalla ko kina da wani ne bayan ni"?Yana dariya yafaɗi hakan.

Nima dariyan nakeyi ina bubbuga ƙafa na a kasa nace , "nikan kadaina mun sharri ba kallonka nakeyi ba, kawai naga kamun kyaune, Besty ashe gashin giranka yana da yawa?"

Wani irin dariya yakeyi da ban taɓa ganin yaƴi ba yace, "Beauty ashe dai kina sona tunda har

yau kika ga kyauna," yana kan kallo na can a hankali naji yace, "Beautyn Besty! Wallahi ina so naga munyi rayuwan aure nida ke da ƴaƴanmu har abada."

Kallon shi nayi bansan lokacin da bakina ya furta, "Nima haka nake fata Besty nah".

Nima Aunty nice ina gefe nace, "ayya har sun tuna mun da nawa Bestyn nima haka da nayi fatan naga munyi rayuwa da shi har ƙarshen numfashina, Allah yajiƙanka Mijina Allah yasa kana cikin rahmar Ubangiji😭😭😭👏🏻👏🏻

*KU KASANCE DA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*
*1441H/2019M.*

®☄
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION✍*
_{Gaskiya ɗaya ce daga kinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira.}_

🎐G•W•A🎐
_*GASKIYA DOKIN ƘARFE•* 🏇_

Story and written
By
*AUNTY NICE*

*_WANNAN BOOK SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Wattpad@GaskiyaWritersAsso.~

{innalillahi wa'inna ilaihir raji'un, ina miƙa ta'aziya wa iyalen Alhaji Babagana Zaki, na rashin ɗansu, ƙaninsu, Aliyu zaki (Abba)da akayi ranan saturday, matar shi kuma ƙanwata Fauxy ina miki ta'axiyan rashin miji da kikayi, tabbas na tausaya miki Fauxy, domin mutuwan miji sai Allah, Allah ya jiƙan mijinki ya mishi rahma yasa yana cikin Rahma, Allah ya baki haƙurin wannan rashin da akayi, 😭😭😭.

*PAGE* 34----35

*__________*📖Murmushi yayi yana kallo na yace, "Beauty bari nabarki kije ki huta nima kaina yana ɗanmun ciwo ne, gara naje na kwanta da wuri, kuma Baba ma yana son ganina" ya faɗa yana duba na, nima sallama na mishi na juya cikin gidan mu.

Besty bai sake leƙoni ba sai ranan Friday da safe, ina gidansu Besty Feenah ya ƙirani na faɗa mishi ya sameni acan, lokacin kuma angama cire mun jan lalle saura baƙin, haka nabawa Aunty ya gana haƙuri akan bari naje na dawo sai a saka mun.

Can wurin side ɗin Yayah Kamal yayi parking ganin babu mutane ta wurin, ina ƙarisowa na mishi sallama kenan sai ga Yayaah Kamal ya fito daga palon shi, har inda muke ya kariso.

Abin mamaki sai naga ya miƙawa Besty haannu, Besty ma da hanzari ya miƙa mishi fuskar shi ɗauke da fara'a yana faɗin,"barka dai ango, yayah hidima"?

Yayah Kamal abin mamako shima fuskan shi da fara'a yana kallon Besty yace, "ae kaine ango domin gaka ga amaryah baka ko ɗaga mata ƙafa, ga adon lalle duk an maka, domin burgeka" ya ƙarisa dukkansu suna dariya.

Kallon mu yayi yace, "ku shiga cikin palon mana ko,inaga hakan ae zaifi tsayuwa wajen" ya faɗa yana miƙo mun key ɗin palon shi.

Sallama suka yi cikin barkwanci wanda bantaɓa ganin Yayah Kamal yana yi ba, haka muka

karisa ƙofan palon na buɗe mana, muka shiga.

Muna zama Besty ya dubeni yace, "Beauty anya bazaki burkita mun tunani ba da irin wannan kyau da kike ƙarawa? dubi wani jan lallai da aka miki kaman na sa harce na lashe shi" yana faɗa kaman zaiyi yayah.

Ina masa wani rausaya wanda bansan yaya akayi nakeyi ba nace, "sai ma anjima idan an karisa mun baƙin na ƙara wargaza maka tunanin" na faɗa ina rufe ido na.

Dukkan mu dariya mukeyi,sannan yace "Gaskiya Beauty idan donni zakiyi wannan kwalliyan toh bana son baƙin lallai, ni jan kawai ya wadatar dani, amma bakin gaskiya bai cika burgeni ba".

Kallon shi nayi nace " insha Allahu Besty har abada bani sake yin baƙin lallai sai ja, tunda don kai zan dinga kwalliyan".

Daga dukkan alamu maganan dana faɗa ya mishi daɗi, don kasa rufe bakinshi yayi sai murmushi yakeyi, dai-dai lokacin wayan shi ta ɗauki ƙara.

"Hlo Hammah yayah kake?" ina ji nasan da Hammah Umar yakeyi, abin mamaki Besty har wani mantawa yayi dani sai labari yake bawa ɗan'uwanshi, kaman daga sama naji yace, "lah Hammah gata nan ma muna tare" sai ya miƙo mun wayan fuskar shi ɗauke da murmushi.

Kara wayan nayi ina mishi sallama shima daga ɗayan side ɗin yake amsama mun, lokaci guda kuma duk sai mukayi shiru, har na ɗauka wayan ta yanke ne, zan miƙawa Besty sai naji muryan shi yana cewa.

"Me kuke shiryawa ne?Zainab tazo ta duba kin?" lokaci ɗaya ya haɗa mun tambayoyin, cikin rufewa da jin voice ɗinshi nace, "walaimah zamuyi yau," batare dana amsa ɗayan tambayan ba.

Amma kawai sai na sake jin shi yace, "Zainab jiya tazo"?

"Hala tazo bata sameni ba, don jiya munje saloon" na faɗa har wani rawa muryah na yakeyi.

"Batazo ba kenan, don data zo ae da angaya miki" yafaɗa yana jan tsaki, ina sauri na miƙawa Besty wayan kawai saiji nayi yace.

"Shikenan daga gobe kinzama mallakin shi ko"?

Nidai sallama kawai na mishi na miƙawa Besty wayan don gaskiya baxan iya bashi amsa ba.

Hiransu suka ɗan taɓa kaɗan, sannan Besty ya tashi ya tsaya yana kallona yace, "kema naga alaman kin kasa sakewa da Hammah nah, don naji muryanki har rawa yakeyi", ya faɗa yana

dariyan yanda nayi da fuskana.

"Hmmm ina zan iya sakewa da shi? Nifa wallahi tsoron shi nakeji"  dariya Besty yayi yace, "kar kidamu wataran zaku saba, bayida matsalah idan ka fahimce shi, shidai baya son rashin gaskiya ne, kuma yana son ka bashi girma sosai, kuma shi mai tsafta ne sosai, da son faɗin gaskiya, idan ka gane mishi zaku zauna lafiya" ya faɗa yana matsuwa kusa dani.

Ganin munyi daf da daf nace, "ammm Besty kaima goben dakai za aje kafin madakin"?

"kai kaji mun yarinya idan banje ba wazaije mun"? Ya faɗa yana harara na, dariya nayi nayi hanyan waje ina ce mishi, " toh yaushe zaka dawo"?

matsowa ya ƙarayi yace, "yaushe kike so my wife na dawo?"......... Murmushi nayi cikin shagwaɓa nace, "anjima idan mungama walimah".

Shima cikin kwaikwayona yace, "insha Allahu zaki ganni don na lura baki gajji da ganin haɗaɗɗen mijinkiba" ya faɗa yana fita waje bakin shi ɗauke da dariya, nima dariyan nayi nabi bayan shi.

Tunda na shiga Adda Umaima da Besty suke mun mitan na daɗe, wai shi Babaganan nan ya cika rashin haƙuri shida gobe za'a kai mishi mata amma yake ta rawan kan zuwa, inji Adda.

Nidai hawa kan gado nayi ina ra musu dariya, "ki sauƙo a miki zanen baƙin lallan" inji Besty dake ta harara na.

"jan ma kaɗai ya isa inji mai abin, don shi baya son baƙi" na faɗa ina jan blanket ina rufe fuskana don ganin irin kallon da suke mun.

"ae kuwa baki isa ba inji Besty, jomai iri ɗaya za'a mana"   kallon ta nayi nace, "sannan Babagana Nuhu Jama'are, toh naga wanda zanyi don shi yace iya haka ya isa, ke kuma a sowa"? Na faɗa ina murguɗa mata baki

Dariya Aunty yagana tayi sannan tace, "gaskiyanki amarya abinda mijinki ke so shi zakiyi", kowa yagama mitan shi ina shiru, babu yadda suka iya dani haka suka barni.

Ana sallan la'asar aka fara kai mutane wurin waliman wanda za'ayi acikin multi-purpose, lokaci guda gidan ya kachame da hayaniya.

Haka mai make-up ta gama mana, aka bamu kaya iri ɗaya, lemon green, ba ƙaramin kyau mukayi ba, Motan Aunty ladidi ne yazo ɗauke da Fauxy a ciki, wanda duk kanmu kaya kala ɗaya muka saka.

Har hall ɗin aka kaimu lokacin mutane sun cika maƙil, bayan mun shiga ne malama juwairy ta buɗe taro da wa'azi, gaba ɗaya hall ɗin bakajin komai sai sautin muryanta.

Duk jikina yamun sanyi yadda take mana bayanin daraja irin na miji, lokaci ɗaya naji hawaye ya zubu mun domin tunawa danayi da wancan satin mijin ƙawata Fauxiyyah AA Othman ya rasu a hatsarin mota, hanyar shi ta dawowa daga ɗaurin aure dayaje Azare.

acikin zuciyata nace, "Allah sarki Fauxy lallai kinyi rashin abokin rayuwa, duk auren nasu bai wuce 2yrs ba fa, Allah kabamu zaman lafiya da mazajen mu, Allah kasa muyi rayuwa mai tsayi tare dasu" kawai saiji nayi Besty tace "Ameen".

Da sauri na ɗaga kaina na kalleta, saita saka tissue ta share mun hawayena tace,

"insha Allahu zamuyi rayuwa mai tsayi da su,nasan rasuwan mijin Fauxiyyah AA ya ɗaga miki hankali, ba komai insha Allahu za muna saka ta cikin addu'an mu, ki maida hankali kinga su Ummi idon su yana kanmu.

Ina ɗaga kaina kuwa muka haɗa ido da Ummi na, kawai saina samu kaina ina mata murmushi, ita ma martani ta maida mun.

Har goma da rabi na dare ya wuce banji Besty yace mun gashi ya iso ba, sai naji banji daɗi ba ko kaɗan, haka na tashi nayi shirin kwanciya na shiga ɗakin kusa da Besty na kwanta ,ita kuma banda hira da friends ɗin mu babu abinda sukeyi, ku ta kansu banbi ba na kwanta na rufe ido na.

Ana sallan asuba muka tashi mukayi sallah, ina kan sallaya sai wayan Besty ya shigo mun, ina kallo kaman bazan ɗauka ba don gaskiya jiya raina ya ɓaci na rashin zuwan shi, amma wata zuciyar ta kwaɓe ni, nace abinda zuwa anjuma kaɗan nazama mallakin shima.

Ɗauka nayi kawai nayi shiru, jin nayi shiru bance komai ba, sai yayi ɗan murmushi amma mai sauti yace,

"a mun uzuri wallahi Beauty zazzaɓi ne ya rufe ni, dana sha magani ban san nayi bacci ba, sai after 1 na tashi.

Kema kinsan bazanɓiya ƙun zuwa ganinki da gangan ba, domin kinfi kowa sanin hakan".

Ajiyan zuciya nayi sannan nace, "good morning my noroul qalbi"! Rufe ido nayi kaman muna tare saboda wani irin shauƙin so nakeji a wannan lokacin, don gaskiya bansan ina son Besty ba sai kwanan nan.

Murmushi yayi yace "bansan yaya zan gaya miki irin farin cikin da yau nakeji ba, gaskiya muna dawowa daga ɗaurin aure Insha Allahu direct wurinki zan taho na ganki, domin shi ne kaɗai zai sakani samun nutsuwa yau ɗinnan.

Dariya nayi nace, " haba swit luv ni na ɗauka ma cewa zakayi yanzu zaka zo naganka, ni wallahi bazan iya jiran sai ka dawo ba, kawai kazo kafin ku tafi kaga kwalliyata" na faɗa ina mishi kukan shagwaɓa.

Dariya yayi yace zai biyo ya ganni,

"Hmm baby nah yau zan sha shagwaɓa, kaman na taho na ganki nakeji, amma bakomai yau dai insha Allahu zan dawwama a rayuwar farin ciki domin kasancewa tare da abinda nafi so a rayuwata" ya faɗa yana jan iska a bakin shi.

Hira mukayi tayi har wurin ƙarfe bakwai, sannan akace na fito nayi wanka ,haka mukayi sallama kaman ba muƙi abar mu akan wayan ba.

Ina wanka muka saka dogon rigan atamfah na super, Da sauri na wuce gidan mu.

Daidai lokacin su Hammah Walid suka fito zasu wuce Kafin -madaki, gaishe su nayi, bappah yana cewa "kai amaryah kinyi kyau kaman ba gobe, wannan ae sai ace ba ƙanwar Sadiq bace tsabar kyau, domin gaskiya babu haɗi ta wajen kyau" ya faɗa yana dariya.

Hammah Sadiq ya harare ni yana cewa, " kada ma ki yadda yarinya don wallahi dariya za'a miki, bandake ina kika taɓa ganin baƙar amaryah tayi kyau"?

Murguɗa mishi baki nayi, na wuce cikin gida don ganin Hammah Khalifa ya fito, don ni shima

shakkan shi nakeyi saboda rashin sake fuskan shi.

A can giɗan su Besty kowa ya shiga mota domin wucewa wurin ɗaurin auren, Gidaɗo dasu Abdallah tun 9:30 suka wuce da Baba  Kasancewar 11:00 za'a ɗaura auren, kowa yayi kwalliya mai kyau.

Can na hango Besty yasha fara Gezna sai walƙiya yakeyi, daga gani babu tambaya kaga ango ɗan gaske.

Side ɗin Mama ya wuce cikin sauri, yana shiga palon aka fara ga ango ga ango, yana dariya ya gaida kowa sannan ya wuce ɗakin Mama.

A kan bedside drowa ya hango Mama zaune , ƙasa kuma Umma ce ke breakfast, har kasan ya durƙusa ya gaisheta, tana fara'a ta shafa kanshi tace Allah yabada sa'a maigida na, Allah yasa adace, Allah yasa agama taro lafiya kowa ya koma gida lafiya.

Da farin ciki ya amsa da ameen, sanan ya ƙarisa bakin gado inda Aunty Fanna da Aunty Falmata suke zaune, suma har ƙasa ya duƙusa ya gaishe su, fuskan su ɗauke da fara'a suka amsa mishi, kowa bakinta ɗauke da addu'a.

Tashi yayi ya ƙarisa gaban Mama ya durƙusa, ya ɗaura hannu shi duka biyu kan cinyanta yace,

"sweet mum antashi lafiya?" Mama bata amsa mishi ba, sai ya ɗauki kanshi ya kwantar kan cinyanta yace.

"Mama nasan irin  soyayyar dake tsakanin mu da ke babu mai iya raba mu, Sai Allah amma bawai ɗan adam ba, kisaka aranki ni ɗanki ne mai biyayyah agareki, kuma babu abinda zai sa na kauce akan haka,kiyi haƙuri ki yafe mun, kada kiga kaman naƙi miki biyayyah, wallahi kullum zuciyata bata da sanyi akan wannan al'amarin, amma babu yadda muka iya da abinda Allah ya aiko, kawai kimun Addu'a, ni kuma na miki alƙawarin zaki same ni da mai ƙara miki biyayyah sama da wanda nake miki yanzu.

Tashi yayi yakama hanyan fita baice wa kowa komai ba, har saida yaje bakin ƙofa tukun ya waiwayo ya kalli Mama yace.

"Mama amana addu'a sai mun dawo, sannan ya juya ya fita idon shi cike da hawaye, yau ranan auren shi amma Mama bata farin ciki da auren.

Suna shiga motan ya juya ya kalli Hamza abokin shi yaace "don Allah mubi gidan si Riyyah zan bata saƙo,"   Hamza hararan shi yayi yace, "kasan saura mota uku ne kawai kowa ya tafi"?

"ehh abu kawai zan bata mu wuce"

Wajen 10:15 sai ga wayan Besty akan nayi sauri na fito don kowa yayi yagaba kusan su kaɗai ne basu wuce  ba.

Jiki na rawa na fito, amma kafin na ƙarisa yayi sauri ya buɗe motan ya fito zuwa inda nake, yana zuwa yace.

"Baki taɓa mun kyau irin na wannan rana ba, kuma har abada bazan taɓa daina ganin wannan kyau a idona ba.

Ya miƙo mun wata diary yace ki ɓoye mun Beauty bayan auren mu hankali ya kwanta zan karɓa, kada fa ki buɗe mun sirri na" ya faɗa yana dariya, nima dariyan nayi nace "Allah ya kaiku lafiya "ganin ya juya da sauri ya shige motan.

Baba ne yake magana da Yusuf abokin Hammah Umar cewa ya akayi su Babagana suka so su makarane? Yana kallon agogon hannun shi, yana cewa ƙirashi mana Yusuf muji ina suka tsaya ne? Saura 15mint a ɗaura fah.

Yusuf yana ta ƙiran number amma ba a ɗauka ba, can sai ga Abdallah da sauri yazo wurin da Baba suke tsaye dasu Yusuf, da sauri ya riƙo hannun Baba yace.

"innalillahi wa'ina ilaihir raji'un, Baba yanzu wani abokin su Hammah Babagana ya ƙirani wai Hammah sun samu accident a hanya.

Kama hannun shi Baba yayi da ƙarfi ƴace, "ƙira shi ka tambayamun yayah Babagana nawa yake?

Wayan Abdallah ne ya shiga ringing, da sauri ya ɗauka yana cewa "hello Salisu yaya kuna ina ne fatan dai babu wani matsalah mai girma ko ? Muma gamu nan zuwa."

Sai kuma naji yace "innalillah" .

Dayake zuciyata a cikin rauni take, sai naji nakasa sauraron abinda zasu ce da kyau, saboda alhini rasuwan Aliyu dana ke ciki, abu ɗaya kawai naji yace, abokin Babagana ɗaya ya rasu ko waye, Allah dai yasa ba Hamza bane..

*KU KASANCE DA ALƘALAMIN AUNTY NICE, DOMIN CIGABA DAJIN ABINDA YA ƘUNSA* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*
*1441H/2019M.*

®☄
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION✍*
_{Gaskiya ɗaya ce daga kinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira.}_

🎐G•W•A🎐
_*GASKIYA DOKIN ƘARFE•* 🏇_

Story and written
By
*AUNTY NICE*

*_WANNAN BOOK SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Wattpad@GaskiyaWritersAsso.~

*PAGE* 36---37

*__________📖* Baba ne ya matso kusa da Abdallah gaba ɗaya illahirin jikin shi rawa yakeyi, riƙo hannun Abdallah yayi yana cewa "me kaji sunce ƴan biyu"?

Rungume Baba Abdallah yayi yana ƙara sautin kukan shi, lokaci ɗaya Baba yaji hankalin shi ya na neman birkicewa, riƙo Abdallah yayi jikin shi sosai, ya rasa kalma ko ɗaya da zai fito a bakin shi.

Abdurrahman na gani mutane sun ɗago shi ana neman motan da za'a saka shi domin daga dukkan alamu suma yayi, hankali a tashe Baba ya dubi Yusuf yace, "wai me yake faruwa ne Yusuf?"

Da sauri Yusuf ya matsa kusa da abokin Abdurrahman yana tambayan shi abin da ya faru?

Daga nesa na hango Abba yana sauri hannun shi rike dana Abban bch suna tahowa inda su Baba suke.

Abba ne ya riƙo hannun Baba yana faɗin "Alhaji kada ka ɗaga hankalinka, dolen mu murungumi abinda Allah ya aiko mana hannu bibbiyu, yayaj zamuyi Babagana lokaci yayi, yanzu sai muyi sauri mu wuce bauchin".

"Bana fahimtan fah abun da kuke faɗa"inji Baba dayake riƙe da Abdallah har lokacin, kuma daga dukkan alamu Baba ya shiga ruɗani ne.

Kafin kace komai jar gurin ya ɗauka da batun hatsarin su Babagana da kuma rasuwar shi.

Babu ɓata lokaci taron ɗaurin auren ƴa fara watsewa, domin dukkan illahirin jama'an wurin mota kawai ake shiga ana komawa bauchi.

Gaba ɗaya haraban specialist hospital bauchi cike yake maƙil da motocin ƴan ɗaurin aure, wanda ya rikeɗe yanzu ya koma na karɓan gawan su Babagana.

Allahu Akbar kullu nafsin zaƙikatul maut, dama duk mai rai sai ya ɗanɗani zafin mutuwa, yau kuma an wayi gari da raɗaɗi da ciwon mutuwar Babagana Nuhu Jama'are, wanda ya rasu a tafiya ɗaurin auren shi da Fatima Badariyyah.

Dayake Babagana mutumin mutane ne, wanda zan iya cewa duk gidan su babu wanda ya kai shi yawan jama'a da abokanai, domin kuwa shi koda abokan Baban shi ne sunfi sabawa da shi, ga dayawa kataɓa a garin bauchi zaka samu akwai mu'amalah mai kyau tsakanin su, shidai Babagana mutumin mutane ne.

Babu ɓata lokaci aka wuce dagawan zuwa gidansu dake GRA.

Tunda Besty ya shiga mota suka tafi naji zuciyata kaman zata tarwatse, haka kawai naji zazzaɓi yana shirin kamani, a cikin hankali da nutsuwa na wuce gidan mu, kai tsaye ɗakin Abba nah na buɗe na shiga na kwanta, domin hayanin gidan namu yayi yawa.

Ko minti ashirin banyi da kwanciyaba naji gaba na yana ta faɗuwa, lokaci ɗaya naji babu abinda nake so sai kawai naji muryan Besty na, da sauri na ɗauki wayana da nufin na neme shi, sai naji gabana yana faɗuwa, bazan iya ƙira ba.

Komawa nayi na kwanta, amma sai naji bazan iya hassala komai ba, sake tashi nayi na zauna na zubawa ƙasan ɗakin ido na rasa tunanin me nakeyi.

Ƙaran buɗe ƙofan ɗakin ne yasa na maida ido na bakin ƙofan, Ummi na nagani ta shigo tare da Aunty na, kallona Aunty tayi tace, "auta nan kika dawo?halan hayaniya ya miki yawa ko"? Ta faɗa tana ajiye coolern da ke hannun ta.

Bansan me nake ji ba a raina kawai samun kaina nayi da fashewa da kuka, wanda duk kansu sai da suka dawo da kallon su kaina.

Aunty ne tazo inda nake ta jawo ni jikinta ta rungume ni, tana cewa "haba Riyyah ke da yau shine rana mafi ranaku girma awurinki da zakiyi sallah ki miƙawa Allah godiyanki, amma sai ki nemi ɗagawa mutane hankali? Ko kina kukan rabuwa da Ummin kine?" ta faɗa tana bubbuga baya na.

Samun kaina kawai nayi dacewa "Aunty gaba na yana faɗuwa, ki ƙira mun wayan Besty na naji muryan shi don Allah ko hankalina zai kwanta" na faɗa ina kara sautin kuka nah.

Ummi ce tayi tsaki tafita a ɗakin tana cewa, "na ɗauka rabuwa da iyayenki da ƴan'uwanki kike ashe ke can ta mijinki kike yi, toh Allah ya shiryeku yaran yanzu".

Ko kulata Aunty na batayi ba, ɗaukan wayan tayi da niyyan zata ƙira shi, dai-dai lokacin wayanta ya fara ringing, ganin number Gidaɗo ya saka ta ɗauka da sauri, tana cewa "an ɗaura ne Gidaɗo"?.

Da ƙarfi yake faɗin "Aunty mun shiga uku Hammah Babaganan mu yayi accident ya rasu Aunty, wayyo mun rasa ɗan'uwan mu Aunty" haba daya ihu yake mata kaman zai fasa mata dodon kunne.

Sandarewa Aunty tayi na zuwa wani lokaci, dukkan idonta a zare suke, kaman wata zararriya kuma sai ta fasa wani irin ihu wanda saida illahirin gidan ya ɗauka, sannan ta koma tayi shiru kaman mai tunani.

Da sauri Ummi tashigo ɗakin tana faɗin "innalillahi wa'inna ilaihir raji'un, haba Fatima keda zakiyi addu'a mai yakai ki da ihu kuma," ta faɗa itama tana fashewa da kukan, amma marar sauti.

Da sauri ta rungume ni tana faɗin "kidinga faɗin Innalillahi Badariyyah na" nidai dukkan su ƙura musu ido nayi don ban fahimci me suke faɗiba, amma cikin zuciyata cewa nakeyi hala Mama ta hana Besty ya aure ni, hmmm lallai matar nan tsinanniya ɗe, toh komai masifarta da bala'in ta saina aure Besty, don bana jin zan iya rabuwa dashi ko shi ya sjiryawa rabuwa dani.

Kuma hawaye nakan zuba mun a ido na wanda ko ɗaya na rasa dalilin shi.

Muna cikin haka saiga Mummy da bataliyan gidanta duk sun shigo sai kuka sukeyi.

Da gudu Besty tayi kaina tana "wayyo Besty munyi rashin Besty Babagana a rana da muka fi buƙatan shi a rayuwar mu".

Miƙewa nayi na tsaya ina kallonta nace, "Maman shi ta hana ya aure ni ko"? Kowa ɗaga ido yayi yana kallo na.

Aunty ce ta dawo dani kan cinyanta tana kuka tace," Riyyah nah dama hana auren tayi aka fasa yafi mun sau dubu, amma yau munyi rashin ɗanmu mai son zumunci ,ɗan mu nagari mai halin dattaku, Badariyyah yau Allah  daya fimu son Babagana ya karɓi abun shi a lokacin da muke tsaka da ƙauna dashi" fashewa Aunty tayi da kuka mai ciwo, irin wanda kake rasa wani irin zafi zakaji cikin ranka.

Basu ankara ba kawai sai suka ga na suma musu, gaba ɗaya ɗakin ya sake hargitsewa da kuka.

Da ƙyar suka samu na farfaɗo amma ban sake cewa uhm ba bare uhm-uhmm, kawai bin kowa nakeyi da ido.

Aunty ce ta ɗauke mu cikin motan ta muka wuce gidanta,  Mummy ma ta ɗauki su Besty suka wuce anata motan.

Kafin kace me ƙofan gidan ya cika maƙil da mutane, da ƙyar muka samu hanya muka shigo gidan, kowa ka dubi fuskan shi kuka yakeyi, ba maza ba bakuma mata ba, haka muka shige har palon side ɗin Mama.

Umma ce riƙe a hannun Aunty Fanna banda salati babu abinda takeyi, gaba ɗaya palon bakajin kuka wane ko wane, duk ya kachame da kuka.

Mama na hango durƙushe a ƙasa kusa da ƙafan Aunty Falamata ta riƙe ƙirjinta sai kuka takeyi tana faɗin.

"Babagana na yafe maka, ashe dama mutuwa zakayi kabarni? meyasa ban maka magana ba tau daka shigo ? Wayyo Allah na rasa ɗana mai tsananin ƙaunata da yimun biyayyah, Allah na tuba kayafe mun abinda na yiwa ɗana, nabar shi ya auri wacce yake so ko sunkai guda huɗu ne ƴan uwan Fatima, wayyo Babagana na".

Kowanmu samun wuri yayi zauna suna ta kuka, amma ko alaman hawaye babu a ido na, nasamu na zauna ma  a wannnan lokacin amma abu ya faskara, narasa me nakeji alokacin, kawai binsu nakeyi da kallo.

Aunty Fanna ce ta taso tazo ta rungumeni jikinta tana kuka tana cewa, "Badariyyah munyi rashin Babagana, yau kan ya tafi ya barmu a lokacin da muka fi buƙatanshi, innalillahi wainnah ilaihir rajiun".

Kamo hannu  na tayi har inda Umma take zaune ta zaunar dani, amma nakasa yin komai Umma ce ta rungumeni tana faɗin.

 "kiyi kuka ƴar nan kada ya kume miki a zuciyarki, tabbasa Babagna ɗane da ya haihu kuma munyi rashi mai girma yau a cikin zuriyar mu, don babu tantama ina son Babagana sama da ƴaƴan da na haifa a cikina, ba komai ba sai saboda biyayyan shi da kuma son ƴan'uwa, amma baiyi sa'ar uwa ba, nidai amatsayina na kakar shi na yafe shi Allah ya karɓi baƙuntan shi", ta faɗa tana riƙe ni kaman zata shiɗe don kuka.

Lokaci ɗaya na dinga jera ajiyan zuciya kaman zuciyata zai fashe nakeji, da sauri Auntƴ Falmata ta miƙo mun goran ruwan Faro tana kuka tace.

"kisha Badariyyah tabbas yau kinyi rashi kema,mai girman gaske, don jiya Babagana yake gaya mun irin tsananin ƙaunar da yake miki da irin burikan da yaci akanki idan ya aure ki, ashe Allah

bai nufa za'ayi rayuwar auren tare ba" ta faɗa tana ƙara fashewa da kuka.

Nidai babu abinda nakeyi sai kallon Mama kuma ko zaka yankani bansan kallonta nakeyi ba, a haka an a zaune mata ke ta shigowa kowa ta shigo sai kaji tana faɗin halin Babagana masu kyau.

Bamufi minti arba'in ba, saiga Abdallah dasu Gidaɗo sun faɗo palon kowa kuka yakeyi, da sauri aka tafi aka rungume su.

Abdurrahman kan cinyan Umma ya kwanta yana, "Umma Hammah nah, Hammah na yau yatafi ya barmu, dama jiya yace yabamu amanan  Maman shi aduniya ita da Riyyah baya son ya saɓawa kowansu, don Allah mukala mishi da su, wayyo Hammah na dama tafiya zakayi kabarmu"? Ya faɗa gaba ɗaya palon sai kuka akeyi.

Khalifah ne ya zo har inda nake ya tsuguna ya riƙo hannu na yace,

"Adda Riyyah addu'a kawai Hamman mu yake buƙata daga garemu, jiya yace mun idan Allah ya nufa ya aure ki sai ya nunawa duniya babu mace mafi girma da daraja a wajen mijinta sama da yadda zai nuna miki, idan kuma ta Allah ta kasance akanshi bai aureki ba, toh ya bamu amananki dukkanmu masoyan shi yace mukala mishi dake har ƙarshen rayuwar mu".

Sannan ya tashi ya koma gaban Mama ya dafa cinyanta yana kallon idon ta yace,

"tabbas Mama kinyi rashi mai girma a duniya, kullum Hammah na yana gaya mun babu abinda yake so sama dake, kuma babu abinda ya damu da shi sama dake, amma a daren jiya sai yace mun Khalifah kai yaro ne amma zan gaya maka wani abu, duk ranan da akace na mutu toh kacigaba da kula mun da Mama na kaman ina raye, kuma kace mata taya femun duk wani abu dana mata a rayuwa, kace nata idan aure na da Badariyyah zai zamo abin mafi girma da bazata ƴafe munba toh ina roƙan Allah Albarkacin biyayyan dana ke mata kada yabani daman yin wannan auren.

Amma yau da safe sai yace mun tun da yaga har yau ba'a fasa ba yana ji aranshi wataran Mama zata so Riyyah, yana farin ciki yace mun yau ya tashi da wani irin farin ciki, ko hala yana dawowa daga ɗaurin auren Mama zata ƙirashi tace, Babagana nah na yafe maka duniya da lahira ku zauna da matar ka har abada , ya faɗa yana ta dariya".

Saboda haka Mama kinyi rashin Hamman mu mai tsananin ƙaunar ki, yau dai kam ki yafe mishi saboda Allah," ya faɗa yana fashewa da kuka.

Gaba ɗaya palon kuka akeyi, Gidaɗo yana kan cinyan Aunty sai juya kanshi yakeyi kaman

shima mutuwan zaiyi.

Ana haka su Baba suka taho da gawan Babagana, ba a ɗauki lokaciba aka mishi wanka cikin gaggawa, sannan aka aika Mama su zo tare da ni mu mishi addu'a na ban kwana.

Mamace da Umma suka fara zuwa kanshi, Mama ta tsuguna tana "Babagana na yafeka duniya da lahira, dama baka mun komai ba, nima ka yafe mun kaji ɗana!" ta faɗa tana ta jero mishi addu'a tana kuka tana ta yafe shi duniya da lahira.

Baba ne yazo ya ɗaga ta yana ya isa haka Zahra, Mama tana kuka tana riƙe da Baba tana, " wayyo Alhaji banyi ban kwana da shi ba ɗaxu, amma wallahi har cikin raina na yafe shi domin kuwa yayi mun biyayyah yaron nan, Allah dai ya karɓi baƙuntan shi,

Umma ce tazo ta dubi fuskan jikanta tana share hawaye tace,

"Allah ya haɗaka da mala'ikun rahma Babagana Allah ya karɓi baƙuntanka, Allah ya maka rahma, Allah yasa halinka nagari ya bika, tabbas kamana biyayyah Allah ya jiƙanka ɗana, domin kuwa kai ɗane mai albarka agareni, ta cigaba da mishi addu'a daga nan ta tashi.

Har inda yake Aunty Fannah ta ajiyeni, sai a sannan naji wani ƙarfin hali yazo mun ina kallon fuskarshi wanda yayi kaman yana bacci nace.

"Tabbas mutuwa wa'azi ce, kuma ba a sabo da ita, Babagana bakayi gaggawan tafiya ba, kuma bakayi jinkiri ba, inda ka tafi ko yau ko gobe ko anjima ko yanzu yanzu dole muma zamu tafi idan lokacin mu yazo, kaima yau ne naka lokacin yaxo, Allah ya jiƙanka Babagana Allah yasa mutuwar ka tazama hutu a gareka, Allah yasada ka da rahma, muma idan ta mu ta zo Allah ya bamu sa'an tafiya, kallon shi nayi sai naji kaman zai amsa mun amma babu, wannan ya wuce tsakanin mu kenan har abada, tuno shi nayi kwanaki dayake ce mun Besty da a faɗa mun an fasa auren mu gwara nabar numfashi, don bazan taɓa rayuwa babu kebahar abada".

Ɗago Kaina nayi ina bin kowa da kallo wanda sai alokacin naji hawayw yana bin kunci na, ido na bai sauƙa akan kowa ba sai akan fuskar Yusuf abokin Hammah Umar da yake ta share hawaye.

Cije leɓe na nayi sanan na dubi fuskar gawan Besty nah nace, "Hammah Yusuf kai kan kasan ina son Babagana ko?" juyar da kanshi yayi gefe yana share hawaye bai cemun komai ba.

Ɗagowa  nayi ina kallon Abba nah nace, "Abba kaga gawan wanda zan aura, kuma kaima kasan ina son shi sosai ko Abba? na dawo dakaina daidai fuskan Besty nace, Ina sonka mijina, nasan an ɗaura auren kuma babu wanda ya isa ya ɗauke mun kai kaji Mijina ina sonka zan zauna da kai yau a nan wurin," na faɗa ina kifa kaina akan shi domin sai lokacin naji ƙirjina ya sake wani kuka mai ƙarfin gaske ya taho mun.

Abba nane ya matso har inda nake ya saka hannu ya ɗaga ni, ina girgiza mishi kaina, alaman ya barni amma ina haka ina gani ya fito dani zai wuce inda su Aunty suke tsaye.

A wurin da zamu fita naga su Hammah na dukkansu tare da Yayah Kamal a tsatstsaye kowa yana share hawaye .

"Hammah Saduq ɗina kaga wai wancan gawan mijinane da zan aura fah, Besty nane fah wai suka ce ya rasu, kaima ae kasan ina sin shi ko"?

Rungume ni yayi muka fita a wajen, ina kuka shima yana kuka, haka Hammah Walid yazo ya haɗa mu ya rungume mu shima yana zubar da hawaye, ina kallo aka ɗaga Babagana na aka fita dashi.

Hmm mun rabu kenan ko na faɗa, daidai ina sulalewa a wurin a sume.

Nima Aunty nice barin wurin nayi ina kuka kaman mutuwan na gidan mu ne, Misa Xerks na riƙe da hannu na tace kawai ki dakata da rubutun nan Besty kije ki hutu haka, itanma fah kukan tayi, domin ta daɗe ta na roƙan na sato mata number shi, don kawai suyi soyayyah amma nayi biris da ita, dama nabata ko ɗan gaisawa suyi.

*BADARIYA FANS*

*MUYI NISHAƊI GROUP*

*GASKIYA WRITERS*

*UMMU ASMA'U NOVEL*

*NOVEL 3 NA MAMAN AFEE*

*NOVELLA NA EASHAA*

*NABILAT LADY GROUP*

*_TABBAS WANNAN SHAFI NAKU NE, DOMIN NASAN ZAKU TAYA BADARIYYAH JIMAMIN MUTUWAN BESTY, DUK DA NASAN KUN DAƊE KUNA MISHI FATAN MUTUWA, AMMA YAU ƊAYAN NAN KAN KU MATA GAISUWAN RASHIN SHI_*

*DAGA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*
*1441H/2019M.*

®🖋
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION✍*
_{Gaskiya ɗaya ce daga kinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira.}_

🎐G•W•A🎐
_*GASKIYA DOKIN ƘARFE•* 🏇_

Story and written
By
*AUNTY NICE*

*_WANNAN BOOK SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Wattpad@GaskiyaWritersAsso.~

{*_Aisha Usaman (mama Abdallah) na Miss Xeks Novella@, wannan shafi kyautace gareki, don

ƙaunarki da books ɗinmu, Allah ya barmu tare._

*page* 38___39

*_________* 📖 Bani na farfaɗo ba har saida aka dawo daga kai Besty nerh! .

Tunda na buɗe ɗaki naga mata ƴan office ɗin su Aunty da ƴan uwan Baba daga jama'are cike a ɗakin Aunty nah wasu suna palo, sai na tabbatar wa raina lallai na rasa Besty har abada.

Babu wanda ya lura da kukan da nakeyi sai Adda Humairah a hankali ta dafah baya na itama tana kukan, Mummy ce ta matso kusa damu tana ta bamu haƙuri.

A can karshen gadon na hangi Aunty nah ta kudundune cikin hijabin ta tana ta kuka.

Gefe ɗaya kuma Umma ce zaune akan kujeran ɗakin, Goggo na gefenta kowansu zaune cikin alhinin wanna rashi da mukayi.

Tunda akayi rasuwan nan ban samu na leƙa koda palon Aunty ba, ballantana ya danganani da waje, don ko Baba har ɗakin Aunty ya shigo muka gaisa, yayita bani baki, har yana gaya mana rikecewan da Hammah Umar yayi, amma inda yake sun hana shi zuwa, saidai sun nemi alfarman tura matar shi ko hankalinshi zai kwanta.

Nidai babu abinda yake damu na kowani lokaci sai tunanin irin rayuwar da mukayi da Besty nerh!.

Hmmm ajiyan zuciya na sauƙe lokacin da muke cin abinci da su Adda hummy, duk da tunda muka faraci bai fi spoon uku na ciba, saidai inata juya spoon ɗin a cikin plet ɗin.

Kallona Adda Hummy ta tsayayi cike da tausayawa, domin tunda na saka abincin a baki na, nake ta sauke ajiyan zuciya.

"Riyyah don Allah kiyi haƙuri kici abincin nan mana, Babagana fa addu'an ki yake buƙata bawai kiyi ta kuka kina saka damuwa a ranki ba Riyyah ta!" Adda Hummy ta faɗa tana kallo na fuskanta ɗauke da tausayi nah.

Share hawaye nayi nace mata, "naji Adda insha Allahu zan daina kukan," na faɗa ina kan share hawayen.

Tunda akaje aka dawo daga kai Besty Baba yace ana sallan azahar a ɗaura auren su Besty da Fauzy, don bai yadda ace antara mutane kuma a haƙura da auren ba, mutuwa dai anriga da anyi shi, sai dai addu'an Allah ya jiƙanshi.

Haka akayi ana ɗaura auren aka saka kowani ango ya ɗauki amaryar shi, ba tare da anyi wani rakiyan amare ba.

Washe gari kuma saiga kowacce amaryah angonta ya kawo ta, ranan Besty tayi kuka kaman ranta zai bar ruhinta, nidai saidai binsu kawai nake da ido.

Bayan anyi sadakan uku kowa ya koma inda yake.

Washe garin bakwai ɗakin daga ni sai Aunty ina tayata muna gyaran ɗakin, sai jifa-jifah mata suna shigowa ƴan gaisuwa, har lokacin nakasa daina zubar da hawayen rashin Besty nerh!.

Aunty ko rana ɗaya bata taɓa ce mun uffan ba, koda zan zauna ina kukan, saidai itama ta nemi wuri ta zauna tayita kukan.

Muna cikin haka saiga Baba ya shigo har ɗakin Auntyn bayan shi kuma Gidaɗo ne,   "haba Fatima mau zangani haka? Kinsa yarinya agaba kuna ta kuka, abinda ya kamata ke kibata hakuri amma saiki biyeta kuna kuka?Babagana ya riga ya barmu a yanzu tsakanin mu da shi fah addu'a yafi buƙata.

dama kin hanata tafiya ne, don ta zauna kuyita kuka Fatima?"

share hawaye Aunty tayi tana duban Baba tace, "Baban Umar dole ne nabar Riyyah ta zubar da hawaye duk lokacin daya zo mata,domin ita mai yawan haƙuri ce, idan na hanata to tabbas zai mata lahani, amma kayi haƙuri zamu gyara daga yau", ta faɗa tana share hawayen idonta.

Nima ina zaune bakin gadon Aunty sai share ido na nake tayi, inda Gidaɗo ya zo ya zauna a gefe na yana riƙe da hannu na bai ce komai ba, har saida su Baba suka gama maganan su, sanan yace "kiyi haƙuri Adda nah, kuma kiyi ta mishi addu'a kinga muma kullum cikin mishi addu'a mukeyi, don shine kawai ƙauna da yayi saura a tsakaninmu ".

Ɗaga kaina nayi na dube shi,nace "insha Allahu ".

Baba yace wa Aunty, " Fatima ɗanki Umar an samu sun barshi zaizo yayi sati ɗaya, toh inaga zuwa jibi zai iso," ya faɗa yana juyawa yabar ɗakin hannun shi riƙe dana Mujaheed da shigowan shi kenan.

Kuma daga dukkan alama shima fa hawayen yake tarewa, kawai karfin hali yakeyi.

Duk yadda naso Aunty ta barni na koma gidanmu taki, don gani nakeyi idan nayi nesa da gidan su Besty zan samu sauƙin abun a raina, amma firr taƙi.

Allah sarki yau saiga Besty Feenah da Hammah Umar sun shigo bayan sallan ishaa, har ɗakin Aunty suka shigo suka same mu.

Kaman yau akamana rasuwan daga ni har Aunty kowa tana gefe ɗaya tayi shiru, babu mai kula ɗan'uwanshi, palo kuma su Gidaɗo ne zaune kowa ya riƙe waya a hannun shi, don kuwa babu mai iya koda kunna TV ne a gidan.

Bayan mun gaisa da Hammah ne, Besty ma ta gaisa  da Aunty, Hammah yanata mana nasiha akan muyi haƙuri, sannan yace, "Allahn daya bada Babagana ae yafi kowa son abinshi, saboda haka kada muyi butulci wa ubangiji,kuyi ta mishi addu'a Allah yasa yana kyakkyawan wuri"

 Kowa tace hakane, sannan yake cewa Aunty yazo mata sallama ne domin gobe zasu wuce da Besty domin ta karisa hutunta acan kafin ta koma school.

Aunty tace "hakan yana da kyau Haidar Allah dai ya baku zaman lafiya ya kawar da idon maƙita akanku" sannan ta ɗan taɓa musu nasiha shida matar shi.

Bayan mun raka su mun dawo Aunty take cemun, "Riyyah mun yanke shawara dasu Babanki akan zamu mayar musu da kayan auren tunda Allah bai nufa anyi auren ba" ta faɗa tana juyadda da kanta ɗayan side ɗin.

Ban iya cewa komai ba sai share hawayen da nayi na hau kan gado kawai na kwanta.

Allah sarki ranan da Hammah Umar ya iso, sai ranan ya zamawa jama'an gidan kaman shine ranan da akayi rasuwan, don yazo da safe kuma washe gari su Aunty Fanna zasu tafi, gidan gaba ɗaya rikicewa yayi da kuka, har Baba ya shigo akan ya musu magana, amma sai shima ya ɓuge da kukan, domin ko baka da imani ka kalli yadda Mama ta koma a cikin sati ɗayan nan sai ka tausaya mata.

Hammah komawa yayi ya rungume Baba yana kuka yana, "Baba baza a sake mutuwan da zai mun zafin irin na rashin Ɗan'uwa naba, Baba Babagana ya nuna mun so a duniya, ya mun biyayyah ko ɗan dana haifa iya kaci, bai taɓa mun fushi ba ko na rana ɗaya, Baba duk ranan

dana nuna ga abinda nake so toh daga ranan shima zai so abun, nayi rashin ɗan'uwa Baba nah".

Baba kama shi yayi sukabar side ɗin Mama.

Muna zaune a palon Aunty saiga Baba ya shigo rungume da Hammah bayan su kuma twins ne ke binsu kowansu kuka yakeyi.

Da sauri na tashi daga kwancen danake na zauna ido na na kansu.

Har gaban Aunty Hammah yazo ya tsuguna ya riƙe dukkan hannuta yace, "Aunty ɗan'uwa na mai sina yabarni har abada, Aunty bazan sake ganin Babagana ba , wayyo nayi rashi Aunty" itama Auntyn kuka ta farayi.

Baba yafara mata faɗa "haba yaya za'ayi Umar yayi haƙuri bayan na ɗauke shi can side ɗin Maman shi donke ki kwantar mishi da hankali kuma saike ma ki biye shi kina taya shi kukan? Ni a gidan nan har sai yaushe zaku daina sani tuna Babagana ne"? ya faɗa yana ta share hawayen shi shima.

Tashi nayi a hankali ina nawa kukan na wuce nayi hanyan ɗakin Aunty, ina daidai zan shiga naji muryan shi yana cewa.

"Fatima yayah mukaji da haƙuri? Wannan rashin namu duka ne", ya taso yana zuwa inda naja na tsaya.

"Fatimah!" naji ya sake kirana dai-dai lokacin da ya iso inda nake tsaye.

*GASKIYA ƳAN ƘUNGIYAR GASKIYA WRITERS BABU ABINDA ZANCE MUKU, DOMIN NA YARDA MUN ZAMA TSINTSIYA MAƊAURINKI ƊAYA, DOMIN IRIN ZUMUNCIN DA KUKA MUN ALLAH NE KAWAI ZAI BIYAKU,BABU WACCE BATA ƘIRANI TAJI YAYAH JIKIN ƊANA BA, GASKIYA NA GODE ALLAH YA BAR ZUMUNCI*.

# *Vote Comment Share&Follow*.

*DAGA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*
*1441H/2019M.*

®☄

*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION✍️*
_{Gaskiya ɗaya ce daga kinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira.}_

🎐G•W•A🎐
_*GASKIYA DOKIN ƘARFE•* 🏇_

Story and written
By
*AUNTY NICE*

*_WANNAN BOOK SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Wattpad@GaskiyaWritersAsso.~

*page* 40

*___________*📖 Juyawa nayi na kalli su Aunty da dukkansu idon su yana kanmu, sannan na maida kallona kanshi, lokaci guda naji zuciyata ta karye domin irin raman danaga Hammah yayi kaman wanda ya shekara yana jinyan ƙanjamau, ga wani hawaye dayake bin fuskanshi.

A hankali na amsa mishi da "Alhamdulillah"nima sai na samu kaina da fashewa da kuka.

Jiki na rawa yakamo hannu na ya riƙe ko kunyan su Aunty da Baba baijiba yace, "Fatima kiyi haƙuri Babagana ya riga ya tafi, munyi rashin shi har abada saidai muyi haƙuri da hukuncin Allah" ya faɗa jikinshi sai rawa yakeyi.

Da sauri naja hannu na na wuce ɗakin Aunty batare da na sake cewa komai ba, shima juyawa

yayi ya koma gefen Baba ya cigaba da zubar da hawayenshi.

Haƙuri su Aunty sukayi ta bashi ita da Baba har ya haƙura yayi shiru, sannan Aunty ta wuce kitchen domin ta ɗaura musu abinci.

Nidai gaba ɗaya ban sake fitowa ba wannan ranan ina kwance a ɗakin Aunty.

Washegari da safe na fito kitchen domin na taya Aunty haɗa break-fast, muna cikin aiki take cemun, "Riyyah yau idan Umar ya shigo zan gaya mishi maganan kayan Babagana da za'a dawo dashi, domin ita Maman su bawai fahinta zatayi ba" nidai har tagama maganan bance nata ƙala ba, har saida ta sake tambayana naji abinda tace? sannan nace, "duk yadda kukayi Aunty daidai ne".

Bayan sun gama break-fast sai Aunty ta gayawa Baba yadda suka shiryah maganan mayar da kayan.

Kallonta yayi yace, "Bari zan yi magana da ɗan'uwan shin, duk yadda muka ga zaiyi sai ayi" ya faɗa yana tashi domin wucewa side ɗin Mama su gaisa da su Umma.

Baba yana shiga ya samu duk suna zaune a palon Mama suna break-fast gaba ɗayansu, samun wuri yayi ya zauna suka gaisa da Umma dasu Aunty Falmata.

Daga nan ya sanar dasu yadda sukayi da Aunty'a game da kayan da za' dawo dashi.

Umma ce tace "ikon Allah shikenan Babagana wato an rabu kenan har abada" ta faɗa tana share hawaye, suma su Mama gaba ɗaya saida suka share hawayensu.

Hammah yana kallon Baba yace, "Baba adai da kata tukun bayan zu ba sai munyi magana daga baya" ya faɗa yana ture pilet ɗin gaban shi.

Mama ce da sauri tace, "haba Hamman su wani irin bayanzu ba, so kake abar kayan su ɗauka an bar musu ne? Kafa san bata da gadon Baba nah" ta faɗa jaman zatayi ihu.

"ikon Allah ashe bazaki taɓa hankali ba? Na ɗauka mutuwan nan kaɗai ya isheki ishara"? Umma ta faɗa ranta duk ya ɓaci da halin Mama.

Baba ma idon ya zuba mata cikin zuciyan shi yana cewa, "Allah kaɗai yasan irin zuciyar da ya bawa wannan baiwa tashi na baƙin kishi" a fiƙi kuma tashi yayi zai fita yace, "Zahra Allah ya shiryeki don girman ma'aiki, amma wannan halinkin gaskiya yana bani tsoro yanzu kam, na ɗauka keda tada hankali akan ko wani ɗanki ya wuce domin wannan rashin da mukayi? amma sam babu haka a ranki". Ya saka kai ya fita yabar palon.

Aunty Fanna ta miƙe tace, "Umar akai mu airpot kada mu makara, nima maidugurin zanje ɓa duba jikin Umman mu," sannan ta juya inda Mama take tace, "Yayah Zahra Allah ya kara hakuri sai munyi waya" dukkansu tashi sukayi suna mata fatan alkhairi sannan duk sukayi waje.

Mama tana kuka ta musu rakiya ta dawo.

Abdallah suka shigo duk fuskansu babu daɗin ganin, saboda abinda Mama tayi, Abdurrahman yace, "Mama muma idan Allah ya kaimu gobe zamu wuce school" ya faɗa yana wuce ɗakinsu.

Mama tana jallon Abdallah tace "kuma tafiyan zakuyi biyu?" ....... "toh Mama me zamu zauna muyi? Bayan duk wannan zafin rashin da mukayi amma kike ɗaga hankalinki akan wani kaya na rayuwan duniya, kaman wanda kika manta kinyi rashin ɗanki?"

"Ni wai har yaushe zaku na fahimtana ne?" Mama ta faɗa tana share hawayenta.

"Mama sai ranan da kika yadda da ƙaddara, tukun zamu na fahimtanki" ya faɗa shima ya bi bayan ɗan'uwan shi.

"oh ni  Zahra! Gaba ɗaya Fatima ta asirce mun yarana, babu mai bin ra'ayi na ko ɗaya?"

Lokacin da su Hammah Haidar suka isa garin kano, kai tsaye gidan su Adda Humairah suka wuce, acan sukayi dinner.

Suna gama dinner Adda ta shige ɗakin ta, ganin haka Besty ma ta bi bayanta, aka bar Hammah da Ahmed mijin Adda a  palon.

Suna zama Adda ta buɗe fridge ɗin ɗakinta ra miƙowa Besty wani robern faro me ɗauke da

wani abu mai zaƙi ta miƙawa Besty tace, "shanye kibani cup ɗin Feenah na".

Dariya Besty tayi tace, "kai Adda nikan sai yaushe zaku daina bani wannan abunne kam?"

"kaji ƴar rainin sence, kede kisha keda kika samu gatan kowanmu tana koƙarin burge ki, amma kina mana yanga, hmmm yarinya wataran da kanki zaki nema".

Besty tana dariya tace, "haba Adda ni danake autan ku ae dolen ku kuyita mun gyara don na zama tafisu tafi sauran mata" ta faɗa tana dariyan Adda da ta buɗe baki tana kallon ta.

"ehh dole kice haka yarinya, amma dai tsaya feenah, gaskiya ina ƙara jaddada miki duk wani gyara da zamu miki na banza ne, idan bazakiyi mishi biyayyah ba, sannan ki zama mai riƙe sirrin mijinki Nafeesah, kizama mai tsafta da iya kissa a wurin mijinki, ki kuma riƙe dangin mijinki da mutunci especially iyayenshi, kinji ko".

Ɗaga kai tayi idon ta ɗauke da hawaye, Adda ta kalle ta tace, "kada kiyi mun kuka auta kawai shawaran da kowa yake baki shi zakiyi aiki da shi.

Mijin Adda ne ya shigo yace "ke auta fito ku tafi gidanku muma kwanciya zamuyi," ya faɗa yana dariyan shaƙiyanci.

Adda tana hararan shi tace, "amma dai kaikan akwai babba na ƙotalo, kaida zaka bata haƙuri sai kazama kaine mai tsokananta.

"ke akwai wanda ya lallashe kine da za akawo mun ke? Ina haka kika zo kina ta kuka, duk da hakka bashi ya sani na haƙura ba"....... Jifanshi da pillow Adda tayi tana.

"don Allah ka fita bamu gayyace kaba muma gamu nan fitowa" fita yayi yana dariyan su, dama shi mai yawan barkwanci ne.

Suna isa gidan su dake janbulo, gida ne mai two bedroom, Besty duk a tsorace take ganin haka Hammah ya wuce ɗakinshi bayan ya nuna mata nata ɗakin.

Jiki a sanyaye na shige ciki, kallon ɗakin na tsaya yi domin gaskiya ɗakin yamun kyau, daga gani sabbin gado ya saka.

Toilet na wuce na haɗa ruwan wanka mai zafi yadda Adda ta mun bayani na dinga nayi, especially wanka dare, komin zafi na dinga yi da ruwan ɗumi, haka yasa na zuba ruwa kuma a buta mai zafi nayi tsarki dashi bayan na gama wankan, na ɗaura alwala na fito ɗaure da towel.

Ina fitowa kawai nayi naga Hamma zaune akan gadona , ae kuwa da sauri na koma cikin toilet.

Dariya Hammah yayi yace, "ƴan mata don Allah fito ki shirya abunki ni nafita.

Ina fitowa da sauri-sauri na shiryah na saka kayan bacci na wando da riga masu kyaun gaske.

Tana kwanciya saiga Hammah ya sake Shigowa, da sauri ta sake tashi ta zauna sai raba ido takeyi kaman tayi wa sarki karyah.

Kallonta yayi yace, "toh tashi muyi sallah ƴan'matan Hammah" ya faɗa yana shinfiɗa musa sallaya.

Babu yadda ta iya ta tashi ta ɗauki hijab ta saka, ta ɗauki zani ta ɗaura ta zo kan sallaya ta tsaya, haka ya ja su sallah.

Bayan sun idar yayi musu dogon addu'a, sannan ya saka hannun shi ya dafa kanta yayi mata addu'a.

Tashi yayi ya ɗauko musu ledan kaza da roban fresh milk mai sanyi, duk yadda yayi taci ƙi tayi, daya matsa mata kawai saita fashe da kuka.

Kwashe komai yayi ya kai kitchen, yana dawowa har ta koma kan gado ta dunƙule cikin blanket, dariya yayi ya wuce toilet ɗin shi ya wanko baki ya dawo.

Kan gadon ya hau ya buɗe blanket ɗin ya shiga,  ya matso da ita jikinshi, kuka ta sake fashewa dashi tana ƙokarin matsawa, riƙeta Yayi yace, "babu abinda zan miki ƴan mata na, kawai zanji ɗumin jikin kine, ko baki so kema kiji na mijinki?"

Amsawa tayi da sauri tace, "nikan bana son ji" yana dariyanta yace, "nikan ina son ji" da muryan da tayi mishi maganan da shi.

Ganin drammern da sukeyi Kawai sai na fita na rufe ɗakin nace gara naje can inda Riyyah take naga me ake toyawa, don naga yau Besty Feenah rikici ta keji da shi.

# *Vote, Comment, Share &Follow*

*DAGA ALƘALAMIN AUNTY NICE*✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*
*1441H/2019M.*

®🖋
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION✍*
_{Gaskiya ɗaya ce daga kinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira.}_

🎐G•W•A🎐
_*GASKIYA DOKIN ƘARFE•* 🏇_

Story and written
By
*AUNTY NICE*

*_WANNAN BOOK SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Wattpad@GaskiyaWritersAsso.~

*page* 41----42

*__________*📖Ana idar da sallan magarib ko abinci Hammah bai tsayah yaci ba, ya fito da mutanshi yayi gwallaga.

Dama tunda yammah ya gayawa Abbah nah zuwan shi, shiyasa lokacin da ya isa sallama kawai yayi, bayan Ummi ta amsa mishi ya shigo har palon Abban.

Suna gaisawa da Ummi ta sake yi mishi gaisuwan rashin Babagana sannnan ta tashi ta basu waje.

Hammah har ƙasa ya sake sunkuyawa ta gaisa da Abba nah, shima Abban ya sake mishi sabon gaisuwan, bayan sun gama gaisuwan ne kowa yayi shiru.

Har zuwa wani lokaci tukun Abba yace, "yaya akayi ne malam Umaru?"...... gyara zama Hammah yayi tare da tanƙware ƙafafun shi kaman mai shirin ɗaukan karatu yace, "Abba dama maganan mu na shekarun bayane nake so mudawo da shi, kasancewar ga abunda Allah ya shiryah, Babagana Allah bai nufa mai nisan kwana bane".

"Haka yake Umar, nima nayi tunanin haka, toh amma abin dubawa anan shin yayah za muyi da maganan ita mahaifiyar ku"?

"Baka ganin wancan ma ba a son ranta akayi niyyan yi ba? baka tunanin duk wannan ɗin ma haka zataƙi?"

"Abba babu damuwa ni nasan yadda zanyi, nidai kawai amincewar nake so".

"don tani kam baka da matsalah Umar, haka kuma itama Ummin nasu tun wancan karon da na mata bayani ɗari bisa ɗari ta goyi bayan al'amarin amma kasancewar ga ɗan'uwanka sai muka hakura da zancen".

"Abba kada ka damu insha Allahu ni zan karkato da hankalinta, zata aminta babu matsalan komai."

"Toh Umaru yanzu sai ka nemi haɗin kan ita Badariyyan, domin mukan babu komai ta wurinmu sai fatan alkhairi."

"Abba babu komai zan  mata magana itama" Hammah ya faɗa yana kara godiya wa Abba, sannan ya mishi sallama ya wuce har palon Ummi ya mata sallama, har ƙofan gida Abba ya raka shi jikin motan shi yana mishi fatan alkhairi.

A hankali na buɗe ɗakin su Besty Feenah da Hammah Haidar kaman bani da gaskiya na shigo ɗakin cikin sanɗa, abin mamaki har lokacin Feenah kuka takeyi, shi kuma Haidar sai rarrashinta yake yana cewa.

"Ƴan mata na kiyi haƙuri bazan sake ba daga yau kinji, jiyan ma bansan yayah akayi har haka ta faru ba, kiyi haƙuri cwit zumana," ya faɗa yana ɗaurata kan cinyan shi, yana ta aikin lallashi.

Irin kukan iskanci da shagwaɓan da rake ta mishi ne, ya sani juyawa na bar ɗakin ina ta mitan samun wuri dai, bari na leƙa Riyyah ta na  bata labarin da ta daɗe tana son ji, na lokacin da Hammah da daɗewa ya taɓa zuwa ya samu Abba suka tattauna, ashe dama so ne.

A palo na samu Baba da su Gidaɗo suna break-fast, Aunty ma cikin shirin tafiya office tana tsaye gaban dinning ɗin tana ta uzulzulan su suyi su tashi kada suyi letti.

A haka nima na fito daga kitchen hannu na ɗauke da coolern dana zubawa Mujaheed abincin tafiya school.

Jakan shi na ɗauka ina shirya mishi kusa da lunch box ɗinshi dake cikin wani blue basket, dai-dai lokacin Hammah ya shigo palon bakin shi ɗauke da sallama.

Kaman ance na ɗaga kaina, charab idona da na shi suka haɗu wuri guda, kafin nayi wani abu har ya ɗauke nashi idon daga cikin nawa, kai tsaye wucewa yayi har kan dinninh wurin su Baba.

Suna gaisawa Baba yace, "bismillah ga abun kari Baba nah".

Cikin nutsuwa da kwantar da kai yace, "ina azumi Baba", neman wuri yayi ya zauna kusa da Baban shi, gaba ɗaya ƙannen shi suka gaishe shi.

Zama yayi idon shi nakan wayan shi da yake ta dannata kaman da gaske akwai abinda yake yi a ciki, har suka gama sallama sukayi suka wuce suka tafi school, Gidaɗo ne kawai ya wuce ciki palon don shi yanxu yana ATBU ne yana level 1, kuma bashi da lectures sai nine, gefen riyyah ya zauna yana ce mata ƙanwata yayah me zaki mana yau da lunch? Hararan shi nayi bance mishi uffan ba na wuce cikin ɗakin Aunty na barshi yana ta mun dariyan shaƙiyan ci.

Aunty ce tayi musu sallama ganin ta kusa yin late tace, "Ranka ya daɗe nikan na wuce idan ka bani dama," ta faɗa idon ta yana kan Baba, kallonta yayi cikin fara'a yace, "Ranki ya daɗe an baki dama, ta nan baki da matsalah Allah ya tsare hanya my queen." ya faɗa yana jifan ta da kallon so.

Itama martanin kallon ta maida mishi, sannan ta dubi Hammah tace, "Hamman su me za'a maka na shan ruwa"?

Ɗagowa yayi fuskan shi ɗauke da murmushi yace, "lahhh Aunty ki huta kawai babu komai, ke da zakije office ki dawo a gajjiye? Zainab zan sakata tayi babu damuwa."

"Kada kaji komai Riyyah zatayi insha Allahu, saidai idan kafi son na matar kane kawai kafaɗa mun" ta faɗa tana mishi dariya tsokana

Shima dariyan yayi yana sunkuyar da kanshi ƙasa yana cewa,"lahh Aunty wani irin na fison na Zainab? Kawai dai kada na saku aiki da yawa ne, amma ba komai tayi mun ɗin nagode Aunty".

Aunty na dariya ta ƙwalawa mun ƙira, da sauri na fito, tana kallona tace, "auta na don Allah kiyiwa Hamman ku abin shan ruwa ko, ina fatan duk wani abu da zaki buƙata akwai? Idan babu kimun waya sai na turo ko autana" Ta faɗa tana saɓa jakanta a kafaɗa, daidai nan Gidaɗo yace, "Aunty ni kuma mai zata shiryah mun na lunch?don na mata magana bata kula ni ba" ya faɗa yana duba na da tsokana yana wani smilling na rainin hankali.

Hararan shi nayi nace, "sannu Abbah" Aunty tana mana dariya ta wuce ta fita tana," kunfi kusa nasaka baki anjima naji kunya a tsakainin ku, Baba ma dariyan yayi yana miƙewa yace, "Fatima kada ki damu da Gidaɗo ko ba komai dai kin riga shi shan iskan duniya, kinga ae dole yace miki Adda ko yaki ko yaso".

Haka suka fita suka barmu muna ta haurawa da Gidaɗo, wanda da kamna yayi sauƙi da tsokanan amma yanzu firr tunda Besty na yayi sati da rasuwa ya sakoni gaba yaa dawo da shi sabo.

Suna fita Baba ya kalli Hammah yace, "akwai wata matsalah ne" Hammah yana ɗan murmushi yace "Baba dama maganan saika dawo daga office zamuyi domin na zama ne" ya faɗa yan sunkuyar da kanshi.

Dariya Baba yayi ya shiga mota yana saina dawo toh.

Ana idar da sallan magrib Hammah ya shiga side ɗin Aunty domin ya sha ruwa, akan dinning

ɗin ya haɗu da ni ina jera mishi kayan buɗa bakin.

Gaida Aunty yayi ya wuce kan dinning ɗin dai-dai lokacin ni kuma na kawo bowl ɗin fruit-salad na ajiye.

Kujera ya jawo ya zauna, ina kallon shi nace, "Barka da shan ruwa" ba tare da ya dube ni ba ya ɗaga kanshi alaman ya amsa.

Juyawa na yi zan wuce kawai sai ji nayi yace, "dawo ki yi saving ɗina mana "ya faɗa idon shi yana kan wayan shi.

Haka na tsaya na zuba komai a cikin pilet sanan na juya zan koma sai kuma naji yace, "ki fara zuba mun kunu tukun" zaro ido nayi ina kallon shi bance komai ba.

Ba tare daya kalle ni ba yace, "kuskurenki kenan na farko, baki tambayeni mai nake so ba, kawai kika mun abinda kika ga dama ko"?

Ina kallon shi bance komai ba, amma cikin zuciyata nace "kaji rainin sence sai kace ni matar shi ce da zance sai na tambayi mai yake so? Ina ga matan shi nan amma bata mishi ba, saini zai takura na faɗa a zuciyata a fili kuma na murguɗa baki na ni kaɗai.

"dama kin bar gulmana ke da zuciyar ki kin nemi mafita da zaifi" ya faɗa yana kan duba wayan shi.

Ina kallon shi nace, "toh me kake so na maka yanzu? na faɗa cikin ƙaramar muryata marar ƙara , fuska na ɗauke da alaman zanyi kuka don gaskiya na gajji da yawa yau ɗinnan.

Sai lokacin ya ɗago ya dube ni har zuwa wani lokaci sannan yace, "me zaki iya yimun yanzu"? Ina kallon shi nace, "duk abinda kace shi zan maka".

Murmushi yayi wanda zan iya rantsuwa ni ban taɓa gani a fuskan shi ba sai yau, kuma dayasan tana mishi kyau da kullum cikin yi zai dinga kasancewa.

"kinsan ni ƙosai da kunu na fiso nayi buɗa baki da shi, idan ya samu kuma ina son ferfesu, zaki iya yimun"?

Kallon shi nayi nace, "zan iya yi mana Hammah amma yanzu ae zakaji yunwa idan nace har sai nayi, don bamu da gyararren wake".

Murmushi ya sake yi yace, "toh next time ki gyara ,amma yanzu zanyi manage da wannan".

Da sauri na bar wurin kada ya sake tsayadda ni, amma abin mamaki sai ganin Baba nayi zaune shida Aunty a palon ta, wanda ni banga wucewar shiba, domin palon su Khalifah ne kawai na barsu a ciki kuma tun shigowa na su suke zaune a wurin suna assignment shida Mujaheed.

Tsayawa nayi ina cewa "Baba sannu da dawowa banga shigowanka ba", na faɗa ina diriricewa.

Dariya yayi yace, "ta ina zaki ganni Hamman ku ya haɗa ki da aiki!"

Sannan ya dubi Aunty dai-dai zan shige ɗakin ta yana cewa, " bari naje idan ya gama cin abincin sai muyi maganan, don tun safe yace yana son magana da ni, gara naji kafin ya canja mine ɗinshi" ya faɗa yana ficewa daga palon.

Toh nima Aunty Nice bari naje gidan makama wurin su
*Ummi yawale*
*Ai yawale*
*Zainab yawale*
*Fati yawale*
*Indo yawale*
*Mahir Usman*(BABANAH)
Wanda na sadaukar musu wannan page ɗin gaba ɗayan ta naji yau kuma me zasu ce game da Hammahn jarirai.

#Vote, Comment,Share,Follow.

*_DAGA ALƘALAMIN AUNTTY NICE_*✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*
*1441H/2019M.*

®🖋
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION✍*
_{Gaskiya ɗaya ce daga kinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira.}_

🎐G•W•A🎐
_*GASKIYA DOKIN KARFE•* 🏇_

Story and written
By
*AUNTY NICE*

*_WANNAN BOOK SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Wattpad@GaskiyaWritersAsso.~

_*NABILA RABI'U ZANGO WANNAN SHAFIN KYAUTACE DAGA NI MUMCYN KI, KUMA INA MIKI FATAN SAMUN LPY DA DACEWA DA ABOKIN ZAMA NAGARI, ALLAH YA ALBARKACI RAYUWARKI AMEEN*_

*page* 43---44

*_____________*📖 Baba yana shigowa palon ya samu Hammah bai gama ba,kawai sai ya wuce wurin su Gidaɗo ya zauna suna kallon tare.

Lokacin da Hammah ya gama sai ya taso ya taho inda Baban su yake, shima ya nemi wuri ya zauna ya cigaba da kallon.

Ganin haka yasa Baba yayi bazawarar murmushi, sannan ya ce su Khalifah, "ku bamu wuri zamuyi magana da Hammanku" jin haka da sauri kowan su ya wuce palon Aunty.

Gyaran murya Baba yayi yana duban Hammah don ganin ya sunkuyar da kai baice komai ba.

Da murmushi ya ɗago fuska ya kalli Baban na shi sai kuma ya maida kanshi kasa yana ta

murmushi.

Dariya Baban yayi yace, "toh ko yau ɗin na zama surukinka ne?ka ce zamuyi magana kuma kazo ka sakani gaba kana ta ƙaramar murmushi kai kaɗai"

Dariya mai ɗan sauti Hammah ya sakeyi yace, "Baba ni narasa ta yaya ma zanyi maganan ne,"....... Baba ya dube shi yace "hakanan zaka ɗame kayi, ko na tashi nayi wucewa na ɗaki na huta".

"Baba dama akan maganan kayan nan ne, nace mai zai hana amaida auren ya dawo kaina idan har babu damuwa, domin a tunani na haɗa zuriya da Aunty nan gaba zai kawo maslaha a zuciyar Mama, don dole idan Allah ya saka akwai rabo ae zata so abinda aka haifah babu yadda ta iya, kuma zata saka wa ranta bakomai kake ƙin shi ya zama maka sharri ba, wataran abinda muke ki shine kuma alkhairi a rayuwarmu".

Shiru yayi kanshi na kallon ƙasan carpet ɗin yana jiran mai Baba zai ce, don shiru shima yayi na zuwa wanu lokaci, kaman daga sama yaji Baba yace.

"Alhamdulillahi da kai da ƴan'uwanka kuka fahimci Fatima Alkhairi ce a zama da ita, wanda nayi baƙin ciki da har yau ita mahaifiyarku ta kasa fahimtan hakan, sai kuma hanzari ba gudu ba, shin zakaiya jure halin Maman ku idan taji wannan batun?".

"Baba ni a wurina babu matsalah idan har kai ka amince, Mama biyayya ce kawai zan mata don ba haramun zan aikata ba, saidai bana so ma taji sai an ɗaura don shawaran da mukayi da Ummanta da Aunty Fanna kenan".

"Toh duk da haka banƙi ta taka ba Babanah, amma ita kuma wife ɗinka da mahaifiyarta shin zaku samu fahimta kuma"?

"Baba nifa nake aurenta bawai ita take aure na ba, kuma dama tasan mata huɗu aka yadda mun na aura, saboda haka ni ita da mahaifiyarta duk basu gaba na, ita ma Aunty Falmatan ban bata room ɗin ta dinga shiga mun hidiman gida naba kawai ta tsaya a matsayinta na ƙanwar Mama, Baba nifa amincewanka kawainake so, don ko ita Mama ma nasan yadda zanyi da ita," ya faɗa yana ƙara risinawa.

Baba yana kallon shi zuciyar shi cike da jinjinawa ɗan na shi yace, "yau ɗaya Baba nah na yadda da zaka iya adalci a tsakanin iyalenka, kuma na amimce kai ɗin namijin gaskine , Allah ya muku albarka sannan kuma ita Riyyah yaya zaka tunkareta da maganan ne, ko kuma mu zamu mata?".

"Baba ita ma inaga babu matsalah tunda na daɗe da maganan da Abbanta sai daga baya yake cemun kazo mishi da maganan Babagana, shi kuma yakasa gaya maka yadda mukayi, yanzu ma ban ɓata lokaci ba na same shi da maganan, kuma ya amince, kawai yace na nemi amincewan ku ne".

Baba ya jijjaga kai alaman ya shiga al'ajabi yana duban Hammah yace, "Baba na dama ka daɗe kana son Fatima ce"?

Hammah ya sunkuyar da kanshi ƙasa yana murmushi yace, "Baba ae tun tana ƙarama naji hankali na ya kwanta da ita, kuma har na samu mahaifinta na nemi izini a wurin shi, toh amma daga baya saiga maganan ɗan'uwa na, shi yasa na haƙura".

"ikon Allah" Baba yace yana duban Hammah, sanann yace, "toh ita Fatiman tasan da maganan kenan"?

"Babu abinda ta sani sai dai yanzun ma nafiso a ɗaura auren, idan yaso a barmu mu fahimci juna daga baya".

Baba ya ɗago cike da mamaki yace, "kaman yayah Baba nah"?........ Hammah yana kallon shi yace, "Baba kasan ba lallai bane ta fahimci hakan anayi yawanci idan sun rasa wani na su sai suga kaman duniya zatace sunyi gaggawan yin aure, kuma ma zan fiso kawai Mama taji anyi kaga duk wani daru da zatayi daga baya ne, kuma nasan yadda zanyi da ita".

Baba ya amince da maganan sannan yake tambayan Hammah saura wata nawa ya gama training ɗin da yatafu?

Hammah yace, "saura six month Baba, yanzu nafiso a ɗaura auren kafin na tafi, don 2wks kawai suka bani".

Baba yace "insha Allahu yau zamuje mu sami mahaifinta duk yadda ake ciki zakaji".

Cikin farin ciki Hammah yayi godiya wurin Baba sannan suka cigaba da hiransu akan yanayin rayuwa.

Lokacin da Aunty ta shigo side ɗin Baba domin ta kwanta, Baba ya bata labarin duk abinda ya

faru tsakanin su da Hammah.

Aunty tayi matuƙar murna sosai tace, "gaskiya Babansu na daɗe banji abinda yamun daɗi irin wannan al"amari ba, domin nasan Hamman su zai riƙe auta tsakanin shi da Allah, kai Alhamdulillahi naji daɗin wannan labari, dole yau na bada tukwaici mai girma," ta faɗa tana kallon shi da dariya.

Shima dariyan yayi yace, "don Allah kibar ɗan tsoho kada ki ƙara sa shi Fatima"  ya faɗa gaba ɗayan su suna dariya.

Lokacin da Baba ya samu Abba, babu ɓata lokaci Abba ya ƙira Bappansu ya sanar da shi, shima cikin murna yace yau yake so a ɗaura auren, kuma baice musu su zo har kafin-madaki ba, kawai su ɗaura a masallacin gwallaga, sannan ya bisu da addu'a yace

su gayawa Umar ɗin shima yana ciki ya bashi daga nan zuwa sallan Azahar aga wazai kada wani.

Suna dariya suka rabu akan daga anyi sallan azahar za'a ɗaura.

Lokacin da Umar yaji ba karamin daɗi yaji ba, atake ya turawa friends ɗin shi ta txt messege, dayake lokacin bai wuce 10:00 na safe ba, toh kafin lokacin friends ɗinshi da dama sun iso, hattah Hammah Haidar dasu Hammah Walid saida suka zo.

Abban bauchi shi yayi mun alwali, inda ɗan'uwan Baba kuma, yayi wa Hammah alwali, dubban mutane suka shaidah ɗaurin auren mu da akayi akan sadaki naira dubu hamsin.

Tunda na tashi naga Aunty tayi wanka ta saka wani sabon atamfan da ta ɗinka akan ranan buɗan kanmu da Besty tayi niyyan sakawa, ɗinkin ya amsheta ba kaɗan ba.

Duk inda tayi binta da kallo na keyi can nace, "Aunty gaskiya kinyi kyau babu karya".

Tana ɗan murmushi tace, "kema ta shi kiyi wanka wani hidima zamuyi,"  sannan ta wuce toilet ta haɗa mun ruwan wanka mai ɗauke da kayan ƙamshi.

Haka naje nayi wanka na fito fess dani, nima kayan shigen irin ɗinkinta ta bani na saka, shima na lura acikin wanda tamun na fitan biki na ta bani na saka.

Muna zaune naji tsayuwar motan su Baba sun iso, da sauri Aunty ta tashi tayi wajen shi, zuwa

wani lokaci ta ƙirani a waya tace nazo palon Baba.

Cikin sauri na ƙarisa palon inda naga su Gidaɗo ansha wankan farar shadda babban riga suna zaune gefen Baba, hattah Hammah Umar ma Babbar rigan farar shaddan ne ajikin shi yayi matuƙar kyau sosai.

Zama nayi agefen Aunty ina hararan Gidaɗo, wanda tunda nazo shima yake harara na da wasa.

Kallonshi nayi nace, "dube shi yana cika yana batsewa kaman wani sabon anga, anya Gidaɗo akwai wacce zata so ka kuwa? Kalleka fa babu wani kyaun kirki"na faɗa ina dafa kan cinyan Aunty.

Gaba ɗaya palon dariya akeyi banda Hammah Umar da ya rike wayan shi yana ta dannawa.

Baba ne yace, "haba Fatima keda nace yau aure zan ɗaura muku keda amininki, gashi yaci farar shaddan shi din ya burge ki" ya faɗa yana kallon Gidaɗo da dariya a fuskan shi.

Gidaɗo ta sowa yayi ya miƙawa mun kuɗin dake hannun shi yace "gama sadakin ki baɗon halinki ba na karɓo miki a wurin Abba domin yau nanu miki na isa da ke, na bada auren ki akan sadaki naira dubu hamsin, da nayi niyyan karɓan dubu ɗari, sai kuma naga yayi yawa don ke baƙa ce sai hamsin ɗin".

Karɓan kuɗin nayi nace, "wallahi kayiwa kanka don bazan baka ba tunda ka miƙo mun ya ko zama nawa don kashewa zanyi".

na faɗa ina kallon Aunty nace, "Aunty ki zama shaida yaron nan ko yazo daga baya bazan ba shiba, don yau zanyi maganin rainin daya mun"

Aunty tana dariya tace, " Nima ina bayan ki auta, kada ki bashi, duk yadda zaiyi".

"Aunty toh ae dama hakkinta ne, shiyasa na karɓo na kawo mata ,fata ni dai yau tasan ni nayi mata gaba, don ni nabada aurenta, ƴar baƙa am" ya faɗa yana shigewa side ɗinsu yana dariya.

Baba ne ya gyara zama yana kallona sannan yace,

"Fatima tabbas babu maganan wasa wannan kuɗi da Gidaɗo ya baki sadakin kine, wanda yau

dinnan don mun isa dake muka ɗaura miki aure da Hamman ki, kuma na tabbatar ke ɗin mai tarbiya ce, da kuma biyayyah bazaki watsa mana ƙasa a ido ba, fatana Allah ya baku zaman lafiya da fahimtan juna".

Da sauri na ɗaga ido na da suka ciko da hawaye na dubi Baba nace, "Baba Babagana bai daɗe da rasuwa ba fa."

"Babu matsalah Fatima acikin wanan auren tunda babu takaba ko iddah akanki" cewar Aunty da take kallon mu.

"Aunty shifah Hammah yana da mata ae" na sake faɗa cikin ruɗewa.

"Riyyah shin akwai haramci ne a auren mai mata? Bakiga nima mai mata na aura ba? Idan kina mana biyayyah kada na sake jin bakin ki , ko angaya miki akwai aibu ne a auren mai mata?".

Baba ne cikin murmushi yace,

"Fatima ki barta ta faɗi abida ke ranta ae nasan bazata kimana biyayyah ba ,don ita ta gaji biyayyah ta kowa ni gefe".

Kallon Baba nayi kaman zanyi magana sai kuma nasaka hannu na rufe bakina ina kuka.

Kallo na yayi yace, "faɗI abinda kike so my doughter

Da sauri na sake cewa, "Baba toh shi Hammah yace yana sona ne"?

Dukkan jikina rawa yakeyi. Baba yana dariya ya dubi Hammah dake ta danna wayanshi, yace, "Toh kai Hamman su wannan tambayan kai keda amsa, saboda haka muna saurarenka".

Hammah ɗan dariya yayi ya miƙe tsaye yace, "Baba bari naje can side ɗin Maman, sanan ya dubi Aunyty yace Aunty bari naje, zan dawo nayi dinner anan".

Sannan ya kalle ni baice komai ba ya wuce ya bar palon.

Baba ne cikin murmushi yace, "namijin duniya kenan".

Kallona Aunty tayi tace, "tashi ki wuce ɗaki, sannan ki san me zaki shirya mishi na dinner, don

dake yakeyi ba dani ba".

Sannan ta dubi Baba tace, "Dadai kabi bayan shi domin ka taimaka mishi ya fahimtar da Maman shi".

Yana dariya yace, "wane ni? wannan ae aikin na sojoji ne, duk da ma Ummansu tace ana ɗaurawa mu barta ita zata sanar da Maman shin, kinga ni na huta da tashin hankali, shi kuma nasan zai iya da su, barshi zuwa la'asar idan munji shiru sai mu leƙa don nasan yau sanbisa za a shiga" Baba ya faɗa yana dariya.

Kallona Aunty tayi tace, "Aunty nice don Allah ki bishi ki Taya shi lallaɓa Mama.

Da gudu nayi hanyar side ɗin Mama don jin me ake toyawa, chabb ashe ink ɗin biro na ya kare, dole naje nayi aron na Besty nerh miss xerks.

#Vote, Comment, Share, Follow.

*_DAGA ALKALAMIN AUNTY NICE_* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*
*1441H/2019M.*

®✍
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION✍*
_{Gaskiya ɗaya ce daga kinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira.}_

🎐G•W•A🎐
_*GASKIYA DOKIN ƘARFE•* 🏇_

Story and written

By
*AUNTY NICE*

*_WANNAN BOOK SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Wattpad@GaskiyaWritersAsso.~

*page* 45---46

*____________*📖Ina shiga palon Mama na hango Hammah zaune a gefenta yana ta daddanna wayanshi, ita kuma sai masifah take ta zubawa, abin mamaki kaman ba da shi ta keyu ba, gefe ɗaya kuma Zainab ce rungume da Nabeel akan cinyanta sai juka take tayi kaman an aiko mata da mutuwar iyayenta gaba ɗaya.

"shin Umar bada kai nake magana bane? Don tsaban raini ka rike waya kaman mahaukaciya ce tsaye akan ka?"

Ɗagowa yayi yana duban Mama amma abin mamaki idon shi kaman wanda ya shekara yana kuka babu rarrashi, tsabar irin jan da sukayi, buɗan bakinshi yayi da ƙyar yace.

"Mama toh naga kinsani agaba kina ta zagina kaman wanda aka zo akace miki nayi kisan kai ko kuma na aikata shirka, abin takaicin ma agaban wannan yarinyar da ta saka mutane agaba tana ta shirme, kaman wanda aka mata albishir da shiga wutan jahanna ma".

Ya faɗa yana hararan Zainab.

Mama kallon banza ta mishi kaman ta tsinka mishi mari tace,

"Toh meye maraba da kisan kan? Wannna ae kaman ka kasheta da ranta ne Umaru, ballantana ni da na tsuguna na haife ka amma ka watsa mun ƙasa a ido na,

Toh bari kaji idan har ni na haife ka ban yadda ba kuma ban amince ba ka zauna da auren wannan shegeyar baƙar yarinyar, yau ɗin nan kuma yanzun nan nake so ka saketa, ko kuma na

tsameka acikin ƴaƴa na" ta faɗa kaman ta tsinka mishi mari.

Kallon idon shi nayi lokaci ɗaya naji gaba ɗaya na tsorata, domin a sani na Hammah Umar manyan ido gareshi, amma abin mamaki idon a buɗe suke amma tsabar ɓacin rai kaman a rufe suke duk sun ƙanƙance wuri guda.

"Mama duk abinda kike so shi zanyi, amma kuma dole ne itama Zainab na gutsire igiyan aure na da ita na kuma yafe mata ɗan data haifah, don ni ma bazan riƙe shi a matsayin ɗa ba,

Mama zan miki biyayyah amma bazai saka na ƙiyiwa mahaifina ba, domin shi ma yana da hakki akaina, don wannan auren nima ba'a son raina nayi shiba, amma saboda kwanciyar hankalin Baba yasa nayi,

Kinga Zainab ma saboda ke nayi saboda haka duk zan iya rabuwa da kowansu, akan na ɓata miki kona ɓata wa Baba".

"Nikan my honey bance dole ka saki matar ka ba, ko nace maka na shiryah rabuwa da kai ne?" Zainab na kuka take faɗin haka, sannan ta juya ta kalli Mama tace.

"Nikan don Allah Mama idan ma don nine kike cewa ya sake, toh gara ma ki bari, don ni kan ban shiryah rasa mijina ba, saidai ki gaya mishi nikan kada ya yadda ya haɗa mu gida ɗaya da ita, don ni gaskiya bazan iya jure ganin yarinya ƙarama ƴar talakawa tana zaune da mijina ba, kuma ta ishe mu da warin miyar daddawa, kuma Mama ki gaya mishi kada ma ya fara haɗa matsayina da nata kawai shine damuwa na"

Hammah hararan ta yayi cikin tsawa kaman zai tashi ya daketa yace,

"Kada ki ƙara saka bakinki kina faɗun duk abinda yazo miki, dan mahaifiyata tana mun magana, kema har wani matsayu kike tunanin kina da shi? Ballantana ita ma yarinya ƙarama wanda bata wuce raino ba".

Ba Zainab da ɗanta da ya fashe da kuka ba, hattah Mama sai da taji ta razana da tsawan shi.

Kallon Zainab da take ta kuka Mama tayi, sannan taja bakinta tayi shiru domin tana da tabbacin ba karamin halin Umar bane ya sauwaƙawa Zainab idan ta sake maganan ya sake ni, tunanin haka da Mama tayi ya saka ta harari Hammah tace.

"Toh uban kowa tunda ka gama kafa mana dokokin naka sai ka tashi ka fita kabani wuri, don yanzu na yadda kai ne Fatima da zuriyarta suka mallake ba Babagana na ba, domin Shi kan kullum cikin lallaɓa ni ya keyi ba irinka ba," lokaci ɗaya kuma ta fashe da kuka tana cewa,

"lallai da gaske nayi rashin ɗana wanda yafi kowa sona a cikin ku, kaidai kawai Allah ya saka mun sonka ne fiye da kowa a acikin su, amma kai kuma kafi kowa ƙin jin magana na, yanxu

kam na yadda da maganan Babanah ashe shiɗin mai tsananin ƙauna ne, Allah dai ya jiƙanshi da rahma" ta faɗa tana ta sharen hawayenta.

Tashi Hammah yayi yakama hanyan fita, da sauri Zainab tabi bayan shi da kallo tana share idon ta, sannan ta dawo da kallonta kan Mama tace.

"Don Allah Mama kibar shi da maganan sakin yariyar nan kada nima ya sake ni, jinga wallahi ina son mijina" ta faɗa tana ƙara share hawayenta.

"hmmm, ki barni da shi Zainab insha Allahu ko ba yanzu ba na miki alƙawarin sai ya sake ta, don ni ko kaɗan na tsani zuriyar Fatima, ballantana kuma har aure ya haɗamu da su"

Mama ta faɗa tana jijjiga kanta.

Tunda akayi sallan la'asar Aunty dole ta sakani na shiga kitchen domin nayiwa Hammah girki, ina kallonta nace.

"Aunty toh aini ban san me yake son ci ba?" dariya Aunty tayi sannan tace,

"Hamman ku yawanci abincin gargajiya yafiso, saboda haka sai ki fara duty daga yau, kisan me yaka mata kimishi, ni dai abu ɗaya zan gaya miki shine kullum dare yana shan tea kafin ya kwanta" ta na faɗin haka ta juya tayi hanyan ɗakinta.

Raina duk a jagule natsaya tunanin me zan dafah mishi, can a raina nace bari na mishi gudun kurna ae shima abincin gargajiyane, kuma abincin sarakai ne, don shima bai wuce sarkin ba yanayin shi da tsarin shi, na faɗa ina duba abinda zanyi amfani dasu a kitchen ɗin.

Zoɓo na fara haɗawa wanda yaji kayan ƙamshi zallah ban saka na zamani ba, ina gamawa na saka shi a fridge.

Kaza na ɗauka guda biyu na gyara su na ɗaura su akan wuta bayan na zuba wadataccen albasa da kayan ƙanshi.

Kafin a ƙira sallan magrib na haɗa gudun kurna na, wanda yaji naman kaza da yagama rugurgujewa a ciki, daga kofan palon Baba dake side ɗin Aunty zaka fara jin ƙamshin girki na.

Gidaɗo ne ya leƙo wanda ya yi shirin tafiya mosque yana ta gyara hannun rigan shi da yayi alwala yana cewa "kaaiiii yau zan kwashi gara a gidan nan, lallai na iya zaƙulo Mata inaga abokaina zan gayyato su suzo cin dinner yau a gidannan", ya faɗa ya nabuɗe coolers ɗin dana ke zubawa a lokacin.

Buge hannun shi nayi ina cewa, "kaji rainin sence abincin Hamman ne kake cewa zaka kira friends ɗinka suzo suci? Har ma kake iya saka ƙazamin hannunka kana buɗe mun girki"? Na faɗa ina ƙara make hannun shi daya sake miƙowa zai buɗe yana dariya nah.

Muryan Baba naji yana cewa, "Rabu da shi Fatima zai haɗu da Sojan Hamman shi yau, don nima yanzu dana hango fuskanshi ne yasaka ni canja hanya na dawo sai ya wuce  nima na wuce, don naga yau amazan faman yake," ya faɗa shima yana buɗe abincin sannan yace ," uhmmmm gaskiya ƙamshin ne ya jawo ni nima, yakamata a zuba mun nawa ni kaɗai kafin sojan nan ya shigo mukasa zama a palon," yana dariya yake faɗa.

Duk kanmu dariya mukayi don jin abinda Baba yake faɗi, kaman shiɗin ma yana ƙasa da Hamman ne.

Basu suka shigo ba sai da akayi sallan ishaa, lokacin nima na fito a wanka na saka wani Dogon riga Mai irin roban nan, sannan na yafa wani Ƙaramin gyale akai na.

*Don Allah kumun hakuri zuwa dare zakuji ni insha Allahu da wani page ɗin, domin nayi baƙi ne yanzun nan*

#Vote, Comment, Share, Follow.

*DAGA ALKAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*
*1441H/2019M.*

®☄
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION✍*
_{Gaskiya ɗaya ce daga kinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira.}_

🎐G•W•A🎐
_*GASKIYA DOKIN ƘARFE•* 🏇_

Story and written
By
*AUNTY NICE*

*_WANNAN BOOK SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Wattpad@GaskiyaWritersAsso.~

(Aunty faraa na Badariyyah fans wannan shafin nakine kyauta, domin nuna mun ƙauna da kikeyi.)

*page* 47---48

*___________*📖Inagama shafa turare na, na wuce palon domin jan kunnen da Aunty ta mun akan kada ta yadda ta jirani nazo nayi saving mijina, faɗa sosai ta mun ta wuce.

Ina shiga shima yana shigowa, lokacin Aunty da su Baba da yaran gaba ɗaya suna kan dinning, Aunty ce tacewa Hammah.

"Hamman su ka wuce palona Riyyah ta ajiye maka dinner ka a can".........ba tare da yace komai ba yayi murmushi ya wuce palon Aunty.

Nima bin bayanshi nayi kaman zanyi kuka saboda ƙasa-ƙasa Gidaɗo dariya yake mun.

Ina tsaye na ɗauki pilet na zuba mishi gudun-kurnan da ƙanshin shi lokaci guda ya cika wurin, miƙa mishi nayi zuwa gaban shi, sannan na zuba zoɓo ɗin cikin cup na ajiye mishi, kaman an dasa ni a wurin naja na tsaya.

Ni ban tafi ba shi kuma bai ci ba, ina kallonshi nace "Hammah kada yayi sanyi fah".

Ɗago idon shi yayi ya sauƙe su a kaina, bansan lokacin da baki na ya furta, "ya rabbi" da sauri na sunkuyar da nawa idon ƙasa.

Murmushi yayi sannan yace, "idon mugu ko"?   Da sauri nace, "a'a kayi haƙuri ni tsoron idon kawai na keji".

"Zaki mun bayani," sannan ya kalli pilet ɗin ya ce, "baki iya sannu da zuwa ba, ballantana ki gaisheni, kuma Aunty tayiwa mijinta abinci kin ɗauko kin kawo mun".

Turo bakina gaba nayi nace, "ahhh Hammah ni nayi fah, ka tambayi Auntyn".

Zaro ido yayi yana kallo na yace, " jagwalgwalen jaririya zanci"?

Bansan na harare shi ba nace, "nifa na girma".

Jan pilet ɗin yayi yana murmushi ya fara cin abincin ba tare daya sake kallona ba, ganin haka na juya zan shige ɗakin Aunty.

Hannuna naji ya kamo ya dawo dani, ƙasa-ƙasa naji yana cemun, "haka ake kula da miji"?

Kujeran da ke kusa da shi naja na zauna da ɗayan hannun, domin yaƙi sake mun hannu na.

Ina zama ya ajiye spoon ɗin hannun shi yace, "bani zoɓon" ......zaro ido nayi ina kallon shi.

"ina wasa da ke ko?" naji ya faɗa.

Da ƙyar na ɗaga cup ɗin na kai bakinshi, yana buɗe bakin nayi sauri na rufe ido na, amma don neman fitina sqi naji yaƙi yasha.

Buɗe idona nayi ina dubanshi, Harara na yayi ganin haka da sauri na sake miƙa mishi, a haka babu yadda na iya na bashi yasha.

Yana ta murza mun hannu wanda lokaci ɗaya naji hannayenmu suna zufa, amma bai fasa murzawa ba yana cin abincin shi hankali kwance.

Yana gamawa nayi saurin miƙewa zan kwashe kwanikan, ƙura mun ido yayi da sauri na koma na zauna.

Dai-dai lokacin wayanshi ta farq ringing, ɗauka yayi naji yana, "hello aboki yaya kake"? Yana wani ɓata rai naji yace, "kamai da ni irin kane? Yayah zanyi da jaririya Baba ya maƙala mun ya haɗani da raino".

Haushi kaman zai kasheni ina taso na ƙwace hannu na kawai sai ya harare ni, haka na hakura ya cigaba sa wayanshi yana ta cimun fuska a gaban abokinshi, don daga gani Yusuf ne, don naji yana tambayanshi yaushe zai dawo?.

Yana gama wayan na dube shi idona sun ciko da hawaye nace, "nidai ba baka ni akayii ba", na faɗa hawayen suna sauƙowa.

Rufe idon shi yayi kaman mai bacci ya kwantar da kanshi, bai sake kula ni ba sai aikin matsamana hannun mu da yake yi.

Buɗe ido yayi ya dube ni yace, "9:30 ki kawo mun lipton side ɗina"......... Da sauri nace, "na bawa Gidaɗo ya kawo".

"idan ya zama mata na ki bashi ya kawo"  matsa hannu na yayi da karfi har saida nayi kara, sannan ya miƙe ya fita.

Hawaye naji suna zuba mun, ina sharewa sai ga Aunty ta shigo, kallo na tayi tace, "ke kuma fah lafiya"?

"Aunty wai fa cewa yayi 9:30 na kai mishi tea",  "toh sai me Riyyah? ina dama na faɗa miki yana shan tea ɗin dare irin na Babanshi".

Hawaye suka gangaro mun nace, "Aunty idan Maman shi ko Matar shi suka ganni fah?.

"Sai ki nuna musu cewa kema matar shi ce, gaskiya Riyyah kiyiwa kanki faɗa, yanzu ne fah lokacin da zakiyi yaƙi ki kama mijinki, ita matar tashi kinga wani alama da takeyi na nuna ita matar kirkice wurin kula da miji"?.

Girgiza kai nayi alaman a'a.

"Toh yanzu ne nake so ki nunawa mijinki ehh lallai ki jini nane, ki kula da shi fiye da kulawan da uwa zatayiwa ɗanta, ki nuna ke mace ce bawaimun raku mata duniyaba, saboda haka kinsan dai yadda nake haɗa tea ɗin Babaku? Toh yau ke zaki dafa sai ki tabbatar kin sake wanka kin canja kaya kafin lokacin, kuma bana son african time".

"Aunty ae zai rainani yace bani da class".

Dariya Aunty tayi ta ƙara matsowa kusa dani ta zauna, tana kallo na tace.

"Ba kowacce mace bace namiji yake ganin bata da aji don ta nuna mishi kulawa, ki ɗauka kawai babu irinki a cikin mata a wurin mijinki, ki saka wa ranki ke ɗin dole saida ke zai iya rayuwa, ki nuna mishi so mai tsabta da kulawa zaki zo kice mun baki kallon ko wacce mace a duniya wurin mijinki sai ke".

"Aunty ae yaa raina ni fah, cemun yakeyi wai bashi ni akayi kuma ni jaririyace".

Aunty tana dariya tace, "Alhamdulillah tunda ganin jaririya yake miki, ke kuma ina so ki nuna mishi keɗin jaririyar ce kinji auta".

"Tayaya zan zama jaririyar kuma Aunty"?

"Abinda nake so kenan, ina ce  jarirai rikici ne da su?su hanaka saƙat, kullum suna jikinka?

 Toh haka nake so ki kasance wa Hamman ku, har sai yaji nan duniya babu wata mace a sama da ke, kuma kasancewa ajikin namiji yana saka shaƙuwa mai girman gaske, wanda duk inda ɗaya yayi hankalin shi yana kan ɗaya".

Rufe ido nayi ina dariya nace, "Aunty tsoron shi fa nakeyi, shifa baya sake fuskan shi wallahi".

Dariya itama tayi tana miƙewa tace, "soon zaki koya mishi my Riyyah nah, insha Allahu idan har jininmu yana yawo a jikinki sai Hamman su ya dawo miki kaman bawa da ubangidan shi, ke kuma kada kice lokacin zaki raina shi, sam babu raini tsakanin miji da mata, kinji ko my Riyyah".

Tashi nayi na shiga ɗakin Aunty ina dariya, wurin 8:00 na fito na haɗa komai na kayan tea na daura, bayan na zuba kayan ƙamshi.

Gaba ɗaya Kamshi ya cika wurin, ina gamawa na juye a flask ɗin Baba dana Hamma, Komawa ɗaki nayi na shiga wanka.

Ina fitowa naga Aunty ta ajiye mun wani cutoon riga da wando akan gadon, gefe ɗaya kuma wani hijabine har kasa ta ajiye mun duk ta tirara su da turaren wuta mai ƙamshi, wanda har ɗakin ya ɗauki ƙamshin su.

Jikina na shafe da wani humrah da naga ta ajiye mun, sannan na shafa ajikin pant ɗina da bra na, na ɗauko wando da rigan na saka.

Kai masha Allah dana dubi kaina a jikin mirrow, hips ɗina kaman zasu faso wandon, ni kaɗai naji ina Dariya domin gani nayi na dawo kamar wata ƴar india, amma baƙaƙen su.

Ɗaukan hijabin nayi na saka bayan na gyara packing ɗin gashi na daya kwanta har gadon bayana.

Ganin har 9:25 nayi sauri na shiga kitchen na fito da flask, dama Aunty tace mun ɗakin shi akwai cups ɗinshi acan, da sauri na wuce, ta ƙofan kitchen ɗin na fita saboda bana so na haɗu da su Gidaɗo.

Knocking nayi har kusan minti biyu tukun akazo aka buɗe mun, tsayawa nayi kallon shi yamun kyau yana sanye da wani three quater da riga armless.

Matsa mun yayi na wuce, shima ya shigo ya rufe kofan hannun shi riƙe da remote.

Kan center table ɗin na ajiye flask ɗin, a lokacin na tuna da maganan gaisuwan, da sauri nazo har inda yake na durƙusa nace.

"Hammah barka da dare" baiko kalleni ba ya miƙo mun hannun shi, ganin haka yasa na gane manufar shi, wato mutumin nan ina ganin shi salihi ashe ba haka bane.

Tashi nayi na ƙarasa har kan cinyan shi na saka hannu na riƙe na shi hannun, na kwanta akan cinyan shi, wanda ƙarfin hali ne takai ni hakan, domin na nuna mishi ni ba iya hannun kawai zan tsaya ba.

Da sauri ya dube ni amma bai iya hanani ba sai ma ƙara gyara mun kwanciyar  da yayi, idon shi ya mayar kan news ɗin dayake gani yayi.

Tsabar kunya rufe ido na nayi, amma sai acan zuciyata nace Aunty fah tace mun namiji babu abinda yake so, sai ka dinga shiga jikinshi.

Hannu na na mayar dai-dai saitin cikin shi kaman ance dole sai nayi ido na a rufe na matsa cikin, lokaci daya ya ɗan saka kara yana kallona yace.

"Zaki mun tiyata ne"? Buɗe ido nayi ina duban shi nace, "kawai zanji ko kana jin yunwan shan tea ne, ina so na gudu gida ne kada a rufe kofan".

Maida kallon shi yayi kan tv yace, "nan kuma jeji ne ko? Tashi ki cire mun wannan zunbuleliyar hijabin naki, sai ki xuba mun tea ɗin a cup ki miƙo mun".

Kaman bazan tashi ba, sai wani zuciyar ta sakani tashi domin nafara ɗamara daga yau domin nima inaji sai na shiga filin sanbisa anyi daga dani kafin na samo zuciyar Hamman nan naga alama.

Tashi nayi na cire na ajiye kan kujeran gefen shi bayan naninke hijab ɗin.

Ido ya zuba mun kaman ya ga abin mamaki don har buɗe bakinshi yayi, juyawa nayi zanje na ɗauko cup kawai naji ya dawo dani da hannun shi na faɗo kan cinyanshi.

Ɗaura fuskanshi yayi kan nawa fuskan ya rufe idon shi, da ƙarfi naji yayi ajiyan zuciya, hannu na saka na giwaye shi ta bayan shi ido na a rufe.

Har kunnena nakejin ɗumin numfashin, "Baby Nerh!" naji ya furta mun cikin cool voice ɗinshi wanda idan baka sauraraba ko kaɗan baza kaji ba.

Kasa amsa mishi nayi, dukkan mu shiru mukayi sai shi da yake ta goga fuskan shi akan nawa fuskan yana ta sauƙe ajiyan zuciya.

Can nayi ƙarfin halin cewa, "Babyn jaririya naje na kawo maka tea ɗin"?

Matseni yayi da karfi yana ɗan dariya ƙasa-ƙasa yace "ina wasa da ke"?  Nima dariyan nayi nace "a'a baby nerh!"

Kaman za'a fasa ƙofan irin buga ƙofan da mukaji anayi, muryan Mama ce ke cewa, "Zaka buɗe ƙofan ne Hammansu ko saina saka an ɓalla mun ƙofan?".

*Aunty fara ga wannan page ɗin dominki nayi don kawai kiyi break-fast da shi nayi*

#Vote

Comment
Share
Follow.

*DAGA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*
*1441H/2019M.*

®☄
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION✍*
_{Gaskiya ɗaya ce daga kinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira.}_

🎐G•W•A🎐
_*GASKIYA DOKIN ƘARFE•* 🏇_

Story and written
By
*AUNTY NICE*

*_WANNAN BOOK SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Wattpad@GaskiyaWritersAsso.~

(*_MAMAN ABDOUL NA GROUP ƊINA MUYI NISHAƊI, WANNAN PAGE NAKI NE, NAGODE DA KULAWANKI*_)

*page*  49---50

*___________*📖 Kura mishi ido nayi zuciyata kaman zata faɗo tsabar razanan da nayi, shima kallo na yakeyi idon shi duk ya canja kala, haka zalika Mama bata fasa buga ƙofan ba.

A hankali ya tashi ya zaunar dani akan kujera, ya ɗauka hijab ɗina ya warr mun ya miƙo mun, nidai kallon shi kawai nakeyi cike da tashin hankali.

Ƙofan ya nufa zai buɗe da sauri na bishi da ido bansan me nakeyi ba kawai naji ni nayi nilldown, hawaye yana ta bin fuskana.

Buɗe ƙofan yayi, kaman an jeho ta kawai sai ganin Mama nayi ta shigo palon bayan ta bangaje shi gefe guda, tsayawa tayi tana kallona, ni kuma sai ji nayi na ƙara sautin kukana, tana harara na tace.

"me kikeyi anan tuɓ ɗazu"?......... Bansan lokacin da naji bakina yana furta,
"Hammah ne na kawo mishi tea ya sakani nilldown".

Dariya Mama tayi tana kallon na tace, "ya mun dai-dai ae, wato ku mayun mazaje, matar shi nacan kwance ke kuma kin ɗebo ƙafa kaman na Ruƙayyan Bangies kin taho wurin miji ko? wato kinga abinda uwarki takeyi kema zaki ɗauka ko? Toh wannan kam ba shanyayye bane kaman ubanshi, ɗana kam namijin gaske ne gara ki sarara mishi, kinji ko bakiji ba"? Ta faɗa tana zaro mun ido.

Da sauri na ɗaga kaina alaman naji abinda tace, tana harara na tace tashi ki bani wuri ki wuce, da shegen tea ɗinku da bansan abinda kuke sakawa ba a ciki na jaraba.

Nazo bakin ƙofan zan wuce amma Hammah ya tare bakin ƙofan ya ƙura mun ido, da kyar na ratsa ta gefen shi na wuce, ina fita naji kuka ya zo mun, ni narasa me nayi wa wannnan matar ta tsaneni.

Ina shiga palo na samu Aunty suna zaune tare dasu Gidaɗo, ko tsayawa banyiba na wuce ɗakinta na kwanta ina kuka.

Dafa ni Aunty tayi tana "me kuna ya faru Riyyah"?  Ina kan kuka na mata bayanin abinda ya faru.

Murmushi tayi tace mun, "kin ban kunya Riyyah, tun daga yanzu har kin fara nuna ragwantanki a fili? Toh gara ma kiyi ɗamara sosai don ban goyi bayanki akan kibari a samu ƙofan tozartaki

ba, bance ki raina ta ko matar shi ba, amma babu kukan da zaki sakeyi a kowaye a cikin su, Umar mijinkine bawai farkan ki bane, haka zalika ganinki yayi yace yana so bawai manna mishi ke akayi ba, saboda haka ko da wasa kada na sake ganin kin zubar da hawayenki, da ga yau kuma zaki fara ɗanmarar yaƙin karɓan ƴancinki cikin ruwan sanyi kinji ko"?

Kallon Aunty nakeyi yadda ta zauna take ta mun bayanin yadda zanyi da uwar miji na mu zauna lafiya, ba tare da na sake nuna gazawa naba ko nuna karayana, kuma ba tare dana raina taba.

A can palon Hammah kuma ina fita Hammah ya dube ta yace,

"Mama yanzu tsakani da Allah hakan yayi dai-dai ace kin biyo surakarki har ɗakin mijinta? Don Allah Mama kidinga kwantar da hankalinki akan wannan al'amari, nima fah bawai son yarinyar nan nakeyi ba,kina gani babu yadda na iya ne na karɓi aurenta don kada na kasa farantawa Baba ranshi, ko kina so idan kin matsa ne nima na mutu yadda Babagana ya tafi ya barmu"?

Jiki narawa Mama tace, "sam ni bawai na matsa bane Hamman su, ni yadda suke wani nuna zaƙewa akanka ne yake bani haushi, ga can matar ka ita ko nuna ɗan kishin nan bata iya ba sai tsabar son jiki da kwanciya, ni tsoro nakeji kada ka juya mata baya akan wannan mai baƙar fuskan, don wallahi yadda kasan Fatima ce ta bata nono tasha haka halinsu yazo ɗaya".

Murmushi yayi yana duban Maman yace, "ita Zainab ko ɗaya Mama bata san meye hakkin miji akanta ba, ballantana ta nemi sauƙewa, yanzu ko sau ɗaya kin taɓa ganin ranan da Zainab tazo don ta gyara mun ɗaki, ko ta dafa mun wani abu naci?.

Ita dai sai dai kabata kuɗi tayi wanann tayi wancan shine kawai abinda ta sani,

amma ita wannan tea kawai ta kawo mun kuma akan idon ki kingani punishment ma nabata saboda ba yadda nace amun ba ta mun don kawai na nuna mata bata da wani matsayi a wurina, kuma da baki zo bama belt nayi niyyan ɗaukowa na zane ta da shi, Allah ne ya taimake ta kika xo, amma hakan ma bata tsira ba zan san hanyan da zan nema ta shigo nayi niyyah kafin na tafi saitaji ajikinta, wanda ita da kanta zata nemi na sauwaƙe mata batare da Baba ni yaga laifi naba".

Dariya Mama ta kwashe da shi tace, "shegiya ashe nayi hanzarin zuwa ne da ka lallasata da belt ɗin sojoji"?

Wucewa yayi ya zauna yana zuba tea ɗin acup, bai sake cewa komai ba ya cigaba da kallon TV.

Mama tana kallonshi da harara tace, "amma dai har ranka baka sonta ko"?

"Me nagani a wurin da zan so ta Mama? Matana fara sol ƴar gayu wannan fah baƙace Mama, kawai dai nayi biyayyah wa Baba ne, amma komai akwai lokaci da kanki zaki saka mun albarka, kedai kije ki kwanta, bana so kina yawan shigowa nan saboda Baba idon shi yana kanmu, don ɗazu ma saida yace mun yaga kaman bana sonta nafi son zaɓinki, saboda haka ina so ki tayani mubi abun a hankali," ya cigaba da shan tea ɗinshi.

"Babu komai zan daina shigowa, amma kaima kana kiyayewa kada su janye hankalinka, yanzu ma bari na turo maka matarka ta tayaka kwana, ni narasa Zainab wacce irin mace ce wallahi kwata kwata mijinki bai dameki ba" ta faɗa tana fita a ɗakin.

Ajiyan zuciya Hammah yayi yana tunanin abinda ya faru, murmushi yayi a ranshi yana Allah sarki wato tasan Mama bazata mun da daɗi ba sai tayi ƙaryan nasata nilldown ko? Allah sarki sai yaji tausayinta a ransh.

Mama tana shiga ɗakin da Zainab take ta samu tanata  bacci gefe ɗaya kuma Nabil idon shi biyu yana kallon cartoon a wayan Mamanshi.

Mama tashinta tayi tace, "Zainab tashi kije wurin mijinki, ke wacce irin sakaryace kina yashe anan sunan kun kwana biyu baku tare da mijinki amma bazakiyi ɗokin zuwa ba? gashi har yarinya ƙarama ta san taje wurin miji".

Zainab ya mutsa fuska tayi tace, "Mama honey ɗinne ya cika fitina wallahi kuma yace dole sai kayi wanka, kuma koda da yamma kayi sai yace sai ka sake, nidaiɓkawai Mama kada kibar shi ya kwana da ita don Allah, don idan ni nayi magana mugun saɓa mun zaiyi".

Hararanta Mama tayi tace, "kaji mun shirme wai na hana shi kwana da ita? Ae kece zaki hana shi idan kina zuwa kina kwana a wurinshi, amma ke ba tsohuwa ba ki raba ɗakin kwana da mijinki? Gaskiya ki tashi kibi mijinki Zainab".

Kaman zatayi kuka tace, "Mama wallahi bana iya jure fitinan shi ne, ni wlla...    Bata ƙarisa ba Mama ta buge bakinta tace, "ke ni meyasa bakida hankali ne, wannan kam ae sirrin kune keda shi bawai kina faɗa mun ba, kuma idan baki jure fitinan mijikiba so kikeyi ya fara neman mata"?

Zunɓura baki tayi ta tashi tana cewa "nikan toh babu wankan da zai sakani nayi don nayi da yamma".

Ɗaukan Nabil Mama tayi ta wuce da shi dakinta, ita kuma zainab ta wuce ɗakin Hammah.

Tana shiga ta zauna kusa da shi tace, "Honey me yakawo yarinyar nan ɗakinka don Allah idan ba raini kake nema mun ba"?

"Tashi a kusa dani idan rashin hankali kika zo yimun".

Tashi tayi tayi hanyan bedroom ɗinshi, yana binta da harara yace, "ki tabbatar kinyi brush kinyi wanka, idan bakiyi ba kuma kada ki hau mun kan gado, don yanzu na saka bedsheet ɗina".

Batafi minti biyu zuwa uku ba ya ɗauki wayan shi ya ƙirani, Ina gani yagama ringing ɗinshi ya yanke, kafin nayi wani abu ya sake  shigowa, ɗauka nayi nace.

"Hello" daga ɗayan gefen naji yace, "me kikeyi baki dawo kin bani tea ɗin ba"?

Turo bakina nayi gaba kaman yana gani na nace, "Nidai babu ruwa na, ina tsoron Mama, saidai ka ɗauko ka kawo nan na baka".

"kin tabbatar idan na ɗauko zaki bani da kanki nasha"?

"Hammah toh meye aikii nah? ae duk abinda kake so shi zan maka".

"ki jirani yanzu zan shigo, hope baki canja wannan kayan ba"?

Kunya naji ya kamani ina tunanin dama haka Hammah yake ne? Ƙasa nayi da muryah na nace, "nifa har nasaka nighty na"na faɗa cikin shagwaɓa.

"ina shigowa yanzu" ya faɗa yana kashe wayan.

Toh idan ba gulma ba mezai zo yi ni Aunty Nice na faɗa a raina, sanan nace gara na tafi na barsu babu ruwa na da gulman da ba a aike ni ba..

#Vote
Comment
Share
Follow

*DAGA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*
*1441H/2019M.*

®☄

*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION✍*
_{Gaskiya ɗaya ce daga kinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira.}_

🎐G•W•A🎐
_*GASKIYA DOKIN ƘARFE•* 🏇_

Story and written
By
*AUNTY NICE*

*_WANNAN BOOK SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Wattpad@GaskiyaWritersAsso.~

*page* 51---52

*____________*📖Yana shigowa palo suka haɗu da Aunty da ta fito ɗauke da tray ɗin kayan tea ɗin Baba daga kitchen, kallon mamaki ta bishida shi tana tambayanshi.

"Kada dai yarinyar nan bata kai maka tea ɗinba"?

Cikin inda-inda yake amsa mata, "takaimun Aunty, dama tambayanta zanyi ko akwaizuma ne dama dashi nake son sha", ya faɗa yana dafa kan kujeran kusada shi.

"Bari na miƙo maka ae bamu rabuwa da zuma ko dan Baban ku da khalifah da suke son shi",ta faɗa tana ajiye tray ɗin ta wuce kitchen ɗin ta ɗebo mishi a cikin wani container mai kyau.

Karɓa yayi da sauri yana mata godiya, sannan ya wuce yafita, haryaje bakin ƙofan kaman munafuki ya juyo da sauri yana kallon ƙofan ɗakin kawai sai suka haɗa idoda Aunty, da sauri yafita bai sake juyowa ba.
Itama dariya tayi tace, "kaji dai dashi idanma matarka kabiyo na koraka ae, kayi haƙuri har akai maka ita mana".

Taje ta rufe ƙofan ta shige parlon Baba tana dariya.
Kallon ta Baba yayi yana tambayan, "Lafiya ƴan mata", dariya ta cigaba dayi tana cewa.

"ina fa lafiya, yaran yanzu kunya ta musu ƙaranci, wai Hamman sune fah zai raina mun hankali, ya shigo inaga matat shi yake nema sai ya ganni, shine ya wayance da cewa zuma yake nema", ta faɗa tana dariya.

Shima Baban dariya yayi yana cewa, "amma kema ƴar sa ido ce, mutum da matar shi don ya miki kara ya nuna kunyan shi ae sai ki kau da ido kiyi kaman baki gani ba, toh ina kin nuna mishi matat shi"?

"haba ma na nuna mishi ita? Zuman na ɗauko na bashi, yana fita kuma na rufe ƙofan".

"Amma baki kyauta ba Fatima, ina ke yanzu wurin tsohon mijinki kika taho?toh ae shima da sai ki bashi matar shi su wuce side ɗinshi".

Hararan wasa Aunty take bin Baba da shi tace, "chabb ya zuƙe zaƙin amarcin tun a gida basu wuce na su gidan ba, gaskiya bazai yiwuba, da safe ma zan ƙara mata bayani duk yadda za ayi tafa kiyaye", ta faɗa tana matsuwa kusa da Baba.

"kudai mata kuna da matsala kawai ki bashi matar shi zaifi ganewa, bawai ace sai ta tare ba, tarewan da sai ya dawo nan da kusan wata shida".

Tana dariya tace, "kasan yaran yanzu bazasu rasa ɗan ƙananun abubuwa ba ,amma ma'in ɗin yayi hakuri sai an kaita".

Baba ma hararanta yakeyi cikin tsokana yace, "amma ƙananun ina cewa bazaki hana shi ba ko"?

"na isa na hana shi? Wannan ko na hana ae bazan san lokacin da zasu saci ido na ba, kuma ma namata lecture akan ta dinga shige mishi saboda shaƙuwa, da kuma samun fahimtan juna", ta faɗa tana matsawa kusa da Baban.

Dariya mai ɗan sauti yayi yana binta da kallo yace, "amma ƙwaƙwalwar ku mata kaɗan ne take aiki, ta yayah ma za'ace mace ta dinga shigewa namiji batare da ya aiwatar da abinda yayi niyyah ba? ae wannan mannuwan ƙara ɗaga mishi hankali zaiyi, kuma yadda nasan ɗana bazai baku sararin ja mishi rai ba,

kawao dai ki koma ki bawa ɗiyarki wani lecture akan ta dinga kulle kanta a ɗaki kawai shi zaifi sauƙi".

ya faɗa yana miƙewa zuwa toilet yana dariyan Aunty da ta buɗe baki tana kallon shi.

Shiru Aunty tayi alaman tunani, ita dai a ranta tasan hakan zai saka shaƙuwa tsakanin su kafin ya tafi, ita so takeyi Mama tasan sun isa da shi bawai Riyyah ta zama ƴar kallo ba, amma kuma maganan Baba yana bata tsoro, don ita bata so wani abu ya shiga tsakaninsu batare da an tare ba.

Wani zuciyan yace ke rabu da Baba shi mutumin da ne, yaran yanzu zasu iya mannuwa da juna batare da wani abu ya faruba, kuma su samu shaƙuwa da fahimtan juna, insha Allahu Riyyan ta sai ta tare tukun komai ma idan zai faru ya faru.

Hammah yana komawa side ɗinshi ya nema kujera ya zauna yana jan tsaki shi kaɗai, a cikin zuciyar shi yace.

"amma yau Aunty ta shiga hakkina wallahi", ɗaukan wayan shi yayi ya ƙirani yana cewa.

"Na tabbata kinji shigowa na amma kika nuna bakijini ba ko?" ya faɗa yana jijjiga kai kaman bazawarin ƙadangare.

Dariya ƙasa-ƙasa nayi ina taɓe bakina nace, "Hammah na to bakai kace mun zakazo ba? Na ɗauka idan kagama magana da Aunty shigowa zakayi? Har nayi sauri na canja rigan"  ta faɗa cikin muryan shagwaɓa, wanda lokaci ɗaya Hammah yaji notinan kanshi kaman zasu kwance, shima ƙasa ƙasa yace.

"wanne kuma kika sake sakawa"?

Cikin muryan shagwaɓa kaman wanda zanyi kuka nace, Hammah nah nasaman fa na cire na bar mai kama da net ɗin, kuma har wani humrah fah na sake shafawa saboda kai Hammah nah", na faɗa kaman ina mishi kuka.

"wayyo Allah Baby zaki kashe ni" batare da ya sani ba yaji kalmar ta fito daga bakin shi, gyara kwanciya yayi idon shi a rufe yace, "yanzu yayah zanyi Baby nerh"?

"Ham...ma..a..nah" na ƙira shi a hankali ina muryan kuka, Ina jinshi yayi wani ɗan kara yace, "wayyo baby nah yau zaki kashi ni fah, me kike so ne?

ni kaina bansan meye cikin ƙwaƙwal wata ba, nidai Aunty ta gwada mun yadda zan shigewa

Hammah amma abinda yake zuwa mun akaina ban san waya koya munba.

"uhum..uhmm Hammah nah nikan kazo" na faɗa ina kara shagwaɓa mishi muryana.

"Baby nah don Allah kimun rai ki fito,ban san me nakeji ba fah" ya faɗa yana ƙara mirginawa zuwa ƙasa daga kan kujeran.

"Hammah toh ae cinya na fah a buɗe suke, ta yayah zan iya fitowa? Kawai kazo ka ɗauke ni a kafaɗan ka, hammah kazo ka goye ni", ina faɗa da muryan dana san zai birkita mijin Zainab gaba ɗaya.

Inaji Hammah ya kasa magana sai wani irin nishi da gurnani yake yi wanda lokaci ɗaya naji tsoro, ƙyat na kashe wayan ina kama bakina, toh ni meya kaini nema na faɗa ina kama baki nah.

Kaman an tsokaleni na razana da naji wani ƙiran yana sake shigowa ina kallo har yagama ringing ya katse da sauri na ɗauka na kashe wayan gaba ɗaya don wani kunya ne naji ya rufeni lokaci ɗaya.

Nayi shiru ina tunani kawai sai naji Besty ya faɗo mun a raina, sai naji banji daɗi ba, lokaci ɗaya hawaye ya zubo mun a ido na, nayi shiru ina tuna ranan da yake ce mun.

"Beauty ranan da na ganki a ɗakina matsayin mata na, ranan zan kwanan ina sallah ina godewa Allah da yabani ƴar duma-duman yarinyar nan, washe gari kuma na kwana ina kallon cinyoyinki ya faɗa yana bina da murmushi".

Lokaci daya naji na fashe da kuka, babu abinda yake mun daɗi a raina naji, kuka nayi sosai kafin na tashi naje nayi alwala nazo na fara sallah, ina son nayiwa Besty nah addu'a.

Washe gari ido na dana tashi gaba ɗaya sun kunbura saboda kukan danayi, ina kunna wayata kaman ance dama na kunna sai ga wayan Ummi nah ya shigo.

"hello Ummi nah" bayan mun gaisa take faɗa mun Adda Umaimah ta haihu yau da Asuba, an samu baby boy, da murna na amsa mata dacewa, "Allah ya raya itama yabata lafiya, insha Allahu anjima zan zo Ummi nah".

Da dauri naji Ummi tana cemun, "ki nemi izini fah a wurin maigidanki, idan bai amince ba toh kiyi zamanki, sai ya yadda kinji ko"?Cikin sanyin jiki na amsa mata da "toh " tukun mukayi sallama na ajiye wayan, jikina a sanyaye.

Ina zaune Aunty ta buɗe ɗakin ta shigo bakinta dauke da sallama, amsa mata nayi cikin rashin walwala, kallo na tayi tace.

"Me yafaru Riyyah"?
Ina zunɓura baki gaba nace, "Ummi ce wai don Adda Hafsat ta haihu wai bazan zoba sai Hammah ya barni" na faɗa ido na yana Cikowa da hawaye.

Toh neye abin fushi da kukan, dama ae dole yanzu duk inda zakije sai da amincewan shi, kuma ma nasan zai barki, yaushe Umaiman ta haihu?"

Ina kallon ta nace, "Aunty yau da asuba ta haihu, amma dai Aunty ke zaki tambaya mun ko"?

"Dayake nice mai bakin tambaya ko? Ko kuma ce miki akayi iyaye suna shiga cikin irin wannan shirgin? Gara ma ki zage kidinga abu da kanki, kuma bana son rawan kai wurin magana, ki zama mai nutsuwa sosai da kamewa a wurin mijinki, ki zama mai kwantar da murya idan zatai magana da miji kinji ko"? Ta faɗa tana shigewa toilet.

#Vote
Comment
Share
Follow.

*KU KASANCE DA ALƘALAMIN AUNTY NICE*✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*
*1441H/2019M.*

®☄
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION✍*
_{Gaskiya ɗaya ce daga kinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira.}_

🎐G•W•A🎐
_*GASKIYA DOKIN ƘARFE•* 🏇_

Story and written
By
*AUNTY NICE*

*_WANNAN BOOK SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Wattpad@GaskiyaWritersAsso.~

*page* 53---54

*__________* 📖Ranan ko kitchen ban bi Aunty don tayata ba, daga ita sai masu mata aiki suka haɗa break-fast, ina ganinta gudu-gudu ta shigo ta wuce toilet bata kula ni ba.

Tana fitowa a wanka har lokacin bakina a zunɓure ina ta binta da kallo kaman zanyi kuka.

Juyowa tayi ta kalleni ta taɓe baki tace, "kina da aiki Riyyah idan tsakaninki da mijin ki bazaki iya gaya mishi magana ba sai wani ya shigo? Toh wallahi sirrinki zai zama a waje" ta cigaba da shirinta bata kalleni ba kuma.

Haka na shige toilet ɗin nayi wanka na fito ita kuma tana saka uniform ɗinta don tafiya office, kallonta nayi nace.

"Aunty na ƙira shi a waya idan ya yarda na biki ki ajiye ni"?

"duk wanda ya miki" ta faɗa fuskanta babu walwala ta quce ta bar ɗakin.

Jikina naji yayi sanyi, matar nan tana iya ƙoƙarinta akaina don taga ta sama mun ƴanci amma ni kuma ina neman watsa mata ƙasa a ido, ni bata san na tsokano Hammah bane kuma ina tsoron haɗuwan mu da shi.

Wani dogon riga na lace na ɗauko nasaka, na fita zuwa palon, akan dinning na samu Aunty da Baba suna break kuwa cikin sauri yake, har ƙasa na tsuguna na gaishe da Baba sannan na miƙe na koma ɗakin.

Aunty ce ta buɗe ɗakin ta shigo tana kallona tace, "kin tambaye shin ne"?

"Aunty kiyi haƙuri naga kaman na ɓata miki raine, ban tambaye shi ba, zan jira idan ya shigo sai na tambaye shi".

Murmushi tayi tace "ba komai ƙirashin kawai, duk yadda yace sai ki sameni a parlo ko", ta juya ta fita bayan ta ɗauki handbag ɗinta.

Jiki na a sanyaye na kira number shi, amma har saida ya gama ringing bai ɗauka ba, zuciyana ya fara bugawa kodai yayi fushi ne? Kawai sai naji ya biyoni da ƙiran.

Da sauri na ɗauka ina sallama, shima daga ɗayan side ɗin ya amsa mun, sannan kowan mu yayi shiru, "wani abu kike so ne"? Naji ya tambayeni.

Cikin muryan tsoro tsoro nace dama zanbi Aunty ne ta sauƙe ni a gidan Adda Umaima ta haihu ne".

"Yayi safiya kije gidan mutane, ki bari idan na tashi zuwa 11:00 zan kaiki, Allah ya raya mata abinda ta haifah cikin musulunci", ko jiran mai zance baiyi ba ya kashe wayan.

Kallo na bi wayan da shi cikin ɓacin rai naji haushin abinda ya mun, nace "lallai ma Hammah nan don ba so na yakeyi ba ko? Yanzu da Besty nane da gudu-gudu zai yadda baya son abinda zai ɓata mun rai, amma ji wannan mutumin hmmm zan rama kuwa" na faɗa ina komawa na kwanta.

Aunty na shigowa cikin sauri tace, "ke nake jira fa" ina turo bakina nace, "bayan yaƙi, wai sai ya tashi wurin 11 zai kaini" dariya tayi tace "hakan ma yana da kyau, sai ki kula da kanki ki fita kuma kiyi break, sai na dawo" ta faɗa tana fita.

Komawa nayi na kwanta na ɗauki wayana, whatsapp na buɗe najira zuwa wani lokaci message suka gama buɗewa.

Da sauri na duba status ɗin Besty Feenah saiga photon babyn kuwa yadda nayi zato, "Masha Allah" na faɗa don kyaun baby da girman shi, tura mata nayi sannan na sauƙa ina bin chtt ɗin mutane ina karantawa ina reply.

Bani na kashe data na ba sai wajen 10:15 da sauri naje
nayi break na dawo na gyara ɗakin Aunty cikin sauri sauri.

Jikin mirrow naje naga kayan yayi ba aina canja ba, sannan na ɗauko gyalen kayan na feshe shi da turaren Arabian oud, ina gamawa naji an turo ƙofan ɗakin da sallama.

Ido na ɗaga da sauri naga Hammah ne jikinshi cikin ƙananun kaya, a raina nace,"yaushe mutumin nan zai dinga saka manyan kayane, kullum cikin shigan ƙananan kaya".

Ƙora mun ido yayi yana kallona, sai na samu jikina da ɗaukan rawa, murya yana rawa na gaishe shi.

Bai amsa ba ya tako har inda nake ya miƙa mun hannu alaman na ƙaraso, zuciyata kaman za ta fito don nasan yasan gidan babu kowa sai Baba mai aiki da take kitchen.

Haka nayi dauriya na ƙarasa bai wani jira ba ya rungume ni ƙam-ƙam ajikin shi, har ina jin bugun zuciyar shi, rafe ido na nayi saboda bana son ya kalle ni, ashe shima idon ya rufe, babu wanda yayi yunƙurin ɓanɓare ɗan'uwan shi har kusan 10mnt.

Muryan shi naji kaman a sama yana cewa, "jiya kika kashe mun waya ko"? Nidai kasa bashi amsa nayi sai ƙoƙarin neman na bar jikinshi na fara, da sauri ya kara ƙanƙameni yace, "kull bana son taurin kai" shiru nayi ina tajin faɗuwan gaba.

Raba jikin mu yayi yana riƙe da hannu na yana ta kallon fuskana, da sauri na maida ido na na rufe.

Kaman bazaice komai ba sai kuma ya sake ni yace, "fito muje," shima ya juya yayi hanyar waje, har jikin motan na ƙariso na samu yana zaune ya haɗa kanshi da sitiyarin motan.

Buɗe motan nayi cikin tsoron kada Mama ta fito na shiga, da sauri yaja muka bar gidan, babu wanda ya ƙara magana har muka isa ƙofan gidan Adda Umaima.

Hannu ya saka ya ɗauki handbag ɗina ya buɗe ya zuba mun kuɗi a ciki wanda ban san ko nawa bane, nidai naga ƴan two-two hundred ne.

Kallon shi nayi nace, "Nagode Hammah" abin yaso bani dariya danaga ya turo mun fuskan shi akan na mishi kiss.

Rufe ido na nayi ina dariyan ƙasa-ƙasa, shima dariyan naji yana yi sannan yace, "Plzzz mana Baby nerh!"

"Hammah nikan kunya nakeji" na faɗa ina rufe fuskana,   "lallai yarinya bakiyi wa mijinki godiya ba kenan, kuma zan ɗaukeki baki godiya idan an miki alkhairi" ya faɗa yana tura bakinshi yadda nakeyi.

Baki na buɗe ina kallon shi nace "Hammah nah nace na gode fah, kaga yanzu rana ne wallahi wani zai fito ya ganni".

"Yauwa Babyn Hammah toh yanzu mubari sai anyi sallan magarib ma dan zo ɗaukanki lokacin babu maiganin mu sai kimun ko"?  Ya faɗa yana kashe mun ido ɗaya.

Buga ƙafa na nafara yi acikin motan ina faɗin "nikan Hammah wallahi kunya nakeji don Allah ka bari sai na ƙara girma".

Yana kallona ya fara tada motan yace, "toh bari na maida ki gida kuma bazaki ƙara fitaba sai kin ƙara girma" ya faɗa yana ɗaure fuskan shi kaman ba yanzu ya gama dariya ba.

Riƙo hannunshi nayi da sauri nace, "no Hammah baza ayi haka ba, na yadda sai kazo da daren, amma zaka shigo kaga babyn ko"?

Yana murmushi yace, "mubari idan nazo sai nazo naga babyn ko ƴanmata nah". Dariya nayi nace "nagode Hammah sai kaxo".

Shima dariyan yayi yace, "ki riƙe godiyanki sai anjima kimun".

Buɗe kofan motan nayi cikin kunya nace, "Hammah sai kazo" da sauri na wuce cikin gidan Adda Umaima, har saida na shige tukun naji tashin motan shi, dariya nayi na kaɗa kaina nace lallai hammah.

Da sallama na shiga nasamu Mummy da Ummi na zaune a cikin ɗakin Adda an zuba mata ferfesu dayaji kayan ƙamshi sai tashi yakeyi tana ci gefe ɗaya kuma cup ne cike da tea, Ummi kuma rike da Babyn a hannunta tana bashi ruwan zam-zam.

Gefen Ummi naje na tsuguna ina riƙe da kafan babyn ina ta murmushi, Mummy ce tana dariya tace, "yau kuma babu wacce ta samu darajan gaisuwa ko? Sai babyn ku mummuna da Kikaje kika riƙewa ƙafa?

Ina dariya na juyo na gaisheda Mummy sannan na gaishe da Ummi, ina kara dariya na gaishe da Adda da take ta hararana,  dariya nayi nace, "Adda mai nayi kuma"? Kallona tayi tace, "meye na rufe wayanki, ke nayi niyyan yiwa waya na miki albishir amma na rasaki har saida na faɗawa ƴan kano" ta faɗa tana kan harara na.

"Madallah" Ummi nah tace "wato anyi niyyan wariyan ƴan gari wa ƴaƴana ko? Toh Allah ya kamaku ƴar'uwar taki ta kashe wayanta" dukkan mu dariya mukayi.

Mummy ana sallan azahar ta tafi ta barmu, Ummi kuma zasu zauna kafin wacce zata zauna mata ta iso.

Muna ta hidima da ƴan barka har akayi la'asar Ummi na kallona tace, "ke kuma da yaushe zaki tafi"? Ina dariya nace, "yace idan anyi magrib zaizo".

Muna nan har magarib ina sallah na wuce toilet nayi wanka, wani humran Ada na shafe jikina da shi tsab, sannan na ɗauki kayana na saka ina ta shafe shafena a fuskana, ganin gaka Ummi ta fita ta wuce kitchen.

Adda tana dariya tace, "kai yaran nan, iyayinku yana ɗaure mun kai".

Nima Aunty Nice ina gefe sai mamakii nakeyi, a raina nace anya wannan Riyyan bawai kaɗai lectures ɗin Aunytyn ta kaɗai take aiki da shi ba, itama ina  gani gwanar kanta ce.

#Vote
Comment
Share
Follow.

*KASANCE DA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*
*1441H/2019M.*

®🖋
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION✍*
_{Gaskiya ɗaya ce daga kinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira.}_

🎐G•W•A🎐
_*GASKIYA DOKIN KARFE•* 🏇🏽_

Story and written
By

*AUNTY NICE*

*_WANNAN BOOK SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Wattpad@GaskiyaWritersAsso.~

(Jama'a ga dama ta samu, domin wannan haxiƙar Marubuciyar nan
HAFSAT A GARKUWA wanda tayi suna a cikin littatafanta masu matuƙar daɗi da faɗakarwa wato

 *KUNCIN RAYUWA*
*ZAMANTAKEWA*
*GIDAN MIJINA*
*DR HISHAM*
Yanzu kuma ta taho muku da sabon novel ɗinta mai taken *TSANTSAR BUTULCI* Wanda zai zo acikin sabon shekara a farashin ₦100 kacal,  game so ya tuntuɓeta a wannan number 09038178773, kada kubari a baku labari

*page* 55---56

*___________*📖Dariya nayi ina kallon Adda nace, "haba ma Adda kawai don kaina nayi wanka bawai don Hammah ba, nida ko tarewa banyi ba wani rawankai wa miji zanyi? a haka ma yayan besty nane fah".

"Hmmm ke kika sani lokacin da zaki manta yayan Besty ne, ni ina wurin ne?"

Dai-dai lokacin wayata ta fara ringing, ina dubawa naga number Hammah ne, share wayan nayi har saida ta tsinke aka sake ƙira shima kaman zai tsinke tukun na ɗauka.

A hankali na ɗauki wayan nayi sallama, daga ɗayan gefen yace mun yana waje ya iso, kashe wayan nayi batare da na ce uffan ba.

Ɗaukan gyale nayi na fita xuwa inda yake, ina zuwa na buɗe mishi ƙofan inda yake batare dana sake fuskana ba na mishi sannu da zuwa.

Ƙura mun ido yayi yana kallon yanayin fuskana, hannu ya miƙo zai riƙe nawa nayi saurin janyewa na juya ina cewa, "mushiga ciki Hammah".

Har parlon na kai shi, saida naga ya nemi wuri ya zauna tukun na wuce ɗakin Adda na gaya mata Hammah yana parlor.

Tare muka shigo parlon nida Adda, ni ina riƙe da boy ɗin a hannu na, ita kuma tana bina a baya, waje ta saku ta zauna suna gaisawa, ni kuma na miƙa mishi babyn.

Da sauri ya saka hannu ya karɓi ɗan bakin shi ɗauke da murmushi, yana faɗin "masha Allah", yana cigaba da murmushin ya dinga jero addu'o'i wa babyn.

Nidai kallon shi nakeyi ina mamakin yadda yake addu'o'in cikin ƙwarewa, wato shi Hammah komai ma ya haɗa ne?.

Ɗago idon shi yana duban Adda yace, "yayah jikin ki, bawani matsalah dai ko"?

Tana sunkuyar da kanta tace, "babu komai Hammah mungode sosai".

Tana tashi ta wuce ɗakinta shi kuma ya ƙora mun ido yana tambayana, "madam akwai wani matsalah ne"?

Murguɗa baki nayi batare dana kalle shiba nace, "babu komai nikan".

Dariya yayi yace "toh zoki maida shi kizo mu wuce ko".

Miƙa hannu nayi zan ɗauki babyn yayi sauri ya ɗaura mata bunch na ƴan 200 a kan cikin babyn, kallon shi nayi ina zunɓura baki nace, "baby da mamanta sun gode".

Ina zuwa naje na ajiye babyn da kuɗin akan gadonta, Ummi tana kallona nace, "Ummi nah zamu tafi" sannan Adda Umaimah ta ɗauki kuɗin kan babyn tana, "kai Hammah ango haddah ɗawainiya daga zuwa? gaskiya mungode Riyyah kimana godiya don Allah".

Haka na musu sallama na fito, a mota na same shi yana zaune, buɗewa nayi na zauna batare dana ce mishi uffan ba.

Jan motan yayi muka kama hanya batare da yace mun uffan ba, haka muka yita tafiya shiru babu wanda ya kula wani har muka zo kwanan gidan su da yake GRA makurɗi road.

Gefen titin yaja ya tsaya, dayake layin bai cika hayani ba, shiyasa banga mota ko ɗaya ba a kan titin, da sauri na juyo na kalleshi, idona ɗauke da alaman tambaya.

Batare daya kalle niba yace, "ina alƙawarin mu"?

Juyowa nayi kaɗan na kalleshi nace, "Alƙawari kuma? Ni ae babu wani alƙawari a tsakanunmu da ya wuce ka kawo ni gidan haihuwa".

Shiru yayi kaman bazai ce komai ba, har zuwa wani lokaci sannan yace, "abinda kika ce kenan ko"?

"Hammah da gaske nifah na manta" na faɗa mishi kaman babu wani abu dana tuna.

Jawo ni yayi zuwa ƙirjinshi yana faɗin, "bari na tuna miki da alƙawarin mu" lokaci ɗaya na buɗe baki cikin razana zanyi magana, kawai naji bakinshi cikin nawa.

Duk yadda naso na ƙwaci kaina amma gaba ɗaya na kasa, saboda wani irin kiss na fitan hankali da yake mun, lokaci ɗaya naji numfashina na shirin ɗaukewa, ina jin shi sai laluɓan riga na yakeyi amma ya rasa inda zai buɗe rigan haka ya gama laluɓen shi jikin shi sai rawa yakeyi amma yakasa samun kan rigan.

Da yarasa yadda zaiyi kawai sai ya matseni da ƙarfi acikin jikinshi, yana ta ajiyan zuciya, a hankali ya sake ni ya kifa kanshi akan sitiyarin motan, duk yadda naso na mishi magana akan mu wucce gida amma nakasa saboda har lokacin jikina rawa yakeyi.

Ɗagowa yayi yana kallona batare da yace mun komai ba.

Tsarguwa nayi da kallon, na juyo na harare shi a hankali nace, "nidai kada ka ƙara mun haka, kasan ae ni matar ƙaninka ne amma kake raruma na" na faɗa raina a jagule don wani iri nakeji har zuwa lokacin.

Tada motan yayi muka wuce gida ba tare da yace mun uffan ba.

Muna isa ya juyo ya kalleni, lokacin ina ƙoƙarin buɗe marfin motan yace, "nine nake rarumar ki a matsayinki na matana amma kike cemun matar ƙani na ko"?

Kallon shi nayi kaman zan fasa ihu don ganin lokaci ɗaya duk ya koma Hamman shi na da, sunkuyar da kaina ƙasa nayi ban iya na bashi amsa ba.

"Good hakan yana da kyau, gara da kika nuna mun ni amatsayin danake a wurinki, fita kije Allah ya bada sa'a".

Yana faɗa ya maida hankalinshi yana kallon gaban motan, buɗe baki nayi zan mishi magana, amma yadaka mun wani mummunan tsawan da sai danaji hanta na yana neman kaɗawa.

Ban san lokacin da na buɗe motan na fita da gudu ba nayi cikin gidan.

Harara yabini da shi, yana cewa "inbanda yarinta har nine zata kalleni tace wai ina dadumanta"? Yaja tsaki yace "ashe mata duk halinsu ɗayane"?

Ina kallonshi nafaɗa a hankali dai-dai zai shiga side ɗin shi nace, "wallahi Hamman jarirai ba ɗaya sukeba, itama razana tayi da kai, amma idan kana son wata ina da mai hankali zan haɗaku da ita, besty nah zan baka" na  juya da gudu nabi bayan Riyyah don ganin halin da take ciki.

#Vote
Comment
Share
Follow.

*KUKASANCE DA ALKALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*
*1441H/2019M.*

®☄
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION✍*
_{Gaskiya ɗaya ce daga kinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira.}_

🎐G•W•A🎐
_*GASKIYA DOKIN KARFE•* 🏇_

Story and written
By
*AUNTY NICE*

*_WANNAN BOOK SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Wattpad@GaskiyaWritersAsso.~

*page*  57---58

*____________*📖Ina shiga parlor naga babu kowa sosai naji hankali na ya kwanta, share hawayen fuskana nayi da sauri na wuce ɗayan ɗakin Auntyn.

Toilet na shige na wanke fuska nah, sannan na dawo ɗakin na shafah powder da ɗan kajal, na wuce ɗakin Aunty.

Aunty na kwance saman gadonta tana ta rubutu a wani takarda, gefenta kuma Mujaheed ne yake ta danna mata kafanta, kallona tayi ta maida kanta kan ɗan littafin tana cewa, "har kundawo ne? yayah mai jego da angon namu"?

Dariya nayi kaɗan na zauna akan stool ɗin dressing mirrow ina amsa mata da, "ango mijin ƴan mata yace agaisheki da kyau, har yabani goro yace na kaiwa Mummy" na faɗa ina jifan muja da gyale na.

"Babu wani Mummyn nan, dani yake auren bari kiga gobe naje zamu dai-dai ta kanmu"ta faɗa tana dariya, dai-dai lokacin kuma ta mike zaune  tana duban abinda ya hana Mujaa yi mata matsan ƙafan.

Kallonshi tayi taga yana hararah nah kaman zaiyi kuka, kama haɓanta tayi tana cewa, "waya ta ɓa autan Baba da Aunty"?

Jijjiga kai yayi ya ɗauki gyalen dana jefe shi yace, "kuma na ƙwace gyalen ki" ya faɗa kaman zaiyi kuka, ni kan dariya nayi ina cewa, "ayyah Mujaheed am naga duk kayan ka sun koma gwanjo shiyasa na baka gyale nah ɗan kanti"  tashi yayi yana kuka ya jeho mun gyalen yana "bana son kayan ki nima" yana kuka ya fita a ɗakin.

Aunty tana dariya tace, "gaskiya Riyyah kin ta kura auta na, shifah ya tsani maganan gwanjon nan, gani yake da gaske duk kayanshi gwanjon ne" ta faɗa dukkan mu muna dariyan.

Hira mukayi da Aunty har zuwa 10:00 da yake yau ba girkinta bane, saida mukayi hiran tukun

na wuce ɗayan ɗakin, bayan nayi wanka na saka nighty nah sai tunanin Hammah na ya faɗo mun, ina tambayan kaina toh ni me na mishi yayi fushi yau? Haka dai nayita saƙa da warwara a raina har bacci ya ɗauke ni.

Da safe wajen karfe 9:30 wayan Besty Feenah ya tashe ni, a razane na ɗaukin wayan nakai kunne na, ihuu ta saka mun tana dariya tace mun "albishir besty" miƙewa nayi na zauna ina cewa "goro".

"Adda Hafsat ma ta haihu yanzu nan, an samu baby boy ita ma" bansan lokacin dana dirƙa daga kan bed ɗinba nace, "Alhamdulillahi Allah ya raya mana su da imani, ashe zamu zo kano ƙawata".

"wani irin ƙawa kuma? Na bar matsayin Bestyn kece yanzu"? Ta faɗa tana ɓata rai.

Dariya nayi mata sannan nace, "kinsan duk ranan da nace miki besty sai na tuna Besty Babagana araina, shiyasa ma na yankewa wa raina gara nace miki ƙawata, don ranan da kika kirani sai da naji faɗuwar gaba, shiyasa na maida sunanki akan phone ɗina da Kawata, ina fatan kin fahimce ni"?

Jiki a sanyaye tace, "na fahimce ƙawata, kuma na gode da tunatar dani da kikayi, don wallahi ranan saida Adda hummy ta faɗa, tace kullum taji nace basty saita tuna da Bestyn mu, Allah dai ya mishi rahma".

A hankali murya ƙasa-ƙasa na amsa mata da "Ameen", itama jin yanayin dana koma sai tayi saurin yimun sallama ta katse wayan, ta gumi nayi a zuciyata ina cewa "da yanzu besty ne miji na, da kowani irin rayuwa zamuyi"? Sai naji hawaye na biyo fuskana, ban ankara ba naji wani kuka yazo mun mai azaban ƙona zuciya, besty yana sona baya mun fushi, amma wannan kam baya sona shiyasa yake mun fushi.

Tashi nayi na shiga toilet bayan nayi brush nayi wanka na zo na shiryah cikin wani skirt da riga na wani material yellow, har lokacin hawayen dabana so yana gangaro mun, don gaskiya babu ƙaryah ina missing besty nah, don irin kayan gyaran da aka shirgah mana yana yawan sakani naji ina ma besty yana raye kuma shine mijina.

Share hawayen nayi na fito parlon Aunty don na leƙa ɗakinta bata ciki, ina gaisheta na wuce kitchen na haɗo abin kari nazo ƙasa kusa da inda ƙafan Aunty yake na zauna ina break-fast.

Duk abinda nakeyi idon Aunty yana kaina, don haka kawai tunda na fito na kalli photon su da sukayi su duka sai naji zuciyata ta sake rauni, wani hawayen yana biyo mun fuskana.

"Meyake damun ke ne Riyyah"? Aunty ta jeho mun tambayan wanda yayi dai-dai da shigowan Hammah parlon, wuri ya samu kusa da Aunty ya gaisheta.

Ni kuma sunkuyar da kaina ƙasa nayi ina cin abincin a hankali kuma ina share hawaye nah.

Aunty ce ta ɗauki wayanta da ake ƙiranta, dagaji Ummi na ce suke waya, don naji maganan haihuwan Adda Hafsat sukeyi wanda na manta ban gaya mata ba.

Suna gama wayan ta juyo ta dube ni fuskanta ɗauke da murmushi tace, "kinji Addanku Hafsat ma ta haihu yau ko"?

Kaɗa mata kai nayi alaman na sani, tana duba cikin damuwa tace, "Basariyyah me yake damunki ne kike ta kuka haka? Wani abun aka miki ne"?

Shima Hamman kallo na yakeyi yana jiran jin abinda ya same ni, don tun shigowan shi ya lura da irin share hawayen da nake tayi.

"Aunty babu komai fa" na faɗa ina ture pilet ɗin abincin gefe.

"wani irin babu komai riyyah? Baki da lafiya ne toh"? Ta faɗa hankalinta a tashe.

"Aunty rabu da ita, idan bata faɗa miki abinda yake damunta ba to mawa zata faɗa? Idan bata da lafiya ita yarinya ce da zata zauna tana kuka? Ae faɗa zatayi bawai ta sa mutane a gaba tana kuka ba" Hammah ya faɗa fuskan shi a ɗaure.

Ƙara sautin kuka na nayi jin abinda yake faɗa, wato shi haushina ma yakeji kenan, toh ni mena mishi?

A hankali nace "Aunty kawai na tuna Besty ne" sai na sunkuyar da kaina kan cinyana ina kukan a hankali.

"Haƙuri zamuyi Badariyyah, Babagana addu'a kawai yake buƙata a wurinmu idan mun tuno shi, bawai muyita zubar da hawaye ba kinji" ta faɗa muryanta na rawa, sannan ta tashi ta wuce ɗakinta ta barni a zaune a wurin tare da Hammah.

Shiru parlon yayi sai sautin kuka na da yake ɗan tashi a hankali, tasowa yayi ya zauna a gefe na, batare da yace komai ba yasaka hannun shi duka biyu ya ɗago ni har kan gefen 8nda yake zaune ya ajiyeni, cinyan shi ya na gogan nawa.

Ya saka hannun a aljihun shi ya dauko hanky shi ya cire mun nawa hannun ya goge mun hawayen da suke zubuwa.

Buɗe idona nayi na kalle shi, da sauri na juyar da kaina wani hawayen yana ƙara zubu mun don abin mamaki ganin hawaye nayi a fuskan Hammah nah.

Ina kuka naji ya jawo ni zuwa ƙirjinshi, a hankali naji yafara magana.

"Haba Fatimah yayah za'ayi ki dinga yiwa ɗan'uwa na kuka? Ke da nake tsammanin kullum addu'a zakina binshi dashi? Toh Babagana addu'an mu yake buƙata ba kuka ba, kiyi haƙuri kinji" duk maganan da yakeyi muryan shi na rawa, ban san yaya akayi ba sai naji bakina yana furta.

"Hammah toh yayah zanyi? Nifah kullum tunanin shi nakeyi idan na zauna ni kaɗai, kuma ina son Besty na, domin duk duniya idan ka cirre iyayena babu mai sona irin shi", na faɗa ina ƙara rungume Hammah nah.

Ɗagoni yayi ajikin shi ya ƙora mun idon shi, wanda nakasa fahimtan wani irin kallo yake yimun.

Tashi yayi ya fita yabar parlon, nima ganin haka na wuce ɗakin danake ina mamakin meye ya ɓata mishi rai kuma.

Da yammah Aunty ta shiryah zataje gidan maijego, da sauri na fito cikin shirina nace, "Aunty nima zan biki", tana kallona tace, "ba jita kinje ba? Kuma kin tambayi mijinkine"?

Zunɓuro baki nayi gaba ina cewa "Aunty don Allah kije dani mana, ko na tambayeshi shareni zai yi wallahi".

Dariya tayi tace, "gaskiya ki tambayeshi, don Baba ma faɗa zaiyi idan kina fita bada izinin mijinki ba, tun farko yamun kashedi".

Da sauri na dauki waya nayi dialling na ƙarya, xuwa can nayi magana a hankali kaman da Hamman nake magana na tambayi zuwa gidan maijego.

Wucewa mukayi maka shiga mota, daidai motan zai tashi sai ganin Hammah nayi ya fito daga side ɗin shi yana tahowa inda motan mu yake, ji nake kaman na tura hannun Aunty tafara driving mu tafi kafin ya iso.

Yana zuwa ya dafa marfin motan inda nake yana ƙara gaida Aunty yana tambayanta "Aunty sai ina da yamman nan"? Tana ɗan dariya tace zanje gidan maijego na duba su.

Shima dariyan yayi yace, "zan rage miki ƴar rakiya, ina so tamun gudun kurna ne for dinner idan

babu damuwa" Ya faɗa yana kallona.

"Iahhhh Hammansu babu damuwa dama sai da nace mata ta gaya maka, ashe ƙarya tayi tace mun ta faɗa maka har ka yadda, ta sauƙa kawai muma sai tayi har da mu".

Yana ɗan dariya yace, "ta gaya mun ban ɗauka hadda ke bane, dama nace mata tamun idan yaso sai na kaita daga baya".

"kabar ta kawai ba jiya taje ba, nima da wuri zan dawo Insha Allahu" ta faɗa tana cemun "toh fita naja mota nah".

Buɗe motan nayi na wuce gida da gudu ina kuka, dariya Aunty tayi taja motan ta tafi, shima dariyan yakeyi ya biyo bayana.

Mama taja tsaki ta sake Iabulen tana cewa, "ko uban me zai sa ya fito da ita daga motan? Ita kuma uwar banza don tsabar gulma tabar shi ya fito da ƴar a gabanta, toh zuwa zanyi naga uban da zasu ci acikin gidan da babu kowa sai su kaɗai", tana hararan Zainab tace, "ganki sakara babu hali aganki inda mijinki yake saidai kina nan yana can, ni narasa ke wacce irin yarinya ce, sai an ƙwace miki mijin tukun kiyi hankali ko"?.

Zainab ta tura baki gaba tace, "Mama don baki san irin fitinar Hammah bane? Ni ina zan iya mishi, Ga shegen saka mutum aiki sai dai baka zauna a inda yake ba".

Tana ɓata rai tace "yanzu ma fah wai saidai nayi mishi gudun kurna ne ko gudun meye ohoo ni bazan iyaba wallahi, gara ita da ta saba aikin wahalan taje can ta mishi, nidai kawai Mama ki hana shi kwana da ita kawai" ta faɗa tana miƙewa kwance akan three sitter parlon tana buɗe handset ɗinta.

Hararanta Mama tayi ta buɗe ƙofan parlon ta wuce side ɗin Aunty inda taga Hammah ya shige, cikin zuciyarta tana ayyah na irin abinda zata mun yau.

#Vote
Comment

Share
Follow.

*KU KASANCE DA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*
*1441H/2020M.*

®🖋
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION✍*
_{Gaskiya ɗaya ce daga kinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira.}_

🎐G•W•A🎐
_*GASKIYA DOKIN ƘARFE•* 🏇_

Story and written
By
*AUNTY NICE*

*_WANNAN BOOK SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Wattpad@GaskiyaWritersAsso.~

*page* 59---60

*____________*📖Yana shiga parlon yayi dai-dai da zan wuce ta corrido ɗin da zai sada ka da parlon Aunty, cikin hanzari ya ƙariso gaba na, yana kallo nah yace.

"tsabar kin rainani  shine zaki fita bada sani naba? Ko kin maidani Iusarin namiji ne wanda bai san kansaba? Toh wallahi ina miki kashedi na farko kuma na ƙarshe da kada ki ƙara gigin fita ko nan da bakin gate ba tare da izini na ba, tsabar kin rainani har zakice wai kin ƙirani ni nabaki izinin fita don rashin kunya ko".

Jikina har rawa yake yi don jin irin masifan da yakeyi mun, ina kallon shi cike da jin tsoron shi nace.

"Hammah nah don Allah kayi haƙuri wallahi tsoro naji ne yasa da Aunty tace na tambayeka nakasa, naga kafita ranka a ɓace shiyasa naji tsoro".

Hararana yayi yace, "saboda tsabar munafunci zakice baki san abinda kikayi ba"?....... Yana rufe bakinshi Mama tana shigo, sai jin murtanta mukayi tana cewa, " nagode Allah daka fahimci munafurcin wannan mai baƙar fuskan da uwarta masu son abin duniya, da na ɗauka ae kabiyota ne don soyayyah, ashe kaima kagane haline", ta faɗa tana bina da harara.

Jin abinda tace kawai yasani fashewa da kuka, juyowa yayi yana kallona tukun ya kalli Mama yace, "Mama meyasa kike son shiga abinda bai kamata bane? Nace kibar ɗaga hankalinki akan yarinyar nan ni kaɗai na isheta har saita buɗi baki tace bazata iya aurenba,  sukuma wanda suka haɗa auren daga nan zasu san tayi batare da sunga laifinki ko nawa ba" ya faɗa yana kama hannun Mama, sanann ya cigaba da cewa.

"amma yanzu da nayi niyyan dukan tane, ganin idonki yasaka naji jikina yayi sanyi, saboda kada wani abu ya faru azo ana cewa da saninki, kawai kizo ki tafi Mama nima me zanci da baƙar mace"? Ya faɗa yana jan ta zuwa hanyan waje, ita kuma sai cewa take.

"Bansani ba Hammansu, ae da bazan biyoka ba har saika naɗa mata na jaki irin na barikin sojoji, wallahi bana son yarinyar nan, tsorona kada Babanku yaƙi raba auren nan nazo ina haɗa zuriya dasu shine damuwa na".

Tana fita ya dawo inda nake bayan ya rufe kofan, ya ƙura mun ido ganin irin kukan dana ke tayi mai tsuma zuciya, can yace.

"Toh me aka miki ne Fatima? Na dukeki ne? Baki san na faɗa bane don Mama ta tafi amma ke kuma sai kike kuka"?

"Hammah toh ni mena muku ne kai da Mama kuke kina haka"? Na faɗa ina kara sautin kukan.

Kawai ji nayi ya jawoni ya rungumeni gam-gam a ƙirjinshi, a hankali yace, "toh kibar kuka bake bane kikayi laifi."

"Hammah ni mena maka ne? Fitane kuma na dawo don Allah kayi haƙuri, da wanne kake so naji? Kinda kuke mun ko masifan da kake mun"?

Shiru yayi yana ta bubbuga mun bayana, zuwa wani lokaci na bar kukan sai ajiyan zuciya danake ta sauƙewa, can naji shi ƙasa-ƙasa yana cewa.

"Me yasa kullum magananki Babagana ne kaɗai mai sonki? Idan su Abba sukaji ae zasuyi tunanin sun bani ke ina wulaƙantaki kuma bazanyi mutunci a idon suba, ae koda ba bani ke sukayiba ae ya kamata na karrama wanda ɗan'uwa na yaso aura ko? amma kullum sai kidinga cewa shi yafi kowa sonki, bayan na taɓa gaya miki akwai wanda yake miki sonda ko ke da kanki bakiyiwa kanki, ko kin manta"?

Shiru nayi ina ta ajiyan zuciya, kamar bazan ce komai ba, can kuma sai nace, "Hammah waye yaje sona ɗin? Bayan yanzu ina matsayin matarka ma yana sona?".

"Wataran zan nuna miki amma ki bari ki ƙara girma".

Ɗagowa nayi ina kallon cikin idon shi nace, "Hammah kuma idan yazo yace yana ona zaka bashi ni lokacin"?

Tsuke fuskanshi yayi har saida idanun shi suka ƙara shigewa ciki, sannan yasaka lips ɗin shi yana cijewa cikin bakinshi, ..... Yatsa na saka ina jan lips ɗinshi ƙasa ina cewa.

"Hammah zai maka ciwo ka sake shi" cikin muryan mai shirin yin kuka.

"kin damu danaji ciwo ne ko kindamu da wani abu ƴa faru dani ne?ki ke sakani jin zafi a zuciyata Fatima"?

"kullum magananki ɗaya, don Allah kibar yimun maganan kowa idan ina da daraja a idonki kinji"?

"Toh ka gayamun wanda yake sona ɗin, ko idan naji yamun in aure shi idan ka rabu dani" ko.......... Kafin na ƙarisa ya daka mun tsawa, wanda har sai da corrido ɗin ya amsa.

Bansan lokacin dana shige ɗakin Aunty da gudu na turo ƙofan na saka key ba, da sauri yazo jikin ƙofan ya buga yana cewa.

"Fatima ki buɗe mun ƙofan nan kafin ranki ya ɓaci".

Kaman zan ganshi a cikin ɗakin jikina yana rawa nace, "Hammah na tuba bazan sake cewa

komai ba".

Shiru yayi can yace, "ki buɗe ƙofan nan babu abinda zan miki",....... Ina jin shi nace, "Hammah kaida baka sona ae idan na buɗe duka na zakayi, garamaɓidan Aunty ta dawo ta kaini gidanmu nagayawa Abba ya raba auren nan, tunda shi ya matsa maka ka aure ni ko Hammah? Kaima ka huta da  ganin baƙar fuska".

Dariyan shi naji ƙasa-ƙasa, can naji yace, "wallahi kika bari Aunty ko Abba wani yaji maganar nan sai na ɓallaki".

Matsowa nayi jikin ƙofan nace, "Haba mijin farar mace taimakon ka zanyi a rabaka da baƙar fuskan da baku so kaida mumcyn mu", na faɗa ina murguɗa baki kaman yana kallona

Dariya yayi yace, "nidai ban aike kiba ki bari ni zan faɗa musu da bakina amma ki buɗe ƙofan na kalli baƙar fuskan ki nan, hala ma babu dogon hanci.

Buga cinya nayi da ƙarfi don yaji ni nace, "duk da haka nafi farar fuskan dai cikan ƴa mace ae, don nasan ko gasan kyau aka je wallahi daga kai har farar matar kan ni za'a zaɓa abar fara fuskar taku ihee bari ma kaji da kyau", na faɗa cike da tsiwa ina murguɗa baki.

"Banda ke miye abin burgewa a wurin ki da har zaki ƙira kanki da cikakkiyar mace"? Ya faɗa ina jinshi shima yana jun gunuwa da jikin ƙofan.

Matsowa nayi jikin ƙofan nace, "cikan breast da hips ae shine mace, kuma kasan saidai agani a wurina badai a wirin shamuleren mai fara fuskan ka ba kam".

Abinda ya mugun ban mamaki da ban taɓa jiba shine dariyan Hammah da ƙarfi kaman yana gaban abokanshi sannan yace, "don Allah baby Fati na buɗe naga wannan cikan mana"? Kuma har lokacin dariya yakeyi.

Buɗe baki nayi ina tarewa da hannu na daga inda nake na sake cewa, "cab ɗijan naki wayon, kalan kaga kayan alatu ka shefeni ko? Bayan ranan ma Allah ne ya taimaki baiwar Allah a mota ae daka shefe musu ƴa".

Wayyo Allah bansan lokacin da na tsuguna ƙasa ba ina rufe baki don jin Hammah yana dariya har da ɗan ihun shi.

"Don Allah ki buɗe mana Babyn Hammah wallahi kallon marasa kunyan idonki kawai zanyi, ni ina ruwana da wasu ƴan nunuwanki wanda basu wuce cikin cokali ba" ya faɗa yana buga mun ƙofan.

"Hammah kaface fah zan maka girki, toh ka tafi mana don Allah na fito, kaga Aunty yanzu zata dawo", na faɗa don na kaucewa maganan.

"Baby ni na ƙoshi da abincin kawai ki buɗe mun ƙofan, yawo fah zan kaiki ko baki son zuwa gidan mai haihuwan"?

"Hammah da gaske zaka kaini? Kuma zaka kaini gidan ƙawata Aishatu Trouble"? Na faɗa ina jin murnan zan fita.

A hankali ya matso jikin ƙofan yace, "duk inda kije so zan kaiki, idan yaso sai muje vannillah na saya miki ice cream ma".

Tsalle nayi nace, "wayyo Hammah na shiyasa nake madarar son ka wallahi", sannan na faɗa a hankali  nace , "Hammah kodai na maka rashin kunya ne zaka kamani da wayo", ina zaro ido na daga cikin ɗakin.

Shima jinshi nayi yana cewa, "haba babyn Hammah wallahi babu dukan da zan miki , yau har goyonki idan kina so zanyi, don Allah ki buɗe ƙofan nan".

Key nasaka ina shirin buɗewa, ni kuma Aunty nice nace mata "uhm uhm Fatima Badariyah" da sauri ta juyo ta ƙura mun ido tana zare su waje.

Da gudu na kama window ɗakin Aunty nace gara na dirƙa waje kada ta buɗe na haɗu da mugun sojan nan ya haɗa dani.

*Don Allah akwai wacce na mata alƙawarin read more dayawa, don Allah kiyi haƙuri har na gama typing ya goge, yanzu kuma wallahi sanyi nakeji kuma na gajji, kii haƙUrI sai wani lokacin zan daure nayi dayawa*

#Vote
Comment

Share
Follow.

*KU KASANCE DA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*
*1441H/2020M.*

®☄
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION✍*
_{Gaskiya ɗaya ce daga kinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira.}_

🎐G•W•A🎐
_*GASKIYA DOKIN ƘARFE•* 🏇_

Story and written
By
*AUNTY NICE*

*_WANNAN BOOK SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Wattpad@GaskiyaWritersAsso.~

*page* 61---62

*_____________*📖 Har nayi niyyan murɗa key ɗin kuma sai wata zuciyar ta haneni, komawa da baya nayi ina kallon ƙofan nace, "Hammah kayi haƙuri tsoro nakeji, kuma yanzu Aunty zata

dawo fah", na faɗa ina wucewa kan gadon.

Ƙwafah yayi yace, "zamu haɗu ne yarinya sai kin eaina kanki, zaki san da soja kike wasan", sannan ya faɗa da karfi don naji, "ki tabbatar kin haɗa mun dinner".

Saida naji ƙaran motan Aunty tukun na buɗe ƙofan da sauri nayi hanyar kitchen, ina ji ta shigo ni kuma da sauri na fito daga kitchen ɗin na iso wurinta ina mata sannu da dawowa.

"Mekike girkawa banji ƙamshin komai ba"?  Ta faɗa tana bina da kallo.  Turo baki gaba nayi ina cewa, "Aunty nifa nakasa sanin abinda zanyi ne, shiyasa najira ki dawo".

"amma Riyyah tunaninki kaɗan ne, ta yayah ma zaki zauna zaman jiran saina dawo? Idan kuma nayi dare fah? Don Allah tashi ki wuce kisan me zaki dafa, ae nagaya miki abin da yafu so".

Dama abinda nake nema tamun kenan, don bana so ta gane a shiriritana na ɓata lokacin, kitchen na wuce na fitar da kifi guda uku manya, wanke su nayi na gƴara, don ina son nayi irin gashin *(Maman hazeek*) don ya mun daɗi babu karya.

Gwaten dankali nayi wanda yasha vegetables sosai, sannan na gasa kifin, na haɗa mishi ginger kuma wanda yasha pineapple a ciki.

Ina gama aka ƙiea sallan isha, da sauri na fitar mishi zuwa parlon Baba don nasan Baba yau yana side ɗin Mama ne, sannan na wuce ɗaki donyin sallah.

Da ƙyar na nutsu na shiryah lokacin da Khalifah yazo yace mun Hammah ya shigo, wai naje nayi saving ɗinshi inji Aunty, haka na fito badon raina yaso ba.

A hankali na karasa wurin dinning ɗin inda shima lokacin ya kariso ya zauna, dai-dai zai zauna ya saka ƙafan shi ya taka nawa sannan ya murtsuka don mugunta.

Da sauri na matsa ina faɗin "washhhh Allah Hammah me na maka kuma"?

Ko kallona baiyi ba ya ja sit ya zauna, turo baki nayi inata ƙananun mita na, tukun na zuba mishi dankalin kaɗan a cikin wani pilet mai kyau, sannan na ɗauka kifin da yaje naɗe a cikin poil paper na ɗaura akan ɗatan pilet ɗin, sannan na ɗaura fork akai, gefe naja kujera na zauna ina hararan gefe ina ƙunƙunin takani da yayi

Ko ɗaga kai baiyi ba ya kalle ni, abincin shi kawai yake ci babu wani damuwa a tattare da shi ko kaɗan.

Yana gamawa yaja kujeran ya miƙe ba tare da ya kalli inda nake ba ya bar wurin, da ido na bishi cikin mamaki ina buɗe baki.

Har gefen kujeran da Aunty take yajw gefe yaɗan zauna, yan mata magana wanda ni tsabar ɓacin rai ban ko ji me yake cewa ba, daga baya ya tashi bayan ya mata sallama ya fita a parlon, ko juyowa baiyi ba ballantana ya kalle inda nake.

Yana fita su Gidaɗo da Aunty suka zo kan dinning ɗin Aunty tana cewa, "gara muma muyi dinner ɗin don duk ƙamshi yagama cika mun ciki tun Hammanku yana ci".

Kowan mu zama yayi mukayi dinner a tare, gefe ɗaya zuciyata sai ta fasa ta keyi da abinda Hammah ya mun, wato gani ƴar iska na mishi girki shi kuma yaci ya tafi gurin wanda yasan darajanta sama da ni ko"? Na faɗa kaman zan fasa kuka a zaune a wurin, kawai daurewa nakeyi don kar su gane halin da nake ciki, har muka gama.

Washegari abin mamaki kaman an hana Hammah shigowa side ɗin Aunty, har sai dare tukun ya shigo yana ce mata yaje jama'are ne shida Zainab da Nabil, hira suka taɓa kaɗan shida ita ,kafin ya sakai ya tafi abinshi.

Har tsawon kwana biyu zuwa uku banga idon Hammah ba, don ko Aunty saida tace, "Hammanku kam zama ya gagare shi, kullum yana bisa hanya".

Ana gobe sunan Adda Umaima su Feenah suka iso, kaman zanyi yayah ita da Adda Hummy, waya mukayi kawai nace musu ina zuwa anjima nima.

Har akayi la'asar roƙon Aunty nakeyi akan ta barni naje gidan Adda Umaima amma firr taƙi barina, tace saidai na tambayi mijina idan shi ya barni sai naje.

Ana idar da sallan magarib na fita raina a ɓace naje side ɗin Hammah ina knocking ƙofan parlon shi, har kusan 2min banji an amsa ba, sake bugawa nayi a hankali tsoron kada Mama taji ta leƙo nakeyi.

A hankali naji an buɗe ƙofan ana leƙa kowaye, ganin Nabil ne nayi saurin sunkuyawa ina ɗago shi sama, murmushi nake mishi nace, "ɗan nabilo na kana nan kaƙi zuwa mun ko"? Shina dariya ya keyi da fuskan shi mai tsananin kama dana Hammah yace.

"Mama tace kada naje wurin Aunty wai tana bulala, amma zan tambayi mami nah idan tace nazo"ya faɗa kaman baya son maganan amma fuskan shi ɗauke da fara'a.

Ajiye shi a ƙasa na kama hannun shi muka shiga parlon ina tambayan shi ina Daddyn shi yake?.

"Yaje mosque" ya bani amsa, dai-dai lokacin Zainab ta fito daga ɗakin da yake matsayin na Hammah, kallo na takeyi kaman taga kashi tana wani ya mutsa fuska.

ko kula abinda takeyi ban yiba, na  juyo na maida hankalina kanta ina faɗin, "an wuni lafiya maman Nabil"? Cikin ɗaure fuska ta amsa mun da "Lafiya" sannan ta maida hankali kan tv lokacin da take cewa Nabeel, "ka maida shi cartoon Nabeel kafin Daddyn ka ya dawo kaji" da sauri ya ɗauki remote yana murna ya mayar channel ɗin da akeyin cartoon ɗin.

Kallon gefen da nake tayi fuskanta a ɗaure kaman zatayi magana kuma sai naga ta fasa ta juya ta koma ɗakin.

Ajiyan zuciya nayi nasaka hannu na jawo Nabeel har gefe na na rungume shi ta gefe ina tambayan shi me ya hana shi bin Daddyn shi mosque ɗin?.

Dariya yayi yana kallo na amma rabin hankalin shi yana kan TV yace mun "Mamie tace nayi small naje mosque".

Riƙo hannun shi nayi nace, "Yaronah bakayi small ba kaji, kullum kaga Daddyn ka zaije kace mishi kaima zakaje, zai barka kuje kaji ko my boy", na faɗa ina duban shi da murmushi, wanda shima ina ganin shi murmushin yake ta bina da shi wanda kuma lokaci ɗaya naji yaron ya shiga mun rai, ɗan kyakkyawa da shi kaman na gudu da shi

Kwantawa yayi ajikina yana kallona yace, "ina tsoron gayawa Daddy, saida ki gaya mishi kinji Aunty"!.....dai-dai lokacin naji an buɗe ƙofan parlon.

Saida naji hantar cikinah suna neman hautsinewa, domin ganin shigowan Hammah fuskan nan kaman an mishi albishir da mutuwan shi yanzu.

Da sauri naga Nabeel yaro ƙarami ya tsuguna har ƙasa yana, "Daddy sannu da dawowa" kai kawai ya ɗaga mishi idonshi yana kan TV, nima da sauri na buɗe baki nace.

"Barka da dawowa" ko kallo na baiyiba ballantana nayi tunanin zai amsa mun, shiru nayi ina riƙe da hannun Nabeel sai murzawa nakeyi kaman zan ranta da gudu, don abinda yaban tsoro harta ɗan shi ƙwalli ɗaya ya nutsu kaman babu jini ajikin shi tsabar tsoron Babanshi, ina kuma ni dana mishi laifi?.

Channel ya canja ya mayar BBC NEWS, bai ko kalli inda muke ba, ya cigaba da kallon shi, a hankali na buɗe bakina nace, "Hammah don Allah kayi haƙuri", na faɗa duk illahirin jikina rawa yakeyi.

"Idan abinda ya kawo ki kenan ki tashi ki bani wuri, bana son hayaniya", ya faɗa ko kallona baiyi ba.

Duk yadda naso naji ki akan kujeran sai naji na kasa, samun kaina nayi da tashi na karasa har inda yake zaune na tsugunna dai-dai gaban shi nace, "Hammah tun ranan banje gidan Adda ba, kuma har gobe suna banje ba, gashi su Feenah sunzo" na faɗa jikina da muryah na sai rawa sukeyi.

"Sai akayi yayah?kina tunanin suna yiwa mazajen su rashin kunya ne? Ko kina tunanin rashin kunya zaisaka mazajen su subar su suzo koda ciki ɗaya suka fito? Ko suna ne baza kije ba ballantana ganin wata Feenah ballantana maijego" yana cigaba da kallonshi fuskan shi a ɗaure ya faɗa.

Fashewa da kuka nayi ina roƙonshi da yayi haƙuri wallahi bazan sake ba, ko kallona baiyiba ya cigaba da kallonshi, ganin ina kuka yasa Nabeel tashi da gudu Yayi ɗakin Maman shi, don naga alaman tsoron Daddyn shi yake sosai.

Sake faɗin yayi hakuri nayi, amma ko kulani baiyiba, ina cigaba da kuka na wanda har a lokacin ina tsugune a gaban shi, sai ganin Zainab nayi ta fito kanta ɗaure da gyalen kayanta.

Kallona ta tsayayi can naji tana cewa, "don Allah baiwar Allah kina cika mun kunne da sautin kukan ki, wannan ae rashin hankaline kishigo kina tada mana hankali, ki bari mana idan an kawo ki tukun kiyi abinda kike so bawai yanzu lokacin hutun mu ki damemu ba" ta faɗa kaman zata sako mun duka.

Tsawa Hammah ya daka mata wanda har saida na nemi wuri a ƙasa na zauna batare dana shiryah ba, "Zaki ɓace mun a wurin nan ne ko sainayi ball da ke i?idot, ae kece baki san ciwon kanki ba, ke da nake fama da kiyi zumunci da mutane amma babu inda kika shiga kika gaishesu, kaf garin nan ƴan'uwan Baba ne amma babu abunda ya dameki, sai ita da takeneman taje tayi zumunci zaki zo kina mun ihu akaina"? Fita kiban wuri.

Da sauri ta juya tayi cikin bedroom ɗin, nima ganin haka nayi saurin tashi da niyyan guduwa kada a dawo kaina.

Charab naji ya jawo hannu na har saida na faɗo kan cinyan shi, ido na zaro ina kallon shi nace,

"Hammah na haɗa ka da Allah kayi haƙuri, wallahi bazan sake ƙinjin maganan kaba", na faɗa ina haɗa hannu na biyu alaman neman afuwa, zauciyata kuma sai harbawa takeyi don tsoro ina zubar da hawayen da ban san adadin su ba.

Sako kanshi yayi kan ƙirji na, dai-dai inda zuciyata ke harbawa ya kwantar da kanshi, ni kan sai maƙyarƙyata kawai nakeyi, ashe Hammah har matar shi bai bari ba? Ashe ina samun dachewa baya mun ne, da ga yau bazan sake tsokanan shi ba, na faɗa a zuciyata.

Ina so nace zan tafi amma ina jin tsoron mishi magana, muna haka har naji an ƙira salan ishaa, a zuciyata nace, "Alhmdulliah".

Dawo da kanshi yayi saitin kunne na , a hankali yace, "kije kiyi sallah sai na kaiki gidan Umaiman ko? Amma kada ki ɓata mun lokaci" ya faɗa yana ɗaga kanshi daga jikina.

Da sauri na tashi na tsaya ina kallon shi nace, "Hammah da Nabeel zamuje"? Hararan da yayi munne yasa ni ficewa da gudu banjira abinda zaice ba.

Murmushi yayi bayan fitana yana shafa fuskan shi yace, "silly girl, wato tana tsoron haɗa hanya dani shine zata ce muje da Nabeel ko"? Ya faɗa yana miƙewa tsaye.

Nima ganin ya miƙe tsaye nace bari naje nacewa Riyyah ta ɗauki Mujaheed idan baizai yadda suje da Nabeel ɗinba, sabida tsaro.

#Vote
Comment
Share
Follow.

*KU KASANCE DA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*
*1441H/2020M.*

®🖋
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION✍*
_{Gaskiya ɗaya ce daga kinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira.}_

🎐G•W•A🎐
_*GASKIYA DOKIN ƘARFE•* 🏇_

Story and written
By
*AUNTY NICE*

*_WANNAN BOOK SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Wattpad@GaskiyaWritersAsso.~

*page* 63---64

*_____________*📖Ina shiga cikin sauri na haɗu da Aunty dake fitowa a kitchen riƙe da cup ɗin tea a hannunta, bina takeyi da kallon mamakin irin saurin da nakeyi, ganin ba kula ta zanyi ba tayi saurin cewa.

"ke kuma meya faru kike sauri haka"?

Dawowa baya nayi nace, "Aunty wallahi sauri nakeyi, Hammah ne yace nayi sauri ya kaini gidan Adda Umaimu" ina gama faɗi na wuce ɗakin batare da na jira mai zata ce ba.

Ban wani ɓata lokaci ba na saka wani dogon riga na lace, ban wani ɗaura ɗankwalin kayan ba, wani gyale ɗan ƙarami kawai na yafa, har zan fito na koma sauri-sauri na shafah wani humran Aunty dana gani akan mirrow ta.

Ina fitowa na fita ganin babu Aunty a parlon, cikin sauri-sauri na isa inda na hango shi a jikin motan shi, da sauri na buɗe gaban motan na shiga, saida ya shigo har yana shirin tada motan, tukun nayi saurin cewa.

"Lahhh Hammah na manta ban ɗauko Mujaheed ya raka mu ba", ina kama bakina ido na a zare.

Hararana ya juyo yayi yana tada motan shi yace, "wallahi idan kin fita a motan nan, babu inda zan kaiki kuma", ina kallo yaja motan muka tafi.

Har muka isa bai kalli inda nake ba, ganin bai ce komai ba na kalle shi nace, "Hammah bazaka shiga bane"?

Bai kalle ni ba yace, "shiga ki fito ina jiranki".

Da sauri na buɗe motan na shige da sauri, tunda ga parlor nake jin muryan Feenah, cikin sauri na ƙarisa ɗakin ina ihuun ƙiran sunanta.

Itama da gudu ta rungumeni tana, "wayyo ga best... Ga ƙawata" ta faɗa tana canja abinda tayi niyyan faɗa, faɗawa mukayi kan gadon muna ihun murnan ganin juna.

Ummi ce tayi mana tsawa tana. "anya zakuyi hankali kuwa? idan kun taka mutane fah? sokaye kawai baku san kun girma bane"?

Dariya muke tayi, Adda Hummy ma tana taya mu, da sauri na koma kanta ina "sorry Adda nah wallahi tun ɗazu naso zuwa Hammah ne bai barni ba sai yanzu"na faɗa ina turo bakina.

Dariya tayi tana kallon babyn da ke rungume a hannunta tace, "Toh Riyyah nah gara ya hanaki yawo ae, don ku yanzu baku san nauyi ya haukanku ba sai ana tuna muku" ta faɗa tana miƙo mun babyn.

Da sauri na jarɓa ina gaishe da Adda, sannan na gayar da Ummi dake zaune kusa da Adda Umaimah.

Feenah ce ta dawo kusa dani tana cewa "ina Hamman jarirai"? ta faɗa tana dariya hannunta yana riƙe da ƙafan babyn.

Nima dariyan nayi nace, "yana mota yana jirana, me kika kawo mun a kano? And kuma yayah Hammah nah"?

Adda Hummy ce tayi sauri tace, "shine kika barshi a waje Riyyah? don Allah kije ki shigo da shi, yaufa sanyi ake zubawa kya barshi a mota"?

Ummi ce ta chafe maganan dacewa, "ke kike da wannan tunanin, ita tasan abinda yakamata ne"? ta faɗa tana bina da harara.

Dariya nakeyi nace, "Adda nace ya shigo wallahi shi yaƙi shigowa".

Shareni Ummi tayi, ita kuma Adda ta biye mu aka cigaba da hira, sai labarin Adda Hafsat da babyn ta ake tayi, kowa dariya yakeyi don tace ita ma sai tazo sunan Umamah.

Ƙarfe tara nayi Umi tacr, "toh sarkin hankali tashi ku tafi kada dare yayi".

Babu yadda na iya na dubi Feenah nace, "ƙawata don Allah muje ki tambayamun shi da safe nazo da wuri", kowa dariyan shirmen mu da Feena sukeyi, haka na musu sallama muka fito waje.

Har jikin motan muka ƙarisa, buɗe gaban motan nayi ba tare dana shiga ba, Feenah ce ta matso tana gaishe shi, ni kuma ina ta taka ƙafan ta don tayi magana.

Kallon shi tayi tana dariya na rashin gaskiya tace, "Hammah gobe da wuri Riyyah zata zo muyi aiki da ita"? Ɗago manyan idon shi yayi ya dube ta yace.

"Haka tace ki gaya mun ko"? Rufe baki nayi ina cewa, "Hammah ni kuma? Wallahi cewa tayi na kwana, shine nace idan nazo da wuri ma taci sa'a, saboda ba lallai bane abarni na fito da wuri".

Kallonta yayi yace, "Allah ya kaimu goben", bai sake ce mana uffan ba, ganin haka yasa Feenah ta mun sallama ta juya tayi cikin gidan da sauri saboda sanyi.

Shiga nayi ina gyara gyalen kaina, banyi tsamnani ba naji yace, "dare yayi bazamu samu zuwa gidan friend ɗinkin ba".

"haba Hammah kaifa kace za muje" na faɗa kaman zan masa kuka.

"Toh ae kin ɓata lokacinki anan, saboda haka sai nxt time" ya cigaba da driving ɗinshi hankali kwance, turo baki nake tayi bance komai ba.

Bamu muka tsaya ba sai agaban shagon SSG dake titin winti street, kallona yayi yace "fito mu shiga".

Muna shiga yace, "Zaɓa mun kayan Jarirai na baby boy set 5, ko wanne bibbiyu".

Wuri na samu na  zauna na fara zaɓa, har jusan goma saura tukun muka fito a shagon, abin mamaki ko wanni kayan ka kallah sai ka ɗauka babu wanda yafi shi kyau.

Bamu tsaya ko ina ba sai shagon sabo gwaram na zannuwa, haka muka shiga naga ya nuna waso chiganvy masu kyau kala biyu iri ɗaya, sannan ya sa aka miƙo mishi wani material wanda

yakai kusan 12k, shima kala biyu, leda aka saka mana muka shiga mota.
Muna hanyan gida ya ratsa da mu ta bauchi clup.

Fita yayi shi kaɗai, bayan wasu ƴan lokuta ya dawo hannun shi riƙe da leda guda uku, bayan motan ya buɗe ya ajiye, motan yaja muka wuce gida.

Muna parcking na buɗe motan zan fita, yana kallona yace, "wa zai kwashe miki kayan da kika fita".

Juyowa nayi ina duban shi domin neman ƙarin bayani, harara na yayi yace, "bana son shiririta ba haihuwa akayi miki ba? Sai ki raba musu biyu ita da ƴar'uwarta na kanon".

Godiya na mishi ba kaɗan ba, sannan na buɗe motan na fita, sit ɗin bayan na buɗe na ɗauko ledodin kayan na rike.

Ina fara tafiya naga yana bina da leda a hannun shi, har parlor muka shiga tare inda naga Aunty da su Gidaɗo a zaune suna kallon wani indian film.

Wuri na samu na zauna kusa da Khalifah, wanda yayi saurin karɓan kayan hannuna ya ajiye a gefe na, sannan ya gaida Hammah ninkuma yamun sannu da dawowa.

Aunty ne suke hira da Hammah, wanda yake gaya mata tafiyan shi saura 2dys, wanda koni sai yanzu na tuno ashe fah Hammah bai gama ba zai koma, duk sai naji babu daɗi araina.

Tashi yayi zai fita yana miƙo min ledan da ke hannun shi sannan ya fita, a parlon su Gidaɗo suna mishi saida safe, amma nikan kaman an ɗinke baki na ban iya ce mishi komai ba.

Yana fita Gidaɗo ya sauƙo ya ɗauki ledan da sauri yana cewa wannan duk tsaraba ne husbyn ki ya miki? Gaskiya ba laifi gara ana ɗan yawan fitan kona dinga ɗan lasawa", ya faɗa yana buɗe ledan.

Ƙamshin gasheshshen hanta ne ya cika wurin ,da saurI ya ɗauka yakai bakinshi, Aunty ce tace, "toh acici sai ka miƙo a ɗiba muku tukun kafara ci ko"?

A pilet ɗaya ta zuba mana muka hau ci nida ita, shi kuma shida khalifah ta zuba musu, mujah kuma aka aje mishi don yayi bacci, sai miya Gidaɗo yakeyi wai Aunty ta zuba namu yafi yawa.

Ko kulashi bamuyi ba, muna gamawa na jawo ledan kayan masu haihuwan na nuna mata, yaba kyaun kayan tayi tana fewa, "gaskiya kin fito da masu jego keda Hammanku, Allah ya ƙara buɗi,

kuma acigaba da yimishi biyayyah da kyautatawa".

Dariya nayi bance komai ba, haka muka gama kallonmu kowa ya wuce makwancin shi.

Gari na wayewa wurin ƙarfe takwas na yi wanka na shiryah bayan har nagama haɗa break, waya na ɗauka ina tajin tsoron ƙiran Hammah, amma haka na daure na ƙira shi, har yagama ringing bai ɗauka ba.

Tsoro naji nayi tunanin ko yana bacci ne na ƙira? Bangama tunanin ba naji ƙiranshi ya shigo mun.

Da sauri na ɗauka, bayan na mishi sallama na gaishe shi sai kuma nayi shiru, ....... Jin shirun ya saka shi cewa, "na ajiye ne baki da abin faɗa kika hanani bacci"?

"Hammah dama nace zuwa gidan Adda Umaiman ne nake tuni" na faɗa ina jin faɗuwan gaba.

"Fatima baiyi safiya ba"?

"Hammah Allah baiyi ba, kasan zamau haɗa abincin sunan fah".

"Toh ni wa zai haɗa mun nawa idan kin tafi"?ya faɗa da murya kaman wani marayan da ya rasa uwa da safiyan nan.

Dariya nayi don jin muryan nashi nace , "Hammah baga Aunty Zainab ba,? Ita sai yau ta haɗa maka , Ki kuma insha Allau gobe zan maka, kafin na tafi kano"?

Ɗagq murya yayi yana cewa, "innalillahi bayan yau ma zaki fita har kuma wani kano kike maganan zuwa"?

"Hammah kamanta sunan ɗan Adda Hafsat ne"?

"ina sane, amma ae yawon zaiyi yawa Fatima, gashi baki wani saka hijabi haka kike fita abinki" ya faɗa yana jan tsaki a hankali.

"Hammah idan kana so zan dinga sakawa, yanzun ma don naga da kai nake fita ne shiyasa bana sakawa, amma insha Allahu zan kiyaye".

"Toh ni ɗin da kike saka gyalen me kike nuna mun na gani? Bayan jiya ina jin ƙamshin turare amma kika mun rowa".

"Hammah ae baka ce mun kana so ba, dana kawo maka ka shafa, amma kuma fah na mata ne, humrah ne".

"nima ae na mata ne, kuma ni na jikinki nake so ba wanda yake kwalba ba".

Shiru nayi ina tunani sannan nace, "na jikina kuma yayah zanyi na shafa maka?" Dariya yayi yace.

"idan na rungume ki ae kullum da ƙamshin ki nake kwana, kinga jiya ma da baki mun rowan jikin kiba ae dana kwana da ƙamshi", ya faɗa yana wani jan iska mai ƙara a bakin shi.

Cikin shagwaɓa nace, "Hammah ni ba kin kulanikayi ba? Ko kulani bakayi ba sai ɗaure fuska kakeyi".

Dariya yayi yace,"toh ba ke kika ce sai da ɗan rakiya zamu fita ba? Toh yayah zan miki tunda tsoron Hamman ki kikeyi? Shiyasa na barki kawai don kada ki fara gudu idan kin ganni".

Dariya nayi cikin neman magana nace, "Hammah taso muje mana idan yaso zamuyi maganan a hanya, ko kuma sai a hanyan kano zamuyi labarin ko"?.

Da sauri naji yace, "zamu tafi kanon tare ne Babyn Hammah"?

Da sauri na miƙe zaune nace , "wallahi kam Hammah kuma zan baka wani labari a hanyan, kuma zan taho maka da duk kalan turaren da kake so Hammah nerh!".

"toh je kiyi wanka ki shiryah kafin nima na shiryah sai na kaiki".

"Hammah nikan na shiryah kai kawai zan jira ka shiryah,", sannan nace, "I luv u Hammah na, nagode".

Da sauri na fito da kayan da zan saka idan nayi wanka, sannan na fito da gudumawan Adda Umaima da babyn mu, parlor na fito na samu Aunty, sanan na gaya mata Hammah zai kaini yanzu.

Addu'an dawowa lafiya ta mun, sa'an nan na nemi wuri na zauna muna ɗan taɓa hira kafin ya fito.

#Vote
Comment
Share
Follow.

*KU KASANCE DA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*
*1441H/2020M.*

®🖋
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION✍*
_{Gaskiya ɗaya ce daga kinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira.}_

🎐G•W•A🎐
_*GASKIYA DOKIN ƘARFE•* 🏇_

Story and written
By
*AUNTY NICE*

*_WANNAN BOOK SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Wattpad@GaskiyaWritersAsso.~

*page* 65---66

*___________*📖Ba tare daya shigo ba ya kira wayana akan yana mota, sallama nayiwa Aunty na ɗauki kayana na fita.

Ina shiga motan naji wani kunyan shi yakama ni, kasa nayi da kaina ina faɗin, "Hammah an tashi Ipy"?

Dariya kaɗan yayi bai amsa mun ba ya ja motan muka wuce, har muka isa kofan gidan bai ce mun uffanba, nima bance komai ba har muka isa.

Yana packing ya juyo ya ƙura mun ido, duk sai naji nakasa kallonshi, ƙasa nayi da idona ina wasa da zoben da yake yatsa na.

Shirun naji yana yawa a hankali na ɗago kaina na kalleshi, amma irin kallon da yake mun da sauri na maida kaina ƙasa, ba tare da abinda zan faɗa na iya faɗiba.

Riƙo hannu na yayi har lokacin bai ce komai ba, sai murza mun tafin hannu da yakeyi, lokaci ɗaya naji jikina yana ta ɗan ɓari a hankali.

Jinake kaman na buɗe ƙofan na fita da gudu, don har yanzu murza mun hannu yakeyi batare da ya ce uffanba.

Fitowan mijin Adda Umaimah ne ya dawo dashi kan hanya, ni kuma na samu saukin abinda nakeji, jiki a mace yace.

"idan anyi magarib zanzo ɗaukan ki, sannan ya buɗe ƙofan ya ƙarisa wurin mijin Addan, nima jiki a mace na fito, sama-sama na gaishe shi na wuce cikin gidan.

Ina shiga parlon na haɗu da Ummi nah ta fito daga kitchen, da sauri na ƙarisa na rungumeta, gaisheta nayi, bayan ta amsa tace mun xata tafi gida yanzu, sai yammah ta dawo, saboda mai zama da Adda yau zatazo daga Alkaleri.

Ɗakin na wuce na samu mai jego tasha gayu cikin wata super, Feenah na mata make-up, Adda Hummy na shiryah Babyn da aka saka mishi *MUHAMMAD* ina dariya na ƙarisa gefen maijego ina cewa.

"kyau kenan Adda"? ...."gaskiya Adda kinyi kyau sosai, kaman ba haihuwa kikayi ba? gaskiya ko Feenah ma dani babu abinda muka isa nuna miki", ina faɗa dukkan su suka saka dariya,

Feenah tana cewa.

"gaskiya ƙawata ban yadda ba, nifa Adda Umaima 3yrs ta bani hala ma hadda watanni, kinga ko dole na fita ƙira da haɗuwa", ta faɗa tana jijjiga jiki kamar wata tarwaɗa.

Adda Hummy sai dariya take mana tana cewa, "nidai babu wadda ta kai ki a wurina kyau da haɗuwa, don duk kyaun yarinya a bayanki take baby nah"! Kowa dariya yake yi.

Wurin Azahar ƴan alkaleri duk sunzo, Aunty ladidi a gidanta akayi abinci da su coslow, da pappe chicken.

Dama Aunty ta bada aikin Cake a gidan Hajiya Addayo sister Daddy, da sauran kayan snacks, mu kuma kunun aya da kunun gyaɗa, alale, zoɓo muka haɗa nida su Adda da feenah, ana sallan Azahar mukayi wanka muka chakare, kaman wasu amare muka fito.

Da yammah *SHAGARI AUSHER* da *AHMED MISAU* sukazo sukayi ta kashe mana pics.

Gaskiya taro yayi kyau, su Aunty sai yamma suka iso, ana sallah magarib na shiga alwalah naga nayi baƙo, a zuciyata nace, "shiyasa nayita jin ciwon mara, duba pad nayi kawai nayi na saka.

Ina fitowa na tarar Aunty zasu tafi, da sauri nace "Aunty zan biko'.

Bata so ba haka na fito na bisu, muka tafi tanata mitan idan Hammah yazo fah?, ina dariya nace, "Aunty mara na ne yake ciwo".

Muna zuwa gate shi kuma yana shirin fita, yayi kyau kaman wani ba indiye, Aunty ce ta tsaya tana jiranshi don ganin ya fito yana ƙarasowa, gaisuwa sukayi tana tambayan shi inda zaije.

Kalloni yayi ya juya kanshi gefe yace, "zanje gidan Abba wazeery ne da gidan Abba na musu sallama", ya faɗa ko sake kallona baiyi ba.

Aunty ta mishi sallama tana wucewa damu ciki, nidai sauri-sauri na wuce ɗakin Aunty na faɗa kan gado.

Tana shigowa tace, "ke ko kafin ciwon yaci ƙarfinki ae yakamata kisha magani ko"? Tashi nayi na buɗe maganin na sha, da sauri naja bargo na kwanta, babu abinda nakeyi sai muƙurƙusu.

Aunty da tausayi ta dubeni tace, "Riyyah da kinje kinyi wanka da ruwan zafi, zakiji daɗin jikinki kaɗan, hala kinje kisha kayan zaki bayan ga date ɗinki kinsan ya matso".

Juyi kawai nakeyi ban kula Aunty ba, dai-dai nan wayata ta fara ringing, da ƙyar na jawota na daga jikina sai rawa yakeyi na dauka, a hankalu ɓace, " hello".

"Ke kuma don kin rainani nace kijira nazo ɗaukanki amma kijayi tahowar ki? Bayan nufina na kaiki ku gaisa da gidan Abba Wazeery", kashe wayan yayi bai sake kula ni ba.

Kuka nasaka ina kallon Aunty, kallona tati tace, " Hammanku ko? Toh meyasa baki mishi bayani ba, sai bayan ya kashe zaki saka mun kuka"? Tashi tayita fita.

Ɗaukan wayan nayi na sake ƙiranshi, yana ɗauka na saka kuka, bance komai ba, naji yayi tsaki yace.

"Meye kuma"?..........kukan na cigaba dayi sannan nace, "Hammah ciki nane yake ciwo shine na biyo Aunty don nasha magani".

"tsakani da Alƙah Baby idan kika ƙira kika ce mun bakida lpy ae zan fahimce ki ko? amma sai kawai na ganki kun dawo"?

"Hammah kayi haƙuri bazan sake ba", na faɗa sai sheshsheƙan kuka na keyi.

"Toh kukan ya isa haka, kisha magani ki kwanta, inaga baza ki iya tafiya zuwa kanon ba, kawai da safe kafin na wuce sai muyi sallama ko"?

"Hammah nikan zan iya zuwa, yanzu nasha magani idan nayi bacci zaiyi sauƙi".

"Toh ki shiryah by 10:00 zamu wuce ko".

Haka mukayi sallama, wanka na shiga nayi da mai zafi, ina fito na ɗale gado, addu'a nayi na kwanta.

#Vote

Comment
Share.

*ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻

*BADARIYA*
*1441H/2020M.*

®✍
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION✍*
_{Gaskiya ɗaya ce daga kinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira.}_

🎐G•W•A🎐
_*GASKIYA DOKIN ƘARFE•* 🏇_

Story and written
By
*AUNTY NICE*

*_WANNAN BOOK SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Wattpad@GaskiyaWritersAsso.~

*wannan shafi na baka kyauta ƙanina 80k, Allah ya bar xumunci*

*page* 67---68

*____________*📖Bani na tashi ba sai wurin 9:00 lokacin Feenah ta ƙirani akan su zasu wuce, sannan take roƙona, "don Allah ƙawata idan kunzo ki sauƙa a gidana kinji" dariya na mata nace, "kimana addu'an isowa lpy kawai ƙawata, ki kuma fara shirin komawa school, don saura 2wks mu koma, bawai kin shantaƙe kina ta zuba amarci ba".

"Wayyo Allah kawata ki daina yankar mun da zuciya don Allah, yanzu yayah ma za'ayi na iya barin Hammah na? Ni karatun ma ya isheni ƙawata" ta faɗa kaman zata mun kuka.

Dariya nayi nace, "nikan barni na je na shiryah, gara ke mai Hammah" kashe wayan nayi na shige toilet.

Ina fitowa na ɗauki ɗan ƙaramin traveling bag ɗin Aunty na shiryah kayana a ciki, sannan na zuba cosmetics ɗina a cikin handbag ɗina, cikin sauri-sauri na shiryah cikin wani skirt da riga na wani fari da yellow atamfah, irin na sallan bana, wanda nayiwa mum sayyeed da innaro gaskiya writers, ina cikin fesa turare Aunty ta shigo, kallona tayi tace.

"Riyyah na kinyi kyau sosai, amma don Allah kisa wani abu a bakin ki mana, sai kisha maganin ko"?

Ɗan ya mutsa fuska nayi nace, "Aunty ni tashin zuciya nakeji, kawai zanci cake ko guda ɗaya sai nasha maganin".......da sauri Aunty ta ɗauko mun cake ɗin guda biyu ta miƙo mun da ruwa a cup, ina kallonta cike da ƙauna nace.

"Aunty ina madaran sonki wallahi" itama dariya tayi kaɗan tace, "mee too my Riyyah".

Ina gama shan maganin Hammah yayi sallama a ƙofan ɗakin Aunty, ana amsa mishi ya sako kanshi ciki, a bakin ƙofan bayan sun gaisa da Aunty yaja ya tsaya hannun shi rungume a ƙirjinshi, ƙura mun ido yayi kaman bai taɓa gani na ba, gaishe shi nayi ina ɗaukan gyale na, "idan kingama kishiga wurin Mama ki gaisheta" kawai ya gaya mun sannan ya juyagun Aunty yana cewa.

"Aunty mukan zamu wuce don Allah a bimu da addu'a" ya faɗa yana fita daga ɗakin bayan Aunty tana ta jero mishi addu'an tafiya lafiya da samun nasara a duk inda yaje.

Kallon Aunty nayi kaman zanyi kuka nace, "Aunty kiji wai naje na gaishe da Mama, idan taci mutunci na fah"? Na faɗa idona na cikowa da hawaye.

"Hakanan zaki daure Riyyah, kinsan fah duk lalacewanta uwace a gareshi, kuma dole zai so ki dinga girmamata duk da masifan da take miki, kuma idan kinje kina nuna haƙuri da halayenta, tunda Allah ya haɗa aure tsakaninki da ɗanta".

Ta faɗa tana ɗaukan jakan kayana, da sauri na saka hannu zan karɓa, sai ta harareni tayi gaba,

Ina ɗan murmushi na bi bayanta, lokacin tana cewa naje nayi sallama wa Baba.

A parlon shi har ƙasa na sunkuya na gaisheshi, fuskan shi ɗauke da fara'a yake amsa mun, sannan ya ɗauki bunch ɗin ƴan two two hundred ya miƙo mun, yana cewa nayi tsaraba wa mutanen kano.

Kaman bazan karɓa ba sai ya hau ni da faɗa, dole na saka hannu na karɓa ina mishi godiya.

Har waje Aunty ta rako ni, inda Khalifah ya ke saka kayan Hammah a boot ɗin motan shi, ganin kayan hannun Aunty yasa ka shi tahowa ya karɓa ya saka a boot ɗin, daga nan nayiwa Aunty sallama na wuce side ɗin Mama.

Sallama nayi har abakin ƙofan parlon ta amma shiru babu kowa, kawai sai na wuce har ɗakinta inda nakejin muryansu, sallaman na sakeyi amma babu wanda ya amsa mun, sai daga baya naji muryan Hammah na yana cewa, "shigo mana Fatima".

Shiga nayi bakina ɗauke da wani sallaman, amma hararan Mama kawai na fara cin karo da shi, har ƙasa na sunkuya na gaisheta, cikin tsawa da masifa tace, "yau kuma sabon salon munafurci ne kika fito da shi? don naga ban taɓa samun darajan zuwa ki gaisheni ba sai yau agaban wanda ni nan na haifeshi har kuka samu na gadara da yangan an samu mai maiƙo", ta faɗa kaman ta zabga mun mari.

Da sauri na sunkuyar da kaina ƙasa, dai-dai kuma Zainab taja wani tsaki tana ya mutsa fuska tana cewa, "ni wallahi duk rayuwata bana son haɗa wurin zama da talaka wallahi" tana faɗa tana bina da kallon ƙasƙanci.

Juyowa nayi ina gaisheta gudun kar ace ban gaishetaba, amma sai tsaki taja mun, inda Mama kuma ta karɓe da, "ni narasa irin wannan baƙin maitan naki mai baƙar fuska? Sai kace an ce dole muna buƙatan gaisuwan ki"? Ta faɗa tana hararan inda nake zaune.

Hammah ne ya tashi daga bakin gadon daya ke zaune kusa da Zainab, hannunshi riƙe dana Nabeel yace, "jeka gaida small mum ɗinka ko my boy" ya faɗa yana turo mun Nabeel da tunda na shigo yake ta bina da murmushi, wanda gaba ɗaya fuskan yaron kaman na Besty na nake gani, domin gaba ɗaya fara'ar Besty irin na yaron ne.

Da sauri yazo gaba na, ni kuma nasaka hannuna duka biyu na riƙe shi, yana gaisheni Mama ta saka hannu ta jawo shi ta miƙa shi wa maman shi tana cewa,  "ke riƙe abinki kada bakisan me ake niyyan yiwa ɗanki ba a cutar da shi".

Hammah ne naga fuskan shi ɗaukeda wani irin muushi kaman wanda akace dole sai yayi, ya dubi Mama yace.

"Mama amana addu'a mukan zamu wuce yanzu".

Tana kallonshi shiƙeƙe tace, "wucewa kai da wakuma"?

Hannunshi cikin aljihunshi yana kallon Mama yace, "nida Fatima, zan ajiyeta a kano zasuyi suna gobe".

"amma baka da kan gado Hammansu, kaida kasaka tafiya mai muhimmanci agaban ka, meye na bibiyar mace? Bayan idan ma tafiyan kake so amaka rakiya ga matar ka na gaban mota fara wacce zaka nunata agaban kowa ba irin wannan baƙar fuskar ba? Sai dai kawai idan asirinsu ne ya fara kamaka, shi kuma saidai nace Allah ya isa tsakanina da Fatima", ta faɗa sai wani haki takeyi kaman wanda tayi tsere.

"Mama addu'an ki kawai nake buƙata ba wasu maganan ganu ba, kika san ko zan dawo na sameki? Ko ma bazan dawo ba ballantana ma nayi zama da wacce baki so? Mama duk wannan abun bai kamata kina yawan daga hankalin ki ba, ko mutuwan ɗan'uwa na ya isheki ki dinga haƙuri da abinda Allah ya kawo".

Jikin Mama a sanyaye lokaci guda ta ƙurawa Hammah ido, shi kuma ya matso yamata kiss a goshinta ,sannan ya fita a ɗakin, yana fita Zainab ta bi bayan shi hannunta riƙe dana Nabeel, ganim haka yasa na koma na zauna.

Har zuwa wani lokaci naji ya ƙirani a waya akan na fito, juyawa nayi na kalli mama nace, "Mama sai mundawo", tana bina da harara tace, "toh baƙar jaraba wanda tasha a nono, sai a kula kada alashe mun kurwan ɗana", da sauri na fice a ɗakin, a parlo kuma nayi arba da Hammah rungume da Zainab sai kuka take ta mishi ajikin shi.

Zuwa nayi na tsaya ajikin motan, zuciyata sai tafasa take mun akan abinda Mama ta mun, ban wani daɗe ba sai gashi ya fito rungume da ita sai kuka take takan yi mishi.

Buɗe mun ƙofan motan yayi na shiga na zauna fuskana a ɗaure kaman naga mala'ikan na ɗaukan rai, da ƙyar ya ɓanɓareta ya shiga motan bayan ya ɗaga Nabeel yayi ta kissing fuskan yaro, shi kuma sai murmushi yake ta yi wa Babanshin.

Motan shima ya buɗe yaja muka fita daga gate ɗin, ina ganin mun fita bansan lokacin dana ajiye wani kyakkyawan ajiyan zuciya ba, wanda ban shiryawa fitowan shi ba, da sauri ya juya ya kalleni, nayi saurin sunkuyar da kaina a ƙasa.

Baice mun komai ba har muka fita wajen gari, muna kama hanyan kano ya juyo ya dubeni, sannan ya maida hankalinshi kan hanya.

A hankali yace, "don Allah ga amanan Nabeel ɗanki, ina so ki kula mun da shi da tarbiyanshi, da kuma cin abincin shi da karatun shi, don nasan mummyn shi kam bata da time ɗinshi, sannan kuma ina so kullum kishiga ki gaida Mama koda zata na zagin kine, wannnan yazama kaman nine nake sauƙe nauyin da yake kaina, kuma kiyi haƙuri da Mama saboda sanin halinta kinji?"

Ɗago kaina nayi na dube shi, sannan na maida kaina ƙasa, shi kuma ya cigaba da driving ɗinshi, duk yadda naso dauriya zuwa wani lokaci kasawa nayi, kawai sai na fara kuka ina juya jikina kaman tarwaɗa , saboda ciwon da marana yakeyi.

A hankali ya ɗan tsagaita tafiyan, yasaka hannu ya riƙoni yana, "ku dai bazaki iya tafiyan ba"? Ina ɗan juya kaina nace ,"muje Hammah zai daina" na faɗa ina kan share hawaye.

Muna shiga kano naga ya ɗauki wayanshi ya ƙira Hammah Haidar, suna gama magana ya ɗauki hanyan gidan Hamman da ya turo mishi address, nidai sai juyi na nake tayi, lokaci lokaci yake riƙo hannuna ya sake ya cigaba da tuƙinshi, har muka isa cikin compound ɗinsu wanda yake ɗauke da gidaje guda goma Duk sama da ƙasa.

Muna packing Feenah ta fito da gudu jikinta sake sda hijab har kasa, muna tsaryawa ta buɗe gaban motan ta rungumeni tana "oyoyo my Aminiya"!

Shi kuma Hammah Haidar yana tsaye a bayanta, bayan yaga Hammah na ya gyara packing motan ya ƙarisa wurinshi, mu kuma har mun shigo cikin gidan, wanda yake ɗauke da three bedroom, ɗaya a cikin parlo da toilet ɗinshi, biyu kuma idan kin wuce parlon zakibi wani corrido mai kyau zaki ga ɗakunan guda biyu, ɗaya na kallon ɗaya, kowanne da toilet ɗinssi, sai kitchen da store da yake gefe, gaskiya gidan yayi kyau sai ƙamshi yakeyi kaman ba yau tadawo ba, duk wurin a gyare.

Muna shiga ɗakin na ajiye handbag ɗina, jakana da yake hannun Feenah na karɓa na buɗe na ɗauki towel da soson wanka da pad da pant na wuce toilet, ina shigewa ita kuma ta fita.

Wanka nayi fess na ɗauro towel na fito,wani material mai laushi na ɗauko na saka mai ruwan ja da fari, sannan na ɗauki miski da wasu turarukan na shafa a jikina, hattah gashin kaina ban bar shiba, saboda gaskiya ni idan ina period su nake aji ƙamshi ajikina bawai kishiyar hakan ba.

Ina gamawa Feenah ta shigo, zare ido tayi tana kallona, sannan tace, "gaskiya aminiya kina wuta irin wannan ƙamshin ae sai ki hana shi tafiya yau".

Dariya nayi nace, "ke kuma yaushe kika iso har kikai gyaran gida kikayi girki," don ganinta ɗauke da coolern abinci ta ajiye mu.

Dariya tayi tace, "nifa matar likitane, kinsan su kuma da tsafta, toh shi kullum sai ya gyara gidan. Abinci kuma daga gidan Adda Hafsat akayi damu, tunda tasan yau zamu dawo har gidan Adda Hummy, kuma tasan da zuwan gwarzon ki" ta faɗa tana zama akan kujeran dressing mirrow.

Kallonta nayi nace, "toh kizo muci tare" sauƙa tayi mukaci wanda kaɗan naci na tashi nasha magani, sannan naje na wanko bakina na kwanta.

Bamu daɗe ba Hammah Haidar yayi sallama ya shigo, da sauri na tashi na gaishe shi, sannan yace naa fito na taya Hammah na zama shi zai koma office.

Bai daɗe da fita ba na tashi zan tafi wurin Hammah, da sauri Feenah ta miƙo mun humrah tace "Aminyyata ga wannan ki shafa saboda gudun jin ƙarnin jini".

Karɓa nayi na shafa a tsakan kanin cunyoyina, sannan na shafa a ƙasan brest ɗina na miƙo mata na wuce.

A parlo na same shi, ganin na shigo ya miƙe ya riƙo hannuna muka shiga ɗakin dana gani a cikin parlon.

Muna shiga ya tura kofan ya rufe sannan ya tsaya ta bayana, ya sako hannun shi ya rungumeni ta bayana ,hannun shi yana rungume da shi a ƙirjina, sannan ya ɗaura kanshi akan wuyana, yana ta shanshanani.

A hankali yake ta zagaye hannun shi a cikin jikina, wanda hakan ya sani ƙoƙarin ƙwacewa, da sauri ya kara matseni a jikin shi, daidai saitin kunnena yace, "kada kimun gardama Baby nerh"! Kikasan ko bazan dawi ba?"

 sannan  ya sakaɓhannun shi akan mara na yana matsawa a hankali, muya ƙasa ƙasa yana cwwa, "gashi wannan baƙon da ba a son baƙuntan shi yazo" ya faɗa yana shafa mun saman marana, wanda lokaci ɗaya naji wani yarrr ajikina, da sauri na maida jikina a jikin shi.

Juyo dani yayi a hankali yasaka bakin whi cikin nawa yana kissing ɗina mai zafin gaske cikin gaggawa, duk jikin mu rawa yakeyi daga ni har shi, lokaci guda yajani kan gadon cikin sauri yana ta nishi kaman zai sume ajikina.

Rigan jikina kawai naga ya kama ya cire cikin nishi mai ɗan karfi, sannan ya tashi da sauri ya cire kayan jikin shi, ya dawo ya jawoni ya kara matseni a jikin shi, sai nishi yakeyi.

Riƙo shi nayi ban shirya hakan ba saboda wani irin daɗi da nakeji har tsakan kaina sai Nishi nakeyi shima yanayi, har ina tsoron kada Feenah ta jiyo mu..ido na duk a rufe sai nishu nakeyi.

Niko ganin haka nace bari na koma wurin Feena muyi ta gulman wannan masu nishi kaman zakunan, ga tafiya ga jaraba ga kuma baƙo ya zo..

#Vote
Comment
Share
Follow.

*KU KASANCE DA ALƘALAMIM AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*
*1441H/2020M.*

®☄
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION✍*
_{Gaskiya ɗaya ce daga kinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira.}_

🎐G•W•A🎐
_*GASKIYA DOKIN ƘARFE•* 🏇_

Story and written
By
*AUNTY NICE*

*_WANNAN BOOK SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Wattpad@GaskiyaWritersAsso.~

*page* 69---70

*___________*📖Ganin irin birkicewan da Hammah na yayi, yasa na fara jin tsoro, don gani nakeyi ya gama mantawa ma da ina period ne.

Ƙokarin ƙwace kaina na fara, ganin yadda yake tatse mun nono kaman zai ɓalle su a jikina, hannun shi naji ya na ƙoƙarin kai shi kan pant ɗina, rike shi nayi ina "Hammah mara na yana ciwo, Hammah kamanta ina period?kada ka cire mun pant, zamu ɓata musu gadon su", na faɗa kaman zanyi kuka.

Lokaci ɗaya ya ɗaga hannun shi akan pant ɗin, cikin sauri-sauri ya maida duka hannayen shi kan breast ɗina, bakin shi yana cikin nawa yana sauke mana kiss kaman zai cire mun baki na.

Ban san lokacin da naji bakina yana ta ambatan sunan shi ba, sai faɗin "Hammah nah! Hammah nah!! Kawai nakeyi ina juya kaina ko wani gefe cikin dauriyan kada nayi magana da ƙarfi.

Da ƙarfi naji shi ya matseni,  naji muryan shi da ƙarfi yace, "ohhhh....my....god....hold me plzzzz".

Can kuma naji ya maida kanshi kan ƙirji na ya kwanta yana ta sauƙe ajiyan zuciya da sauri-sauri, jin ya bar daduƙana ya sa na buɗe ido na ina kallon fuskan shi, gaba nane ya faɗi dana ga fuskan Hammah na yayi wani ja, ga kuma hawaye da ya zuba a kan fuskan shi.

Da sauri na saka yatsa na ina share mishi hawayen da ya zubu mishi, a hankali ya buɗe idon shi ya ƙura mun su, ƙura mishi ido nayi shima ya ƙura mun, can sai nace, "Hammah yaushe zaka dawo"?

Ajiyan zuciya yayi, ya juya ya bar kaina sannan ya saka hannun shi yana ƙoƙarin maidani kanshi.

"Wayyo Hammah nah kabarni duk jikina ya ɓaci" na faɗa ina ƙara haɗa ƙafafuna waje ɗaya, don jin yadda yake zubumun babu ƙaƙƙautawa.

Dariya yayi yace, "ni ae wannan yayi mun rashin adalci da yaxo a wannan lokacin".

Kallon shi nayi nace, "Hammah yayah zanyi na tashi? Ina tashi zubowa zai yi".

Tashi yayi ya ɗaga ni cakk har cikin toilet yace, "baby gyara jikinki idan yaso kije ɗakin ki ɗauka wani pad ɗin kizo".

Fita yayi ya barni, wanka nayi da ruwan ɗumi don duk jikina naga ya ɓaci, ina gamawa na fito na wuce ɗakin Feenah.

Ina shiga na samu tana waya da su Adda Hummy, da sauri na ɗauki leda pad da wani pant ɗin na shiga toilet, ina fitowa ta kalleni tana dariyan shaƙiyanci.

Hararanta nayi nace, "meye kike wani dariya"?   Dariyan tayi da ɗan ƙarfi tace, "nikan yanzu kinji nace wani abu ne? Kawai me kike so a dafa muku for dinner"?

"Duk abinda kike so" nace mata sannan na nemi bakin gadon na zauna na cire rigana, sai ya mutsa fuska nakeyi yadda naji breast ɗina sai zafi sukeyi.

Dariya Feenah tayi ta tashi taje ta buɗe walldrove ɗinta tanata dariya, ɗauko wani wando da riga tayi masu kyau, three quater ne da riga half-vest, wasu masu kyau pink da popule a jiki.

Miƙo mun tayi tace, "Kawata ki cire bra ɗin kawai ki huta, ga wannan kayan suna da kyau, tsaraba aka kawo mun, ki saka ko babu bra zakiji daɗin kayan" ta faɗa tana dariyan shaƙiyanci.

Hararanta nayi nace, "in banda ke da gulma me kike tunanin zai mun? Bayan kinsan abinda nakeyi"?

Miƙo mun kayan tayi tana, "ni kinji nace wani abu ne? Kawai don na sama miki mafita zaki ce mun waji waye waye".

Karɓa nayi ban saka ba na koma na kwanta, ina runtse ido na, can a hankali nace, "marana yana mun ciwo Feenah nah, kaman nayita ihu wallahi".

"yanzu dai tashi kije wurin mijinki, nima kiitchen zan shiga ina sallan la'asar, kinga yau zai tafi gara kije ki kafa kanki sosai a zuciyr shi".

tashi nayi ta miƙo mun wannan humran ɗazun, karɓa nayi na shafa a jikina, sannan na ɗauki katan na saka.

"masha Allah, wannan kuwa yau zai iya tafiyan nan kuwa Besty nah"? Ta faɗa tana rike haɓan

ta.

gaban mirrow naje na tsaya, nima gaskiya sai da naji gaba na ya faɗi saboda irin kyaun da nayi kaman wata gold nake ganin kaina, dariya nayi kaɗan sannan na dauki hijab ɗinta mai zuwa har kasa na saka.

Fita nayi ban kula abinda ta ke cewa akan ina shiga wai na cire wannan hijab ɗin don Allah.

Ina shiga shi kuma yana fitowa daga toilet, daga gani wanka yayi ya fito, kallona yayi yace, "bari nayi sallan la'asar ko madam".

Sallaya ya shimfiɗa ya tada sallah, ina jiran shi har ya idar da sallan ya zauna ya daɗe yana addu'o'i.

Yana tashi yazo kusa dani ya zauna, hannu ya saka ya fara cire mun hijab ɗin yana faɗin, "wannan ae ya miki nauyi baby nah" ganin zai cire ya sakani tashi nace, "bari na cire Hammah nah".

Wurin da ya ajiye sallayan naje na tsaya na cire hijab ɗin, sannan na naɗe na ajiye a wurin, ina juyowa naga Hammah ya wani kafe ni da ido.

Kallin shi nayi ina murmushi, kawai sai ji nayi na samu kaina da juya mishi kaina ta kowa ne side, ina jijjiga mishi jikina.

Buɗe mun hannunshi yayi alaman na taho, da sauri na ƙarasa na ɗale kan cinyan shi ina murmushi, kanshi ya saka a wuyana yana ta lashe wuyan da harshen shi, cikin muryan shagwaɓa nace,

"Hammah don Allah ka tafi dani" ɗago kanshi yayi da sauri yana , " baby ba a zuwa da mata, kuma idan na tafi dake ae babu abinda zan iya saidai abokanen gaba ma su harbeni bansan inda kaina yake ba, Allah baby kina rikita Hammanki sosai".

Hannu na saka na ɗago fuskan shi, duk tafukan hannu na suna riƙe da fuskan shi, ƙura mun ido yayi hannun shi suna rungume da ni ta bayana, cikin muryan kaman wanda zaiyi kuka nace.

"Hammah toh ni bazan ji daɗi ba idan baka nan, kuma...." sai nayi shiru naƙi ƙarasa faɗin abinda zance.

Matso da fuskan shi yayi kusa da nawa, murya ciki-ciki yace, "baby me kike so kice? Don Allah

kada ki ɓoye mun me kije son faɗin".

Lumshe ido na nayi sannan nace, "Hammah bana so ka tafi ka barni ne, kuma bansan yaushe zaka dawo ba"? Na faɗa ina kumar da kaina saman kanshi nayi shiru, shi kuma fuskan shi yana kwance akan chest ɗina.

Hannun shi yasa ya matseni sosai sannan yace, "kimun addu'a baby nah, inaga idan Allah ya yarda ba zamu wuce six month ba" ya faɗa yana maida bakinshi cikin nawa.

Jan ƙofan nayi na kuma kitchen ina ganin yadda Feenah take ta aikin abincin dare, ba wani abu mai wuya tayi ba, faten doya ne tayi sai naga tana gasa kifi, gefe ɗaya kuma tana ta aikin waya da maijego.

Da ƙyar Hammah ya iya barin jikina ya shiga toilet yayi wanka, ina ganin ya tada sallah na tashi na shiga toilet domin na canja pad ɗin jikina, tunda yace kada na tafi na barshi, yana kan sallayan har aka ƙira sallan ishaa, ya miƙe yayi ina ganin shi ya maida shafa'i da wutiri.

Gaban gadon ya dawo ya durƙusa, yaja hannu na ya riƙe gam-gam, sannan yace, "Baby na baki amanan kanki, dana ɗa na, sannan ban yadda da yawo ba kinji princess! Zuwa school kuma nayi cancelling kwana acan, don munyi magana da Hammanku yace itama Nafeesan a gidan su  akwai side ɗinshi toh anan zata zauna, zai na zuwa mata weƙend, ita kuma idan anyi hutu sai ta taho kano gidanta".

Turo bakina nayi gaba nace, "Hammah toh aini ban tare ba, kuma bakaga kullum a gidanku nake zaune ba? Nima zan dinga zuwa gidanmu ina kwana" na faɗa ina juya kaina gefe dan kunyan mu haɗa ido nakeyi.

Ƙara matse hannuna yayi yace, "gidan mu ae ko babu aure na akanki ae gidanku ne, ballantana yanzu igiyoyina har uku akanki, saboda haka ki kiyaye,na barki kina zuwa a weƙend shima ba kullum ba, don ina so ki maida hankali a karatunki, da kuma kula da ɗanki, ko kin mata da kula da Nabeel ne"? Ya faɗa yana ɗan buɗe mun idon shi kaɗan.

Ɗagowa nayi na ƙura mishi ido, shikuma ya tashi ya jawo jakanshi ya buɗe ya miƙo mun ATM Card ɗinshi na first bank, karɓa nayi ina kallonshi da alaman tambaya.

Sake kama hannuna yayi ya riƙe yace, "wannan every month zakiji shigan alert nawa na salary , duk wani abu da zaku buƙata ke da Nabeel ki muku a ciki, sannan ga wannan motan da mukazo dashi zaki koma saboda kina zuwa school da shi, amma bana son yawo da gangancin

tuƙi".

"Hammah ae ban iya tuƙa mota ba, sannan kuma idan na riƙe ATM ɗinka ae Mama zatayi faɗa, kawai kabawa Aunty Zainab", na faɗa hankalina a matuƙar tashe don sanin irin abinda Mama zata mun idan ta san yana wurina.

"Da sanin Baba na baki, kuma babu ta inda Mama zataji idan bake kika gaya mata ba, dama a hannun Baba yake, shi yaga dacewan na bakin shiyasa aka baki, sannan maganan Zainab babu ruwanki nasan da ita ae na bakin, kuma Baban ma yasan da ita, kawai kiyi abinda na saka ki, Kuma plz ki kula mun da kanki, mota kuma Baba yace zai saka akoya miki".

Hawaye naji suna zuba mun a idona, kawai sai na rungume shi da ƙarfi ajikina ina kuka, murya na rawa nace, "Hammah na kada kadaɗe don Allah kadawo da wuri, baxan iya zama babu kai naji daɗi ba" na faɗa duk jikina da muryana suna rawa.

Allah sarki soja kasa cewa komai yayi kawai shima sai ya rungumeni a jikinshi yana ta goga kanshi a fuskana,........ ƙara wayan da aka munne ya maido mu cikin hayyacin mu wanda muka kusan komawa makarantar su Rukkyn Generation.

Ɗauka nayi na kara a kunne na bance komai ba, ganin sunan Feenah dake yawo akan screen ɗin.

Daga ɗayan gefen naji tace,  "hello Besty ki fito kibar mutumin nan yayi dinner, ga Hammanki ma ya daɗe da dawowa", kashe wayan nayi na juya ina kallonshi.

Fitowa mukayi har parlon domin muyi dinner, anan na sake gaida Hammah Haidar, amma nakasa zama a parlon ɗakin Feenah na wuce, ganin bazan dawo ba yasa ta bini da abincin domin muci acan, amma firr naƙi cin komai, har saida Hammah ya ƙira ya mun magana tukun na zuba kifin naci.

Jirgin su Hammah 12:00 zai tashi, tun wurin 10:00 muka fito domin tafiya airpot, tun daga ɗakin na rungume Hammah ina kuka, babu abinda ya iya na rarrashina sai chiza lips ɗinshi da yakeyi, ga ya wani takura idon shi da naman goshinshi, har parlo muka fito yana rungume dani a gefen shi, ɗayan hannunshi kuma yana rataƴe da jakan shi, jikin shi sanye da wandon su na sojoji, rigan kuma wata green t.shet ya saka sai wani shegen boot a ƙafan shi, kanshi ɗauke da hulan kayan su.

Kuma haƙuri nikan na gajji, sai gobe friday insha Allahu.

#Vote
Comment
Share
Follow.

*DAGA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*
*1441H/2020M.*

®☄
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION✍*
_{Gaskiya ɗaya ce daga kinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira.}_

🎐G•W•A🎐
_*GASKIYA DOKIN ƘARFE•* 🏇_

Story and written
By
*AUNTY NICE*

*_WANNAN BOOK SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Wattpad@GaskiyaWritersAsso.~

*page* 71----72

*___________*📖Hammah Haidar yana kallon mun fito ya miƙe tsaye fuskan shi ɗauke da murmushi yana faɗin, "kaga soja mazan fama, marmari daga nesa".

Shima Hamman murmushi yayi yana gyara zaman jakan shi a kafaɗan shi, ɗayan hannun shi kuma rungume da ni.

Hammah Haidar ne ya ɗauki key ɗin motan shi yana cemum, "ke kuma wani irin sakarci ne? Kin sashi a gaba sai kuka kike mishi bazaki riƙe mishi jakan ba, haka ake bankwanan"?

"Gaskiya Haidar idan ba rarrashinta zaka dinga yiba, gara ka gayamun na kaita inda za a kula da ita kafin na bar garin nan, ina kai ga taka a gefenka baku da damuwan komai, ita kuma fah"? Ya faɗa yana jawo ni jikinshi.

Ƙara sautin kuka na nayi ina ƙara shigewa jikin Hammah ina faɗin, "nidai Hammah zan bika".

Hararan wasa Hammah Haidar yayi mana, yana dariya yayi hanyar waje yana "toh ae sai ka haƙura da tafiyan, don na lura aikin kula da Riyyah yafi maka aikin kula da ɗaruruwan rayukan bayin Allah dayawa", ya faɗa bayan ya ƙarisa fita a parlon.

Juyawa Hammah yayi gefen da Feenah take yace, "Aminiya don Allah kada kibiyewa mijinki kuyita saka mum baby na kuka,kinga rabuwa da miji wanda baka san zai dawo ko bazai dawo ba tashin hankali, ki kwantar mata da hankali kafin ku koma school".

Fita mukayi dukkan mu a parlon, bayan Feenah ta rufe ƙofan gidan muka ƙarasa inda motan yake, baya Hammah ya buɗe muka shiga still yana rungume da ni a jikinshi, ita kuma feenah gaba ta shiga kusa da mijinta.

Har muka isa airpot ina manne da Hammah nah, saida naji Hammah yana gaisawa da wasu sojoji tukun na ɗago a jikin shi, dukkansu gaiswa mukayi tukun na koma gefen Feenah na zauna, babu abinda takeyi sai aikin bani haƙuri.

Ana fara sanarwar tashin su Hammah naji gaba nah ya faɗi, da sauri na ɗago ido na ina duban direction ɗin da yake, shi da wasu abokanan tafiyan shi ne suke magana, gefe ɗaya kuma Hammah ne ke tsaye a gefen shi.

Shima Hamman yana fara jin announcement ɗin tashin su, yayi sauri ya dubi inda nake, ina kallonshi na kwaɓe bakina alaman zanyi kukan, sauri yayi yana juya kanshi gefe da gefe alaman nayi haƙuri, da sauri na sunkuyar da kaina ƙasa.

Hannu ya miƙawa Hammah Haidar suna sallama, sannan ya matso inda muke yana cewa Feenah, "toh aminiya mukan munyi niyyah sai atayamu da addu'a".

Da sauri na ɗago ina dubanshi amma baice mun komai ba sai kallona da yakeyi, ganin juyawa zaiyi ya tafi, yasakani tashi da sauri na faɗa ta bayan shi na rungume shi ina fashewa da kuka, hannu ya saka ya ɗaura akan nawa hannun da yake riƙe da shi ta kan ƙirjinshi, kaina nake ta juyawa a bayanshi, da ƙyar na buɗe bakina nace.

"Hammah nah! Hammah nah!!" sai nasake saka kuka, sai da Hammah Haidar yacewa Feenah taje ta riƙoni.

Da ƙyar ta ɓanɓareni ajikinshi, ko juyowa baiyi ba ya wuce ya bi abokan tafiyan shi, gefe ɗaya ma wata ce ke ta kuka hannunta riƙe da wani jariri da baifi wata shidah ba, wata ƴar budurwa da wani saurayi suna ta bata haƙuri, saurayin yana cemata "addu'a kawai zaki mishi Allah yasa su dawo lafiya".

Har saida mukaji tafiyan su Hammah tukun muka koma mota muka wuce gida, tun ahanya Hammah Haidar na yake ta bani haƙuri da misalai dayawa na rayuwa, sanan yake nuna mun addu'a kawai Hammah yake buƙata bawai kukan mu ba, a haka muka iso gida.

Ɗakin kawai na faɗa ko kayana ban cire ba na faɗa kan gado ina ta kuka, babu irin rarrashin da Feenah bata mun ba amma ko kula ta kanta ban yiba, ganin ina ɓata mata lokaci ta tashi ta shige toilet ta sillo wankanta ta fito ɗakin, har lokacin ina kuka.

Mirrow taje ta gama shirinta ta ɗauko wani nighty mai kyau ta saka ajikinta, sannan ta ɗauko wannan humran data bani na shafah, tana shafawa ina jinta tana munafukin dariya tana fewa.

"wannan an shu'umar Humrah, yarinya da gangan na baki kika shafah don kije a rikita munke da soyayyah, don ma kinci sa'an jini ya ɓullo miki, da wallahi da da guzurin kano  za'a barki ajikinki, toh amma duk da haka nasan wanka ya biya kuɗin sabolu, yadda aka ritsaki a ɗaki wuni guda ana ta miki lugude don ki ƙara haɓaka kibar jerin jarirai".

Maganan tane yasaka ni miƙewa na zauna ina kallunta baki a buɗe, dariya ta sakeyi tace.

"kada kidamu na saka aje a nemo miki, zan tana da miki har sai angon jaririya ya dawo, zan ɗana mishi tarko, nima yanzu bari naje na rikita Hammah nah, kema ki shafaki rikita pillow da katifa" ta faɗa tana kashe ido ɗaya tana wani rawan shaƙiyanci ta fita tana faɗin "na tafi aikin lada".

Tsaki naja na wuce toilet, ruwa mai zafin gaske nayi wanka dashi, ina fitowa na ɗauki miski da oil na muƙallaf badar na shafa na saka wando da riga na bacci na kwanta.

Duk yadda naso nayi bacci abun ya faskara, har sai wurin 2:35 na samu ya ɗauke ni, wajen ƙarfe bakwai Feenah ta tasheni, wanka mukayi kowa ta saka dogon riga muka tafi gidan Adda, inda Hammah ya ajiye mu.

Muna shiga Adda Hafsat ta harare mu tana, "baby yayi fushi daku, don yakamata tunda jiya soyayyah ya hanaku zuwa? Kamata yayi yau tun sallan asuba ku iso amma shiru sai yanzu". Adda Hummy dake shigowa ɗakin ta amsa da faɗin, "ke Hafsisi kada ki takura mana ƴan auta, yayah za'ayi subar aikin lada da neman albarka suzo aikin ƙarfi? Ina laifin zuwan su yanzu ma" ta faɗa tana rungumeni ta baya.

Nima rungumeta nayi ina faɗin, "wayyo my cwit Adda Hmmy, gaskiya yanzu ke uwace bama yaya ba, Adda Hummy gaya mata dai mun zauna...." sai kuma na rufe fuska ina dariya.

Suma gaba ɗaya dariya suka saka harda Adda Hafsat ɗin, sannan Feenah tace, "hmmm Adda jiya ae naga ayu da matar shi muraran a  gida na," ta faɗa tana riƙe haɓanta.

Adda Hummy ta harareta da wasa tace, "toh faɗi ba a tambayekiba, kada ki yadda ki takura mun baby nah, ki barta tasha shagalinta ,ina yanzu ya tafi sai kuma ranan da Allah ya dawo da shi"? Ta faɗa tana neman bakin gado tana zama, hannu ta takai ta ɗauki babayn tana cewa.

"Riyyah ta zo kiga ɗankin",  da sauri na ƙarisa na ɗauke shi ina faɗin "masha Allah dubi yaro da gulma, sak Yayah Kamal ya ɗauka, har ɗan dogon hanci da manyan idon", na faɗa ina ta shafa fuskan boy ɗin.

Feenah ce ta dawo gefe na ta zauna dai-dai kunne na tace, "Besty nikan inaga Hammanki yayi mun wayo, don ajikina inajin abinda zamu haifa shi zai ɗauko, don yafini ƙoƙari a gado".

Buɗe baki nayi ina kallonta, nima a hankalin nace, "ke wani gulman ne yake hanaki ƙoƙarin"? .....wani shafan cikinta tayi na gulma tace, "ina fa ƙoƙari, kawai idan yamun sucking tsabar miƙa kai da suman daɗi sai na hau ihu har sai naji shi a rijiyar burtsa bana iya taɓuka komai, amma zan daure don na haifi mai basiran ɗaukan lectures irin na Abban shi".

Maka mata duka nayi nace, "tashi agefena rasai, ni wallahi Hammah Haidar ya cice ni da ya ɓata mun ke", na faɗa ina turata gefe.

Adda Hafsat ce ta matso tana "kuban ɗana, kafin haukan ku yasa ku kayar dashi, don ni ban manta da ɗakin bone ba", ta faɗa tana ɗauke ɗanta.

Ina dariya na miƙa mata wani leda nace mata "nawa dana Hammah nane," kayan da muka saya

irin na Adda Umaima idan baku mantaba,  sannan na miƙa mata ɗayan nace, "zannuwan ciki guda biyu da riga guda uku na Aunty ce, sai ɗayan ledan akwai lace da riga guda biyu shi kuma na Ummi nane, ɗayan kuma turmin zani ne riga guda biyu da pampers shikuma na Goggo ne.

Kaya masu kyaun gaske, sai murna take tayi, kowa sai saka albarka yakeyi, dai-dai nan motan ƴan bauchi da alƙaleri suka iso, Adda Hummy ce ta fita da saurinta don taro su, mu kuma muka cigaba da tattare kayan da muka baza a kan gadon.

Yauma dai kuyi haƙuri, Zan tafi cin kasuwa ne, yau kasuwan garin mune, kada ayi babu ki

#Vote
Comment
Share
Follow.

*KU KASANCE DA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*
*1441H/2020M.*

®✍
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION✍*
_{Gaskiya ɗaya ce daga kinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira.}_

🎐G•W•A🎐
_*GASKIYA DOKIN ƘARFE•* 🏇_

Story and written

By
*AUNTY NICE*

*_WANNAN BOOK SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Wattpad@GaskiyaWritersAsso.~

*page*  73---74

*___________*📖Zuwa sallan magarib gidan suna ya fara sauƙi da mutane, in banda ƴan bauchi da su mu babu kowa, sai ƴan tsiraru daga dangin mijinta ne kaɗai suke nan.

Wajen ƙarfe 9:00 pm, Hammah Haidar yazo ɗaukanmu, har parlor Feenah ta shigo da shi, sannan ta kawo mishi babyn da yaci sunan *MUHAMMAD*.

Bayan munyi sallama da masu jego ne muka wuce gidan su Hammah, hannu na riƙe da coolern da Feenah ta zubawa Hammah abinci.

Muna shiga nayi musu sallama na wuce ɗakin Feenah, wanka nayi nazo nayi addu'a na kwanta.

Kwanana biyu a gidan Hammah, yace Feenah ta kaini gidan su Adda na kwana, gidan Adda Hummy na fara zuwa na kwana ɗaya, ranan kam mun sha hira da Adda, inda tayi ta mun ƙarin bayanin yadda zan zauna lafiya da Maman su Hammah.

Bayanin yadda ya kasance tsakanin mu ranan da zamu taho nayiwa Adda, haka tayi ta bani shawaran yadda zanyi mu zauna lafiya da dukkansu.

Lokacin kwanciya ta tafi ta barmu da Ammar ɗinta, tare muka kwana da shi, washe gari bani nabar gidanta ba sai wajen 6:00pm, gidan Adda Hafsat ta kaini, itama kwana ɗaya nayi na koma gidan Hammah Haidar.

Tunda na koma na nemi kwanciyar hankali na narasa, saboda rashin wayan Hammah nah, sai

damun Feenah nakeyi akan ta tambayi Hammah akan ko sonyi waya ne da Hammah nah?.

Kullum kwantar mun da hankali na sukeyi akan zai ƙira, haka muka zauna har sati ɗaya ya cika, sannan muka fara shirin komawa, kasuwa muka shiga mukayi sayayyah.

Rannan saturday muka tashi da shirin tafiya bauchi, motan Hammah nah dashi muka taho bauchi, akan shi kuma sai ya biyo jirgi jirgi kawai ya dawo.

Muna isa bauchi kai tsaye gidan su Hammah Umar muka wuce, a parlon Aunty muka yada zango, kamar zata lashe mu don murna haka tayita haba-haba damu, ta kawo wannan ta kawo wancan, Kaman wanda nayi shekara bana nan haka tayita ja na ajikinta.

Har kusan magarib muka kai tare da Feenah, shi kuma  Hammah bayan yaje wurin Baba sunyi hira, Hammah ya bashi key ɗin motan wurin Hammah nah, amma Baba ya saka shi riƙe key ɗin a hannun shi, akan sai gobe idan zai tafi sai driver ya kai shi, idan yaso sai driver ya dawo da motan.

Bayan sun tafi ne, na fitowa da Aunty da tsaraban da nayi, tana farin ciki tace, "ki bari gobe sai ki miƙawa Mama da su Nabeel nasu, sai ki tafi dana ƴan gwallaga da nasu, yanzu sai ki kaiwa Baban ku nashi."

Muna sallan isha Baba ya shigo parlor, hijab ɗina na saka na fita parlon shi, har ƙasa na tsuguna na gaishe shi, yanata tambayana mutanen kano da mai jego, miƙo mishi leda mai ɗauke da wani yadi mai shegen kyau wanda a ƙallah ya kai 25k, sai kuma wani kwalban turare da yakai 12k na miƙa mishi.

Baba ya karɓa yanata saka mana albarka, har na fita a parlon albarka yake saka mun.

Washe gari da misalin ƙarfe 11:00am na fito cikin shirin zuwa gidanmu, bayan na ɗauki tsarabanne nayiwa Aunty sallama, muka fito ina riƙe da hannun Mujaheed, Aunty na ƙara jaddada mun kada na nuna ɓacin raina akan abinda Mama zatayi, sannan muyi sauri mu fito driver yana jiranmu.

Muna shiga parlon muka haɗu da Nabeel da yake break-fast, da gudu ya taho yana "oyoyoh mummy" ya rungume ni, Mujaheed yana kallonshi yana cewa, "Nabeel idan ana cin abinci ba'a tashi, jeka kaci mu unguwa zamuje".

Nabeel ya koma ya zauna yana ci yace, "Mummy nima zanci na biku unguwan",   ina zama a ƙasa dai-dai gefen tum-tum dake parlon nace, "toh yaroh nah" sannan na cewa Mujaheed yaje ya cewa Mama munzo gaisheta.

Hargagin masifan Mama na faraji yana cika wurin, kaman na fella da gudu nakeji, amma haka na gyara zamana har ta fito, da harara ta bini tace, "anya yarinyar nan baki maita kuwa? Ni ko ke kika gama da Baba na ne? Toh wallahi nikan nafi ƙarfin maitanki".

Ta tsaya tana kallona kaman ta mangareni, gaisheta  nayi kaman zan kwanta mata, sannan na miƙa mata ledan dana kawo mata tsaraban hijab gudu biyu da wani chiganvy mai kyau, da turare da kuma ƙaton robern turaren wuta, ɗayan ledan kuma wa Nabeel na cika da kayan sakawa har dana bacci.

Wafce ledan tayi tana cewa, "bsnso karɓa ba amma dole zan rabaki da shi, saboda nasan kuɗin ɗana aka samu ake dana sha da shi".

Zata juya ɗaki sai mukaji muryan Nabeel yana cewa, "Mama nima zan bisu inda za suje"........ Mama hararan shi tayi tace, "idan taje ta Lashe  ka fa?, babu inda zaka bisu".

"Mama ki barshi ya bisu, saboda nima na huta, bata isa ta lashe shiba", Zainab ta faɗa tana hararanah, da sauri Nabeel ya tashi akan abincin.

Zainab ta koma ta ɗauko mishi kayanshi da su kayan wankanshi, tana ya mutsa fuska tace mun, "ga kayan shi don baiyi wanka ba, kuma amishi a hankali kada kuma yayi wasa cikin kwata", tana faɗa ta juya ɗaki.

Muna juyawa mukayi  hanyan waje, har jikin motan mukaje inda driver yake jiranmu.

Gidan mu muka fara isa, mun samu Hammah Waleed da Hammah Sadiq duk suna nan, ranan ji nayi kaman zan sume don murna, ga Abba ranan shima kasa fita yayi, Ummi nama sai haɗa can da nan takeyi, don yau ji take babu ya ita, ruwan wanka ta saka taja Nabeel ta mishi, yana fitowa ta kawo mun shi na saka mishi kaya.

Tunda na fara saka mishi kaya yake ban labarin school ɗinsu, nidai sai mamaki yake bani ashe daman yaron yana magana, tsabar ta kura ne yake hanashi magana.

Tsarabarsu na fito da shi, komai cartoon Aunty ta sakani na saya musu, ga yadin wagan bari da takalmi dana sayawa Abba nah, Ummi kuma chiganvy ita da Aunty, Mama da Goggon bch da

Mumny na saya musu, kowa kuma da robern turaren wuta, turare kusan guda biyar na fito dasu nace, "Hammah gashi ku ɗauki naku".

Hammah Walid yana murmushi yace, "auta yau zamu fara cin moriyar ki da wuri, shiyasa akace da ja haifi gomna gara matar gomnan" guda biyu ya dauka tace shida Khalil, shima Hammah Sadiq yana ɗauka yace shida Hammah Bappah, sannan Abba yace, "ɗayan a kaiwa Baban bauchi."

Muna sallan Azahar muka shiga wurin Mummy, Allah sarki sai naji gidan gaba ɗaya babu daɗi, don ma ta samu wani yayanta ya bata kyautan ƴa, hira mukayi tayi har la'asar, bayan munyi sallah na bata tsarabanta muka mata sallama, har gidanmu ta rako mu tana ta jin daɗi.

Bamu muka bar gidanmu ba sai wajen karfe shida, gidan Goggo, Hammah Waleed ne yakaimu, saida mukayi ishaa tukun ya maida mu gidan Aunty.

haɗuwa mukayi akayita hira a parlon , har wajen 10:00 su Hammah suka tafi, muma sallama mukayi kowa ya wuce ɗakin baccin shi.

Ina cikin saka kaya naji wayata ta fara ringing, da sauri na ɗauko, amma abin mamaki sai ganin number Hammah nayi, da sauri na koma kan gado na zauna, sannan na saka hannu na ɗaga Ƙiran.

Don Allah kumun haƙuri da ƙarancin typing.

#Vote
Comment
Share
Follow.

*KU KASANCE DA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*
*1441H/2020M.*

®☄
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION✍*
_{Gaskiya ɗaya ce daga kinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira.}_

🎐G•W•A🎐
_*GASKIYA DOKIN ƘARFE•* 🏇_

Story and written
By
*AUNTY NICE*

*_WANNAN BOOK SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Wattpad@GaskiyaWritersAsso.~

*page* 75---76

*______________*📖Ina ɗauka na samu kaina da kasa cewa komai, shirun mun ne ya ɗan ɗauki lokaci, sai daga baya naji yace, "kodai na ajiye ne baki da buƙatan jin muryana"?

Girgiza mishi kaina nayi kaman yana gani nah, jin nayi shiru ya daka shi ajiyan zuciya a hankali sannan yace, "akwai wani matsalane kuma"?

Da ƙyar na buɗe bakina na gaishe shi, wanda gaba ɗaya muryana rawa yakeyi, sautin murmushin shi naji, daga baya naji muryan shi yana cewa.

"Naga alama bakiyi missing ɗina ba ko"? .......ajiyan zuciya na yi sannan na buɗe baki na da ƙyar, muryana yana rawa nace, "Hammah ka tafi ka barni, kuma banji yayah ka isa ba? Hankalina kullum yana tashe", na ƙarisa hawaye yana gangaro mun.

"Sorry ƴan mata naj, wallahi inda muka je babu network ne, yauma mun fito ɗaukan wasu ne shiyasa na samu sararin yi muku waya, kiyi haƙuri baby nah, kimun addu'a komai yazo ya wuce lpy".

Hira muka cigaba dayu kaman zan lashe shi nakeji, ga wani tausayin shi da nakeji, haka muka yi sallama yace duk ranan da ya samu sarari zai ƙira.

Ranan monday Hammah Sadiq ya fara fita dani koyan mota, hanyan yalwa mukaje, zuciyana cike da fargaba.

Abin mamaki ko rufa sati ba muyi ba na fara ƙwarewa da iya tuƙi, da shike motar Hamman auto ce.

Jama'a baku tambayeni yaya aka ƙare da ita ba akan ganin mota da tayi a wurina? Hmmm ranan da muka fara fita da motan, aiko muna dawowa mama ta shigo har side ɗin Aunty, lokacin Aunty tana office, ni kaɗai da masu aiki ta samu, inda take shiga bata nan take fita ba, sannnan ta saka hannu ta karɓi key ɗin motan tana ,

"ae ba mai baƙar fuskan nan bace ta tsuguna ta haifa mun ɗa, iya kaci ke mai baƙar fuskan ta tsuguna ta haifa, balle kumun gadara," ta juya ta tafi ta barni ina ta kuka a parlon.

Sai da akayi sallan ishaa Aunty taje ta samu Baba ranta a ɓace tace, "Baban su kamun aikin gafara kada abinda zan faɗa ya ɓata maka rai, gaskiya kaja kunnenn matar ka, don ban taɓa kawo maka ƙararta ba, amma yanzu kam na gajji, abu kaɗan sai ta kwaso ƙafanta ta zo har side ɗina ta zageni ta zage mun iyaye da ƴan'uwa? Toh gaskiya ka taka mata burki don daga yanzu bazan ɗauka ba", Aunty ta faɗa ranta a matuƙar ɓace.

Kallonta yayi cikin nutsuwa ya nuna mata wurin zama, bayan ta zauna ne yamiƙo mata ruwa a cup, babu yadda ta iya ta karɓa ta sha, sannan ya bita da murmushi, amma Aunty ko mayar mishi bata yiba saima murguɗa mishi baki da tayi.

Dariya yayi kaɗan yace, "gaskiya yau Zahra ta ƙware ni, haka kawai zata mayar mum da kyakkyawan fuskan kin nan wani iri? Amma babu komai Fati nah, ki ɗan yi murmushi ko zan fahimci abinda kike mun bayani".

Da sauri Aunty ta dube shi baki a buɗe tace, "kana nufin duk abinda na faɗa baka ji ba"?

Ɗaga mata kai yayi alaman baijiba, sannan yace, "ta ina zanji kin shigo mun da irin kaman da ban taɓa gani ba, ai tunani na fara yi ko dai anbani aure ne a wani wurin kika zo mun albishir", ya faɗa yana ƙureta da kallo.

Hararan shi tayi cikin wasa tace, "Wani auren kuma? Kai yanzu ko aure aka baka mai zakaci da ita? Nidai kawai kadaina faɗa bana jin daɗi".

Ta faɗa tana juyar da kanta gefe, dariya yayi sannan ya matsu kusa da ita yana, "mai ya faru tsakaninki da ƴar'uwar kin? Shin ba na ce kada ki biyeta ku zama mun abin ɗaya ba"?

Bayanin abinda ya faru ta mishi cikin nutsuwa, fuskan shi a ɗaure yace, "lallai matar nan bata da hankali ya faɗa a zuciyar shi, a fili kuma yace kiyi haƙuri wannan faɗan ae bada ke tayiba dani tayi, don ni tanuna banida mutunci, shigowa gefen ki kuma insha Allahu idan bana arziki bane ba zata sake shigo ba".

Sannan ya miƙe yayi wurin Mama,muna zaune da Aunty a parlon ta, ina mata kitso chiku, sai ga Baba ya shigo, miƙo mun key yayi sannan yace, na shiryah gobe naje nayi registration, har ƙasa na sunkuya na mishi godiya,sannan ya juya ya fita.

Washe gari monday da wuri Hammah Sadiq yazo ya ɗauke ni, sannan muka bi kan Feenah a gidan goggo, wacce take can side ɗin Hammah mai parlo ɗaya da two bedroom, sai kitchen da store, sallama muka shifa muka yiwa goggo da take tamana addu'an da wuwa lafiya.

Sai bayan azahar muka gama, kai tsaye gidan mu na wuce wurinsu Ummi, har sai kusan 5:30 tukun muka dawo gidan Aunty.

Rayuwa babu wuya yau har su Hammah sunyi four month da tafiya, mu kuma dai-dai mun gama exam ɗinmu na first semester, kwana ɗaya Feenah tayi Hammah Haidar yazo da niyyan ya kwana ɗaya ya ɗauki matar shi, xuwa lokacin cikin Feenah ya shiga na four month, don har ya ɗan taso da maran ta kaɗan.

Duk yadda tayi na bita kano Aunty taki yadda, tace su tafi tukun ni zan zo daga baya, idan an faɗa wa Hammah nah, ina ji ina gani suka tafi.

Nabeel kuma tunda ya lura da yafi jin daɗin zama dani sama da uwar shi, gaba ɗaya ya tattaro ya dawo wurina hattah bacci a waje na yakeyi, saboda tun asuba zan tashi haɗa mishi abinda zaije school da shi, Duk yadda Mama ta matsa wa Zainab ta hana shi firr taƙi yadda, don Zainab mace ce mai ƙiyiwan aiki, lokaci ɗaya yaro yayi fari yayi ƙiba, ga yana maida hankalinshi akan karatu, don har na saka shi a islamiyan gidan awak.

A wannan lokacin babu inda ban iya shiga da mota ba, don dai ba a barina yawo ne, sai idan muhimmin abu, amma kai Nabeel school da ɗan wani abu duk ina fita .

Hutun three wks aka bamu, wanda yayi daidai da yin hutunsu Nabeel, lokacin kuma Aunty Fannah tazo daga kaduna, haka ta saka Baba agaba har saida ya barta mutafi wurinta hutu.

Tun ana washe gari zamu tafi, Aunty tayi ta jamun kunne bayan irin wanda Ummi nah ma ta mun, amma shidai Abba na cewa yakeyi, "babu inda auta na zataje a ƙi zama lafiya da ita, saidai idan mutum baya sonta, saboda haka ki mata addu'an zuwa lafiya da dawowa lafiya kawai, domin ko bani da haufi a irin tarbiyan da muka bata".

Shiryah kaya na nayi dana Nabeel, inda Mama ta hau sababi, amma Zainab cewa tayi suje kawai itama Maiduguri take son zuwa ta ɗan huta, babu yadda Mama ta iya domin daga Baba har Aunty Fannah kwatale ta sukayi, sannan uwa uba, mai ɗan ma bata son wahala acewarta, kuma bata da haufi akan kulan  da nake yiwa ɗan nata.

Ranan da zamu tafi tunsafe Hammah Sadiq ya kawo mun kilishi mai yawa da masan bauchi wanda Hammah Waleed ya saka a sayamun don yin tsaraba wa Aunty Fanna, bayan Ummina ta gaya mishi maganan tafiyan.

Da misalin 10:00 am muka kama hanyan kaduna, muɓa baya nidaAuntyfanna, tsakiyan mu kuwa ɗana ne Nabeel daya kwanto mun akan jikina.

Toh jama'an kaduna ga Riyyah tahowa duk gamai niyyah ya bada tsaraban kaduna ta kawo mun, idan zata dawo, nagode ina gaida mutan kaduna garin governar.

#Vote
Comment
Share
Follow.

*KUKASANCE DA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*
*1441H/2020M.*

®☄️
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION✍️*
_{Gaskiya ɗaya ce daga kinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira.}_

🎐G•W•A🎐
_*GASKIYA DOKIN ƘARFE•* 🏇_

Story and written
By
*AUNTY NICE*

*_WANNAN BOOK SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Wattpad@GaskiyaWritersAsso.~

*page* 77---78

*___________*📖Muna shiga garin kaduna kai tsaye gidan Aunty dake unguwar Malali muka wuce.

Muna shiga gate ɗin farko kyaun gidan ya burgeni,shiganmu gate na biyu kam sai da naji kaman ba a nigeria nake ba, gaskiya gidan Aunty ya burgeni, gidane na sama amma mai masifar kyau, don babu haɗi bazaka haɗa shi da gidan su Hammah ko gidan Aunty Falmata ba, saidai kawai gidan su Hammah yayi biyun wannan a girma, amma babu haɗi ta wurin kyau kam.

Muna tsaya da motanmu Faisal ya fito da gudu yayi hugging Mamin shi cikin murna,  banyi mamaki ba don tunda muka taso ba mu wuce 20mnt zakaji ya ƙirata ya tambayeta suna dai-dai ina? Itama ba a ɗaukan lokaci zata ƙira shi kaji tana "yanzu muka wuce wuri kaza son" har muka iso basu bari ba, bayan ya saketa ne yana kallona yace.

"Aunty yayah hanya"? Fuskar shi ɗauke da murmushi, da wasu sexy eyes ɗinshi, nidai murmushi na mishi don duk sun burgrni  shida mamin shi, sannan ya sunkuya ya ɗauki Nabeel yana "oyoyo my son, me ka kawo mun from bauchi"? Ya faɗa yana ɗauka shin zuwa parlor.

Muna shiga Aunty Fannah sai sannu take jero mun, kaman ni ɗaya nayi tafiyan, nidai sai murmushi kawai nakeyi, daga nan ta ja ni mukayi sama.

A saman ma abin mamaki side biyu ne, ɗaya yana side ɗin dama, parlor ne da one bedroom a ciki, sannan a left side ɗin kuma parlor ne da two bedroom, ko wanne da toilet a ciki, ɗakunan wasu manya manya har fani nakeyi idan an zuba set na gado biyu zasu cinye har da sauran space.

Ɗayan ɗakin da yake manne da natan ta buɗe mun, wanda sai zabga ƙamshin borno yakeyi, dama tun shigowan mu gidan ƙamshin da nake ji kenan, ɗakin muka shiga tana nuna mun inda zan saka kayana, sannan ta kunna mun heater toilet, ta juya tayi ɗayan ɗakin, bayan ta roƙeni dana sake don Allah.

Bayan nayi wankane na saka wani dogon riga mara nauyi da gyalen shi, ina fesa turare Aunty Fanna ta shigo hannunta riƙe da kaskon turaren wuta da kuma kabbasa a ɗayan hannunta, da sauri na ƙarisa zan karɓa, amma sai tayi murmushi tace.

"cire kayanki mu turara shi, don so na keyi ki saba da al'adanmu na borno, wanda na san irin yadda mijinki yake so, amma abin haushi ƴar mu da ta zama cikakkiyar kanuri taƙi koyi da hakan, sai amfani da turaren nasara kawai take so, kuma mijinta yafi buƙatan namu na borno", ta faɗa tana ajiye kaskon da ya ke ɗauke da gaushi a ciki.

Da sauri na ɗauki zani na ɗaura, sannan na cire kayan na ɗaura hijab akan zanin da yake jikina, Aunty ko sai zuba turare tayi a cikin kaskon, sannan ta ɗaura kayan akan kabbasan, nidai kallonta kawai nakeyi, domin gaba ɗaya ƙamshin turaren naji ya kaure wurin, sai samun kai na nayi da jin daɗi a zuciyata, don gaskiya ni ina son ƙamshin borno.

Tana gamawa ta miƙo mun wani kwalban turare tace, " in-law ki shiga toilet kiyi alwala sai ki zuba wannan a cikin ruwan ɗumi ki sake ɗauraye jikinki da shi", da sauri na karɓa na shige toilet

ɗin nayi yadda tace, tun a toilet ɗin nake shin-shina jikina, haka na fito zuciyata wasai da ita.

Bayani Aunty ta mun akan kullum idan idan zanyi wanka na dinga saka turaren a ruwan.

Bayan mun sauƙo munci abinci ne, muka gyara wuri ana ta hira a parlon, Faisal yana da matuƙar kirki wallahi, sai kallon yadda yake ta nuna mana kulawa shida Mamin shi kawai na keyi.

Muna nan har aka ƙira sallan magarib, sannan muka watse zuwa sallan, bamu muka fito ba saida kowa yayi ishaa muna fitowa hannun Faisal riƙe dana Nabeel ɗina, yana kallona sai murmushi yake yi, yazo ya zauna a gefena yana ɗaura kanshi akan kafaɗa nah.

Wajen ƙarfe tara mijin Aunty Fannah ya dawo, da sauri muka gaishe shi, yana ta fara'a har ya zauna yana amsa mana cikin jin daɗi, tashi mukayi muka haura sama domin mu basu wuri su sake shi da matar shi, muna hawa sama Faisal ya kunna mana tashan arewa24.

Muna cikik kallo bamu fi minti biyar ba, saiga wayata ta fara ringing, ina dubawa naga number Hammah nane, cikin jin daɗi na ɗauki wayan ina kaiwa kunne na.

"hello babyn Hammah"........ɗan murmushi nayi na amsa mishi da, "na'am cwityn babyn jarirai" dariya ya yi mai ɗan sauti yace, "wallah baby ina missing ɗinki sosai".

Nima dariyan nakeyi nace, "wallah Babyn baby nima ina madaran missing ɗinka, kaman na taho da gudu ta jirgin ruwa", nayi mamakin irin sautin dariyan da Hammah na yakeyi, yana cewa "lallai baby kin falle fa, wato a kan idona kuma ba za ace mun haka ba ko"?.

Buɗe baki nayi ina dariya nace, "cabbb ae Hammah a gabanka kam abinda zanyi ae sai an taro mun kai, don hala sai ka felle kan su twins kabani ranan", ina faɗa na juya muka haɗa ido da Faisal da yake ta ƙaramin smilling, lokaci ɗaya naji kunya ya kamani, da sauri nace, "uhmm Hammah ga yarona ku gaisa tukun".

Nabeel saida suka gaisa da Daddyn shi tukun na miƙawa Faisal suka gaisa, sannan na wuce ɗaki don cigaba da waya da Hammah na.

Ina shiga ya cigaba da mun magiya akan shifah missing ɗina ya keyi, yana wani kashe murya yana tambayan, "baby ni yayah zanyi ne?wallahi na gajji fah da rashinki", ya faɗa kaman zaiyi kuka.

Da sauri na canja maganan ina tambayan shi ina labarin Yusuf? Tsaki yaja yana cewa, "ni kuma ina nake tunawa da wannan ƙaton zandagin? Kawai baby ki bani labarin kanki da kuma yanzu wani irin kaya kika saka, wani kalan ƙamshi turare kika fesa"?

Ajiyan zuciya nayi na miƙe na kwanta a hankali nace, "Baby nah!"  da sauri ya amsa mun da " yayah akayi my Heart"?

Sake mikewa nayi akan gadon na jawo pillow na rungume sannan na rufe idona nace, "nasaka light blue ɗin nighty," na sake yin shiru, da sauri Hammah yace, "uhmmm, turare fah"? Jin muryanshi har saida ya saka gaba na ya faɗi, sanann nace.

"Hammah rufe idonka zan matso kusa da kai don kaji irin ƙamshin da nakeyi mai daɗi, don baki bazai iya faɗa ba, kawai Hammah kasaka hancinka akan wuyana kaji", na faɗa a hankali wanda idan baka nutsu ba bazaka taɓa jin abinda nake cewa ba.

Matse idonshi yayi yana wani sauƙe nishi da sauri-sauri yane cewa, "wayyo baby matsu kusa dani sosai, ƙamshin ya mun dadi baby".

Matse pillow danake kai nayi da ƙarfi bayan na sake runtse idonan nace, "Hammah na kazo".

"Wayyo baby zaki kashe ni, mekike so don Allah" ko amsa ban bashi ba yaji an maka mishi duka a cinyan shi, da sauri ya buɗe ido ya ƙurawa Yusuf da yake tsaye akan shi, rai a ɓace yace "wani irin mugun wulaƙanci ne haka, baka san da wa nake magana bane? "

Hararan shi Yusuf yayi yana cewa, "sai ka cigaba da wayan bayan kaji sanarwan da akeyi a fito zamu je kan wancan bordan don kwantar da tarzuman da sukeyi tun daren jiya, yakamata ka dawo namijin ka ka taso kabar jaririyar ka ta huta muje mu bada taimakon gaggawa" ya juya

yana dariya yana cewa, "agaida mun jaririyar", sannnan ya fita daga ɗakin da Hammah yake kwance.

Ajiyan zuciya Hammah ya sauƙe, murya a raunane ya ƙira sunana a hankali, wanda da ƙyar na iya amsawa, sannan ya cigaba da magana yana cewa.

"Baby kinga an hanani jin daɗi da ke ko? Ki mun addu'a Allah ya fito damu lafiya, sannan ki kula mun da kanki".

Ajiyan zuciya nayi sannan nace,
"Hammah kullum ina cikin yi maka addu'a, kuma kowani bugun zuciyata tana tare da kai, Allah yadawo mun da kai lafiya, ka gaida Hammah Yusif shima", na faɗa muryana yana ta rawa.

#Vote
Comment
Share
Follow.

*KU KASANCE DA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYA*
*1441H/2020M.*

®🖋
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION✍*
_{Gaskiya ɗaya ce daga kinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira.}_

🎐G•W•A🎐
_*GASKIYA DOKIN ƘARFE•* 🏇_

Story and written
By
*AUNTY NICE*

*_WANNAN BOOK SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Wattpad@GaskiyaWritersAsso.~

*page* 79--80

*_____________*📖Muna yin sallama na maida kaina kan pillow ɗin na kwanta, duk hankalina a ɗan tashe yake da tunanin Hammah.

Da ƙyar na tashi naje nayi alwalah, sannan na kai Nabeel yayi fitsari, muka zo muka kwanta, addu'a na mana tukun na kwanta a gefen shi, wajejen ƙarfe biyu na dare na tashi naje nayi alwalah, na hau jera salloli, saida nayi raka'a goma sha biyu, tukun na zauna nayi ta jera addu'o'i wa Hammah nah.

Sai wajen ƙarfe huɗu na miƙe na kwanta, da asubah na tashi naje nayi alwala, sannan na ta da Nabeel ɗina yayi shima, tukun mukayi raka'atul fajir tukun mukayi sallan asuba, azkhar muka fara tare da shi, don tunda ya fara kwana a wurina, na fara gwada mishi azkhar.

Ƙarfe bakwai na shiga nayi wanka, na zuba wannan turaren a ruwa shima nayi wanka da shi, dama tun jiya Aunty ta bani wani rober cike da ruwan kanamfari, wanda tace na ringa tsarki da shi, shima ɗauka nayi na yi tsarki, sannan nayi alwalah na fito.

Ina fitowa naga wata dattijuwa ta shigo mun da gaushi kaman na jiya, zuba mun turare tayi da kanumfari a ciki, sakani tayi nazo na ɗan tsuguna akai kaɗan, ya turara ni, sannan na tashi ta ɗaura kabbasa akai ta zuba wani turaren daban akai ta ɗaura mun kayan da zan saka akai, hattah bra na da pant ɗina sai da ta ɗaura.

Wani mai ta miƙo mun na shafah, sanann ta bani wani humrah na shafah a jikina, hatta gashin kaina wani haɗi mai ƙamshi ta bani na shafah na taje kan na ɗaure shi.

Bayan ta gama turara mun kayan ta miƙo mun, sannnan ta ɗauku kaskon ta wuce da shi toilet ta ajiye shi, ta zo ta wuce waje.

Ina saka kayan daɗi kaman zai mun yaya, tsabar ƙamshin da yake tashi a jikina, ina gamawa na fito parlon don duba Aunty, amma shiru ban gantaba, har saida na sauƙo ƙasa na hango ta a kitchen.

Har ƙasa na kai na tsuguna ina gaisheta, da murmushi a fuskanta ta amsa mun, sannan ta miƙo mun wani cup da ke cike da madaran shanu ne kona raƙumi ohoo, amma dai yana da ɗumi, haka na kafa kaina na shanya, komawa nayi kusa da Aunty ina tambayan.

"Aunty mai zan taimaka miki da shi"?  "kaiii kai kai, wace ni da saka amaryah aiki? ae na taho dakene don ki huta kaɗan".

Murmushi nayi nace, "Aunty nikan aikin da babu wuya a ciki? Kawai kibari na dingayi".

Haka babu yadda ta iya ta barni muka haɗa abin break, sai wajen nine muka gama, lokacin Nabeel ya tashi, amma sai naga wannan dattijiyar taje ta mishi wanka, shima sai ƙamshi yakeyi mai daɗi, kai gaba ɗaya gidan Aunty ƙamshi yakeyi mai daɗi.

Muna yin break Aunty ta zauna ta yi ta gwada mun yadda ake kula da jiki yadda ƙamshi zai zauna a jikinka, sannan da yadda zan dinga kula da miji ta wurin yin girki da gyaran gida, da kuma gyaran jiki.

Ko rufe kwana huɗu banyi ba jikina ya kama wani ƙamshi mai sanyin daɗi, hattah kayan bacci na sun kama wannan ƙamshin, sannan ta fannin girki ta gwada mun girki na gargajiya iri da kala, ga kayan spices irin nasu na borno duk ta gwada mun, sannan kullum sai an mun haɗi na kaza ko baru ko kifi, wataran kuma wani haɗi aka mun na kaza amma babu ruwa ko kaɗan ajikinshi, kaman wani naman tukunya akayi shi.

Madara Kam yazama safe da dare sai na sha, ga manda ta saya mun mai masifar gyara jiki, sai wani sulɓi jikina yakeyi, ranan da muka cika sati biyu a gidan ta haɗa mun turare da yawa ta gwada mun amfanin ko wanne, sannan ta nuna mun man da zan dinga sakawa a gashin kaina, shima ƙamshi yakeyi sosai.

Bayan mun gama hutun mu aka haɗa mu da driver ya maido mu garin bauchi, zuciyarmu cike da kewan rabuwa, har jikin mota Aunty ta rako mu tanata mana fatan isa lpy, sannan ta cika mu da goma sha tara na arziki, faisal ma yana tajin babu daɗi da tafiyarda zamuyi.

Bayan mun shiga wurin Aunty mun huta ne take ce mun, "yaka mata kuje ku gaisheda Mama ko, don tasan kun dawo".

Aunty ce ta fitar mun da kayan da zamu mika mata na tsaraba, haka na riƙo hannun Nabeel wanda duk kan mu sai ƙamshi mukeyi, Mujaheed na biye da mu da kayan a hannun shi, muka wuce side ɗin Mama.

A parlor muka sameta zaune ita dasu Abdallah, da gudu Nabeel yaje ya rungume su ɗaya bayan ɗaya yana ta murmushi ya gaishe su, sannan ya ƙarasa ya rungume Mama itama yana gaisheta, gaba ɗaya bakinta a buɗe tana dariya da murnan ganin tilon jikanta, ɗan wanda tafi so a cikin sauran ƴaƴan.

Har kasa na sunkuya ina gaisheta, amma tayi kaman ba taji ni ba, sai tambayan Nabeel ta keyi labarin kaduna.

Abdurrahman ne yace, "Mama yayah ana gaisheki kinayi kaman bakijiba"? Hararan shi ta juyo tanayi,sannan tace "sannu ubana, wato kaine har kaga ka kai isan da zaka ce ana gaisheni ban amsaba? Toh naji ban amsaba, don ni bana son mutum mai fuska biyu, da tana gaisheni ne ko

kuma gulma? Toh bazan amsa ba ayi ƙuli-ƙulin hajiya dani, marasa kunya kawai", sannan ta riƙe hannun Nabeel ta wuce ɗakinta sai mita takeyi da faɗa.

Samun wuri nayi na gyara zamana muna ta hira dasu twins, wanda Abdallah da kyar yake amsawa, don na lura ranshi yayi matuƙar ɓaci da abinda Maman shi tayi, amma da yake Abdurrahman mai ɗan sauƙi ne, sai yanata jana da labari akan na mance da abinda Maman tayi mun, wanda ni har ga Allah bai dame ni ba, don taci darajan ƴaƴanta da suke sona.

Har sai da aka ƙira sallan magrib tukun muka fito tare dasu twins, wanda zuwa lokacin Nabeel ya fito shima zai bi su mosque,har na shige side ɗin Aunty yana ta ɗaga mun hannu, muna tayiwa juna murmushi.

Ban fito parlo ba sai da akayi sallan ishaa, a parlon na samu mutumina Gidaɗo, yana ganina yace "kaga ƴar baƙa tana ta wani wankewa, kodai ana ɗan miki bleaching ne"? ya faɗa yana tamun dariyan tsokana.

Hararan shi nayi ina zaunawa a gefen shi sannan nace, "a'a dialuting ake mun, ɗan rainin sence, kawai kaga ina ta bada kala wanda duk yadda kayi baka zama haka shine kake ciki baƙi ko"?

Dariyan shi yakeyi, sannan yace, "wallahi sis kinga kyaun da kikeyi kuwa?nima inaga idan na tashi aure kalanki zan daure na cije na aura", ya faɗa yana yamutsa fuska kaman ya ambaci kashi.

Maka mishi cushion nayi ina cewa "ya maka kyau da kake ya mutsa fuska, kuma babu kai babu kalata, saidai ka nemo fara kamar zabiya , wannan kalan ya wuce kanka yaro sai Hammah na kaɗai ya dace da hakan" na faɗa ina juya kaina gefe.

Ihu Gidaɗo yasaka yana faɗin, "chakarewan ki yarinya, wato kinga ɗan haɗaɗɗen gaye jinin jama'are, masu gadon kyau ɗan asali ko?"

Nima kallon shi nayi ina juya kai nace, "shima yaga yarinya ƴar madara ƴar duma-duma jinin fulanin kafin madaki masu kyaun asali, duk sunbi sun ruɗe mun," na faɗa ina jujjuya idona.

"kaji mun yarinya, keda ya kamata a miki murna kin samu ƴan farare, qhine zakina wani yauƙi da baƙar fata"?ya faɗa yana jefa mun pillow ɗin.

"wallahi Gidaɗo ka fita a ido na, bayan gaba ɗaya yayunka da kakeji da su sai dana tafi da imanin su"! na faɗa ina hararanshi.

Shima hararan ya mun yana cewa, "saidai ki tafi da hankalin Hammah Babagana, amma Hammah ɗan gaske kam ƙaryanki yarinya, farar macen ma fama ta keyi da shi ballantana ke wallahi, gara ma kije ki kwana kina godiya wa Allah".

Bansan lokacin da na miƙe tsaye ba nace, "dubeni da kyau cikakkiyar mace ne a zaune anan ba kamar firituwar matar shiba, kuma ni mace ce wanda ko wanda yafi Hammah sai ya duƙa mun bama rikicewa ba, kuma yaro albishirinka?

Hammah ya gama tafiya tun ana sanyi sanyi na gama da zuciyar shi".

Tafa mun ya farayi yana cewa, "lallai yarinyar nan kin haɗu, wato har Hammah kike faɗawa haka? Toh bari ya dawo duk zan sanar mishi, idan yaso ki shirya amsan kare kanki a wurin shi" ya faɗa yana jijjiga kai irin alamar zan haɗu da shi.

"yaro ka kwantar da hankalinka Allah ya dawo mun da shi lafiya kaga ikon Allah, nidai yanzu fatana yanzu ya dawo mun da shi gida lafiya, Ni kuma ni since mishi kanshi yadda ya mun".

Miƙo mun hannu yayi muka tafa yana ,"kina wuta my lovely sister" Dariya nayi nace, "ina ƙamshi dai kuna bina da humrah yaro".

Matsuwa yayi yace, "yauwa sisi nah bari na tambayeki, wai wani irin turare ne kam kike amfani da shi? Tunda kika dawo duk inda kika zauna sai kin bar ƙamshi mai masifar daɗi", ya faɗa yana wani zaro ido irin alaman miyi gulman nan da shi.

Kafin na bashi amsa kawai sai muka ji muryan Aunty tana cewa, "wallahi bincikenka yayi yawa yaron nan, naga alama ko gidan aurenta aka kaita sai kaje binciken me sukeyi a gidan, wallahi Gidaɗo kabar son jin gulma, ina jan kunnen ka, ko kuma na haɗaka da Hammanka".

Miƙewa nayi da gudu na shige ɗakin Aunty ina dariya, don naji kunyan jin hiran da taji munayi da Gidaɗo, don kullum jamun kunne ta keyi akan wallahi son jin ƙwaƙwafa ɗin Gidaɗo yayi yawa na kiyaye.

Nima Aunty nice dariyan Riyyah nayi nace, "lallai ashe dama yarinyar nan tana da baki haka"?

#Vote
Comment
Share.

*KU KASANCE DA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYYAH*
*1441H/2020M.*

®☄
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION*✍🏻
{ _Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira._ }

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN ƘARFE*🏇🏻

Story and written
By
*_AUNTY NICE_*

*_WANNAN BOOK ƊIN SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Whatpad@GaskiyaWritersAsso.~

*page* 81--82

*____________*📖Sosa kai Gidaɗo ya fara yana ɗan murmushin shaƙiyanci, a karkace ya wuce ɗakinsu don kada Aunty ta make shi.

Yana wucewa tayi tsaki ta biyo bayana, ina kwance rub da ciki ta same ni, harara na tayi ni kuma na maida kaina ƙasa ina dariya, ta cigaba da harara nah tace.

"wallahi zakiyi dariya da kyau ranan da Hammanku yayi ball dake a gidan nan, ki cigaba da gaya wa Gidaɗo duk abinda ya shafe ku ke da Hammanku, wataran zaki sha mamaki, wallahi Riyyah ki maida hankalinki tam", ta faɗa tana fita a ɗakin.

Rayuwan yau da gobe babu wuya a wurin Allah, bayan mun koma makaranta  sai jikin Feenah ya ƙara birkicewa, kullum cikin laulayi take, Hammah Haidar kuwa kullum weƙend sai ya shigo bauchi kaman kan shi aka fara ciki, wani ƙauna da kulawa yake nuna mata, haka ma goggo take maida hankali akan Feenah kaman ta lashe ta.

Yau su Baba da su Daddy suka tafi kafin-madaki nemawa Hammah Waleed da Hammah Khalil auren wasu twins ƴan uwansu Hammah Khalil ɗin, inda tsabar haɗin kansu saida suka samo ƴan gida ɗaya kuma twins.

Hammah Waleed shi ya dace da babbar wacce ake cemata, *HASNAH* shi kuma Hammah Khalil ya dace da ƙaramar wacce ake ce mata, *HUSNAH*.

Muna gama lectures muka taho gwallaga gidanmu, inda muka haɗu da su Aunty, Goggo da Mummy dukkansu a wurin Ummi nah, muna shiga na wuce kan cinyan Ummi na kwanta ina "washhh Ummi mun gajji yau kam", ............... "ɗaga ni nikan uwar son jiki, kaman ke kaɗai kika gajjin zakizo ki ɗalewa mutum jiki" Ummi ta faɗa tana ture kaina a cinyanta.

Tashi nayi na zauna ina tura bakina gaba kaman zanyi kuka, amma ko kulani batayi ba ta dubi Feenah tace, "Nafisa ga tuwan shinkafa idan zaki ci, idan kuma jeloop rice zakici akwai shi na gidan Mummyn ku a coolern nan", ta faɗa tana jawo mata coololin duka gabanta, nidai ido kawai na ƙurawa Ummi don ganin ko ta kaina bata bi ba.

Ya mutsa fuska Feenah tayi sannan tace, "Ummi nikan ɗanwake nake son ci", ta faɗa tana kara ya mutse fuskan.

Da sauri Ummi na ta miƙe tana cewa, "bari na jefa miji ɗiyata, dama inada guntun flour", ta fita a ɗakin da sauri.

Ɗaga muryah nayi da ƙarfi ina cewa, "Ummi nima zanci ɗanwaken", itama da karfi ta amsa mun da, "kema ki nemi naki iyayen su miki, nima wa ɗiyata zanyi".

Aunty ce ta amsawa Ummi da cewa, "ni yau ina ga rashin kara a wurin matar nan, a gaba na kike ta yiwa ɗiyata wulaƙanci? tun shigowan t baki barta ba, tazo jikinki kin tureta, tace zataci ɗanwake kin hnata bayan ina lura ko ɗan tayin abincin dama baki mata ba, ae ko mutuwa ce tana kunyan idon uwa", Aunty ta faɗa tana ɗaure fuska.

Daga wajen Ummi  nah ta amsa da "toh idan ranku ya ɓaci ar gaku ga kitchen ɗin sai ku shigo kuyiwa ɗiyar ta ku, amma wannan kam nawa ɗiyar zanyiwa".

Mummy ce tana dariyan drammern ta amsa da, "gaskiya ba a mana kara Ummin Riyyah, yayah, kuma aiko don ganin idonmu ae za abawa tamu ɗiyar, amma duk abinda goggo tace shine za ayi" ta dubi Goggo tana , "Goggo kisaka baki a yi ɗanwaken nan da ɗiyarmu ko muhana tata ɗiyar ci".

Goggo dariya tayi ta miƙe tana gyara zaninta, tayi hanyar waje tana, "bari naje nayiwa tawa ɗiyar tunda Ummi taƙi yi mun kara".

Ummi dake tankaɗe flour tayi sauri tace, "Adda kibarsu kawai ki koma ki zauna, sunci darajanki zan tsakurawa ɗiyar sun kaɗan" ta faɗa tana dariyan idon ƴar uwarta Aunty da take binta da harara.

A shagwaɓe na kalli Aunty nace, "Aunty nah mu tafi ma abinmu na fasa cin ɗanwaken, muje gida kawai ki dafa mun kaza naci kinji Aunty nah", na faɗa ina matsawa jikin Auntyn.

Rabu dasu doug nah, ɗanwaken nan sai munci kafin mutafi kuma na gasa miki kaza kici ke kaɗanki ƴar autanah" ta faɗa tana jawoni jikinta, su Mummy kuma sai dariya suke ta mana, bayan Feenah kuma ta tashi ta shige cikin ɗakin Ummi ta Kwanta.

Wunin ranan gaba ɗaya cikin nishaɗi mukayi shi, da akayi magarib ne Mummy da Feenah suka shifa gidan su don ta gaisa da Daddy, sai wurin 8:00pm muka wuce muka sauƙe su Feenah da Goggo, sannan muka wace muma.

Akwana a tashi babu wuya wurin Allah, yau baifi saura two weeks mu fara exams ba, wanda yayi daidai da dawowan Hammah saura sati ɗaya.

Gaba ɗaya hankalinmu ya koma kan karatu, ta ɗayan gefen kuma Aunty kullum cikin gyara take mun, ga Aunty Fannah kuma ta wurinta ta aiko mun da wasu turaruka da kuma wasu gadali, data cewa Aunty a dafa mun budurwar kaza da shi, ɗayan kuma ta dafa mun baru aure da shi, ga wani curin abu kuma da tace a zuba ruwa cikin kwanan sha biyu a dafa dashi bayan an zuba mishi zuma akai, gaba ɗaya sai ya koma tsumi mai matuƙar daɗi da amfani.

Ana saura kwana biyu Hammah ya iso, Zainab ta dawo daga Maiduguri, Nabeel da ƙyar ya yarda na karashi ya gaisa da Mummyn shi, a parlo na sameau zaune itada su twins da Mama, har ƙasa na tsuguna na gaida Mama, da ƙyar take buɗe baki tana amsa mun.

Zainab na gayar da mata sannu da dawowa, amma itama cikin ji dakai ta amsa mun, sannan ta

miƙowa Nabeel hannu akan yazo, da sauri ya ƙarasa ya durƙusa har ƙasa ya gaisheta sannan ya gayar da su Mama da su twins.

Hira kaɗan muka taɓa dasu Abdallah, sannan na miƙe na musu sallama na fita, da sauri Nabeel ya biyoni, babu ƴadda banyi da shi ba ya koma wurin Maman shi amma firr yaƙi, haka muka tafi tare da shibayan Abdallah ya mana rakiya har side ɗin Aunty.

Rannan friday mukayi dambun kaji nida Aunty wanda yaji kayan ƙamshi dasu garlic sosai, sannan washegari mukayi cake wanda yaji inibi wadatacce yayi daɗi, ranan bayan sallan axahar muka tafi saloon ɗin Aunty ladidi, gyaran ƙafa da lalle aka mun, sannan aka zizara mun kitso ɗan gaske, ba ƙaramun kyau nayiba ranan duk yadda nayi Aunty sai bina da ido takeyi tana ta yabani.

Ranan sunday da misalin ƙarfe shida na safe Hammah ya sauƙa a garin lagos, inda Abdurrahman da Khalifah suke jiranshi, daga nan kano kuma Abdallah da Gidaɗo suna jiransu, cikin jin daɗi suka je suka rungumeshi, shima cikin farin ciki ya rungume su gaba ɗaya cikin farin ciki suke.

haka sukayi ta gaisawa da friends ɗinshi, abin tausayi wasu sun dawo wasu kuma acan kwana ya ƙare, Yusuf abokin Hammah ne a gefen Hammah, suna musabiha domin shi jirgin kaduna zai shiga, shima ƙannen shi ne su biyu suka zo taryenshi, a haka su Hammah sukayi sallam akan zaizo ya duba Yusuf saboda shi ya samu karaya a ƙafan shi, amma ya ɗan ji sauƙi tunda haryafara ɗan takawa da sanda.

Tunda muka tashi naga Aunty sai shirye-shiyen abinci takeyi, da mamaki nake kallonta, can nace, "Aunty abincin da idan ya dawo ma mu zamu mishi? bayan ga Mamanshi da matar shi, kada muyi suma sunyinamu yayi kwantai"? na faɗa idona akanta.

Dariya tayi tana miƙo mun green beans da carrot akan na gyara mata, sannan tace, "lallai Riyyah yarinta na damunki, kin taɓa ganin rannan da maigidan yayi tafiya Mama ta zauna ta mishi girki na musamman?ae kullum ita son jikinta baya barinta tayiwa iyalinta girki saidai ta

saka masu aiki suyi, ballantana ita matarshi da take ganin tafi kowa gata, ae inaga ko gyaran side ɗinshi batayi ba,

Duk da dai nasaka su Gidaɗo kafin su tafi sun yi, amma ae yakamata ace yau kafin ya iso an sake gyarawa, amma babu abinda suke da niyyan yi, kawai mu musu don nasan Hammanku baxai iya cin abincin ƴan aiki ba", ta faɗa tana cigaba da aikinta.

Nima cikin mamakin halin Mama da ƴarta Zainab kawai nakeyi, gasu da kishin shi amma basu iya yi mishi Komai.

9:00 jirgin su Hammah ya sauƙa a kano inda su Gidaɗi suke jiran isowar su, basu wani ɓata lokaci ba suka shiga motocinsu suka taho bauchi cike da kaunar junan su, idan kagansu kaman dukkansu uwa ɗayace ta haife su, saboda tsantsan haɗin kan su, abin tausayi gasu dukkan su a haɗe amma yau an wayi gari babu Babagana kaɗai a cikin su, rayuwa kenan.

Abinci yakai kala uku mukayi muka jera su a dinning ɗin parlon Baba, sannan drinks ya kai kala huɗu mukayi, da sauri naje na sakeyi wa Nabeel wanka domin naji ana ƙiran sallan azahar, three-quater da wani riga armless na saka mishi yayi masifar kyau, ga gashinshi da kaman nin shi kaman Hammah sak.

Ina gamawa na wuce toilet nima nayi wanka nayi alwalah, ina fitowa na zauna na shafa mai na da Aunty Fannah ta aiko mun, sannan nabi jiki na da turaren data aiko mun shima har gashin kaina sai daya kama ƙamshin turaren, hijab na saka nayi sallah sannan na ɗauka dogon rigana na atamfah Wanda *ABBA NUHU TELA* ya ɗinka mun nasaka.

Ina cikin  saka ɗan kunne nane naji shigowar motocin su, daga dukkan alama matafiya sun iso lafiya, lokaci ɗaya naji gabana ya faɗi.

Komawa nayi kan gado na kwanta, har tsawon minti talatin da wani abu banji motsin suba, daga dukkan alama wurin Mama suka wuce, ba a daɗe ba naji alaman hayani yain su aside ɗin Aunty, a haka naji Aunty ta buɗe ƙofa tana "fito auta kizo muyi saving ɗinsu, don dukkansu anan zasu ci abincin" ta faɗa tana komawa inda suke.

Kaman wanda ƙwai ya fashe mun a ciki, a hankali na tashi na ɗauki gyale na yafa wa kaina, don ji nake bazan iya ɗaura ɗankwalin ba, a hankali na fita nayi hanyar parlon gaba na yana cigaba da faɗuwa.

Ina doso parlon ido na ya sauƙa akan na Hammah na, kaman wanda aka dasa ni a wajen naja na tsaya na zuba mishi ido, lokaci ɗaya naji idona ya ciko da hawaye don gaba ɗaya Hammah na ya bani tausayi, ya wani rame yayi baƙi.

Ban ankara ba naji hawayen yana zubo mun, da sauri na juya cikin gudu-gudu na koma ɗakin Aunty da gudu.

Ganin haka ya saka shi yin murmushi ya tashi a hankali bai dubi idon kowa ba ya biyo bayana cikin takun shi na jan aji, har bakin ƙofan ɗakin ya iso amma ganin na kwanta ina kuka ya saka shi tsayawa ya ƙura mun ido daga inda yake.

Jin alaman ana tsaye a wurin ya sakani ɗagowa da sauri ina kallonshi, Shima ido ya ƙura mun yayi crosing hannun shi a ƙirjin shi, ya junguna da ƙofan kanshi a ɗan karkace gefe ɗaya.

Ganin kallon namu bazai ƙare ba, ga kuma kaman an sake sake mun sheshsheƙan kuka na daya ƙaru da ɗan karfi ina binshi da ido, ya saka shi buɗe mun hannun shi alaman nazo gareshi.

Ban wani ja ajiba na tashi da gudu naje na faɗa Ƙirjinshi, na ƙara fashewa da kuka, da sauri ya rungumeni Shima.

#Vote
Comment
Follow.

*KUKASANCE DA ALKALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYYAH*

*1441H/2020M.*

®☄️
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION*✍🏻
{ _Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira._ }

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN ƘARFE*🏇🏽

Story and written
By
*_AUNTY NICE_*

*_WANNAN BOOK ƊIN SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Whatpad@GaskiyaWritersAsso.~

*page* 83--84

*____________*📖Rungumeni yayi ƙamƙam a jikinshi kaman zai maida ni cikin shi, nima sai ƙara shigewa jikinshi nakeyi kama za a ƙwace mun shi, haka muka dinga ajiyan zuciya nida shi.

Can kasa naji muryanshi yana cewa, "baby nayi missing ɗinki sosai, nasha wahala da rashinki a

kusa dani, da ƙyar na daure har muka gama".

Ajiyan zuciya na sake sauƙewa sannan na ƙara rungume shi a jikina, a hankali na buɗe baki na nace, "Hammah toh meya sameka ka rame? Hammah na ka sha wahala nasani", na faɗa ina ƙara sautin kuka na.

Murmushi yayi ya ɗago ni daga jikinshi, sannan ya saka hannunshi ya ɗaga fuskana yana kallon yadda nake ta zubar da hawaye nah, a hankali yace.

"Baby kada ki ɗaga mun hankali da kukan kimana, kawai shiga jeji mukayi mai tsananin duhu da abubuwan tashin hankali, shiyasa mukayi baƙi, ga kuma yunwa daya mana yawa a lokacin, amma ae yanzu komai ya wuce tunda Allah ya dawo damu gida da ranmu da lafiyan mu, ae kinga sai mu gode mishi bawai muyita kuka ba", ya faɗa yana haɗa goshina da na shi wuri ɗaya.

Mun daɗe a haka kafin ya raba jikinmu, ya riƙo hannu na yace, "muje kibani abinci naci yunwa nakeji sosai".

Saida muka zo daidai zamu shiga parlon sai na ƙwace hannuna a hankali cikin nashi, da sauri ya dubi inda nake ya ɗaga giranshi alaman tambaya, kawar da kaina nayi bance komai ba, na wuce cikin parlon, amma abin mamaki sai samun su mukayi dukkansu babu wanda ya zuba abinci, duk suna hiransu a zaune akan dinning ɗin.

Hammah ne cikin mamaki yace, "Aunty yayah naga bakuci ba"?.......... Dariya ta ɗanyi tana duban Baba tace, "Babanku ne ya hanamu ci, yace saboda kai akayi, kuma dole sai kai kafara zubawa tukun mu zuba, shine muka tsaya jiranka", ta faɗa tana duban Baba da yayi tagumi da hannu shi ɗaya yana dubanta.

Daga ni har Hammah saida mukaji kunyar maganan, amma da take shi namiji ne sai ya share ya nemi wuri ya xauna, yana duba na yace.

"Baby zuba mun",  kaman zan nutse ƙasa naji alokacin da yace mun baby, gashi yana faɗa Baba ya ɗaga kai ya dubi Aunty, ita kuma ta kawar da kanta gefe tana smilling.

A haka na buɗe duka coolers ɗin iɓa duban shi akan wanne yake so na zuba mishi? Ɗaga kafaɗan shi yayi alaman shi bayida choice sai abinda na bashi, ganin haka yasani zuba mishi abinda naji yamun, ina gamawa Aunty ta turo mun pilet tace na zubawa Baba da nata, babu ɓata lokaci ɓa zuba musu, sannan na koma zan zauna kawai sai jin Gidaɗo nayi yace, "Hammah Abdallah Allah ya bamu haƙuri".

Haranshi nayi don na gane me yake nufi, sannnan na ɗauki pilet na zubawa su twins na miƙa musu, sannan na sakawa Nabeel da mujaheed na tura musu, a ƙarshe na saka wa khalifah da yake ta binmu da murmushi, ina miƙa mishi na koma na zauna.

Salati Gidaɗo yayi a hankali yana zare idon shi, "wato ni bazaki zuba mun ba ko"? Ko amsa mishi banyi ba Hammah ya doka mishi uban hararan da ya saka shi tsuke bakinshi.

Baba sai santin girkin sukeyi shida su Abdallah, don Gidaɗo nawa bai sake daga kanshi ba, tunda yaji idon manya akanshi.

Hammah yana gama cinyewa ya ɗaga kai ya dubeni alaman bai ƙoshi ba, da sauri na tashi na buɗe coolern ferfesoup na zuba mishi, ina tura mishi Baba yace.

"Kada fa sojan nan ya cinye mun abincin gida na daga dawowan shi? Naga ya cinye abincin da mutum biyu zasu ci, yanzu kuma an zuba mishi naman da mutum uku zasu ci shi ɗaya", ya faɗa yana leƙa pilet ɗin Hamman.

kowa dariyan su yayi Aunty tace, "Toh wannan abincinfa don yaci ya ƙoshi mukayi ba don ku ba fah, yaka mata ae ku barshi yaci iya cin shi tukun sai kuyi niyyah ku ci", ta faɗa tana dariya.

Hammah dariya yayi ya cigaba da ci bai sake ɗagowa ba har sai da yagama cu, yana gamawa kuma ya ɗago ya dube ni, sannan ya mike yace, "Aunty bari naje na ɗan huta" sannan ya saje

duban inda nake bai ce komai ba ya juya ya fita.

Da sauri Aunty ta dube ni sannan tace, "Riyyah jeki ki haɗa mishi ruwan wanka mai ɗan ɗumi ko".

Kallon Baba nayi da sauri amma sai naga baya kallon mu, abinci shi kawai yakeci,da sauri na tashi ban ko juyo ba na bi bayanshi.

Ina fitowa na dubi gefen side ɗin Mama naga babu kowa, da sauri na wuce side ɗin Hammah, ina shiga na same shi a tsakiyar parlon a tsaye yana cire wrist wacth ɗinshi.

A kunya ce na ƙarasa inda yake nace, "Hammah bari na haɗa maka ruwan wanka", yana duba na baice komai ba sai kallon da yake bina da shi, a haka na wuce cikin bedroom ɗin shi, gani nayi gadon ko bedsheet babu, da sauri na wuce bathroom ɗin na haɗa ruwa mai ɗan zafi kaɗan.

Ina fitowa na leƙa parloon nagaya mishi na haɗa, sannan na dawo da sauri na buɗe walldrop ɗin na ɗauko wani white bedsheet mai zanen ball blue ajikinshi, ina shinfuɗawa shi kuma ya shigo, bai ko kalleni ba ya wuce bathroom ɗin, ni kuma ina gama shinfiɗa bedsheet ɗin na sake share ɗakin, na goge shi ƙall, ina fesa roomfeshner shi kuma ya fito a toilet ɗin, kugunshi ɗaure da ƙaramin towel.

Da sauri na ajiye gidan akaɓ dressing mirrow zan fita, cikin sauri ya riƙoni ta baya, kafin nayi tunanin ƙwace kaina ya saka hannun shi ya rungumoni ta bayan  ƙirjinshi da yaje jeƙe da ruwa ya ɗaura mun a bayana, hannun shi kuma ya zagayoni ra saman kafaɗa na, ya ɗaura haɓanshi akan kafaɗa nah, ɗayan hannun kuma ya ɗaura shi takan maranah ya rungumeni gam.

Runtse ido na nayi da ɗan ƙarfi din jin danayi jikinshi da ɗan ɗumi, ga kuma hannun shi ɗaya daya ɗaura akan mara na inajin wani irin kasala a jiki na.

Dai-dai saitin kunne nah naji shi yana mun raɗa a hankali, "Ina zaki gudu kuma? Bayan baki

mun wanka kin gasa mun jiki na  haƙura miki, sai kuma zaki gudu baki matsa mun jiki na ba"? Ya faɗa yana ajiye mun wani numfashi mai ɗumi a kunne na da wuya na.

Kasa amsa mishi nayi, domin inaji ya saka hannunshi dake mara na yana ta matsa mun gefen cikina yana wani daddanna shi kaman ni nace ina so a matsa mun jiki.

Ganin yana ta magana bana amsa mishi, shima yayi shiru sai bin jikina yakeyi yana shafawa, a hankali ya dawo da kaɓshi kan wuyana yana ɗewa, "Baby muje ki danna mun bayana kinji".

Ganin babu inda zan motsa yasaka shi janyoni muka faɗa kan gadon, har saida towel ɗin shi ya kunce amma bai faɗiba yayi sauri ya haɗa ni da jikinshi don kada towel ɗin ya faɗi.

Gaba ɗaya kunyan duniya saida ya sauƙo mun don jin gaba ɗaya ya maida ni jikin shi, kuma inajin towel ɗin yana shirin zamewa, da sauri nace,  "Hammah zan tafi".

Gaba ɗaya jikin shi rawa yakeyi bai iya yace mun komai ba, sai jinshi kawai nayi ya riƙo hannuna yana kaiwa jikinshi, murya ƙasa-ƙasa mai haɗe da nishi yana, "Baby don Allah kada kibarni, ki taimaka mun na wahala kinji".

Buɗe baki nayi zanyi magana amma kawai saijin bakin shi nayi cikin nawa, Wani irin kiss yake mun mai tada hankali har saida naji kaman numfashina zai ɗauke, shi kuma sai gurnani yakeyi kaman zai cire mun lips, duk sai naji tsoro ya kamani, gashi naji ƙirjinshi cike da gashi duk a kwance, sai duk na ƙara razana da shi

Lokaci ɗaya jikina ya shiga rawan tsoro, shi kuma narasa rawan me jikinshi ya keyi?

Muna haka sai kara laluɓeni yakeyi ta ko ina, gashi sai neman ya zuge mun zip ɗin rigana yakeyi, duk hankalina ya tashi da yadda yake yi ɗin, cikin ƙarfin hali na buɗi bakina dana kwace da ƙyar nace.

"Hammah ka tsaya na danna maka jikin kan" ae ban samu ikon karasa faɗin abinda nake son faɗi ba, naji ya zuge mun zip ɗin rigana, kafin nayi wani yun ƙurin har yayi ƙasa da rigan, da sauri yakai hannun shi kan breast ɗina da suka ciko kaman zasu fashe, ina ƙoƙarin tunɓuke hannun shi kawai sai naji shi yana wani irin nishi yana faɗin.

"wayyo baby zaki kashe ni, wayyoooo washhhh baby nah," hannun shi nakan ɗayan yana "wannan nawane baby, wayyo baby duka nawane" Jikinshi kan sai wani mazari yakeyi ga wani irin matsa su da yakeyi , wanda har cikin raina zafi suke mun, amma duk ya gama firgita ni, ido na duk a zare zan fara mishi magiya kawai naji shi ya miƙe ya ƙara ɗago ni sosai ya rungumeni yana faɗin.

"Baby daɗi zai kasheni dukkanki fa nawa ne ni kaɗai, baby ina son su sosai dama ina son breast manya Baby, yau zaki kashe ni da daɗi", abin har tsuro ya fara bani yanda ya maida ni kan cinyan shi wanda tunin towel ɗin yayi nashi gefen, ni kuma jinshi zaryan ɗinshi ya sakani runtse idona, amma shi kuma ko kula da haka baiyi ba, sai mateseni kawai yakeyi yana ta mun sumbatu da girman breast ɗina, yana ta aikin neman fitar da bra ɗin jikina.

Gaba ɗaya daga ni har shi tsaya mukayi don jin irin ƙiran da Mama take mishi ta ƙofan parlon, a hankali na dube shi naga ya wani runtse idon shi ya cije lips ɗinshi kaman zai tsinkasu, ya kuma matse Mun breast ɗina ɗaya da ƙarfi, wanda ina sonyin ihu don azaba amma ina tsoron kada Mama tajini.

Ganin haka nima Aunty Nice nace bari na fece kada a haɗa dani.

#Vote
Comment
Share.

*KU KASANCE DA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYYAH*
*1441H/2020M.*

®☄️
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION*✍🏻
{ _Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira._ }

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN ƘARFE*🏇🏽

Story and written
By
*_AUNTY NICE_*

*_WANNAN BOOK ƊIN SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Whatpad@GaskiyaWritersAsso.~

*page* 85--86

*__________*📖"Hamman su baka jina ne"? Ta faɗa tana ƙara ƙiranshi, muna kwance shiru lokacin yaɗan saisaita mun rikon da yayi, can kuma sai mukaji wayanshi ya fara ringing.

A hankali ya saka hannu ya ɗauki wayan, da ƙyar ya buɗe bakinshi ya amsa wayan, daga side ɗin Mama tace yazo ya buɗe mata ƙofan.

Hannun shi ya ɗaura akan goshin shi ya runtse idon shi sannan ya amsa mata da, "toh gani nan zuwa".

Tashi yayi da ƙyar ya ɗaura towel ɗinshi, ni kuma ganin zai tashi ya sakani runtse ido na, ko kallon inda nake bai yiba ya wuce toilet, yana fitowa ya ɗauki kayan da ya cire ya mayar, sannan ya wuce buɗewa Mama ƙofan.

Tare suka shigo shida Maman har parlon shi, zama tayi ta fara mishi tambayan ina tsaraban da ya kawo? Ɗago da idonshi yayi wanda sukayi ja yana kallonta da su yace, "haba Mama wani tsaraba zanyi? Kin manta kashe tarzoma muka tafi yi?"

Kawar da kanta gefe tayi sannan tace, " nayi tunanin da ka tsaya a lagos zaka saya ne ae, danaji shiru nace ko ka miƙawa sabuwar uwar da kayi da ƴarta mai baƙar fuska".

"Hmmm ni babu abinda na saya" ya faɗa yana murtuke fuskan don yaji kunyar zagin da Mama tayi mun ni da Aunty na, don yasan inajin su, kawar da kanshi gefe yayi.

Mama tana duban shi tace, "baka da lafiya ne duk naga idonka yayi ja"? Yana kallon ƙasa yace, "bacci na fara shiyasa, kuma na gajji duk jikina ciwo ya keyi", ya faɗa mata.

Tashi tayi tana shirin tafiya tace, "toh nikan na tafi, amma kuma kamayar da hankalinka akan wannan shegiyar matar nan mai wayon tsiya da ƴar ta, don yarinyar nan tunda ka tafi bata sake ɗaga kai ta dube ni ba ballantana ta gaisheni, don ranan nace tazo ta gyara maka ɗakin nan amma firr taƙi zuwa sai su Gidaɗo ta aiko suka gyara, ta nuna mun ita ban isa da itaba".

Tana gamawa ta juya ta fita, har ƙofa ya rakata ya dawo ɗakin, tana fita na tashi na mayar da kayana, yana shigowa ya samu ina shirin gyara mishi gadon, kallona yayi sannan yace.

"barshi zan gyara kayana, ina Mama ta saka ki kinƙi saboda kin fara raina ta don tana nuna bata sonki ko?  Toh ae taci darajan haihuwa na, ya kamata ki girmamata idan kina son mu shirya da ke, yana faɗa ya hau kan gadon ya kwanta bai sake waiwayan inda nake ba, ganin haka ya sakani fara kuka don ni tsoron nace mishi ba haka bane nakeyi.

Kuka nakeyi babu sassautawa amma ko ya bani haƙuri, zuwa can yace, "Don Allah ki bani waje da kukan kinnan bacci nake sonyi, bana so ki cika mun kunne da kuka".

Shiru nayi ina share hawaye na, sai dana gama ɓa tashi na fita a ɗakin don tafiya inda nafi wayo, ina fitaya bini da kallo har na ƙarisa fita.

Ina shiga parlor Aunty tana kitchen ko bin takanta banyi ba na wuce ɗakin ta ɗayan na kwanta, har lokacin kuka bi daina zuba mun ba, don haushin abinda Mama ta mun na keji, gashi shi kuma Hammah bai ko tambayeni gaskiyan abunba ya hau ya zauna.

Tun daga wannan ranan Hammah bai ce mun uffan ba, sai  hidiman  shi da matar shi kawai yakeyi, nima na tattara shi na watsar na maida hankalina a karatuna, don muna shiri a wannan exams ɗin, ga Feenah na sai fama da jikinta ta keyi.

Aunty duk ta fahimci akwai saɓani a tsakanin mu da Hammah, amma sai tayi biris damu bata ce mana uffan ba, haka mukayi ta muƙu-muƙu bamu kula junan mu.

Har sai da mukayi one week da shi a haka babu mai kula juna nida shi, ranan da muka fara exam Aunty ce ta kaini, don ranan nayi nayi motar ta tashi taƙi tashi, kuma ina ganin Hammah ya shigo gidan ya fito daga gudu amma bai ko kalli inda nake ba, ganin haka na shiga na gaya wa Aunty motar taƙi tashi, haka ta fito ta kaini school ɗin.

Ina fitowa daga paper muna tsaye nida Feenah tana gaya mun ta gajji da zama ba kusa da Hammanta ba, nidai sai mamakinta kawai nakeyi don ga jinya tanayi amma hankalinta yana kan mijinta.

Muna tsaye na ƙura mata ido sai ga wata arniya mita ƙirar *CAMRY* ta shigo kai tsaye inda muke ta ƙaraso, dukkanmu saida muka kalli motan don wani irin shining ta keyi, duban da zanyi kawai sai ganin Hammah nayi zaune a cikin motan ya ƙura mana ido.

Ganin haka sai na kama hannun Feenah na jata har inda motanta take nace,  "ƙawata muje ji ajiye ni a gida don Allah, hiran mun nan ba zai ƙare ba yunwa nakeji, ga kaina yana ciwo sosai"

tana kallona da mamaki tace.

"ƙawata ba Hammah bane yazo ɗaukanki"? Tsaki naja nace, "rabu da shi zo mutafi, ya raina mun hankali yana son kuma sake raina mun, barshi yasan da mace yakeyi bawai mun rako mata ba", na buɗe na shiga, ganin haka ita ma ta buɗe ta shigo tana, "ƙawata a gyara mishi saiti toh".

Motan taja muka wuce gidan Aunty, har parlon muka shiga ta zauna na kawo mata juice tasha, muka ɗan taɓa hira kaɗan gani Aunty bata dawoba ya saka ta yimun sallama ta fito domin tafiya, har waje na rako ta inda motan ta yake, muna tsaye saiga motan Hammah ya kunno kai cikin gidan, ganin haka yasaka na mata sallama na juya da sauri na koma ciki.

Ina shiga na wuce toilet ɗin Aunty na cire uniform ɗina nayi wanka na fito, ina fito kawai naga Hammah zaune akan kujeran dressing mirrow, jinayi kaman na koma toilet ɗin har sai ya fita, amma ganin zai samu kaina yasa ni nuna kaman bangan shiba na wuce kan mirrow na ɗauki sure na fesa, jikina duk rawa yakeyi saboda towel ne ajikina.

Tashi yayi ya taho inda nake, ji nake kaman na ruga da gudu, amma na daure har ya ƙariso, ya juyani da ƙarfi na juyo kaman towel ɗin zai faɗo ƙasa, ina kallonshi nace, "me namaka"?

"tambayana kike don baki da kunya? Me kika mayar danine Fatima? Kin daina gaisheni, kin daina kulani sannan yau don tsabar raini kina ganina motarki taƙi tashi amma baki ce min komai ba sai kika je kika gayawa Aunty, Aunty ce take aurenki? Ko itace ta baki motan?.

Sannan kina ganina a school ɗinku kika maidani ɗan iska agaban kawarki kika wuce kika tafi? And yanzu kuma don raini kina ganina na shigo kikayi kaman baki san ina wurin bako? Meyake damun kine?"

Ƙwace hannuna nayi da ƙarfi na ɗan matsa kaɗan nace, "Kadena mun masifah son ranka Hammah, bayan duk irin girmama ka da iyayenka dana keyi baka gani? Kuma da kake cewa ba Aunty bace ta saya mun mota ba kuma ita bace take aure na toh ka ɓata,

Bari kaji matsayin ta, Aunty uwatace wanda haihuwa tace kaɗai batayi ba, amma yadda nake

jinta a raina ko wacce ta kawo ni duniya albarka, kuma daga yau kada kasake saka ta acikin shirmen mu ni da kai, don matsayin ta ya wuce tunanin mai tunani a wajena, kuma bari ka ƙarajin matsayinta a wajena, darajarta ne ya saka na aure ka babu musu ko tababa, kuma nake daraja mahaifiyar ka duk da sanin bata sona, domin girmanta da sanin ya kamatan ta ya sakani sadaukar da rayuwata don ranta yayi fari nayi niyyan auren ɗan'uwanka don son da take yiwa mahaifinku, na tsakani da Allah ya saka ta sonku, wanda nima har yayi sanadin son da nake muku da kuma girmama ku",  na tsaya da maganan na share hawayena daya ke ta zubo mun.

Shima ido ya zuba mun, sannan na cigaba da magana na, "Hammah nayi tunani zakayi mun uzuri a karo na farko ka nemi sanin me nayiwa mahaifiyar ka, kuma na ɗauka duk abinda ta faɗa zaka mata biyayyah a matsayinta na Uwa, amma ni kuma kamun uzuri don kasan bazan taɓayi mata raini ba Hammah, ko ban aure kaba ae Mama uwace a gareni domin abokiyar zaman Aunty ce, kuma mu an nuna mana daraja manya a duk inda muke koda bamu haɗa alaka dasu ba, amma ka rufe idonka ka koreni a ɗakinka, kuma kana tunanin na dawo inda kake Hammah Umar? Toh sam ka ɓata, ni Fatima zan maka biyayyah wuce tunanin mutum, amma bazai saka na zubar da ƙimata ta ɗiya mace ba, kuma daga yau ka kwana da sanin iyaye na masu daraja ne kuma dole ka daraja munsu yadda nake daraja maka naka, tsakainina kuma da Mama har abada girma take da shi a idona darajan Aunty na da kuma kai ɗanta dana ke aure, amma kada ka ƙara cimun fuska, don bazan ɗauka ba, abin yamun yawa gana Mama gana matarka gana ka?" saina fashe da kuka nakasa maganan.

Ajiyan zuciya yayi sannan yasaka hannun shi duka biyu ya jawoni jikin shi ya rungume ni ƙam ajikin shi, yakasa magana sai ajiyan zuciya kawai yakeyi.

Nima rungume shi nayi ina kuka ina faɗin, "Hammah nah bana son rashin kulawa, meyasa kake mun haka bana son haka Hammah, bayan kasan ina daraja Mama? Ka tambayi su Hammah Abdallah wlh ina zuwa kullum na gaisheta", na faɗa ina ƙara rungumeshi ajikina ina kuka.

A Kunne nah naji bakinshi yana cewa, "Baby kiyi haƙuri nayi laifi bazan sake ba , insha Allahu zan kiyaye kinji baby nah! amma kidaina barina irin haka Don ina shan wuya da rashinki".

Jin sun sasanta kansu Aunty tayi murmushi ta bar bakin ƙofan ta koma ɗayan ɗakin, don tun shigowar Hammah ta taho wurin.

#Vote
Comment
Share.

*KUKASANCE DA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYYAH*
*1441H/2020M.*

®☄
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION*✍🏻
{ _Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira._ }

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN ƘARFE*🏇🏽

Story and written
By
*_AUNTY NICE_*

*_WANNAN BOOK ƊIN SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Whatpad@GaskiyaWritersAsso.~

*page* 87--88

*_____________*📖A hankali na raba jikina da na shi, ina share hawayen daya zubu mun, shi

kuma ya ƙura mun ido yana ta kallona, can yace.

"Baby ina so ki tare kwanan nan", ya faɗa murya ƙasa-ƙasa, kallon shi nayi a tsorace nace, "Hammah sai nagama school ae", harara na yayi ya juya zai fita yana, "kima fara shiri zan yi magana da Aunty".

Har ya daɗe da fita ban iya taɓuka komai ba, duk hankalina saida ya tashi, ni yaya zanyi da Mama ne kam, zama a matsayin surkuwarta ma kaɗai fitina da damuwa ne.

Da daddare muna zaune a parlor muna kallon tarkon ƙauna Hammah ya shigo, bayan sun gaisa da Aunty shima ya maida kanshi kan TV yana kallon.

Muna gamawa yadawo da hankalin shi kan Aunty, ganin haka ta dubi su Khalifah tace subata wuri, ganin zasu tashi ya saka nima miƙewa zan bar wurin, da sauri Hammah yace ni na dawo na zauna.

Duk jikina rawa yakeyi domin bansan me zai ce ba, wurin yayi shiru kaman babu wanda zaiyi magana, sai zuwa can ya fara magana.

"Aunty dama maganan tarewar Fatima nake son sanin yaushe aka tsayar?" sauƙe idona nayi da sauri akan Aunty kaman zanyi kuka ina kallonta, itama kaman ta san ita nake kallo, ta kallo inda nake da saurinta, sannan ta maida kallonta kan Hammah tana ce mishi.

"Hamman su gaskiya ta wurinmu bamu wani tsayar da lokaci ba,don munfi so muji daga gareka tukun, saboda bamu san yayah shirinka yake ba", ta faɗa tana sauƙe idonta a kaina.

Shima cikin nutsuwa yace," Aunty indai shiri ta wurina ne babu matsala, don gaskiya ni nafi son ta tare nan da two weeks, don gidan da zata zauna ya riga da yaza ma ready,shiga ne kawai zasuyi, zan barsu dukkansu anan kowa tana da side ɗinta, amma a Abujazan tafida mace ɗaya,

zasuna canji, kaman idan ɗaya ta zo a hutu ɗaya sai tazo daga baya".

Ɗan murmushi Aunty tayi sannan tace hakan ma yayi daidai, amma maganan sati biyu bazance maka ehh ko a'a ba,domin akwai wanda zanyi shawara da su tukunnah ko"? Ta faɗa tana kallonshi.

Bayan 2dys aka tsayar da rana ƙarshen wata, bayan mun gama exams da 1wk, yanzu sauran sati uku kenan.

Haka akayita shiri domin ban fi kwana biyu ba, Baba ya zo ya ɗauke ni akan muje can gida hakanan tukun, muna can Aunty ta ƙaro mun da kayan gyaran jiki masu kyau, haka akayita gurzaki da kayan gyaran, ga kuma haɗin su riɗi da Ummu take bani nasha da nonon raƙumi, ga wataran za ayina kankana da mazarƙwailah. Kai abin dai yayi babu magana sai ido.

Tunda aka fara maganan tarewa nah Mama ta ɗaga hankalinta ta ɗaga hankalin ƴan gidan, ga gefe ɗaya Zainab ma Mama ta zugata itama ta ɓigyare da nata rashin mutuncin, don ana sauran 1week ma ta bar bauchi zuwa maiduguri.

Tana zuwa Mamanta ta tisa ta agaba da kwana biyu suka wuce Dubai, don tace duk laifin Maman Hammah Umar ne, da tana ji tana gani ta bari aka yiwa ƴar ta kishiya, don baƙin cikin ita an mata shiyasa ta saka ɗanta yayi.

Aunty Fannan tun saura 2dys ta iso bauchi, haka ma Umman su ma ta iso daga maiduguri harda ƴar uwarta mai bi mata.

Yusuf yaso zuwa amma firr Hammah ya hana shi, sai dai babu yadda ya iya matar shi ita ta biyo Aunty Fannah tazo, kuma kai tsaye gefen Aunty aka sauketa, gida ya cika da ƴan'uwa na maiduguri dana Jama'are, gasu Abdallah ma duk sun taho.

Can wurinmu ma ba a bar su Adda Hummy ba duk sonzo, babu yadda ba ayi dani akan ko walima na bari ayiba, amma firr naƙi, daga an takurani sai na saka musu kuka, dole Aunty tace abarni, ita idan an kawoni a matsayinta na uwar ango zata haɗa nata waliman a gidan su.

Hammah Haidar ne da dare yazo ɗaukan Feenah wanda muka wuni dasu ranan a gidanmu, domin ranan aka mana lalle da kitso, sai gashi ya shigo da wani jakan kaya mai masifan kyau, har parlon Ummi ya shigo yana jan troley ɗin.

Feenah ce ta tashi da sauri ta karɓe shi, ta jawo har gabana ta ajiye tana "ga kayan fitan biki da Hamman ki ya miki, ki duba kiga ɗunkunan ko sunyi kyau"?.

Da sauri Aunty ta jawo ta buɗe su, wayyo Allah kayane masu masifan kyau kusan kala shida, super biyu ɗaya mai golden, sannan laces guda biyu sun sha ɗinki na garari, sai wasu shegun riguna convenation na lace da shaddah ƴan senigalis, gaba ɗaya dadî ya kamani ina kallon shi fuskana ɗauke da murmushi nace.

"Hammah na gode Allah ya bar zumunci, Allah ya ƙara maka buɗi" duka ƴan parlon aka shiga mishi godiya da sanya albarka hattah Goggo saida tayita mishi addu'a, shidai banda danne-dannen wayan shi babu abinda ya keyi.

Washe gari mukayi wunin mu wanda gidanmu ya cika maƙil da ƴan uwa daga kafi gana ƴan jama'are ma sunzo, haka akayi taro lafiya, bayan anyi sallan isha aka ɗauke ni sai gidan Hammah nah wanda babu nisa dana su Aunty, don shi a Kaduna Road yayi gidan shi mai girman gaske, don side biyu ne a cikin farfajiyar gidan masu kyaun gaske.

Tunda mukaje nake kuka, babu abinda yazo mun a rai sai yau gashi an kaini gidan wani ba Besty nah ba, Kai Allah ya jiƙan Besty gaskiya nayi rashi sosai.

Wajrn ƙarfe goma Aunty tasaka su Feenah duk suka sake turara gidan, wanda tun daga ka yaanko hanyar gidan kake jin ƙamshi, bayan sun gama gyaran ne tace kowa ya fito a tafi, sannan ta sake jaddada mun akan maganan zuwa walima gobe ƙarfe goma na safe da za'ayi a farfajiyar gidansu, haka kowa ya watse aka barni dani da halina, kuma duk yadda naso muyi sallama da Feenah bai yiwuba saboda sama da ƙasa rasata na yi a cikin gidan.

Duk abinda akeyi ashe abin mamaki Hammah nah tana cikin gidan a ɗayan side ɗin daya kasance na Zainab, har saida yaga duk an watse tukun sai ya fito ya taho inda nake.

Tunda yazo naji hankalina ya tashi, domin ni idan ba magana yakeyiba tsoron shi nakeyi, domin kullum fuskarshi babu sakewa, haka ya shigo ya zauna a gefena bai ce mun uffanba, har zuwa jumuwa sannan yace.

"ki tashi kiyi wanka kiyi alwala muyi sallah", daga nan bai ƙara komai ba ya wuce ɗayan ɗakin, ganin ya daɗe da tafiya ya sakani tashi naje nayi wanka da ruwan turaren da Aunty ta bani tace yau zan fara amfani da shi, sannan nayi alwala na fito, ɗayan humran da tace kada na shafa ko wani turare sai shi.

Ɗauko shi nayi na shafah tun daga gashin kaina har cinyoyina sai dana shafe shi tass, sannan na ɗauko rigan bacci wando da riga na saka, ganin yadda manyan cinyoyina na da hips ɗina sukayi kaman zasu fasa wandon ya sakani ɗauko hijab na saka, dai-dai lokacin Hammah ya shigo ɗakin.

Duk sai naji ni na wani kiɗime kaɗan, haka na bishi yaja mu mukayi sallan, amma abin mamaki muna idar da sallan yana shafah addu'o'in da yaja mu masu yawa naga ya jawoni jikinshi da sauri, don har wani ɓari yakeyi.

Hijabina ya saka hannu ya zare, sannan ya ɗaga ni muka tsaya ya ɗan tsura mun ido kaɗan sai kuma nagan shi da sauri ya jawoni ya rungume tsam ajikin shi yana.

"Baby yayah zanyi yau? Yayah zanyi dake yau? Kinsan ton taushe nake sonki? Kinsan irin son

da nake miki?" ya faɗa sai shinshina wuyana yakeyi, daga baya ya saka harshenshi yana ta lashe mun guru-gurun wuyana, wanda duk saida yasaka jikina ya fara rawa nima.

Kaman a cikin mafarki naji ya ɗaga ni zuwa kan bed, cikin zafi-zafi yake bi dani, don duk inda ya samu ajikina lashewa yakeyi sai surutai yakeyi, nidai duk ya tsoratani na runtse idona kaman zan sume nake ji.

Sama-sama nake jin ringing ɗin wayan shi da yake waƙan, "wayyo Allah Mama nah! Wayyo Allah Mama nah!! Mama na my devoted Mama nah my desire"!.

Da sauri naji ya sassauta riƙon da ya mun, ya saka hannu ya jawo wayan, kaman wani mai tunani ya ƙurawa fuskan wayan ido, yana ta sauke ajiyan zuciya har wayar ta tsinke, bata ɓata lokaci ba kuma ta fara neman agaji.

Jikin shi yana rawa naga ya ɗauki wayan, cikin sallama ya yi magana kuma yana tambayan, "Mama ince dai lafiya kowa yake"? Daga ɗayan gefen naji muryan Mama kamar wanda yake handsfree tana cewa, "Umar! Wallahi ka yadda ka kusanci yarinyar nan bada izininah ba ban yafe maka nono nah daka sha ba, kaga irin baƙin cikin da yau ƴan uwan ubanka suka shuka mun? Toh wallahi ban yafe ba yau idan ka kwanta da yarinyar nan, kai har sai ranan dana baka izini, idan har kana son albarka na". Tana gama faɗi ta kashe wayan.

Ba Hammah Umar da ya saka salati ba hattah ni danake tsoron wani abu ya shiga tsakanina da shi sai dana razana, da sauri na taso na ƙaraso inda yake, domin ganin ihu yasaka ya riƙe kanshi da hannu bibbiyu yana kuka.

Bansan lokacin dana faɗa jikin shi ba na fashe da kuka ina, "wayyo Hammah na shiga uku, me nayiwa Mamane Hammah nah? Don Allah Hammah nah kada ka bari ta raba mu wallahi ina sonka", na faɗa ina ƙara rungumeshi gam-gam kaman za a ƙwace mun shi, ga wani kuka mai tada hankali da nakeyi.

Runtse ido yayi da ƙarfi yana faɗin , "Baby yau na mutu, baby yau Mamana ta kasheni da raina, yayah take so nayi da kaina. Baby na mutu ina xan kai kaina yau? Sannan ya sake fashewa da kuka yasaka hannu ya ɓanɓareni ajikin Shi ya kama hanyar fita a ɗakin yana ta haɗa hanya, har saida yaje bakin Ƙofa ya juyo ya kallen sannan yace.

"Baby kimun aikin gafara kiyi haƙuri har saina samu haɗin kan Mahaifiyata," sannan ya saka kai ya fita a ɗakin.Kuka na fashe da shi
ina jin zuciyata kamar zata fashe, toh menayi wa Matar nan ne?.

#Vote
Comment
Share.

*KU KASANCE DA ALƘALAMIM AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYYAH*
*1441H/2020M.*

®🖋
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION*✍🏻
{ _Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira._ }

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN ƘARFE*🏇🏽

Story and written
By
*_AUNTY NICE_*

*_WANNAN BOOK ƊIN SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Whatpad@GaskiyaWritersAsso.~

*_HUSSAIN 80K, BAKI BAZAI IYA FAƊIN ALKHAIRINKA BA, NAGODE DA SHAWARWARINKA GARENI, WANNAN SHAFI NAKA NE ƘAKINA, AUNTY NICE NA JINJINA MAKA_*

*page* 89--90

*___________* 📖Ranan nayi kwanan baƙin cikin da ban taɓa yin shi ba, nayi kuka har sai da naji hawayena ya kafe, ga zuciyata da take mun wani irin suya kaman zata kama da wuta nake ji.

Bansan wani hali Hammah nah yake ba, amma tausayin shi da nakeji ya ninka wanda nake yiwa kaina, ina jin kiran sallan asubah na tashi da ƙyar naje nayi wanka na ɗauro alwalah, raka'atul fajir nayi, sannan na bishi da aallan asubah, ina zaune ina azkhar naji an buɗe ƙofan ɗakin.

Da ƙyar na ɗaga idona da suka mun nauyi na dubi bakin ƙofan, bansan lokacin dana miƙe da hanzari ba na tsaya na ƙura mishi ido, domin sai da naji wani yankewar zuciya kaman kaina zai fashe naji, domin ba idon Hammah ba hatta fuskan shi a kunbure suke.

Da gudu na ƙarasa na faɗa jikin shi ina kuka nace, "Hammah nah me ya sami fuskan ka? Wani ya dake ka ne Hammah nah?" na ƙara ƙanƙameshi ina fashewa da kuka.

Bai iya ya rungumeni ba yadda ni na mishi, kawai jin muryan shi nayi yace, "Baby ina so ki rufa mun asiri kada wani daga cikin frirnds ɗinki ko ƴan uwanki ya fahimci halin da muke ciki, ki daure idan zakuyi waliman nan kada ki bada ƙofan da wani zai fahimci wani abu kinji my dear!" ya faɗa yana ɗaga ni daga jikinshi.

Kallon shi nakeyi duk hankalina a tashe da yanayin shi, ban iya buɗe baki nayi magana ba saidai ɗaga mishi kai danayi alaman naji, murmushin ƙarfin hali yayi sannan ya juya ya bar ɗakin.

Hawaye naji kaman zai zubo mun amma sai nayi ƙarfin halin mai dasu, jikina a sanyaye na koma kan sallayata na cigaba da miƙawa Allah kuka na, don nasan shi kaɗai ne zai iya yaye mun damuwata.

Ina kan sallayan har ƙarfe tara na safe, duk yadda naso bacci ya ɗauke ni abun ya gagara, sai wani masifaffen ciwon kai da nakeji kaman kan zai rabe gida biyu.

ina kan jan casbi naji kiran Aunty ya shigo wayana, da sauri na ɗaga na kai kunne na ina. "Assalamu alaikum. Aunty an tashi lafiya"?

cikin nuna kulawa ta amsa mun da lafiya sannan take ce mun na tashi nayi wanka yandu mai mun make-up tana hanya, da kayan da zan saka gaba ɗaya, cikin nutsuwa na amsa mata.

Ina tashi nayi hanyar toilet, na fi minti ashirin ina wanka, wai duk don idona ya koma dai dai, sai wanke shi nakeyi, ina fitowa naji sallaman matar tare da Mujaheed.

Har parlour na kaisu sannan na dawo nayi sallan walaha na fita zuwa wurinta, bamufi minti arba'in ba ta gama mun kwalliyata ba mai yawa ba, amma nayi kyau, gashi abinda nake tsoron bai faru ba, domin idona yayi kyau yayihaske kaman banyi kuka ba kwanan jiya gaba ɗaya.

Wani dogon riga ta saka mun na material piech sannan ta ɗaura mun Laffaya akai, nayi masifar kyau sai ƙanshin matan borna kawai nakeyi, a haka ta fito dani har waje, mota muka shiga sai gidan su Hammah, wanda duk hankalina yana kan ko zan ganshi amma shiru.

Muna isa naga canofy har uku, kuma kowanne cike yake da mutane daga ƴan office ɗinsu har ƴan kafin-madaki, Alƙaleri, Jama'are duk suna cike a wurin, ga ƙawayena maƙil a wajen har da su Ai Troble da take riƙe da ɗanta ɗan wajen six month.

Har wajen zamana Aunty ta kaini, lokacin kuma malama Juwairah ta fara buɗe taro da addu'a, sannan ta cigaba da sauƙe mana wa'azi mai taɓa zuciya.

Duk nasihanta akan biyayyan aure ne, da kuma kyautatawa ƴan'uwan miji, especially akan iyayen miji, kaman daga sama sai ga Hajiya Mama tinkis-tinkis ta shigo cikin fili kai tsaye wurin malamar ta wuce.

Karɓan micraphone tayi a wurin malamar, dai-dai malamar tana cewa, "toh jama'a ga mahaifiyar ango ko zata mana wani ɗan nasiha ne, toh Mama bismillah", ta faɗa tana miƙa mata.

Karɓa Mama tayi sannan tayi gyaran muryah ta fara faɗin, "Toh jama'a kundai ji abinda Malama tace ni mahaifiyar ango ce, toh Alhamdulillahi haka maganar take nice nan wacce ta haifeshi ta kuma fi kowa sanin ciwon shi da darajan shi, toh naji tana bayani akan biyayyan aure da kuma kyautatawa iyayen miji, wanda shine dadalin abinda ya tasoni na fito don nayi magana," sai tuja ta dubi inda nake, ta cigaba dacewa.

"Toh ƴan mata ko nace amaryah, naji daɗin yadda kina wurin kikaji ance ayi biyayyah wa miji da iyayenshi, wanda abin baƙin cikin shi ɗana bai dace da mace mai tarbiya ba da kamun kai, don da ina damuwan na haɗa zuriya da masu shegen asiri da mugun kissa ashe duk abin ya wuce nan, abin baƙin ciki jiya bayan an kai amaryah bai daɗe ba sai naji wayan ɗana ango, bayan na ɗauka sai naji shi yana ta kuka yana cemun shikan an cuce shi ashe matar da aka liƙa mishi yayi biyayyah ya karɓa sauran wani ne, don shidai bata kawo mishi budurci gidan shi ba, da ƙyar na hana shi sakinta a daren jiyan nace ya bari yau yazo iyaye suyi zama akanshi, idan kuma baku yadda ba ku shiga side ɗinshi na gidan nan ku duba shi, tun asuba yazo yake ta mun kuka, da ƙyar na lallaɓa shi ya shiga ya kwanta, toh jama'a ku tayi ni roƙon uwar goyonta data karyah asirin da tayiwa mahaifin yaron idon shi ya rufe ya haɗa wannan auren da ya raba baki alaikum, ko kuma na kai kara ga hukuma don a raba ɗana da raƙai".

Juyowa tayi kan Aunty tana riƙe da abin maganan ta cigaba da faɗin, "na haɗaki da Allah ki raba ɗana da muguwar ƴarki mai mugun ɗabi'a, ɗana yana da matar shi ƴar asali masu tarbiya da arziki bama su kwaɗayin abin duniya ba" ta faɗa tana kuka.

Da ƙyar nake jan numfashi na don lokaci ɗaya naji ta mun ƙaranci, ina cikin haka naga Aunty ta taso ta riƙo ni na miƙe tsaye, sannan ta dubi Mama tace, "idan ɗanki wani abu ne kije kijiƙa shi

ki shanye, insha Allahu Riyyah tabar zuriyar ki har abada, shi kuma idan ɗan halak ne acikin ki ki saka shi yazo ya sake ta", sannan taja hannuna muka shige cikin gidan muka bar jama'a da suke ta hayyah hayyah.

Mama tana juya wa fuskanta ɗauke da murmushi kawai taji sauƙan mari a fuskarta, da sauri ta ɗago kanta kawai saitayi arba da Ummanta gefenta kuma Aunty Fannah ce itama ranta a ɓace, Ummah na kallonta tace.

"idan Umar ya saki Fatima, ke kuma kije na yafeki duniya da lahira, kuma nono na da kika sha ban yafe miki ba" sannan ta juya ta fita a gidan Aunty Fannanh na binta a baya.

Hammah nagani kan varandan su ya ƙura wa su Mama ido, sai hawaye ne yake zubo mishi, da kyar ya ɗaga ƙafan shi yabi bayan su Ummah.

#Vote
Comment
Share.

*KU KASANCE DA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYYAH*
*1441H/2020M.*

®✍
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION*✍🏻
{ _Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira._ }

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN KARFE*🏇

Story and written
By
*_AUNTY NICE_*

*_WANNAN BOOK ƊIN SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Whatpad@GaskiyaWritersAsso.~

*_Gaskiya writers wannan shafin kyautane na bawa duk wata member dake gidan, sannan ina miƙa saƙon gaisuwa ta musamman wa ɗiyata Neat lady da innaro, gaisuwan ku da bance na muku_*

*page* 91---92

*______________*📖Duk yadda yaso ya tsayar da hawayen shi abun ya gagare shi, har inda su Ummah suke tsaye ya ƙarasa, bai iya ya furta musu komai ba sai hannun shi da yasaka ya riƙo na Ummah yana ta sheshsheƙan kuka, ɗayan hannun kuma ya rufe fuskan shi da shi.

Aunty Fannah da ta kira number driven ta akan ya fito su tafi, itama hawayen take zubarwa, haka zalika Umma ma kukan takeyi, babu wanda yace uffan har drivern ya ƙara so inda suke yayi parcking.

Aunty Fanna ce ta saka hannu ta riƙo na Umma akan su shiga mota su tafi, wanda ko kayan su

ba suyi tunanin ɗauka ba, jiki na rawa Hammah ya sake damƙe hannun Umma idon shi yana kallon Aunty Fannah yana ta girgizama ta kai alaman kada su tafi.

Share hawayenta tayi ta juya wurin shi tace, "Umar kada ka hana mu tafiya, tafiyan ne kawai zai saka zuciyar mu ta sanyayah, sannan ina mai kara tabbatar maka da kada ka sake matar ka, kajira zuwan Babanka tukun duk abinda ya ce maka akai sai kayi aiki da shi, sannan ta saka hannu ta jawo na Umma suka shiga motan.

Da ƙyar yaja ƙafan shi ya koma cikin gidan, bai tsaya komai ba ya ɗauki motan shi ya fita ya bar gidan, kai tsaye gidan shi ya wuce inda kai tsaye ya wuce toilet don wani irin zafi da ɗaukewan numfashi ya keji, haka yaje ya sake ruwa mai sanyi akanshi.

Muna shiga ɗakin Aunty ta kwantar dani akan gado sannan ta juya ta rufe ɗakin ta fita, babu ɓata lokaci ta sallami dukkan bakin da ta gayyata, sai da taga kowa ta tafi gidan daga ita sai Goggon mu da Mummy tukun ta shigo ta buɗe ɗakin da nake suka shigo, kuma har zuwa lokacin da ake ƙiran sallan azahar ban bar kuka ba, ga wani numfashi na da nake ji kaman zai ɗauke.

Kowar su wuri ta samu ta zauna fuska a murtuke, Aunty naji ta fara magana tana, "Riyyah don Allah zuwa yanzu kukan naki ya isa haka, ki bar ta da sharrinta ni dai nasani kuma kema kinsani babu abinda muka koya miki sai tarbiya, saboda haka sharrinta akan ta zai tsaya".

Shiru nayi da kuka na sai ajiyan zuciya kawai da nake tayi, sannan na maida hankalina inda naji Goggo tana cewa Aunty zata wuce dani gidanta, duk wani shirgina ta aiko mun daga baya.

Mummy tana amsawa da, "wallahi wannan shawarah yayi dai-dai, kuma Abba ya kawo shawarah mai kyau, insha Allahu sai ta zubar da hawayen abinda tayiwa baiwar Allah, an gaya mata ita kaɗai ne ta fara haihuwa? Idan da badan iko na ubangiji bama da kuma kowa da irin rabonshi ae da yanzu Riyyah tana gidan Kamal inda babu wanda ya isa ya takurata ko yagaya mata banzan magana" Mummy na magana tana miƙewa ranta a matuƙar ɓace da niyyan tafiya.

Ina ji ina gani Goggo ta riƙoni muka fita, inda Aunty ke binmu a baya ranta a ɓace ko magana ba ta iyayi, har inda motar Mummy yake  ta raka mu, muna shiga babu ɓata lokaci muka fita a gidan, har kofar gidan Goggon mu Mummy ta kaimu, sannan ta dubi Goggo tace.

"Goggo duk yadda Alhaji Nuhu zaiyi ya lallaɓeku kada a baru Riyyah ta koma har sai yayi kyakkyawan tsakani wa Mama da ita", Goggo na girgiza kai alaman haka za ayi sannan tace.

"Ni ɗan na tane ma bana son auren da shi yanzu, taga idan an bar mata ɗan ƴar mu zata rasa mijin aure ne? Mu da muke da ɗiya Allura cikin ruwa, don kawai Allah ya ƙaddari rabon ƴaƴan tane ƴar shine zata kawowa mutane ɗibar albarka? Toh taje ta riƙe ɗanta muma zamu riƙe ta mu ɗiyar kuma zata san tayi da fullo".

Haka sukayi sallama muka shige gidan, niko sallama banyiwa Mummy ba na shige cikin gidan, inda a parlour muka tarar da Bappah da Abban Bauchi zaune sun dawo a mosque.

Ko tsayawa gaida Abban banyi ba na wuce ɗakin Gogggo nah, ina jin Abban yana cewa Goggo, "yauwa kun taho tare ko? Yanzu ne zaso san sun taɓa ƴar gata, ce musu akayi talaucin haukane? ko ance musu wani abu muke na a wurin su? Ni wallahi banga wani dalili da zaisa a bar yarinyar nan tayi rayuwa da wanda basu san mutuncin mutane ba, amma zasu san sunyi da iyayen da suka san darajar ƴar su", yana yi Goggo na ƙara taya shi, tun ina jin su bayan na idar da sallah har bacci ya ɗaukeni na daina jinsu.

Mama tana komawa parlourn ta , ta haɗu da maƙwociyar ta Hajiya Asabe zaune wanda duk abinda akeyi da zugin ta a ciki, Mama na shigowa ta miƙe ta isa wurin Mama tana cewa.

"Hajiya Zahra kin mun dai-dai da kika fallasa su a bainar jama'a, kunga ae yanzu duk wani asiri da uwargoyon nata tayi zata je ta karya, sannan abinda Umma ta miki kuma kibar shi kawai ae Umma uwace kuma zata sauƙo, idan kun shiryah kin nemi gafarar ta sai kisaka shi Umar ɗin ya sake shegiyar mai baƙar fuskan".

Ita dai Mama sai huci ta keyi, tana jin kaman ta ɗauki wuƙa ta tafi gefen Aunty ta luma mata ita da baƙr ɗiyarta da suka zama mata annoba, a tunaninta.

Tsaki ta ja mai sauti sannan ta dubi Hajiya Asabe sannan tace, "hmmm Maman Najwa bazaki gane bane, wallahi tun ranan da Baban su twins ya auro matar nan nayi sallama da farin ciki da kwanciyar hankali a rayuwata, ga shi ta ɗauke mun hankalin miji, ga na ƴaƴana ga na ƴan'uwa na, sannan abin baƙin cikin kuma ƴar dana fi tsana a zuriyarsu a ɗauko a haɗa mun da ƴaƴana?"

Hajiya Asabe ta sake matsowa kusa da ita ta rusuna sosai tace, "shiyasa nace mu haɗa auren Najwa da ɗaya daga cikin su twins, kinga tunda towu na mai nane zaki samu kwanciyar hankali ta wurinta, don kindai san kina da iko akan Najwa kaman ƴar da kika haifa acikin ki take, tunda itama ɗiyar ƴar'uwar taki ba share miki kuka sukeyi ba, ga kuma wannan da gara kowa da ita" ta faɗa tana murginawa gefe.

Tsaki Mama taja sannan tace, "ni wallahi Hajiya Asabe na rasa me yake damun Zainab da Uwata su gaba ɗaya rayuwar kansu kawai suka sani, amma na wani ko ohoo suke gani".

"Hajiya Zahra yanzu me muke ciki ne game da maganan yaran"? Hajiya Asabe ta ƙara jeho maganan.

Mama na kallonta tace, "yanzu dai babu yadda zance tunda ban kashe wancan wutan bama, kawai ki na turo ta gidan nan ko Allah zaisa ɗaya daga cikin su yaji yana sonta, inaga hakan shi zaifi sauƙi".

Haka sukayi ta hiransu har aka ƙira sallan azahar inda Hajiya Asabe ta wuce gidanta.

Lokacin da Baba yadawo kai tsaye ɗakin Aunty ya wuce, har lokacin fuskan Aunty a murtuke yake, ko alaman fara'a babu a fuskanta, Baba yana shigowa ya tsaya a bakin ƙofan yana binta da kallo a nutse yace "Fatima me yake faruwa ne a gidan nan"?.

Juyo tayi fuska babu annuri tace, "ban fahimci tambayan da kakeyi ba? Wani abu ne ya faru"?.

ƙarasuwa yayi cikin ɗakin ya zauna a gefenta, idon shi yana cikin nata yace, "bangane me kike cewa ba? Ɗazu Hajiya Addayo take ce mun na dawo gida ya hargitse, yanzu kuma ina tambayanki kina tambayana"?.

Kallon shi tayi ta gefen ido bakinta a ɗane tace, "kamata yayi ta gaya maka wacce ta hargitsa gidan ita ka tuhumeta bani ba", ta faɗa tana kawar da kanta gefe.

Cikin mamaki da abinda Aunty tayi ya ɗauko wayanshi ya ƙira ƴar'uwar shi Hajiya Addayo, tana ɗauka yace.

"Addayo ni me yake faruwa ne ɗazu kike gaya mun"?....... Bayanin abinda ya faru tunda ga fitowan Mama har tafiyan su Umma bata ɓoye mishi ba, shi kuma sai kaɗa kai yake kaman ƙadangare, tana gamawa ya maida wayan aljihun shi sannan ya dubi Aunty yace.

"Kinji abinda ta sanar min ko? Toh ke nake so naji ta wurinki da kuma ina ki ka kai matar mutane"?

Tashi Aunty tayi ta tsaya ta riƙe kunkuminta bayanta tsuke idon ta tana duban shi tace,
"matar mutane kake tambaya? Wacce matar kuma waye mijin? Idan baka da abincewa ka tafi wurin wacce ta haddasa fitinan ta gaya maka ina ƴar mutane take?

Domin Riyyah haihuwarta mukayi bawai tsintar ta mukayi ba, kuma tana da gatanta bawai mun kawo ta don bamu sonta bane, yadda matarka tace ƴar mu bata kawo mutuncinta gidan aurenta ba yadda ɗanta ya sanar mata, toh ta saka ɗan nata ya rubuta mata takardar ta, mukan mun yadda da tarbiyar da mukayi, kuma insha Allah ƴar mu zata auro.

amma zama da ɗanta kam ko shine autan maza mun barshi, taje ta jiƙa ɗanta tasha, don naga

alamar idan ta samu sarari auren ɗan nata ma zata iya yi saboda wannan kishin bana hankali bane".

Ko gama rufe baki Aunty bata yiba taji sauƙan mari a fuskanta, jikina rawa cikin ihu ta juya tana kallon Baba da yake ta hucci shi kaɗan shi yana hararanta.

Idonta yana zubar da hawaye tace, "nika mara"?

"Ehh an mare ki ɗin, ko zaki rama ne? Haba mata duk wani halin da bana kiba kin ara kin ɗaurawa kanki", ya faɗa yana kallonta kaman zai mareta yake ji.

"Wallahi Baban su bazata saɓuba, don wallahi ba zan ɗauka ba, ta yayah za ayi wani da laifi wani da shan duka? Saidai kawai idan rashin adalcin naku ne na maza yau ya mutsa ta kaina, toh bari kaji bazai taɓa yiwuba, kuma yau ya kasance rana na farko kuma na ƙarshe da hannunka zai sake hawa kan fuskan na da nufin mari, sannan kuma Riyyah ƴar muce kuma ikon muce, bazata zauna da ɗanku ba, kuje can ku nema mishi mai mutunci, mu kuma ku zuba ido kuga wa zamu bawa ɗiyar mu".

Tana gama faɗin maganar ta ta juya ta wuce toilet tana kuka mai cin rai, Baba da ido ya bita bakin shi a buɗe, yana mamak8n yau Fatima ce ta ke tsulah mishi rashin kunya? Lallai Zahra ta kaita ƙarshe, amma duk da haka ae bai kamata ta mishi haka ba, saboda ae shima Riyyah ƴar shi ce, amma babu komai bari yaje ya samu Maman tukun, haka ya juya ranshi a ɓace ya tafi side ɗin Mama.

#Vote
Comment
Share.

*KU KASANCE DA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYYAH*

*1441H/2020M.*

®☄️
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION*✍🏻
{ _Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira._ }

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN ƘARFE*🏇

Story and written
By
*_AUNTY NICE_*

*_WANNAN BOOK ƊIN SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Whatpad@GaskiyaWritersAsso.~

*page* 93--94

*____________*📖Yana shiga side ɗin Mama ya samu tana fitowa daga kitchen zata wuce ɗakinta, nuna ta yayi da yatsan shi yana zare ido yace.

"ki tattare kayanki na baki minti talatin ki bar mun gidana, tunda ban isa da ke ba, kinje kin zubar mun da mutuncina a idon mutane, kin ɓata rayuwar ƴaƴanki a idon duniya, yanzu a tunaninki akwai wanda zai so bawa sauran yaranki ƴa su aura? Babu wanda zai si haɗa zuriya da ke idan yasan ciwon kanki".

Nuna mata hanyar ɗakin yayi yana, "wuce mana kin tsaya kin zuba mun shegun idonki na rashin son zaman lafiya"

"Allah ya shiryeki Zahra tun da ƙuruciyar ki nake fama da ke, amma har yau baki gyara ba kuma baki duba mutuncinki dana iyayenki ballantana mijinki, saboda haka kafin kiyiwa ɗana baki ki fita ki bar mun gida na na sake saki ɗaya, na laifin da kikayi a bainar jama'a, idan kuma kin saka ɗanki ya saki matar shi Fatima, toh kije na ƙarisa sauran biyun ma".

Yana faɗin haka ta saki ihu iya ƙarfinta, wanda har sai da wurin ya amsa,shi kuma ya saka ƙafa ya fita a parlour.

Faɗuwa Mama tayi a wurin tana kuka, da ƙyar ta ɗauko wayanta tayi dialing number Ummanta, amma abin mamaki sai da tayi misscall goma bata ɗauka ba, sannan ta maida kan na Aunty Fannah ita ma taƙi ɗauka, har saida Mama ta gajji ta haƙura, har ƙasa ta sunkuya tana kuka.

Daga baya ta ƙira Hammah shima firr yaƙi ɗauka, tana kuka tana kallon fuskar wayan hankalinta a tashe tana mamakin abinda Umma da Hammah da Aunty Fannah suka mata.

Daga baya ta kira Abdulrahman yana fara ringing kuwa ya ɗauka, daga ɗayan gefen muryan shi a ɗan murtuke ya amsa mata da "hello Mama".

Tana ƙara muryan kukanta tace, "Abdul Babanku ya sake ni yanzu kuma yace ya bani minti talatin na bar mishi gidanshi, Abdoul na ƙira Umma na da Fannah sunƙi ɗaukan wayata, Hammanku ma yaƙi ɗaukan wayata, nashiga uku Abdoul yayaj zanyi yau kam, wallahi Fatima da ƴarta sun cuceni, sun rabani da mijina da uwata da ƴan'uwa na da ɗana".

Ajiyan zuciya Abdoulrahman yayi, duk da baiji daɗin sakinba amma har ga Allah yasan an ƙure Baban shi ne, domin yasan irin haƙurin da yake da Mamansu, sannan kuma yasan tana shiga hakkin ƴaƴanta, duk da rasuwar ɗanta bai saka ta ladabta ba, toh meye zai girgiza zuciyar Mama?.

Shiru yayi yana sauraran kukanta da yake ji har cikin ranshi, da ƙyar ya buɗe baki yace.

"Mama gaskiya ni ɗanki ne amma kuma zan gaya miki gaskiya, abinda kikeyi baki kyautawa ko kaɗan, ko daga rasuwar Hammah Babagana ya kamata ki haƙura da abinda Allah ya hukunta, sannan ae bai kamata ki yi abinda kikayi a cikin mutane ba, ko don darajar mu ƴaƴanki da mahaifiyarki da take wurin, ɗazu Ummah ta ƙirani bakiji irin kukan da takeyi ba, wallahi sai da hankalina yayi mummunan tashi, ga Hammah Umar ko amsa wayar mu yakasa, toh Mama me kike so ne? Kinfi so idan da rabo ki mutu a haifah? Gaskiya Mama shawara zan baki a matsayina na ɗanki kawai ki barwa Allah ya yi ikon shi, don baki isa ki hana abinda ya nufa ba, saidai ki shiga matsalah wanda muma ya iya shafan mu".

Mama babu yadda ta iya, don ita dai bata ji har gobe zata so Aunty da zuriyarta ba duk abinda zai faru, saidai bata san yayah zatayi ba, don tana son ƴaƴanta ba kaɗan ba.

Cikin muryan kuka tace, "toh Abdoulrahman ka bawa Babanku haƙuri, ban san inda zanje ba nikan, don Allah kuma ka nema mun Hammanku ya taho ya ɗauki matar shi ko Babanku zai barni na zauna",  ta faɗa tana kuka kaman ranta zai fashe.

Ajiyan zuciya yayi sannan yace, "Mama toh don Allah ki kwantar da hankalinki ki dena kuka, ko ban samu Hammah ba zan nemi Abdallah yazo mu sami Baban muga abinda zamu iya akai".

Haka sukayi sallama ita da Abdoulrahman, ɗakinta ta wuce ta kwanta ta cigaba da neman wayan Hamman.

Saida Goggo ta mun jan ido tukun na bar kukan dana keyi, ta nuna mun idan ban bata haɗin kai ba ta yayah zasu karɓa mun ƴanci na? Haka na haƙura na bar kukan na tayata muka shiga kitchen.

Ana sallan ishaa sai ga Baba yazo wurin Abban Bauchi akan maganar mu da Hammah, amma babu yadda Baba bai yiba Abba ya hana tafiya da ni, yace sai Maman da kanta ta amince kuma tayi alƙawarin babu ita babu sake shiga rayuwar Riyyah tukun su duba suga yadda za ayi, ran Abba a ɓace  yace.

"Maganan gaskiya Alhaji Nuhu abinda matar nan tayi ya wuce rainin hankali ya koma rashin mutunci da rashin sanin mutuncin mutum, abinda ya mun zafi shin arziki da talauci kam bana

Allah bane? Kuma kalmar bata kai mutuncinta gidan ɗanta ba, har tana bada tabbacin shi da bakinshi ya faɗa mata ae kaga zance ya lalace, gaskiya ranmu ya ɓaci tunda duk irin haƙurin iyayenta abin saida ya ɓata musu rai har auren ya fita a ransu".

Baba duk sai yaji ya muzanta a wurin gaba ɗaya ranshi ya ɓaci, ranshi a ɓace ya dubi Abba yace.

"Alhaji na fahimce ka kuma insha Allahu komai zai dai-daita, don yanzu ma na sauwaƙe mata aure na igiya ɗaya akanta, kuma na bata tabbacin idan ta dage har ɗanta ya saki matarshi toh itama na ƙarasa sauran biyun da suka saura akanta, kuma maganan Riyyaj bata kai mutuncinta gidan aurenta ba duk sharrin tane.

Domin na ƙira ɗan nata na tambayeshi ya gaya mun gaskiyar abinda ya faru, ita mahaifiyar tashi ce ta ƙirashi tace idan ya kusanci matar shi bata yafe mishi ba, shine hankalin shi ya tashi tun bayan ya idar da sallan asubah ya taho wurin uwar yake neman gafarar ta akan tayi haƙuri ta barsu, shine fa ta fake da wannnan shirmen".

Yana gama faɗa Abbah yace, "subhannallahi, Alhaji Nuhu baka kyauta ba daka sake ta, ita mace ae har ta tsufah bata hankali, meyasa ka biye mata? Gaskiya ina mai baka haƙuri daka janye wannan sakin don Allah, ko duba da yaran da yake tsakani, ita kuma sai addu'an Allah ya shiryeta kawai zamuyi".

Haka suka cigaba da tattaunawa a tsakanin su, daga baya Baba ya ƙira Hammah Umar yace mishi duk inda yake gobe ya dawo.

Haka Baba da Abba sukayi sallama, bayan Goggo tazo sunyi sallama ya bata haƙuri, amma tana ta fara'a tana ba komai, haka Baba ya fita ya wuce gida.

Baba har ɗakin Aunty ya wuce, yana shiga ya samu tana saka kayan bacci a jikinta, kallo ɗaya ta mishi ta juya kanta gefe ta cigaba da abinda takeyi.

Girgiza kanshi yayi ya ƙarasa har inda take, a hankali ya saka hannu ya juyo da ita gabanshi, ƙoƙarin ƙwace kanta ta fara, shidai baice mata komai ba si ƙura mata ido da yayi yana kallonta.

Da taga takasa ƙwacewa kawai sai ta fashe da kuka, yana jin ta fara kuka kawai ya jawota ya rungumeta a jikinshi, ita dai Aunty kuka kawai ta keyi.

Sun daɗe a tare bai ɓanɓareta a jikinshi ba yace, "toh meye na kukan kuma?

Kina tunanin abinda aka muku bai taɓa zuciyana bane? ae komai lalacewa zuciya tasan mai kyautata mata, kuma nasan ke da ƴan'uwanki kun daɗe kuna nuna mun hallaci nida ƴaƴana, kin kasa fahinta nane kawai Fatima banso kika ce komai ba akai, ta yayah ma a kan idona zaki kwatanta ɗa da uwarshi a matsayin ma'aurata? Kina ga kin mun adalci?"

Tana kuka tace, "toh bakaga ɗiyar mu ta ɓata a baina jama'a ba, ta nuna wa duniya ƴarmu ba ta kai mutuncinta ba, kuma tana bada tabbacin ɗan tane ya faɗa mata, ta yayah shi Umar ɗin zai mana haka?"

Ɗago da kanta yayi yana kallon idon ta yace, "duk da haka bai kamata ki faɗa mun haka ba, tunda har na tambayeki ae so nake naji kan maganan, ae angaya mun tukun na tambayeki me ake ciki, da sai ki gaya mun, itama naje na tambayeta naji mai zata ce, kinga sai kijira kiga matakin da zan ɗauka kafin ki ɗau mataki akai, ae ni a tunanina inaga ni Zahra ta ciwa mutunci kuma na ɗau mataki, don yanzu ma na sake ta, kuma idan ta matsa Umar ya saki Riyyah toh itama zan kara sa biyun da ya saura, idan ya so a samu zaman lafiya ta kowani gefe."

Da sauri Aunty ta dube shi tace, "me yasa zaka saketa? Gaskiya haka bai kamata ba".

Yana kallon idonta yace, "toh ku bashi matar shi idan yaso sai itama na yafe mata".

"toh kace yazo ya bamu tabbacin ɗiyarmu takai mutuncinta gidan shi kafin mu bashi ita, sannan kuma a musu tsakani da matarka don gudun gaba", ta faɗa tana saka hannun ta tana ture ɓashi daje kafaɗanta, sannan tace.

"Kuma kada ka sake marina akan matarka", dariya Baba yayi kaɗan sannan yace, "ƙorafi ya

karɓo madam, shima kuma Umar gobe zai dawo insha Allahu, kuma zamu bada haƙuri mu kiyaye".

Washe gari su Abdallah ne suka fara isowa wurin azahar, Hammah kuma sai wajen la'asar tukun ya iso, ko kallon gefen Mama bai yiba ya buɗe gefen shi ya shiga batare da ya kula kowa ba.

#Vote
Comment
Share.

*KU KASANCE TARE DA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYYAH*
*1441H/2020M.*

®☄
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION*✍🏻
{ _Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira._ }

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN ƘARFE*🏇🏻

Story and written
By
*_AUNTY NICE_*

*_WANNAN BOOK ƊIN SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Whatpad@GaskiyaWritersAsso.~

*page*  97--98

*___________*📖Suna shiga da gudu-gudu sauri-sauri ta ƙarisa bakin gadon, yaye bargon tayi ta ƙurawa mun ido yadda nake ta ɓarin sanyi, ga wani zazzaɓi mai zafi da ya rufe ni, idon ta ne ya sauƙa akan bedsheet ɗin daya gama ɓaci da jini kacha-kacha.

Hannu Aunty ta saka don ta jawoni, bansan lokacin dana kurma wani ihu ba, har saida yayi sanadin shigowan Hammah da gudu, tsayawa yayi daga bakin ƙofah yace, "Aunty yayah take ihu"?.

Mama ce ta juyo cike da masifah tace, "ba dole tayi ihu ba, duk ka yagalgala musu yarinya, Allah dai yasa baka haɗata da yoyon fitsari ba, dubi rashin imanin da kayi akan yarinya Hamman su",  ta faɗa tana bin shi da hararah.

Bai sake ce musu komai ba ya juya ya fita ya bar ɗakin, Aunty ce ta taimaka ta kaini toilet ta mun gyara na musamman, bayan ta taimaka mun nayi wanka muka fito ɗakin, inda muka samu Mama ta yaye bedsheet ɗin ta fita da shi, bayan nasaka kaya ne, Aunty ta riƙo hannu na muka fito domin tafiya side ɗinta, sai buɗe ƙafa nakeyi hawaye yana bin fuskana.

A parlour muka haɗu da Mama tana ta yiwa Hammah faɗa, ganin fitowan mune yasaka duk suka juyo suka zuba mana ido, Aunty ce ta dubi Hammah tace.

"Bari muje asibiti zan mata ɗinki",  kanshi ya ɗago da sauri ya dube ni, fuskan shi cike da tsoro, Mama ce da sauri ta amsa da.

"Ba dole a mata aiki ba, irin wannan haukan da ya sauƙe kaman a filin daga, kai wallahi kagyara halinka, ce maka akayi abinci ce da ka kusan cinyeta duk"?.

Bayan Aunty ta mun ɗinki ne muka dawo gida, kai tsaye side ɗinta ta wuce dani, inda ta shiga kula dani kaman wacce na haihu, nidai gaskiya ban san meya ke damuna ba, babu hali na tuna abinda Hammah ya mun sai nayi kuka, don wallahi yaci zalina.

Haka Hammah ya dinga jelan zuwa dubani har na warke garau amma Aunty batayi maganan komawa na ba wanda sai naji na samu nitsuwa har hankali na ya kwanta.

Sai da na ƙara sati biyu bayan na warke tukun Baba ya saka baki na koma gidana, don wannan karon Hammah yana ɗauka na mukayu side ɗin Mama, tana ganinmu tace.

"wallahi baka isa ku zauna mun a ɗakina ba, ka wuce da ita gidanka, kalan kaje wannan karon ta yage ka tara mun fitinannun iyayenta? Wancan ma nayita addu'a kada kakanta yaji labari, don ba kai ba hattah ni sai ya lakaɗawa duka, don tsohun soja ne marar imani".

Hammah tunda muka shiga mota yake ta tuntsura dariya wanda bansan dalilin shi ba, nidai banda faɗuwar gaba babu abinda nakeji, sai mamakin abinda yake saka shi dariya kawai nakeyi.

Har muka isa gidan bai daina dariyan shi ba, muna isa naga yadda gidan yasha gyara, ga wani ƙamshin turare da yake ta tashi a kowane side na gidan, kasancewar tun jiya Aunty ta saka masu aikinta suka je suka gyara gidan, yau kuma tun safe suka je suka saka turare suka shimfiɗa bedsheet a ɗakunan, gida dai yayi kyau abin sha'awa.

Nidai gaba ɗaya tunda muka dawo a tsorace nake, amma sai naga Hammah shi ko nuna ya damu da abinda nakeyi baiyi ba, haka dai na shiga ɗakina, amma nakasa taɓuka komai na zauna a bakin gadon nayi tagumi.

Ina zaune a haka har aka ƙira sallan magarib amma nakasa tashi na taɓuka komai wa kaina, abin mamaki ina zaune har aka idar da sallan a masallaci inaji amma ban iya tashi ba, don wani irin faɗuwar gaba kawai nakeji, ina haka sai naji an buɗe ƙofah an shigo ɗakin.

Da sauri na ɗago kaina ina kallon mai shigowan, Hammah ne yake tsaye a bakin ƙofan hannun shi riƙe da hannun ƙofan ya ƙura mun ido.

Ganin kllon da yake mun baiyi magana ba, ya saka ni miƙewa da sauri nayi hanyar toilet, da sauri ya ƙira sunana yana faɗin, "kaddai bakiyi sallan magarib ba"?
bance komai ba na buɗe ƙofan na shiga da sauri na.

Bayan na idar ne na zauna ina azkhar, ina cikin yi naji an ƙira sallan ishaa, Hammah ya sake shigowa yana kallo na yace.

"yanzu kam ki tashi kiyi sallan isha kafin na dawo", sannan ya saka kai ya fita.

Ina idar da ishaa na ɗaura shafa'i da wuturi, ina zaune har lokacin ban tashi ba, na sake jin buɗewar ƙofan, da sauri na sake ɗago kaina na kalle shi, shima yana kallo na, can ya juya baice komai ba ya fita.

Na kai kusan minti ashirin a haka naji shigowar mota gidan, har zuwa wani lokaci Hammah yazo ya ƙirani na fito muci abinci, duban shi nayi kaman zanyi kuka nace.

"Hammah bana jin yunwa, kaina ne yaje ciwo", dariya yayi ya juya ya fita.

Har naji hankalina ya kwanta sai kuma gashi ya dawo hannun shi ɗauke da pilet cike da ferfusoup ɗin kaza, ɗayan hannun kuma ɗauke da cup daya cika kunun aya da yaji kayan ƙamshi dasu dabino a ciki, har inda nake yazo ya zauna.

Yana kallo na yace, "gashi bana son wani musu ko jayayya, duk ki cinye ki ajiye mun pilet ɗin", sannan ya tashi ya fita a ɗakin yayi parlour.

Babu yadda na iya haka na saka naman a gaba na cinye shi, don ya mun daɗi gashi kana fara ci zaka san girkin Aunty nane, haka naci na shanye kunun ayan, sannan na ɗauki pilet ɗin da cup ɗin na fito domin na kai kitchen.

A parlour na wuce Hammah yana cin nashi abincin, bayan na kai na  fito ne naji ya ƙirani, ina zuwa yace na zauna a gefen shi, babu yadda na iya haka na zauna jikina yana ɗan rawa, ganin yadda na zauna a ɗan ɗufane ya juya ya kalleni kaɗan, sannan ya jijjiga kanshi ya maida kanshi kan kallon da yakeyi yana cin naman shi.

Can naga ya zuba kunun ayan a kofi ya miƙo mun, kallon shi nayi kaman zanyi musu sai naga babu fuskan hakan, da sauri na saka hannu na karɓa, kafa kaina nayi sai dana shanye tukun na ajiye mishi cup ɗin.

Hannu na ya riƙo yana kallon ido na yace, "baby nah kiyi haƙuri da abinda ya faru wancan ranan, banso na miki abinda na miki ba, amma nayi hakane don na nunawa duniya ke ɗin kin kawo mun mutuncinki, sannnan kuma duk rashin imanin mutum idan ya ganki a wannan yanayi ae dole ya tausaya miki especially ma idan macece ƴar'uwar ki, toh Alhamdulillah kinga kuwa Mama ta ɗan sarara miki tunda ta ga dai ɗanta ne ya ɗauki budurcin ki, sannan kuma kinga ae itama mace ce ae ta tausaya wa halin dana sakaki a ciki, don kinga har faɗa ta mun, kiyi haƙuri nayi ne don na rage miki ƙiyayyar da Mama take miki kinji Baby nah", ya faɗa yana sunkuyo da kanshi kan kafaɗa na.

Ajiyan zuciya na sauƙe domin sai yau naji kaman an sauƙe mun damuwan dake raina a game da abinda ya mun, dama nayita tunanin me nayiwa Hammah daya nuna mun rashin tausayi haka? Amma yanzu sai naji na samu nutsuwa domin naga alaman tausayi na a idon Mama a lokacin.

Muna nan zaune a wurin yana kallon shi ni kuma inata saƙa da war-wara a zuciyata, shi kuma ya saka hannun shi a cikin gashi na yanata chakuɗawa.

Har zuwa wani lokacin muna haka, ƙarfe goma tana cika ya juyo ya dube ni yace, "ya kamata muje mu kwanta baby", ina duban shi a ɗan tsorace nace, "amma kai ae a ɗakinka zaka kwana ko?".

Dariya yayi ya tashi ya tsaya yanaɓrike da kunkumin shi ƴace, "haba ƴanmata, wane ni naƙi kwana ɗaya da matata a ɗakinta? Kawai daurewa zakiyi kema ki dawo soja mu tafi filin daga, ba kiji abinda Mama tace bane"? ya faɗa yana dariya.

Kallon shi kawai na tsaya inayi, har saida ta miƙo mun hannun shi tukun na rike na tashi tsaye nima, zagayowa yayi ta bayana ya saka hannun shi ya rungumeni, sannan ya ɗaura haɓanshi

akan kafaɗa muka tafi hanyan ɗakina.

Har cikin ɗakin ya rakani , Sannan yace na je nayi wanka na shiryah yana dawowa, haka na shiga nayi wanka  nayi alwala na fito, gyara jikina nayi sosai yadda Aunty tamun bayani nayi, na ɗauki turaren data bani jiya nabi dukkan ilahirin jikina na shafe shi, sannan na ɗauko nighty na nasaka.

Hammah yana shigowa ya rungumo ni jikin shi yana ta rawa dani a hankali yana waƙan, kinshiga raina hannu biyu zani rikeki ƴan mata, yanayi yana ta juya ni a jikinshi  a hankali, har muka isa kan gadon ya kwantar dani ahankali.

Niko ina ganin sun hau kan gado na juya na fita na bar ɗakin, don bason leƙan asiri bane dani.

Sauda mukayi 2wks da komawa gidanmu, gaba ɗaya mun gama fahimtan kanmu nida Hammah, kaduna muka fara shirin tafiya don dubaYusuf.

Ranan da mukaje Yusuf da matar shi kaman su lashe mu, muna zaune a parlour su bayan mungama cin abinci na matso jikin Hammah na fara bin jikin shi kaman wata kuliya, shi kuma sai shafah jikina yakeyi yana gyara mun kwanciya a jikin shi.

Kawai dariyan Yusuf mukaji yana cewa matar shi, "don Allah zoki ga wannan ƙaton a jikin jaririyar nan, ni narasa yaushe ta girma da har take mishi amfani wallahi, ƙaton banza kawai", ya faɗa yana dariya bayan ya mike tsaye da nufin bar mana parlourn.

Dariya Hammah yayi yace, "kaine ƙaton banzan ae da kakasa shiru da bakinka, idan ana maganan jin daɗi wayake banbanta jaririya da guzuma".

Haka mukayi hutunmu hankali kwance nida Hammah nah, har gidan Aunty Fannah munje mun kwana mata, haka muka rabu dasu hankali kwance muna kewan juna, haka muka dawo bauchi.

Mundawo da 2dys Baba ya ƙira Hammah akan sunyi waya da Baban Zainab zata dawo washe gari, anan Baba ya mishi faɗa akan adalci da zaman lafiya, sannan ya tambaye shi da wa zai tafi Abujan a cikin mu? Gyara zama Hammah yayi yace.

"zan tafi da Zainab saboda Fatima bata gama school ba, amma idan ta gama itama zan tafi da su dukansu", Baba yace, "toh hakan ma yayi Allah ya baku zaman lafiya ya kuma haɗa kanku, kuma ka tabbatar ka haɗa su kaja musu kunne domin ni bana son rashin zaman lafiya, Allah ya wuce mana gaba", ya faɗa yana miƙa mishi wasu takaddu don ya ajiye mishi a wurinshi, na Hammah Babagana ne.

#Vote
Comment
Share
Follow.

*KU KASANCE DA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYYAH*
*1441H/2020M.*

®🖋
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION*✍🏻
{ _Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira._ }

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN KARFE*🏇

Story and written
By
*_AUNTY NICE_*

*_WANNAN BOOK ƊIN SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Whatpad@GaskiyaWritersAsso.~

*page* 95--96

*__________*📖Suna shiga wurin Baban su suka shige, bayan sun gaisa ne dukkan su sukayi shiru kowa kanshi a sunkuye a ƙasa, har zuwa wani lokaci tukun Baba ya ɗauki wayan shi ya ƙira Hammah akan ya same su a parlour shi.

Kafin Hammah ya shigo Baba ya ƙira Aunty, tana shigowa Hammah ya shigo fuskan nan na shi a murtuƙe kaman a filin yaƙi, gashi duk ya rame kaman ba shiba.

Dukkan su gaishe da Aunty sukayi sannan parlour ya koma yayi shiru kaman babu wani halittah aciki,  zuwa wani lokaci Baba yayi gyaran murya, sannan ya sanar musu abin da ya faru tsakanin shi da Mama har akaje batun saki, sannan ya sanar dasu yadda jiya sukayi da Abbah da kuma Aunty.

Baba kallon su yakeyi yana jiran abinda zasu ce, zuwa can Abdallah ya gyara zama ya fara

magana kaman haka.

"Baba Allah ya ƙara maka lafiya da juriya akan iyalanka gaskiya alal haƙiƙa kai mai haƙuri ne da kuma hangen nesa, kuma kai ɗin har ilah yau mai adalcine cikin iyalanka, domin kuwa abinda ya ke faruwa tsakanin ka da Mama tun tashin mu da kai ba mai haƙuri da adalci bane da ko saki ɗari ne idan ya halattah toh da kayi, Mama mahaifiyata ce amma na sani abubuwa da yawa bata kyautawa expecially tsakaninku da abokiyar zamanta, har ilah yau ya fara dawowa kanmu ɗaya bayan ɗaya."

Ajiyan zuciya yayi tukun ya cigaba, "Baba amadadina da sauran ƴaƴanta muna mai baka haƙuri da abinda Maman mu ta maka, ko ince ta muku kaida Aunty da kuma Hamman mu gaba ɗaya".

"Domin bawai wa Riyyah kaɗai Mama ta ciwa mutunci ba, maganan gaskiya wa Baba damu kanmu ƴaƴanta ta ciwa mutunci, domin martabar gidanmu ta taɓa, Baba don Allah ba don halin Mama ba kayi haƙuri ka maidata matsayin ta na matar ka, haka kema Aunty don Allah kiyi haƙuri ki yafe mata".

Shiru wurin ya sake ɗauka babu wanda yace uffan, zuwa can kuma sai Abdoulrahman ya buɗi baki yace.

"Baba da Aunty don Allah kuyi haƙuri ku yafewa Mama," sannan ya maida kanshi gefen da Hammah yake yace, "Hammah don Allah kayi aure ka yafewa Mama, domin kaima an maka ba dai-dai ba", ya faɗa yana share hawayenshi, domin shi mai rauni ne.

Hammah dai zuwa lokacin bai ko ɗago kanshi ba.

Aunty ce ta gyara muryanta sannan ta ce, "Allah ya gafarta mana gaba ɗaya, sannan kuma nidai a gefe nah nayafe mata, amma kuma maganan data faɗa akan Riyyah shikam maganar gaskiya bazan iya cewa ya yafu ba, har sai shi ɗanta wanda yace mata Riyyah bata kai mutuncinta gidan shiba tayi proving hakan tukun zamu yafe, domin gaskiya duk abinda Mama zatayi mun taci darajan mijinta da nake aure, da kuma ku ƴaƴanta da kuke yayun nawa yaran, kuma wallahi da tasan yadda nake so mu zauna lafiya mu rungume yaranmu, da wallahi sai tafi ko wacce mace samun zaman lafiya da zuciyarta, amma kuma gaskiya bazan bari ta saka baiwar Allah a gaba ba, don bazai yiwuba".

"Toh Alhamdulillahi mungode Allah tunda kin yafe mata, sai magana na gaba shine maganan ita Riyyah, shi kuma wannan nasan matsalanku kuna tunanin Baba nane ya zo ya ɓata ta a wurin mamanshi ko? Toh wallahi sam kada ku saka a ranku, domin nayi imani da Allah koda Riyyah bata kai budurcinta gidanta ba toh Baba nah bazai tona sirrin gidan shi ba, kawai ta faɗa ne don ranku ya ɓaci, kuma yau zan ɗauki Baba nah muje har gaban Abba ya basu haƙuri, kuma tare da Mama zamuje domin ta nemi yafiyar su, Allah kuma ya magance mana wannan masifah".

Gaba ɗayansu suka amsa da Ameen mun gode Baba, amma ko kaɗan Hammah bai ɗago kanshi ya dubi kowa ba.

Ita kuma Aunty duk hankalinta yana kanshi, tana ta mamakin rashin maganar shi, amma sanin halinshi tasan zaiyi abinda yafi haka sai kawai ta share, tashi tayi ta nufi ɗakinta domin ɗauko jakanta a wuce gaba ɗaya da ita.

Baba Aunty kawai ya ɗauka a motar shi, shi kuma Hammah ko kula kowa baiyiba ya wuce cikin motar shi, ido Mama ta bishi da shi cikin ranta tana mamakin mai ya hana shi zuwa ya gaisheta? Ko dai haushinta shima ya keji akan matar shi? Hmmm turo baki tayi gaba ta buɗe motar su Abdallah ta shiga tana ta hararan inda Aunty suke zaune.

Mota uku ne suka tafi da su har gidan Abban bauchi, acan gidan Abban suka samu wani ƙanin Bappan su Aunty wanda ake ƙiranshi Bappah Ali, shi kuma mutum ne mai tsananin gaske, domin idan ya ɓige da faɗa to hattah ƴan unguwar basi da zaman lafiya ranan, shi yasa hattah yarah tsoron shi sukeyi, duk garin kirari ake mishi da Ali Master mai buhun dambula.

Yana hakimce a parlour yana kaɗa ƙafah, har ƙasa Baba ya sunkuya yana gaida Bappah Ali, gefe ɗaya ma Aunty  har ƙasa ta sunkuya tana gaishe shi, suma su Hammah duk gaishe shi sukayi.

Mama ma gefe ta koma ta zauna don har ga Allah tana shakkan dattijon, domin akwai lokacin haihuwar Gidaɗo matar shi tazo yiwa Aunty biƙi, data musu rashin mutunci, har gidan yazo yace, idan ta sake sai ya markaɗa ta yaga wanda ya isar mata, gashi dama tsuhon soja ne, hidiman shi babu sauƙi.

Gaishe shi ta fara, shi kuma yayi charaf yace, " rufe mun baki annoba, dama zaman jiranki na tsaya inayi domin na shaidah miki da izinin Allah bamu haifi fasiƙi a zuriyar mu ba, kuma yau ɗin nan ɗanki zai ɗauki matar shi su koma gidansu suyi rayuwar aure mai daraja irin wacce kema kikayi da mahaifin shi, ki ka kuma san daɗin shi,

toh itama yau zata je ta fara, kuma na rantse miki da Allah ko rundanan maiduguri ne yau zasu sauƙa a garin bauchi ina dai-dai da kowa, kuma daga yau banzan kallo ko baƙar magana ya sake haɗaki da jikata, zan ajiye mutunci da surukuta a gefe na chashe ki keda mijinki, domin ku san Fatima ƴar dangi ce bawai ƴar maula bace yadda kuke tunani, domin bamu neman ko sisin ku keda ɗanki da mijinki, daga yau kika sake taɓa mun zuriyata ko bayan raina ne sai kin ɗanɗana kuɗarki".

Duk parlour yayi shiru sai kukan Mama akeji, daga baya Bappah Ali ya tattausa muryan shi yace.

"Alhaji Nuhu kaine yanzu zan bawa haƙuri saboda duk cikinmu babu wanda yakai ka shiga tashin hankali don duk iyalenka ne, sannan kuma ina mai baka haƙuri a matsayina na mahaifin su duka matankan, don Allah kayi haƙuri ka janye maganar sakin da kayiwa ita ƴar mu Zahra, ayi haƙuri a mai da ita ɗakinta ta zauna, kuma inji ɗan'uwa na Bappah yace kayi haƙuri ka maida ta ɗakinta ka daure kuma kaci girma, saboda haka yanzu kafin anjuma nake so kamayar da matarka ɗakinta, Don kuskure babu wanda ya wuce ƙetare shi, saidai a kiyayi gaba kuma", ya faɗa yana maida kallonshi kan Hammah.

Shidai Hammah har zuwa lokacin bai iya yace komai ba, haka Baba yace ya mayar da Mama ɗakinta, inda su Abdallah suka shiga yiwa Bappah Ali godiya, hartah ita kanta Aunty saida ta tausayawa yaran, gasu yara nitsattsu amma basu yi dace da uwa ta gari ba.

Bayan komai ya lafa ne duk masu jawabi sunyi, Mama tayi godiya wa Bappah, Baba ma yayi mishi, Abba ya rufe taron da Addu'a kowa ya tashi, inda Bappah yasa Riyyah ta fito Mama ta

nemi gafarar ta, ita dai sai kuka kawai ta keyi, Bappah ya dubi Hammah yace, "Kai kuma matsoracin soja idan anyi sallan ishaa sai kazo ka ɗauki taka matar ko na tafi da ita muyi zaman mu acan, tayi ta mun kiwon tumaki na," ya faɗa yana hararan Hammah.

Shima Hamman abin mamaki ɗago kanshi yayi yana hararan Bappah cikin wasa sannan yace, "me zatayi da tsohun soja? Wanda da yaji tafiya yaƙi a guje ya dawo wai shi nan yayi Retire".

Sandan hannu Bappah ya jefawa Hammah yana ƙaryan maƙaryaci wallahi, mu yaƙi da mukayi har ku gama soja baza kuyi irin shi ba, kuma na fasa baka matar yau, tafiya zanyi da ita sai kazo anyi shaɗi tukun ta bika, ragon soja kawai da ae tun da kaji za a ɓalle auren ae ba kasake magana ba sai da kaji an baka ita, toh na fasa", ya cigaba da hararan Hamman.

Dariya duka parlourn akayi Baba yana , "lallai Bappah ka karanto mutuminka, inaga tunda yazo banji muryan shi ba sai yanzu", dukkan su parlour dariya suka fara, inda shi kuma Hammah ya tashi ya fita yana dariya.

Ƙarfe tara na dare Hammah yazo ɗauka na agidan Goggo, inda tun safen Goggo take ta bani haɗe -haɗe ina ta sha, ga wani zuma da wani garin abu a ciki da umma ta aiko mun tun safe nake lasan shi, basu barni na ɓata lokaci ba aka saka ni na fito muka tafi.

Tunda na shiga mitan Hammah bai ce mun uffan ba, nima bance mishi uffan ba har muka isa gidan su, a tunanina gidan mu zamuje amma kawai sai na ga mun shiga nasu gidan, kuma kai tsaye side ɗin Mama ya wuce dani.

Muna shiga muka samu Mama dasu twins a zaune a parlour suna kallon news, sannan su twins suna shan tea suna kallon.

Har ƙasa na sunkuya na gaida Mama cikin rawan muryah, abin mamaki sai naga fuskan ta a ɗaure take amsawa a dole, abin ya ban mamaki kaman ba ɗazu ake mata nasiha ba, an ya Mama tana da imani kuwa? Hmm abin kawai sai addu'a.

Muna zaune a haka babu mai magana har goma tayi, sai su Abdallah sukayi mana sallama suka wuce can side ɗin su Hamma nada shida Besty nah, don tun yammah Hammah ya saka su suka maida kayansu can ɗin, yanzu wurin Mama ya zama ita kaɗai take zaune da ɗakunan ta uku ita ɗaya.

Haka mama tagama zamanta ta shi tabar mu batare data ce mana uffan ba, tana wucewa ɗakinta Hammah ya juyo ya kalleni, sannan ya miƙe yace, "tashi muje".

Duk a tsorace nake, haka muka shige ɗaya ɗakin Mama inda yafi kusa da ɗakinta , wanda a ciki Zainab take sauƙa.

Muna shiga naga fuskan shi a ɗaure, babu alaman wasa haka ya saka kanshi ya wuce toilet, can naga ya fito ɗaure da towel ɗin Zainab ajikin shi.

Kallona ya tsaya yana yi can yace, "ke bazaki yi wankan bane"? Jikina yana ɗan rawa nace, "yanzu nayi a gida tukun muka taho".

"kishiga kiyi alwala toh", babu musu na wuce naje nayi alwalan na fito, ina kallo ya miƙo mun hijabin Zainab dake ɗakin akan sallaya, haka shima na karɓa babu musu na saka, ahaka mukayi sallah raka'a biyu, bayan mun idar yaja mana dogon addu'a da roƙa mana zaman lafiya.

Tun daga kan sallayan Hammah ya jawo ni jikin shi, Nikan jiki na sai rawa yake tayi, a haka muka ƙarasa kan gadon yana ta ya mutsa ni kaman ya samu kayan wanki, muryana yana rawa nace.

"Hammah nan fah ɗakin Mama ne, kayi haƙuri mutafi gidanmu mana", na faɗa hawaye yana bin fuskana, don wani masifaffen tsoro naji ya kamani.

Ɗago da idon shi yayi ya dubeni , wanda kallon idon shi kaɗai sai da naji gaba na ya faɗi, yana fitar da nishi da sauri-sauri yace.

"anan ɗakin Mama cikin gidan da Auntyn ki take nake so na nuna musu matata kamila ce acce tazo da mutuncinta gidan aurenta, su shaidah ni Umar na samu matata a killace, kinga kowa zai

shaidah basai na faɗa musu ba", yana gama faɗi ya cigaba da aika mun wasu saƙonni masu azaba don ko ba zance mai daɗi ba, don cikin azaba yake mun.

Can wani lokaci naji ya buɗe mun ƙafa na da ɗan ƙarfin shi, ban ankara ba naji shi yana ratsa ni cikin azaba, ban san lokacin dana cire jarumtana ba na kurma wani ihu mai ƙarfin gaske wanda har sai gidan gaba ɗaya ya amsa, don abinda Hammah yake mun ko maza uku ne suke kaina iya kaci.

A razane Mama ta tashi duk jikinta yana rawa, kallon ƙofan ɗakinta ta fara a ranta tana me nake ji kaman Umar yana kwance mun da matar shi a gidan nan? Lokaci ɗaya taji hawayen baƙin ciki ya zubo mata.

Bata ankara ba ta sake jin ihun kukan na babu ƙakƙautawa, sai ƙiran sunan Aunty nake da iya ƙarfina akan tazo ta ƙwace ni ,Hammah zai kashe ni.

Bata tsinke da al'amarin ba kawai ta fara jin ihun Hammah cikin jin daɗi sai sambatu yake tayi yana ƙiran na, dana taimaka mishi zai mutu, ae Mama bata san lokacin da ta miƙe tayi toilet ɗinta tana toshe kunnen taba, hawaye yana ta zuba mata akan idonta.

Ananidar da ƙiran sallan asuba, Hammah ya ɗauki wayan shi ya ƙira Aunty, tana ɗauka yace, "Aunty don Allah kizo side ɗin Mama Fatima babu lafiya,"  ya na faɗa ya kashe wayan, sannan ya maida kanshi kaina da nake jin numfashi na ma da ƙyar yake fita mun don azaba, don rashin tausayi irin na Hammah sau biyu yana maida kanshi jikina a daren jiya.

Hammah yana jin ƙwanƙwasa ƙofan Aunty ya fito da sauri, a dai-dai parlour sukayi kiciɓis da Mama da take binshi da harara, yana buɗe ƙofan Aunty ta shigo da sauri, tana kallon shi tace.

"ina take"? Nuna mata ɗayan ɗakin Mama yayi da hannun shi.

Daga ita har Maman da sauri suka shiga ɗakin, shi kuma ya nemi wuri ya zauna a parloun yana jiran fitowar su.

#Vote
Comment

Share.

*KU KASANCE DA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYYAH*
*1441H/2020M.*

®☄
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION*✍🏻
{ _Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira._ }

🎐G•W•A🎐
*GASKIYA DOKIN KARFE*🏇🏽

Story and written
By
*_AUNTY NICE_*

*_WANNAN BOOK ƊIN SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

~Whatpad@GaskiyaWritersAsso.~

*page* 97--98

*____________*📖Suna shiga da gudu-gudu sauri-sauri ta ƙarisa bakin gadon, yaye bargon tayi ta ƙurawa mun ido yadda nake ta ɓarin sanyi, ga wani zazzaɓi mai zafi da ya rufe ni, idon ta ne ya sauƙa akan bedsheet ɗin daya gama ɓaci da jini kacha-kacha.

Hannu Aunty ta saka don ta jawoni, bansan lokacin dana kurma wani ihu ba, har saida yayi sanadin shigowan Hammah da gudu, tsayawa yayi daga bakin ƙofah yace, "Aunty yayah take ihu"?.

Mama ce ta juyo cike da masifah tace, "ba dole tayi ihu ba, duk ka yagalgala musu yarinya, Allah dai yasa baka haɗata da yoyon fitsari ba, dubi rashin imanin da kayi akan yarinya Hamman su", ta faɗa tana bin shi da hararah.

Bai sake ce musu komai ba ya juya ya fita ya bar ɗakin, Aunty ce ta taimaka ta kaini toilet ta mun gyara na musamman, bayan ta taimaka mun nayi wanka muka fito ɗakin, inda muka samu Mama ta yaye bedsheet ɗin ta fita da shi, bayan nasaka kaya ne, Aunty ta riƙo hannu na muka fito domin tafiya side ɗinta, sai buɗe ƙafa nakeyi hawaye yana bin fuskana.

A parlour muka haɗu da Mama tana ta yiwa Hammah faɗa, ganin fitowan mune yasaka duk suka juyo suka zuba mana ido, Aunty ce ta dubi Hammah tace.

"Bari muje asibiti zan mata ɗinki", kanshi ya ɗago da sauri ya dube ni, fuskan shi cike da tsoro, Mama ce da sauri ta amsa da.

"Ba dole a mata aiki ba, irin wannan haukan da ya sauƙe kaman a filin daga, kai wallahi kagyara halinka, ce maka akayi abinci ce da ka kusan cinyeta duk"?.

Bayan Aunty ta mun ɗinki ne muka dawo gida, kai tsaye side ɗinta ta wuce dani, inda ta shiga kula dani kaman wacce na haihu, nidai gaskiya ban san meya ke damuna ba, babu hali na tuna abinda Hammah ya mun sai nayi kuka, don wallahi yaci zalina.

Haka Hammah ya dinga jelan zuwa dubani har na warke garau amma Aunty batayi maganan komawa na ba wanda sai naji na samu nitsuwa har hankali na ya kwanta.

Sai da na ƙara sati biyu bayan na warke tukun Baba ya saka baki na koma gidana, don wannan karon Hammah yana ɗauka na mukayu side ɗin Mama, tana ganinmu tace.

"wallahi baka isa ku zauna mun a ɗakina ba, ka wuce da ita gidanka, kalan kaje wannan karon ta yage ka tara mun fitinannun iyayenta? Wancan ma nayita addu'a kada kakanta yaji labari, don ba kai ba hattah ni sai ya lakaɗawa duka, don tsohun soja ne marar imani".

Hammah tunda muka shiga mota yake ta tuntsura dariya wanda bansan dalilin shi ba, nidai banda faɗuwar gaba babu abinda nakeji, sai mamakin abinda yake saka shi dariya kawai nakeyi.

Har muka isa gidan bai daina dariyan shi ba, muna isa naga yadda gidan yasha gyara, ga wani ƙamshin turare da yake ta tashi a kowane side na gidan, kasancewar tun jiya Aunty ta saka masu aikinta suka je suka gyara gidan, yau kuma tun safe suka je suka saka turare suka shimfiɗa bedsheet a ɗakunan, gida dai yayi kyau abin sha'awa.

Nidai gaba ɗaya tunda muka dawo a tsorace nake, amma sai naga Hammah shi ko nuna ya damu da abinda nakeyi baiyi ba, haka dai na shiga ɗakina, amma nakasa taɓuka komai na zauna a bakin gadon nayi tagumi.

Ina zaune a haka har aka ƙira sallan magarib amma nakasa tashi na taɓuka komai wa kaina, abin mamaki ina zaune har aka idar da sallan a masallaci inaji amma ban iya tashi ba, don wani irin faɗuwar gaba kawai nakeji, ina haka sai naji an buɗe ƙofah an shigo ɗakin.

Da sauri na ɗago kaina ina kallon mai shigowan, Hammah ne yake tsaye a bakin ƙofan hannun shi riƙe da hannun ƙofan ya ƙura mun ido.

Ganin kllon da yake mun baiyi magana ba, ya saka ni miƙewa da sauri nayi hanyar toilet, da sauri ya ƙira sunana yana faɗin, "kaddai bakiyi sallan magarib ba"?
bance komai ba na buɗe ƙofan na shiga da sauri na.

Bayan na idar ne na zauna ina azkhar, ina cikin yi naji an ƙira sallan ishaa, Hammah ya sake shigowa yana kallo na yace.

"yanzu kam ki tashi kiyi sallan isha kafin na dawo", sannan ya saka kai ya fita.

Ina idar da ishaa na ɗaura shafa'i da wuturi, ina zaune har lokacin ban tashi ba, na sake jin buɗewar ƙofan, da sauri na sake ɗago kaina na kalle shi, shima yana kallo na, can ya juya baice komai ba ya fita.

Na kai kusan minti ashirin a haka naji shigowar mota gidan, har zuwa wani lokaci Hammah yazo ya ƙirani na fito muci abinci, duban shi nayi kaman zanyi kuka nace.

"Hammah bana jin yunwa, kaina ne yaje ciwo", dariya yayi ya juya ya fita.

Har naji hankalina ya kwanta sai kuma gashi ya dawo hannun shi ɗauke da pilet cike da ferfusoup ɗin kaza, ɗayan hannun kuma ɗauke da cup daya cika kunun aya da yaji kayan ƙamshi dasu dabino a ciki, har inda nake yazo ya zauna.

Yana kallo na yace, "gashi bana son wani musu ko jayayya, duk ki cinye ki ajiye mun pilet ɗin", sannan ya tashi ya fita a ɗakin yayi parlour.

Babu yadda na iya haka na saka naman a gaba na cinye shi, don ya mun daɗi gashi kana fara ci zaka san girkin Aunty nane, haka naci na shanye kunun ayan, sannan na ɗauki pilet ɗin da cup ɗin na fito domin na kai kitchen.

A parlour na wuce Hammah yana cin nashi abincin, bayan na kai na  fito ne naji ya ƙirani, ina zuwa yace na zauna a gefen shi, babu yadda na iya haka na zauna jikina yana ɗan rawa, ganin yadda na zauna a ɗan ɗufane ya juya ya kalleni kaɗan, sannan ya jijjiga kanshi ya maida kanshi kan kallon da yakeyi yana cin naman shi.

Can naga ya zuba kunun ayan a kofi ya miƙo mun, kallon shi nayi kaman zanyi musu sai naga babu fuskan hakan, da sauri na saka hannu na karɓa, kafa kaina nayi sai dana shanye tukun na ajiye mishi cup ɗin.

Hannu na ya riƙo yana kallon ido na yace, "baby nah kiyi haƙuri da abinda ya faru wancan ranan, banso na miki abinda na miki ba, amma nayi hakane don na nunawa duniya ke ɗin kin kawo mun mutuncinki, sannnan kuma duk rashin imanin mutum idan ya ganki a wannan yanayi ae dole ya tausaya miki especially ma idan macece ƴar'uwar ki, toh Alhamdulillah kinga kuwa Mama ta ɗan sarara miki tunda ta ga dai ɗanta ne ya ɗauki budurcin ki, sannan kuma kinga ae itama mace ce ae ta tausaya wa halin dana sakaki a ciki, don kinga har faɗa ta mun, kiyi haƙuri nayi ne don na rage miki ƙiyayyar da Mama take miki kinji Baby nah", ya faɗa yana sunkuyo da kanshi kan kafaɗa na.

Ajiyan zuciya na sauƙe domin sai yau naji kaman an sauƙe mun damuwan dake raina a game da abinda ya mun, dama nayita tunanin me nayiwa Hammah daya nuna mun rashin tausayi

haka? Amma yanzu sai naji na samu nutsuwa domin naga alaman tausayi na a idon Mama a lokacin.

Muna nan zaune a wurin yana kallon shi ni kuma inata saƙa da war-wara a zuciyata, shi kuma ya saka hannun shi a cikin gashi na yanata chakuɗawa.

Har zuwa wani lokacin muna haka, ƙarfe goma tana cika ya juyo ya dube ni yace, "ya kamata muje mu kwanta baby", ina duban shi a ɗan tsorace nace, "amma kai ae a ɗakinka zaka kwana ko?".

Dariya yayi ya tashi ya tsaya yanaɓrike da kunkumin shi ƴace, "haba ƴanmata, wane ni naƙi kwana ɗaya da matata a ɗakinta? Kawai daurewa zakiyi kema ki dawo soja mu tafi filin daga, ba kiji abinda Mama tace bane"? ya faɗa yana dariya.

Kallon shi kawai na tsaya inayi, har saida ta miƙo mun hannun shi tukun na rike na tashi tsaye nima, zagayowa yayi ta bayana ya saka hannun shi ya rungumeni, sannan ya ɗaura haɓanshi akan kafaɗa muka tafi hanyan ɗakina.

Har cikin ɗakin ya rakani , Sannan yace na je nayi wanka na shiryah yana dawowa, haka na shiga nayi wanka  nayi alwala na fito, gyara jikina nayi sosai yadda Aunty tamun bayani nayi, na ɗauki turaren data bani jiya nabi dukkan ilahirin jikina na shafe shi, sannan na ɗauko nighty na nasaka.

Hammah yana shigowa ya rungumo ni jikin shi yana ta rawa dani a hankali yana waƙan, kinshiga raina hannu biyu zani rikeki ƴan mata, yanayi yana ta juya ni a jikinshi  a hankali, har muka isa kan gadon ya kwantar dani ahankali.

Niko ina ganin sun hau kan gado na juya na fita na bar ɗakin, don bason leƙan asiri bane dani.

Sauda mukayi 2wks da komawa gidanmu, gaba ɗaya mun gama fahimtan kanmu nida Hammah, kaduna muka fara shirin tafiya don dubaYusuf.

Ranan da mukaje Yusuf da matar shi kaman su lashe mu, muna zaune a parlour su bayan mungama cin abinci na matso jikin Hammah na fara bin jikin shi kaman wata kuliya, shi kuma sai shafah jikina yakeyi yana gyara mun kwanciya a jikin shi.

Kawai dariyan Yusuf mukaji yana cewa matar shi, "don Allah zoki ga wannan ƙaton a jikin jaririyar nan, ni narasa yaushe ta girma da har take mishi amfani wallahi, ƙaton banza kawai", ya faɗa yana dariya bayan ya mike tsaye da nufin bar mana parlourn.

Dariya Hammah yayi yace, "kaine ƙaton banzan ae da kakasa shiru da bakinka, idan ana maganan jin daɗi wayake banbanta jaririya da guzuma".

Haka mukayi hutunmu hankali kwance nida Hammah nah, har gidan Aunty Fannah munje mun kwana mata, haka muka rabu dasu hankali kwance muna kewan juna, haka muka dawo bauchi.

Mundawo da 2dys Baba ya ƙira Hammah akan sunyi waya da Baban Zainab zata dawo washe gari, anan Baba ya mishi faɗa akan adalci da zaman lafiya, sannan ya tambaye shi da wa zai tafi Abujan a cikin mu? Gyara zama Hammah yayi yace.

"zan tafi da Zainab saboda Fatima bata gama school ba, amma idan ta gama itama zan tafi da su dukansu", Baba yace, "toh hakan ma yayi Allah ya baku zaman lafiya ya kuma haɗa kanku, kuma ka tabbatar ka haɗa su kaja musu kunne domin ni bana son rashin zaman lafiya, Allah ya wuce mana gaba", ya faɗa yana miƙa mishi wasu takaddu don ya ajiye mishi a wurinshi, na

Hammah Babagana ne.

#Vote
Comment
Share
Follow.

*KU KASANCE DA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
*BADARIYYAH*
*1441H/2020M.*
*RAJAB/FEB.*

®🖋
*GASKIYA WRITERS ASSOCIATION*✍🏻
_{Gaskiya ɗaya ce daga ƙinta sai ɓata, burinmu mu faɗakar da al'umma domin ribantar rayuwar duniya da lahira.}_

🎐G•W•A🎐
*_GASKIYA DOKIN ƘARFE🏇_*

Story and written
By
*_AUNTY NICE_*

*_WANNAN BOOK ƊIN SADAUKARWA NE ZUWA GAREKI MISS XERKS._*

*WATTPAD:-* GaskiyaWritersAsso.

*G-MAIL:-* gaskiyawritersassociation@gmail.com.

*FACEBOOK:-* https://m.facebook.com/GaskiyaWritersAssociation.

*TWITER:-* https://twitter.com/GaskiyaWriters?s=09.

```Gaba ɗaya shafin yau ɗungurun-gun sadaukarwa ce xuwa gare ku ƴaƴana yaran albarka, Nabeelah Nuhu Arabi & Nuhu Ahmad Arabi (Bappah),ina roƙon Allah subhanahu wata'ala da yayiwa rayuwar ku albarka, ya kare min ku daga dukannin abinƙi, ya kuma dawwamar daku cikin farinciki da jin daɗin rayuwa,duk abinda ba shi da kyau Allah ya kauda shi daga gare ku, ya baku arziƙin duniya dana lahira, ya kare min ku daga sharrin maƙiya mahassada, ameen ya rahman, ina son ku ƴaƴana Allah ya bar min ku, ya muku albarka, yasa albarka a karatunku.```

*LAST PAGE.*
*page* 99--100

*__________📖* Rayuwa babu wuya yau Zainab ta dawo daga maiduguri, tun dawowan ta Hammah ya haɗamu ya mana nasiha kuma yaja kunnen mu akan kada wata ta kawo mi shi wani rashin zaman lafiya, kowan mu ta ɗauka mi shi alƙawarin kiyayewa, haka mu kayi masa alƙawari sannan mu kai sallama kowa ta wuce side ɗinta, da yake gidan Hammah shima side uku yayi, ɗaya nawa ɗaya nata, ɗaya kuma Hammah yace na baƙi ne.

Ana gabe su Hammah zasu wuce Abuja Hammah ya kawo mu gida don mu wuni acan, muna shiga kai tsaye wurin Mama aka fara shigewa, a parlour'n ta muka zauna dukkan mu, amma ko kaɗan hankalin Mama yana kan Zainab, ganin haka na nuna bai dameni ba tunda ko yaya a kayi Zainab ɗiyar tace.

Goma tana yi naga masu aikin Mama zasu shiga kitchen, ina kallon Zainab nace,

"Maman Nabeel ko zamu shiga muyi ne?".
 Harara na tayi sannan tace,
 "nikan bazan iya ba, amma idan zaki iya kije kiyi".

Ban ɓata lokaci ba na tashi na shiga kitchen ɗin, ko 30mnt ba ayi ba ƙamshi ya fara cika gidan, bani na gama ba dai da aka ƙira azahar ina kitchen ina kintsa wurin, Mama har wurin tazo sai fara'a take tayi tana buɗe coolers ɗin, saida nagama na mata sallana na wuce gun Aunty, muna ta hira da Aunty ranan kaman mun shekara goma bamu haɗu ba.
```

Washe gari su Hammah suka kama hanya shida Zainab, amma an bar mun Nabeel, sannan ga Gidaɗo da Khalifah da zasu na tayani zama, a haka kuma Aunty ta aiko can kafi an kawo mun wata goggon mu da mijin ta ya rasu, ita ma sai wurin Yammah ta iso.

Haka muka yita rayuwar mu dasu cikin kwanciyar hankali, muna zuwa makarantan mu hankali kwance, kullum zanje na sauƙe Nabeel tukun na wuce school, idan ya tashi kuma driver ke kaimun shi gidan su Hammah, sai na tashi nake bi na ɗauke shi.

Duk Friday sai mun wuni a can gidan, wani lokacin kuma gidan mu muke wucewa, a haka har mukayi wannan semester muka gama lafiya, zuwa wannan lokacin Hammah yazo babu iyaka, don duk bayan 2wks sai yazo bauchi.

Muna hutu muka shiryah nida ɗan Nabeel ɗina mukayi Abuja, lokacin ciki na ya kai wata biyar, gidan gashi mai kyau amma rashin tsabta yasa ya zama wani iri.

Washe garin zuwan mu, na cire kayana na gyara kitchen bayan na gyara ɗakin Hammah tsab,na wanke mishi toilet, na dawo parlour na gyara shi na goge ko ina, duk inda ka duba a gidan sai sheƙi yakeyi, ranan ko abinci nakasa yi, sai take-away Hammah yaje ya mana, duk inda na wuce sai ya saka mun Albarka, ana sallan isha na ɓingire da baccin gajiya.

to a haka muka ci gaba da rayuwar mu cikin kwanciyar hankali,sose Hamma yake jin daɗi domin kuwa zuwa yanzu Zainab ta ɗan sauya hali, haka kuma shima Hamma adalin namiji ne, wani sa'ilin har na kanji haushi idan naga zai mana abu ya fara bawa Zainab koya fara shawara da ita, kun san dole dai kishi nan sai anyi shi, sai dai kuma zuciyat ta kan tunasar mani da hakan shine dai-dai.

yanzu ko irin cin magani da ɗaure fuskar nan Zainab bata fiya yimun ba, mukan zauna muyi hira tare har kallo ma idan muna parlo, sai dai wani lokacin kuma idan ta burkice kallo fa bai haɗa mu da ita na arziƙi sai dai aikin aiko mani da harara.

tunda ciki na ya ƙara girma sai Zainab ta ɗauke min yin komai na gidan, ko nace zan yi zata ce a'a maiye amfanin biyun, haka ina kallo zata yi aikace-aikace domin ta sauya don hanyar data ɗauka taga babu riba kuma ba mai ɓullewa bace, sosai take taimaka mani a abubuwa da dama

idan na buƙaci hakan.

ɓangaren Hamma nah kuwa tarairaya da kulawa ba'a magana, kumburin da ƙafafuna suka yi tamkar ana hura su, sai wata uwar rama dana yi, har ciki na ya shiga wata tara shiru kake ji, ni dai duk na koma wata abar tausayi, kowa ya ganni sai ya tausaya mani, haka har ciki na ya shiga wata na goma amma haihuwa shiru kake jin ta, ta kai ta kawo ko ta shi bana iya yi sai da taimakon Hamma ko Zainab duk da yanzu wata gwaggon mu da mijin ta ya rasu ta dawo wuri na da zama domin kula dani, hankali na dana ƴan'uwana ya ta shi, duk tsoro ya kama mu tun ma baya Hammah nah.

wani bin haka zai riƙe hannu na yana min ƙwallar tausayi, yau ina kwance a ɗaki na juya ma ƙofa baya, Hamma ne ya murɗa handle ya shigo, koda ya ƙaraso gare ni ya juyo dani sai yaga ina kuka, taimaka mani yay na miƙe zauna, jiki na ya faɗo tare da bani kyakykyawar runguma, shafa baya na yake a hankali yana lallashi na akan baya son wannna kukan wanda ya zamar min jiki a yanzu, bai skae ni ba sai daya ji na daina kukan sai shashsheƙar sa.

hannu na ya kamo ya sanya cikin nasa ya haɗe yana mammatsawa a hankali, ban san lokacin da wani kukan ya kuma taho mani ba ya sautin sa ya kufce ya fito fili, ɗago idanuwan sa yay ya zuba mani yana mani kallo mai cike da tsantsar tausayi da kuma zallar ƙauna.

da ɗayan tafin hannun sa yake shafo gefen fuskata, muryar sa a sanyaye yace da ni, "Baby nah kin fi kowa sanin bana son zubar hawayen ki, don Allah ki daina domin masu tsada ne".

murya ta a disashe domin kuwa kukan da nayi bana wasa ba, gam na riƙe hannun sa sose ina ce da shi,
"Hamma na nasan mutuwa zan yi....".

ban ƙarasa faɗar abinda zance ba yay saurin rufen baki da hannun sa, take yanayin fuskar sa ya sauya wanda na hango ɓacin rai a cikin domin kuwa Hamma baya ƙaunar wannan kalmar da nake faɗi masa.

bai magana ba sai daya saita muryarsa domin baya son yay min faɗa, da tausasan kalamai yake min magana gami da kwantar da hankali.

"mutuwa dole ce domin kowanne bawa sai ya ɗanɗani zafin ta,, amma bana son kina kwatan ta akan ki Baby nah duk da cewar lokaci ce ba kuma a iya tsere mata, babu tsumi babu dabara in

har tazo sai an tafi,  ko zaki mutu ba yanzu ba insha'Allahu, zaki haihu da ranki da lafiyar ki bi'izinillahi rabbi, da yardar Allah ba zaki tafi ki barni ba".

sauran maganar ya ƙarasa a raunene inda ya kwanto da kansa saman ƙirjina wanda ciki ya tokare girman sa, don cikin kaɗan ya rage ya haɗe da breast ɗina da suka ƙara cika sakamakon cikin.

tausayin kaina da shi da abinda ke ciki na ya kamani, haka mu kai ta kukan mu nida shi.

yau ta kama asabar, zaune nake ina koyawa Nabeel karatun islamiya, daga ni sai shi a gidan sai Gwaggo wadda ita kuma tana can ɗakin ta, Hamma da Zainab kuma sun fita zai kai ta anguwa, bayana naji ya riƙe sose kamin marata ma ta kuma kamawa, dama tun safiyar yau nake jin suna min ciwo sai dai ina daurewa ne kawai saboda kar na ɗaga hankalin Hamma nah, wasa-wasa abin sai yafi ƙarfi na, hannun Nabeel na kamo na damƙe ina cije fuska domin kuwa ni ɗaya nasan azabar da nake ji, shi kansa Nabeel sai da yayi ƙara domin ba ƙaramin damƙa naiwa hannun nasa ba.

wasu hawaye ne suka shiga sauka saman fuskata, tasowa Nabeel yayi yana goge min shima yana kuka yana cemin sannu Mami, kai nake ɗaga masa, Allah ya taimaka Nabeel mai wayo ne nan yay sauri yaje ya kira Gwaggo tazo, hannu na miƙowa Gwaggo ina fama juya kai ina datse laɓɓa na, tambayar da Gwaggo tayi mani ita tasa ni buɗe nauyayyun idanuwa na na kalle ta.

"Riyah lafiya?".

da ƙyar na iya buɗa baki nace mata, "Gwaggo bayana zai cire ,marata ciwo ki taimaka mani".

"toh, ko dai haihuwar ce".

kamin ta kuma yunƙurin maganar da zatayi sai ga Hamma da Zainab sun shigo, dukan su turus su kayi ganin Gwaggo tsaye a kaina tana mani firfita da gefen zanen ta, duk da Ac ɗin parlon amma ni kam wani gumi na daban ke keto mani.

Nabeel ne ya ƙarasa da sauri wurin Daddy'n nasa ya rungume shi yana kuka tare da ce masa Mami bata da lafiya sai kuka take.

tsakanin Hamma da Zainab ban san wanda zance ya riga wani ƙarasowa kaina ba, idon sa ne ya rufe ya hau yiwa Gwaggo faɗan mi yasa bata kira shi ba, bai jira cewar wani a cikin su ba ya kinkime yana faman nishi zuwa mota.

da isar mu asibiti kuwa aka karɓeni tare da miƙa ni labour room, kamin wani lokaci tuni ya sanar da mutan bauchi inda kowa ya shiga min adu'a, Ummi na kuwa hankalin ta duk ya tashi, banyi awa guda ba a labour room na haifo santalelen yaro na mai kama da mahaifin sa tamkar an tsaga kara.

ranar suna yaro yaci sunan Besty Babagana, amma muna ƙiranshi da Amman, anyi shagali sose a wannan rana domin kuwa Hamma nah yay mana bajin ta.

ban shekara guda ba Allah ya kuma azurtani da wani cikin,murna wurin Hamma ba'a magana saɓanin ni, don a target ɗina sai Amman ya shekara biyar zan fara shirin masa ƙani, idan naga Hamma na murna har fushi nake da shi, haka ita ma Zainab domin zuwa yanzu babu wani batun kishi a tsakanin mu, sose mun gama fusknatar juna nida ita.

haka nayi ta ɗawainiyar ciki na har tsawon watanni tara, wannan cikin kam nafi shan wuya fiye dana Amman,  haka zalika ya ninka na Amman ma a girma,kumburin da nayi ba ƙaramin tsoro ya bani ba, munje munyi scaning inda aka tabbatar mani da ƴan biyu ne a ciki na, ranar tsabar farin ciki Hamma ko runtsawa bai yi ba.

yau kam Hamma ya shirya domin tafiya Bauchi, za shi duba Mama da bata da lafiya, kallon sa kawai nake naga iya gudun ruwan sa, domin tunda Mama ta fara ciwo yace ban zuwa nima naji da kaina tunda nayi mata sannu ta waya hakan ma ya wadatar, amma Zainab kam har kusan sau huɗu tana zuwa, haka ya gama shirin sa ina zaune ina ninke kayan wanke, sai daya gama yazo ya shafi kumatuna yana faɗin, "Maman 2wins ni zan wuce".

ban ɗago na kalle shi ba nace masa, "Hamma idan na lura da kai na kuma fahimci take-taken ka so kake ka kuma ja mani baƙin jini a wurin Mama, rashin son da take mani shine farin cikin ka da jin daɗin ka, ai tunda tana son uwar gidan ka komi yayi maka dai-dai".

nai maganar raina a ɓace.

bai tankani ba saboda maganar tayi masa zafi kuma bai taɓa tunanin furta makamanciyar ta daga baki na ba, ji nayi kawai ya kama hannaye na duka biyun ya miƙar dani tsaye, kamin na ɗago na kalle sa naji ya zura min hijabi.

sai wani cin magani nake na ɗago na dubesa, jan hannu na yayi muka fita bayan ya diren takalmi flat yace na zura, ina faman zumɓuro baki na saka, ban iya ƙwatar hannu na ba saboda rashin samun damar hakan da nayi daga gare sa.

muna zuwa parlo naga ya dubi Nabeel yace yaje ya amso Amman a hannun Zainab, ina jinsa yana magana ƙasa-ƙasa yana cewan gwamma mu tafi da shi kamin tace har shi nake jawa baƙin jini.sai yanzu na fahimci magana ta ce tai masa ciwo,kuncina kawai na murmusa, muna tsaye Zainab tazo ta miƙo masa Amman ya amshe shi, tambaya ta tayi lafiya kamin na bata amsa shi ya bata akan cewar zamu wuce bauchi ne.

"Amma kwayi tafiya mai nisa da ita a haka ita da haihuwa zata iya zuwa a kowanne lokaci".

"a'a Maman Nabeel ina so naje naga jikin Mama ne duk na damu wallahi, kowa yaje fa banda ni".

"haba Riyah, in dai Mama ce ai ba sai kinje tunda kuna waya kuma kinji tana lafiya".

"a'a nikam dai ina son zuwa ku barni don Allah....".

ai ban ƙarasa magana ba naji ya figi hannu na munyi waje, tunda muka shiga mota uffan bai ce min ba haka ma inda nake bai kalla ba, sai dai abinci daya tsaya ya saya ita ma take away ɗin gefe na ya aje mani na ɗauka, ina ta masa magana amma sam bai saurere ni ba, Amman kuwa ya hanani shi sai a cinyar sa ya ɗora shi, duk wani salo na kissa da jan hankali da nayi don ya saurare ni amma sam yaƙi bi ta kaina sai ma tsawa daya doka min akan kar na sa shi yin accident tsautsayi ya sami ɗan mutane ace dama ya tsane shi.

wannan kalmar daya faɗa kam sai dana yi dariya, lallai lamarin Hamma sai shi, wai ɗan mutane kuma duk akan maganar dana faɗa ɗazu, nima sai na ƙyale shi har muka iso bauchi.

babu yabo babu fallasa Mama ta tarbeni domin har yanzu kam ba wani ɗasawa muke da ita ba, shi kansa hawan jinin da yayi mata mugun kamu duk akan damuwata data ɗorawa kan ta ne domin kuwa har Hamma ta sanarwa hakan.

koda naje ɓangaren Anty ban wani jima a can ba na kuma tashi na dawo wurin Mama, ban san lokacin da ƙwalla ta cikan ido ba saboda yanda naga Mama ta koma tsabar ciwon dake damun ta,ta rame sose duk tayi ƙasusuwa kamar ba wadda ke cikin jin daɗi ba.

har magriba ina zaune a parlon ta don saboda bata son ganina ma tashi tayi ta barni ni ɗaya kamar mayya, Amman kuwa yana wurin Anty dama sam bata ƙaunar yaron ko kaɗan, don tunda na haife shi ta buɗi baki tace har ta mutu bata ƙaunar abinda yake jinina ne.

bayan nayi sallar magriba ina zaune a ƙasa kan pillow na ɗan kishingiɗa kaɗan da kujera, kamar waccen haihuwar sai naji bayana da marata sun ɗauka amma ina wannan daban yake da waccen, ihu da salatin dana saka shi ya fito da Mama daga ɗaki, farko ƙeƙam ta tsaya a kaina tana aika hararan tare da cewar kar na sake na haife mata a ɗaki, can kuma yanayin da

nake ciki sai tausayi na yayi mugun damƙar zuciyar ta.

riƙe ni tayi cikin ruɗewa tana mani adu'a, gaba ɗaya kasa fita tayi kiran wani sai ƙoƙarin ganin ko zata iya ɗauka na, iyakar ƙarfin muryar ta ta buɗe ta ƙwala kiran da wani a kusa, Allah ya kawo Abba dai-dai lokacin kuwa, jinta yayi saurin shigowa ɗakin, tana ganin sa tace ya kira Hamma amma ya fara taimaka mata su kamani mu tafi asibiti.

acan Hamma ya samemu don kamin zuwan sa har mun fita, Mama ya samu ta rafka uban tagumi,koda yayi mata magana kai kawai ta ɗaga masa sai Anty ce ta sami damar amsa masa.

tun wannan lokacin nake fama wato magriba har zuwa gabanin asuba sannan Allah ya nufa ƴaƴa biyun dake ciki na suka fito, yaran gwanin sha'a da burgewa duk mata, abinda ya bawa kowa mamaki sai ga Mama ce ke murna sosai ta miƙa mashi yaran ta hana kowa, Abba kuwa sai zaulayar ta yake, nida Hamma kuwa abin yayi mani daɗi matuƙa.

ban koma Abuja ba anan Mama tace da Hamma zan zauna nayi wanka na, ranar suna babbar ciki taci sunan Mama inda ƙaramar taci sunan Anty, ake ce masu Afnan da Farhan.

to haka rayuwa taci gaba da tafiya cikin hukuncin ubangiji, Mama yanzu ta sauko duk ta sauya wasu mugwayen halayanta, da kanta ta samu nida Hamma dasu Anty a gaba tana kuka tana bamu haƙurin abubuwan da duk suka faru a baya, lalle ta yarda a rayuwa babu wani wanda ya isa yaja da hukuncin Allah, dole yanda Allah ya tsara hakance zata kasance.

Twins ɗina suna da 3yrs akayi auren su Abdallah da Abdulrahman, haka ƴan'uwa na Sadiq da Bappah suma ana shirin auren su a december, lokacin ɗan Hammah Waleed yayi wayo don ana shirin haifah mishi ƙani ko ƙanwa a wannan lokacin.

Gidaɗo nah ya gama service ɗinshi , Allah ya nufa ya nufa ya samu aiki da NNPC a wannan ɗiban da akayi.

Ranan ɗaya ga watan June ne ranan mafi rikitarwa da tazo mana na rasuwar Kakanmu Bappah, inda yayi fama da hawan jini, haka muka ɗunguma kafi kowa zuciyar shi babu daɗi, bayan an gama zaman makoki da kwana biyar muka dawo saboda zazzaɓin da nake fama da shi mai zafi, dole Aunty ta sako ni gaba muka dawo bauchi da ita.

Direct asibitimuka nufa, inda gwajin farko ya nuna mun ciki ne da ni ɗan sati uku, ranan kam ban san irin kuka da borin da nayi ba, don atafur murtsike ido nayi ina zunduma ihun twins ma fama nake da su har yanzu, ina kukaina faɗin, "Toh baga Aunty Zainab ba, ita tayi mata cikin mana, saini da baya sona yake ta tula mun ciki ko yaushe", na faɗa ina ɗaura hannu akaina ina ihu.

Doka Aunty ta kai mun, amma Mama bata bata dama ba ta saka hannu ta tare ta tana faɗin, "kaji ikon Allah, Yarinya tana fama da laulayi ke kuma kina kai mata duka"? ta faɗa tana hararan Aunty.

"Haba Mama bakiji irin butulcin da take shirin yi wa wanda yanufa zata haifan ba" Aunty ta faɗa ranta a matuƙar ɓace.

Zainab tana kallona hawaye yana bin idonta tave, "haba Mummyn Nabeel, banji daɗin furucinki ba wallahi, ae ki gode Allah daya baki mahaifar da zaki ta haifa mana ƴaƴan ma, kinsan ni tawa mahaifar ina take?" ta faɗa tanaB share hawayenta.

Sun kuyar da kai Hammah yayi bai ɗago ya kalli kowa ba, inda Mama kuma ta zubawa Zainab ido tana cewa, "ina taki mahaifar take Zainab"?

Zainab ta cigaba da kukanta har saida taji ƙirjinta yana zafi tukun tace, "Mama ae mamana ta kaini egypt tun lokacin auren Hammah ta saka an cire mun mahaifah, tace tunda Baba na ya matsa sai na dawo toh ta soke haihuwa na a gidan kafin na tsufah ya ƙarisa daina sona, amma abin takaici sai gashi tunda aka haifi su ƴan biyu sai na samu kaina da masifar son haihuwa amma babu dama, don haka Riyyah ina haɗaki da Allah kiyi haƙuri ki haifah mana yara da yawa, insha Allahu zan taya ki kula da su", ta faɗa tana share hawayenta.

"Malafar uba kenan" cewar Mama data wani zabura da ƙarfi ta tashi ta tsaya tana riƙeda kunkumi kaman zata kaiwa Zainab mari, da sauri Baba dake tsaye a bakin ƙofah ya shigo ya riƙeta, yana duban cikin idon Mama yace.

"kada ki fara ƙokarin ta ɓata, haka Allah ya tsara mata nata jarabawar, Saboda haka ki barta da abinda ta keji a cikin ranta kaɗai ma ya isheta damuwa, amma kada ki ƙara mata da ƙiyayyah ko nuna son kai, ina ga baƙar surakar ki tana ta haifah miki fararen jikoki masu kyau da ban sha'awa? Toh wannan ma ya isheki ishara ki daina takurawa surakanan ki,yanxu mabaki san su Abdallah nawa zasu haifa miki ba, saboda haka kiyi haƙuri da rayuwa a duk yadda ta zo maka, ki kuma gode Allah da shi ɗan naki yana da wata matar kuma shi ɗin zai iya haihuwa, don Allah Zahra ki dinga haƙuri da rayuwa kinji" yafaɗa yana rarraahinta.

Kumawa tayi ta zauna amma ta kasa furta komai,gaba ɗaya parlour yayi shiru babu mai cewa komai sai muryan Zainab da keta fitar da sautin kukanta, ni sai naji duk jikina yayi sanyi, haka Baba yayi ta mana nasiha cikin kwantar da hankali kuma ya rarrashi Zainab ta bar kukan.

Muna nan har yamma sai Mama ta tashi tana kallona tace, "me kike su na dafa miki Riyyah"? Ɗan kawar da kai nayi gefe ban iya cewa komai ba, sai can naji Zainab tana cewa, " Mama ae Mummyn Nabeel babu abinda na lura yanzu take so sai ferfesun kayan cikin sa" Ta faɗa tana dariyan yadda na ke hararanta.

Har ƙarfe goma muna side ɗin Mama da su Abdallah ana ta hira, daga baya Hammah yazo ya ɗaukemu muka wuce gidanmu, don a cewar shi gobe zamu wuce Abuja don yana da wani tafiya da zaiyi idan mun koma, haka muka tarkata muka tafi gidanmu.

Ina fitowa a wanka naji Hammah ya rungumuni ta bayana, wanda har sai da naji tsoro don ban san yana cikin ɗakin ba, ajiyan zuciya ya sauƙe sannan ya juyo dani ina kallon shi, a hankali yace.

"Baby bansan irin son da nake miki ba, shiyasa Allah ya dube ni yake ta sauƙe mun ƙoyayen haihuwata a mahaifarki ki ta ƙyanƙyashe mun yara masu kyau da albarka, amma duk da haka laifin bawan Allah kike gani ko"? Ya faɗa yana maida kanshi kafaɗa na ya kwanta.

Hannu na saka nima na maida mashi martanin runguman da yayi mun, a hankali na furta, "afuwan my heart ba zan sake furta makamancin haka ba har abada, kayi haƙuri na tuba uban ƴaƴana".

Dariya yayi yace toh Maman ƴan uku, Allah ya miki albarka ya ƙara miki ƙauna ta yadda nake sonki.

Nima Aunty Nice dariyan nayi na buɗe ƙofan na fita ina faɗin,muma Allah kabamu masu son mu tsakani da Allah , kuma suna saurin yi mana haƙuri da uzuri.

_*DUKA DUKA ANAN NA KAWO ƘARSHEN LITTAFIN BADARIYYAH, KUSKUREN DANA YI ALLAH YA YAFE MUN, INDA NAYI DAIDAI ALLAH YA BAMU LADAN SHI*_

_*MISS XERKS KE KAM BAKI BAZAI IYA FAƊIN GODIYA A GAREKI BA, HAKA HANNU NA BAZAI IYA RUBUTA KOMAI A GAME DAKE BA, SAI DAI KAWAI KE ƊIN KISAWA RANKI KE TA BANCE A WURIN AUNTY NICE, ALLAH YA BIYA MIKI DUKKAN BUKATUNKI NA ALKHAIRI DUNIYA DA LAHIRA, NAGODE BESTY NAH*_

*NABAWA DUK MASOYA BOOK ƊIN BADARIYYAH KYAUTAR SHAFIN SALLAMA, MAFI GIRMAN KYAUTAN NA BAKI SAHIBATA,(UMMI YAWALE BABA)ALLAHU YA BAR ZUMUNCI, YA BAWA MUMISKO LAFIYA MAI ƊAUREWA*.

#Vote
Coment
Share
Follow.

*DAGA ALƘALAMIN AUNTY NICE* ✍🏻✍🏻✍🏻
An dauko wannan littafi daga shafin www.dlhausanovels.com.ng ku ziyarci shafin na www.dlhausanovels.com.ng domin samun kayatattun littatafan hausa kama daga kan na yake yake dana soyayya

Marubuci ko marubuciya zasu iya turo mana da littatafansu mu dora masu a shafinmu kyauta

don masoyansu su rika Downloading a online,

Sannan marubuta zasu iya turo mana da tarihin rahuwarsu da tarihin rubutunsu, dama sharhin littatafansu don masoyansu su gani kuma su karu da hakan
Domin turo mana da littafi ko tarihin rayuwar marubuci ko marubuciya sai ayi mana magana ta whatssap da wannan nambar +2348140419490

A lura dakyau - kyauta muke saka littafi a shafinmu bama amsan ko sisin marubuci, duk wanda ya amshi kudinku da sunanmu babu ruwanmu,

Alura dakyau - manazarta bama tura littafi ta private ku dena binmu private kuna neman mu tura maku littafi, duk mai bukatar littafi yaje website namu

Alura da kyau - Littatfanmu suna fitowa cikin manhajoji uku ne PDF,TXT da DOC amman munfi amfani da PDF da TXT masu amfani da wayar android ko tablet ko computer zai fi kyau ku riga dauko PDF da DOC

Masu amfani da kananan wayoyi java ko mara java TXT zakuna zaba don shine daidai wayarku

This hausa novel was uploaded and downloaded from www.dlhausanovels.com.ng
You can download more hausa novels there
Also you can send us your novel to upload it in our website for your fans to download it online
It is free we do not charge for uploading novel
Also if you are an Author be it online or Non online you can send us your biography including your book summary,commentary and others via this number +2348140419490 its free we do not charge for our services

Note that - we do not charge for our services we uploaded novels and posted biography free, any person that collect your money in our name is your fault do not blame us

Note that - pls readers stop calling us and be asking us to send you a novels we are not sending novels through whatssap or private our novels is public at any day, any time you can visits our site and download it

Note that - our ebooks came as PDF,TXT or DOC format but the popular format are PDF or TXT, those with android or tablet or pc we suggest you to download PDF or DOC
those with java phone or non-java phone we recommend you to download TXT
—